[2/16, 9:24 PM] Cutie cutie pie: *BAƘIN HAURE....□□*

{Greed for Money is the roots of all evils□}

```Bismillahir rahmanir Rahim
*Alhamdulillahi Ubangiji ya nufa mun dawo a daidai wannan lokacin me tarin albarka. 15/12/2023 na fara, Ya Allah ka bani ikon isar da wannan sakon da na dauko Ya Allah ka bani damar sauke nauyin da na dauka, ina muku
Fatan alkhairi
Ga Jamilah Janafty wacce bata gajiya da dimbin alkharinta a gare ni da sauran marubuta baki ɗaya.

Wannan labarin wani ɓangare na Labarin ya faru da gaske wani ɓangare kuma kwaskwarimar daliban ilimi ne.```

Sadaukarwa ga *BINTUN BATUL*
Wannan labarin na kudi ne!

BAARE GOLDEN EMPIRES.

Niamey. Niger republic

*02:30pm*
Ta zubawa kofar yalwataccen ofishinta idanuwa, kamar kullum da rana zata fito har ta fadi ba tare da ta jira zuwan Yaranta ba, sai dai yau kamar har sun wuce ka'idar lokacin da suke zuwa mata, wayar landline da ke gefenta tayi kara. Ɗauka tayi cikin sanyi ta saka a kunnenta. "Assalamu alaikum!" Ta faɗa cikin sassanyar murya wanda yake cike da dattako. "Ina magana da Chairwoman ne na BA'ARE GOLDEN EMPIRES?"
"Eh" ta amsa zuciyarta na rawa, domin daga jin harshen da aka mata magana tasan daga nigeria ce, domin da harshen turanci ne. "Yawwa Ma'am Captain MJ Mamman Ba'are ya ce a gaya miki ba zai samu zuwa ba, har..."
"Ok ba damuwa!" Ta faɗa cikin sauri da wani raunanen murya, idanunta cike suke da kwallar bakinciki, idan tace bata ji dadin rashin ganin MJ ba tayi karya. Yau shekara shida kenan rabon da ta saka shi a idanun, MJ ba yaro bane balle a ce sai an tuna mishi nauyin da ya rataya akanshi na iyaye, sauke ajiyar zuciya tayi lokacin da aka kirata a wayarta ta ɗauka harshenta yayi nauyi. Amma a zuciyarta addu'a take mishi, a duk inda yake Allah ya kare mata shi.
"Madame ga Amaan Mamman Ba'are yana son shigowa."
"Ya shigo!" Ta faɗa tana dauke kwallar da yake idanunta da wani tissue. Da sallama ya shigo hannunshi dauke da wayar iPhone 14pro. "Barka da rana Hajiya!" Ya faɗa yana kai wayar kunnenshi. "Barka dai Amaan Mamman Ba'are!" D'aga mata hannu yayi, ta kura mishi idanu. A hankali ta kai hannunta kan wata sandar ƙarfen gold, kafin ya ankara ta make hannun da sandar ta watsa mishi harara. "Auch Hajiya, waya me muhimmanci nake son yi?" Ya katse kiran yana kallonta, tare da tura baki. "Fisabilillahi Hajiya daga na dan yi miki alamar ina zuwa sai ki make min hannu?"
"Allah ya shiryaku! Ka gaya min wacce uwar ce zata yarda ka mata haka?"
"Tow Hajiya me nayi?" Ya tambaye ta kamar zai yi ihu, wayarta ce ta kuma kara, ta dauka. "Madame ga Aryan Mamman Ba'are yana son ganinki."
"Ya shigo!"
Ta faɗa tana kallon agogon hannunta, can kuwa sai gashi dogo sambal kamar Amaan Mamman Ba'are, Kyakyawan buzu sak da dan uwanshi, niman wuri yayi ya zauna yana gaida ta a sanyayye. "Sannu Hajiya ya aiki?" "Alhamdulillahi, ya takwarata da Nabeeha?"
"Suna lafiya!" "Hajiya shine ni baki tambaye ni ba, wato don an tsane ni. Ko Yarana ba za'a tambaya ba!"
```

"Da kazo ka bani damar tambayarka?"
"Amma Hajiya fisabilillahi waya nake fa"
"Wayar tafi ni muhimmanci ne?" Shiru yayi yana sunkuyar da kai kasa, shi har ga Allah Hajiya bata mishi gentle, gashi wannan dan iskan Yaron yana zuwa ta wani tsaya tarairayarshi.
"Hajiya kin yi waya da Hamma MJ?" Murmushin takaici tayi, ta ce mishi. "Aryan MJ ba zai sami zuwa ba"
"Amma Hajiya kuri'ar mu ba zata wadatar ba, dole sai da Hamma, ko zan tafi Port Harcourt din ne?"
"Kasan idan na cika matsawa gudu zai sake yi, daga Port Harcourt zuwa wata ƙasa kyale shi."
"Tow Hajiya idan yaki zuwa ki basu abinda suke so mana, tunda shi aikinshi yana gaba da kome"
" Wani lokaci idan kayi magana, kamar baka san zaman aji ba, anya Hajiya ba asarar kudin tara kika yi ba?" Inji Aryan Mamman Ba'are, "Hajiya ki gaya mishi ya fita hanyata, ba da shi nake ba. Dake nake ina ruwanshi da ni."
Lumshe idanun tayi ta bude akanshi, idan da sabo ta saba da halin Amaan, wani lokaci idan yayi abu kamar ba ita ta haife shi ba, idan ta tuna past ɗinta sai ta ga kaman da gayya yake mata wani abu, domin yasan duk yakin da take yi ai domin su ne baki daya, ko makiyinta bata fatan ya ga irin rayuwar da tayi balle masoyinta ko ɗan da ta haifa, amma halin Amaan ya zame mata kamar jinin jikinta ne, yana ganin kamar tafi son Yan uwanshi akan shi, bayan shi bai san bakiɗayansu kaunarsu take ba, tana damuwa da MJ ne ba don kome ba, sai don rashin lafiyarshi. Shi kuma Amaan gabbo ne bai da hankali sam, yayinda Aryan ya kasance mai matukar hakuri amma bai iya faɗa ba, Majeed shine daidai da su, hatta Hajiya Turai kakarsu shakkarshi take, kaf Ba'are estate babu dodo sama da Majeed. "ba zan sallama musu tsinke daga kamfanin nan ba, duk abinda kaga ya faru dama can rubutaccen al'amari ne. Yaushe ka samu duniyar da har ka manta da asalinka? Ka manta nayi aikin tuwo-tuwo domin ka rayu?" Dafe goshi Aryan Mamman Ba'are yayi hawaye na zuba mishi, wasu abubuwan akan idanunsu wasu abubuwan kuma kafin a haife su, past din Hajiya yana da alaka da nisan da MJ yayi. Har ya koma Nigeria da zama duk da dama can Nigeria ita ce inda suka rayu, daidai lokacin da suke buƙatar taimako.

"Hajiya a kara kiranshi saura kwana biyar, idan ta kama naje zan tafi har inda yake." Girgiza kai tayi ta ce mishi. "ina tsoron rasa shi a karo na biyu." "Kada ki damu nayi miki alkawarin zamu dawo cikin amincin Allah."
"Hmm! Da ka hutar da kafarka, gayen da aka ce yazo Babanmu yana gabbar mutuwa bai zo ba..." Maka mishi ƙarfen tayi a kan gwiwarshi. "Kana hauka ne?"
"Hajiya sai nayi shiru? Fisabilillahi nayi shiru fa? Tow nayi shiru." Zata kuma magana Aryan Mamman Ba'are ya ce mata. "Hajiya ya isa haka, kada ki damu zai zo." Mikewa tayi ta dauki tap ɗinta da duk wasu abubuwanta na aiki. Har zata tafi sai ta zauna kamar an ce ta ɗan duka kanta kasa, ta ga wani abu kamar mayen karfe, cirewa tayi tana kallon abun kafin ta saki murmushi ta ce. "Aryan ka ajiye min wannan a wurinka." Karba yayi yana kallon ikon Allah, kafin ya ce mata. "Hajiya na fasa?" "A'a kabar shi." Amsar kayan hannunta yayi, suka nufi waje, a hankali daga Office din sai gaishe su ma'aikatan kamfanin suke, tana amsawa da kai. Sai da suka fito ta tsaya tana kallon yadda ginin kamfanin yake, kafin ta sauke ajiyar zuciya. Burinta bai wuce Yaranta baki daya su rike kamfanin ba, amma MJ yaki bata haɗinka. Lashe bakinta tayi ta nufi inda motar Aryan take ta shiga, cikin Fushi Amaan ya ja Motarshi ya fita.
"Kwantar min da kujerar nan na gaji." Ta faɗa tana me lumshe idanunta, only God knows duk abinda yake faruwa, amma ita ba zata ce yaushe kan Yaranta ya rabu haka ba, sannan ba zata ce ita ce silar fadawar matsalar su ba, tasan da babu da ba dadi haka suka taso, cikin tsannanin bakinciki da bakin zalinci da mugunta da bakar talauci na tsananin tashin hankali..

Kuma a haka ta rike yaran suka kai inda suka kai, amma yau sakamakon da take gani shine na tarwatsewar Yaranta. Bayan gwagwarmayar rayuwar da ta sha, haka bai isa ba sai ta kara amsar wani Punishment, bayan wanda ta gani bai isa ba, ace yau yaranta kamar zasu kashe junansu.

Tsayawa suka yi a traffic Jam, kamar an ce ta bude idanu ta hango Sajjid Mamman Ba'are, tare da wasu turawa suna gaisawa. "Me Sajjid Mamman Ba'are yake yi anan?" Kallon wurin Aryan yayi kafin yayi tsaki, ya ce mata. "waye ya sani? Sharrin da yake cikin duhun BA'ARE GOLDEN EMPIRES Allah kadai ya sani." Ya faɗa yana kara jan motar bayan an basu damar wucewa kwantar da kai tayi tana zare glass din idanunta. "Duk abinda yake faruwa a rubuce yake, amma kuma mutane sun rufe idanunsu kamar basu gani,bayan sun san kome."

"Hajiya yakin nan ba iya ke daya ba ce, har da Hamma MJ, shine kashin yakin." Da wannan suka isa unguwar da suke zama, inda kana gani kasan ba iya su kaɗai ke rayuwa a unguwar ba.

~~~

Port Harcourt
Nigeria Naval barracck
_09:30 pm_

Ruwa ake tun safe, har zuwa yanzu ba a daina ruwan ba. Kallon yan tsintsiyar hannuna nayi a karon farko ina me hadiye yawun tsoro, yau na isa na komawa Addah hannu rabbana ne? Ai yau daga ni har dangin Uwata sai munci zagin da ba zai kare ba, sosa kaina nayi ina kokarin niman hanyar da zan fita. Don haka nayi ta bin layi da gida-gida, domin ya fitar dani barracck din nan wai ma meye ya kawo ni nan? Tambayar da nayiwa kaina kenan, haka na cigaba da bin duhu ina buya, ina jin gara na fake na kwana anan, tow wannan jikar na jikina fa? Wani munafikin sanyi na ji ya shige ni, da sauri na kara makalewa da jikin bangon gidan da nake.

Sai dai kash, ban gama nazarin me zanyi ba, naji hayaniyar mutanen sojan nan. "Innalillahi'wa'inna'ilaihi'raji'un;" na furta a hankali, da sauri na cire takalmina na bazama da gudu, kasancewar ana ruwa. Can naji an hura wusir, kafin kace me sojojin area din sun fito da manya-manyan torchlight ɗin su, ƙaddara ce ko tsautsayi. Kawai dai nasan nazo wani kofar gida, amma daukata aka yi ko janyo ni aka yi ban sani ba, sai dai nasan na buɗe baki zanyi ihu, naji kamar an cusa min wani abu a cikin bakina, tare da ganin wani duhu ya mamaye ganina. Ma'ana gidan baki daya a cikin duhu babu alamar haske ko tafin hannun baka iya gani, amma zan iya cewa fatalwar da ya ɗauke ni, yasan kome na gidan tunda gashi nan har ya kai ni dakin da babu kome sai duhu, ina ji ya bude wani abu ya cilla ni cikinshi. Sannan ya dauki abu ya rufa min gami da danne dakin. "Idan kika sake kika yi motsi suna zuwa harbeki zasuyi."

Ya faɗa min da irin turancin da ake yawan yi a garin patakwal, hawaye ne ya zubo min, ina ji daga can nesa ana buga kofar gidan, bugawa kamar za a b'alle kofar. Can ina iya jiyo hayaniyar mutanen sojan nan. "Oga ya ce meku wuna search any where akwai yaron hausa da ya dauko daga waje, ya gudu."

"Ok ku shiga ku duba!"

"Kambu!" Wato ma zai bar su ne, me yasa ya dauko ni? Jin ana buruntu yasa na kara k'amk'ame jikina, na rantse na gudu daga nan tabbas zai yi wahala na kara komawa wurin Addah, takum zan koma naje wurin Baffana yafi min wannan bakar wahalar.

Ba zato ba tsammani kawai naji ana buga inda nake ciki, wani irin dauke wuta nayi domin nasan shi kenan kwanana ya ƙare. "Oga mu bude nan?" Ban ji me ya ce ba, but naji suna bashi hakuri.

"Oga kayi hakuri! Kayi hakuri." Suka yi ta bashi hakuri, sannan suka fita daga cikin gidan.

Ajiyar zuciya ya sauke, sannan ya dawo dakin yana mamakin yadda wasu daga cikin ƙabilar Hausawa su ka lalace da son abin duniya, yanzu yar wannan yarinyar me zata yiwa namiji? Bubbuga abin yayi tare da bude abin, ya haska min fuskata na kare
~~~

da hannu bibbiyu, "fito!" Ya faɗa da wata irin murya mai dadin gaske, cire hannu nayi a fuska, tare da kara leka fuskarshi, abin haushi bana ganin fuskarshi.
"Fito!" Ya kuma fada min da muryar, da sauri na mike tare da kallonshi. "ban iya fitowa ai!" Shiru yayi, ya juya kamar zai fita kawai sai ji nayi, kamar an dakume wuyata, anyi sama da ni. "Kambu kashe ni zaka yi?" Cilla ni yayi can gefe guda, na zube a kasa "Kum!!" *Wai me yasa sojoji kuka cika mugunta ne?* Na tambayi zuciyata, fita yayi ya bar ni a dakin, na takure wuri guda, Addah tana can tana barci ni ta watso rayuwata gabbar mutuwa. Hasken da na hango yasa na kara k'amk'ame jikina, ya shigo da ƙatuwar bargo ya watsa min, sannan ya kuma fita. Can sai gashi da wasu kaya ya watsa min, zama nayi a cikin duhun. Domin na lura akwai amana a tsakaninshi da duhu. Mikewa nayi na cire kayan jikina, har na sauya kayan, sannan na dauki bargon na lullube jikina, na cigaba da zama a wurin, domin ko wancan da na gudu daga wurin shi. Sai da ya bari na fara barci, kawai naji ya fara min wani abu na daban, rintsa idanuna nayi, tsoro nake kada sai na fara barci shima ya biyo daren.

Commodore Magaji Abba Chindo.
Cirko-cirko Yaranshi suka yi, jikinsu a matukar sanyayye. Shi kuwa yana tsaye a saman barandar kofar gidanshi, sai bunka hayaki yake. Busa sigari yake tare da lumshe idanun, a duniya yana son kwanciya da Yara kananu, musamman wanda shi yake fara bude su da kanshi, haka yasa baki daya yake jinshi kamar mara lafiya. Ya saka buri akan yarinyar nan, amma shegiya sai da ta gudu.

Hadiye yawu yayi, bayan ya kashe sigarin. " Kun duba gidan wancan dan cirani?" "Yes Sir, mun duba." Dukar karfen da yake tsaye yayi yana faɗin. "Taya zata bar barracck din nan? Sannan a wannan lokacin da ake tsuga ruwa? Kai ku bi min gida - gida har gidajenku!"
"Yes Sir;"
Suka fada baki daya, sannan suka juya tare da barin kofar gidan. Daya biyu yarinyar nan tana hannun wancan dan kutumar uba, bai san me yasa gayen yake mishi kallon banza ba.

Koma ciki yayi ya dauko ledar ruwa, ya nufi gidan, dukar kofar da aka yi ne yasa shi jan tsaki, ya fito daga cikin dakinshi da yake kallon arewa da kofar. "Yes!" Ya faɗa yana tsaye a jikin kofar. "Ka bude!" Aka gaya mishi da karfi. Bude kofar yayi ta tsaya a jikin kofar. "Meye?" "B,,.. uba ne!" Commodore Magaji Abba Chindo ya faɗa a fusace. "Ok nawa kenan?" Ya tambaye shi, yana haska kasa. "Ka bani hanya na shiga na dauki kayana." Hannunshi ya kai kunne ya ce mishi. "Magana kake?" "B..,, Uba nake?" "Ok kayi ta yi!" Ya juya zai shiga tare da rufe kofar, yayi maza ya kai mishi tokare, sai da ya fadi, torchlight ya fadi can. Mikewa yayi yana faɗin "An shiga tsakaninmu, ka kama gabanka domin xan iya kiran Admiral" ya fada cikin sanyin murya wanda zai tabbatar maka da baya son hayaniya ko faɗa. "Wallahi ka sake baka fito min da ajiyata ba, sai na ga bayanka idan muka hau teku "
"Kai ne bakon mutuwa, amma ni babu irin mutuwar da ban gani ba. Please zaka iya fita."
"Kai Son of bitch, sai na kashe ka."
Wannan ihun yasa na kara k'amk'ame jikina, tabbas na jefa mutimin nan cikin masifa. Kara k'amk'ame jikina nayi na cusa kaina a tsakanin cinyoyina. Sake kofar da aka yi yasa na razana sai da na mike. Can naji alamar an rufe kofar, ina jin takunshi har ya bude wani kofar ya rufe, ajiyar zuciya na sauke a hankali, ina jin kamar na fito na gudu amma me zan taras a gaba yasa na kara rungume bargon da ya bani.
Haka na raba dare har lokacin, ina zaune kamar mara gaskiya duk tsawon dare nan ban bari raina na rintsa ba, tsoro nake ji kada na kwanta ya farmake ni.
A hankali ruwan ya tsagaita, garin yayi wani irin sanyi me dadi da shiga jiki. Wanda ya haifar min da jin matsananciyar barci, na kwanta a wurin.

....
3:30am

"Don Allah kayi hakuri Alhaji, wallahi ba zan kuma ba. In sha Allah zan yi kokari, Alhaji don Allah ka dube Yarana kada ka ci mutuncina a kan idansu."
Kamar walkiya haka yake hango abin, a zahiri kuma kuka yake har da shasheka, yana surutu.
Ina barci nayi ta jin kuka da shashekar mutum, "shikenan an kama ni" na fada zubur ina mikewa. Ganin babu kowa yasa naji wani irin tsoro ya kara kamani, mikewa nayi ina jin kukan yana kara ta'azzara. Fitowa nayi daga bakin kofar, na nufi hanyar da nake jiyo kukan. Walkiya aka yi naji kamar hantar cikina zata fita, yayyafin da aka aka fara yasa na ji kamar na juya tare da komawa dakin da ya ajiye ni. Amma ina ƙaddara ko Hatsari ya kai ni inda ba zan manta ba.
Walkiyar da aka kara tare da tsawar da ta cika ko ina, yasa na kama handle kofar na tura, ina shiga na ga dakin har tafi nawa duhu. Gurnani da nishin da ake yasa naji kamar kafaffuna ba zasu dauke ni ba, juyawa nayi domin na koma inda na fito domin ta nan kaɗai zan tsira da rayuwata, sai dai tunda na shigo dakin na rasa ta ina na shigo, garin laluben hanya nayi ciki tare da karo da gadon, kifawa nayi bisa gadon akan mutum. Ji nayi an cafko ni tare da shake min wuya, ina ƙoƙarin kwace kaina amma ina, baki daya ya zuba min karfinshi.
Ya danne ni da karfin tsiya, bubuga gado nake ina kokarin kwatar kaina, amma ina. Wani walkiya aka yi, me haɗe da tsawa. Shi ya bashi damar hango wata yar ƙaramar wukar da take kasar pillow da yake kwance. Bayan ya zame rigar da yake jikina dama kuma rigarshi ce. Yan matasan dukiyar fulanin da suka fara fitowa suka bayyana, domin tsirara ya min tare da ɗaukar wukar yana kokarin bude ta daga gidanta, gefe daya yana kara kutsa kai tsakanin cinyoyina. "Innalillahi'wa'inna'ilaihi'raji'un!" Iya abinda na iya faɗa kenan, da ƙaramar muryar da tayi kama da mai shirin mutuwa, azabar da ta ratsa ni lokaci guda.....
Gamu nan mun dawo
1/3/2024...
#Mai_Dambu
[2/16, 9:24 PM] Cutie cutie pie: *BAƘIN HAURE....□□*

{Greed for Money is the roots of all evils□}
Arewabooks:maidambu41
Wattpad:Mai_Dambu
Mallakar:Mai_Dambu
002
Ban zan yi tafiya mai nisa ba, ba tare da na tsaya na miki fatan Alkhairi Hannatu Idris Allah ya shiga cikin lamarinki, ya saka da alkhairi na gode sosai

Operation Anaconda
***
A daidai lokacin da nake tsammanin mutuwata, ta zo gare ni domin nasan abubuwa dayawa sun faru a cikinsu har da rashin ganawa da mahaifiyata, wanda tana raye amma bamu san a wata duniyar take ba, iya hakan idan aka barshi a rayuwata na azabtu da rashin Uwa, nasan duk laifin na Baffa ne da Addah at least ya dace a gaya min inda mahaifiyata take. Soka min wukar a gefen cikina, yayi dai-dai da dawowata daga duniyar tunani da mafarkin zahirin da nake bayan na ga mutuwa. Sake caka min wukar yayi cikin tashin hankali ina kara jin abin da yake fada.
"Sai na kashe ka, idan ka kuma tab'a min Mamana!" Ya kara d'aga wukar zai soka min kamar wanda aka mishi wani abu, haka ya zube a jikina. Azaba da rad'ad'i yasa na kasa aikata kome, ina kwance kasarshi da alamun suma yayi domin ina jin dan bugun zuciyarshi. A hankali na tattara karfin da yaymin saura na tunkud'e shi gefe can, ina

jin yadda jinin yake zuba. Ga zafi gashi yana zuwa da sauri da dumi, a hankali na fara sauka daga bisa gadon sai dai na kasa, komawa nayi ina jin wata iriyar azaba ga zufa da gajiya me haɗe da jiri kamar xan yi aman kayan cikina. Haka na koma tare da kame wurin ina kwance, nayi ta kokarin niman wani abu na rufe ciwon. Na rasa a wurin lalube na tabo fuskarshi. "Tashi ka taimaka min kada na mutu,ka tashi don Allah zan mutu ka ji." Na fada ina jijjiga kafadarshi. Kamar a mafarki yayi ta jin muryata, haka yasa shi bude manya idanunshi da suke cike da barci, "Tashi ka taimaki rayuwata mutuwa zan yi." Na fada da asalin karamar muryata.

Ina jin wani uban tsallen da ya buga, yasa ni ƙara ware idanuna, ina nishi idanuna a rufe naga kamar an haska fuskata. Bude idanuwan da zan yi hasken wuta ya gauraya dakin, sai dai abin mamaki shine bana gani sai dishi-dishi. Lumshe idanu nayi a hankali naji kamar barci ne ko wani abu ne yake faruwa da ni, na dai san ban kuma fahimtar duniyar da nake ba. Wani irin rikicewa yayi wanda yasa shi gaba-daya rud'ewa, wayarshi da yake gefen gadonshi ya dauka, tare da duba lokaci. "Innalillahi'wa'inna'ilaihi'raji'un!" Ya iya furtawa domin kuwa yasan yayi abinda ya dame shi, ya kuma rasa wanda zai kira ya gaya mishi halin da yake ciki. Sake wucewa yayi ban daki ya kalli wandon shi bai ga alamar manhood ɗinsa tayi wani abu ba, amma kuma hannunshi kaca-kaca da jini. *Doctor Umaima!* Abin da zuciyarshi ta ambato kenan, da sauri ya fito tare da ɗaukar wayarshi. Jikinshi na rawa ya kirata.
"Assalamu alaikum!" Ya faɗa ta d'aya bangarenta. Ina bai samu arzikin amsa mata ba ya jifa mata tambayar. "Kina asibiti ne?"
"Yes ina Night ne!"
"Alhamdulillahi! Umamai don Allah ina cikin tashin hankali ne, na yi attempt kisan kai. Please ki taimaka min gani nan."
"Ya Rahaman,tayah hakan ta faru?"
"Ba lokaci gani nan." Ya faɗa mata, sannan ya koma kan gadon ya dauki wani towel ya daure inda jinin yake zuba, sannan ya dauko zanin gado ya nad'e ta da shi, kafin ya kuma ɗaukar bargo ya dunkule ta a cikin, sannan ya dauke ta, ya nufi hanyar waje, ta falonshi ya shiga gareji.
Ya ajiye ta bayan motar, ya koma ya dauko key, yana zuwa ya bude a cikin motar ya sakata, ya koma ya gyara dakin shi tas, yana jin zuciyarshi kamar zata buga, yasan halin Commodore Magaji Abba Chindo, yana samun labarin ya kashe yarinyar kwanar shi ya ƙare. Haka yasa shi kara rud'ewa domin wannan aikin shi ne farincikin shi, shine kome na shi idan ya sake ya rasa shi tabbas sai yayi matukar danasani. Haka ya gama goge dakin ya saka kome a wancan dakin duhu, sannan ya nufi gareji a lokacin Dr Umaima ta kira shi ya kai sau uku, yana shiga motar ya kirata. "On my way!" Ya kashe ya kunna motar sannan ya fito ya bude get din, ya koma ya fitar da motar, sannan ya sake dawowa ya rufe get din ta ciki ya koma ta fito ta kofar gidan.
Har ga Allah ya tsani kanshi, wannan lokacin ya dace ya rabu da wannan laluran, amma ina kamar kara cusa mishi abin ake, kara ji yayi ya tsani ahalin shi idan aka cire Hajiya. Itace har abada ba zai tsaneta ba, tunanin shi ne ya katse lokacin da ya iso bakin get din fita. Ya nuna ID card ɗinshi, haska motar suka yi, sannan suna ga normal bargo ne. "Oga ina zaka?"
"Zan shiga clinic ne an kira ni."
"Ok Oga kayan cikin motar nan fa?" "Idan na gama aiki xan kwanta ne, bargo na ne."
"Ok ku bude mishi kofar!" Haka suka bude mishi kofar, ya fita yana sauke ajiyar zuciya. Da gudu ya nufi titi tare da ɗaukar hanyar asalin cikin barrack din, yadda yake gudu kadai zai tabbatar maka, yana biyayya ne ga zuciyarshi da take bugawa.

Koda ya isa asibitin dake d'an tafiya ne ya raba su, yana isa bakin get din aka tsare shi, mika musu ID card ɗinshi yayi, suka bude mishi domin sun san likita ne, kuma babba, yadda yake tukin har ya isa bakin Asibitin zai saka ka gane Allah kaɗai

ya kawo bawan Allah nan asibitin. Yana shiga harabar asibitin Dr Umaima da wasu Nurse biyu suka fito, zasu amshi mara lafiyar, suka ga ya bude motar ya dauko ƙunshin bargo. "Jeed Ina mara lafiyar?"
"Ba lokaci mu wuce ciki " ya dauki bargon suka wuce cikin asibitin. Kai tsaye emergency room ya wuce da ita. Ya kwantr da ita a saman gadonsu na marasa lafiya. Sannan aka shiga bude ta, har aka bude ta gaba-daya. Har lokacin jini yake zuba.

"Innalillahi'wa'inna'ilaihi'raji'un! Tana zubda jini" Doctor Umaima ta faɗa da sauri tana danne wurin. "Ki taimaka min kada ta mutu."
"Kayi wani abu, a tsayar da jinin nan, a shiga da ita tiyata."
Cikin abinda bai wuce minti ashirin ba,suka nemi yin tiyatar . "We need blood?"
"Innalillahi'wa'inna'ilaihi'raji'un!;babu a bank ne?"
"Ban sani ba!"
Da sauri Nurse Biodun ta bude blood bank, ta ce musu ."Daya ne ba zai wadatar ba."
"Za a samu mutane a lab?"
"Bana tunanin sun tashi,saboda aikin su ba dare ba rana ne." Da sassarfa ya fita ya nufi can wurin lab din, ko minti talatin ba ayi ba, ya isa sun rufe da kyar aka samu wanda yake kwana a wurin. "Duba jini na, group O+ ne" Ciro wayarshi yayi ya kira Doctor Umaima. "Leda nawa ake so?" "Ina ga hudu zai yi, don yanzu na samu an tsayar da jinin."
"Ok ki kokarta gani nan zuwa." Ya faɗa, kallon mutumin yayi, bai mishi magana ba, ya dauki duk wani abun bukata, ya fara aikinshi, cikin ikon Allah dake mutumin yasan shi, kuma yana tambayar shi, sannan yana duba medical records dinshi a computer ɗinshi, sai gashi Allah ya takaita da sai anyi ta tests. Aka dibi leda daya, can aka kuma diban na biyu, a lokacin aka barshi ya huta. Kiran Doctor Umaima ya shigo mishi lokacin ana diban na uku. Cikin tsananin gajiya ya ɗauka. "Saura leda daya, a zo a karbi sauran"
" Captain!"
"I'm okay!" Ya faɗa cikin karfin hali, can kuwa sai ga nurse da wani soja, aka zo aka amsa. Yana isa wurinta ta ce mishi. "Baka saka hannu ba a Matsayin."
"Umaima rayuwar yarinyar ne mai muhimmanci, ba saka hannuna ba."
"Ok"
Haka suka shiga da ita aiki, yana kwance ana diban jinin karshen.
Wurin karfe biyar na Asuba ya fito a hankali yana jin jiri na dibanshi. Dakyar ya isa emergency room. Zama yayi a kujerar da ke cikin dakin, jin kiran Sallah yasa shi nufar masallaci, yana sallah a nan ya kwanta domin wani irin jiri da zazzaɓi yaje ji.
Karfe shida na safe Doctor Umaima ta fito, a matukar gajiye domin babu inda baya ciwo a jikinta. Sannan aka turo yarinyar a gadon marasa lafiya. Aka kaita ward, wucewa daki tayi ta gabatar da sallar asuba, sannan ta shiga hada kayanta. Tana kokarin kiran wayarshi amma ba a dauka ba. Sai da ta cire kayan jikinta sannan ta wuce dakin da aka kwantar da yarinyar, bata ga wani fuskarta sosai ba, ta juya ta fita wurin seven ta bar asibitin. Yana barci a cikin asibitin yaji kiran da wayarshi keyi, kamar a tsakiyar kanshi. Bude idanu yayi da suka yi wani irin fari da ja. Yasa a kunne.
"Sir kana ina ne? Za atafi teku."
Wani irin jiri ne ya kwashi Idanunshi ya ce. "Ok gani nan" kashe wayar yayi ya sauke ajiyar zuciya, kafin ya hada karfinshi wuri guda, ya tashi tare da ɗaukar kome na shi ya fita daga Masallacin domin yasan team lead ɗinsu Commodore Magaji Abba ne, haka yasa ya boye ciwonshi domin ya san halinshi sarai, and yaso ya kuma ganin yarinyar nan, haka ya kwashi motarshi a guje. Sai community dinsu na sojoji. Yana isa a daddafe ya shigar da motarshi, sannan ya wuce kitchen ya haɗa tea me kauri ya sha, kafin wani lokaci ya fara zufa kamar me. Wanka ya shiga yayi sannan ya kimtsa ya fito daga gidan ya turawa Doctor Umamai kudi tare da short Note.
Yarinyar nan idan ta farka please ki bata wannan! Thank you da abinda kika min!
Daga haka ya fita bayan ya dauki duk wani object na aikinsu.

Operation Anaconda plan.

Kai tsaye headquarters dinsu ya nufa, anan ya hadu da Commodore Magaji Abba Chindo, kanshi ya sunkuye yana kallon kasa. "Kun san abin da ya tara mu, mun samu labarin za a fitar da mai ta ruwa. Aikinku shi ne ku dakushe yunkurin yan tada kayar baya shine aikinmu,mu mazaje ne a fagen yaki idan kunso idan kun koma cikin matayenku tow ku daura zanin matayenku,kune kuka sani ba mu ba ku ajiye personal emotion dinku domin dakile aikin yan ta'adda. Muna da Kyakyawar yakinin duk wani sojan kasar nan yana tsaye ne domin bawa al'umma kariya da taimakon gaggawa. Yan kasa ne kaɗai zasu fahimci yadda tasirin kishin kasa yake kun ji ko? Kada wani yayi harbi idan muka kama su, aikin mu shine mu kawo su headquarter ba kashe su ba, domin suma fararen hula ne."
"Yes Sir!" Suka fada da karfi. Sannan suka wuce inda aka ajiye mota, suka shiga shi kam bai wani damu da ya shiga gaba ba, yafi damuwa da baya, haka wani sub-Lieutenant ya bude mishi gaban mota ya shiga, har zai zauna Magaji Abba Chindo ya zo daidai kunnen shi. "I hope kayi ban kwana da danginka! Domin bana fatar ka dawo a raye."
D'ago kai yayi yana murmushi, ya ce mishi. "Kai ne bakon mutuwa!" Ya faɗa yana murmushi. "Wannan murmushin sai ya zame maka mutuwa." Yar dariya yayi ya ce mishi. "Ban sani ba, idan akan aikin da kasan idan na bari ba zai kare ni da kome ba, domin kuwa hmm!"
"Domin me? Kai da aka watsar da kai." Juyawa yayi ya kalli MAC. A fusace yake amma kuma baya jin zai yarda su yi faɗa. Sai ya dauke kanshi yana me kallon gefen driver. "Muje ko!" Wato daga cikin abin da Allah ya hore mishi iya sarrafa fushinsa.

Zai yi wahala ka ga tunzurar shi, idan kuwa ya tunzura yana zame mishi mugun yanayi ne mai matukar tsoratarwa, shi yasa baya son fushi baya son fada, baya son hayaniya, yana ajiye kanshi da yanayin shi a wani aji na musamman. Fushinsa ba haka kawai yake yin shi ba. Maganar Magaji bai dauke ta a bakin kome ba. Har suka bar headquarter suka nufi bakin ruwa. A ka'idar operation Anaconda, kome suka hadu da shi, lakwame shi zasu yi amma daga abinda Commodore Magaji Abba Chindo ya a gaya musu ba a basu damar harbi ba, ba a basu damar kome ba sai dai dakile fashin da za ayi, a motarsu na tafiya kai tsaye ya kira Admiral shugabansu.
"Sir wannan mission din yana da matukar hatsari, idan muka samu kanmu cikin tarkon makiya ya zamu yi? Kasan masu wannan aikin suna dauke da miyagun makamai, sir a bamu damar kare kanmu da rayuwarmu don Allah a tura wannan sakon zuwa ga Oga!"
Admiral duk da ba musulmi ba ne, yana matukar ganin girmanshi, musamman yadda yake da jajjircewar aiki, daukar kasada a kan kowani aiki. Infact shi yana cikin SISA, wato (special intelligent Soldier Agent) sannan ya ajiye haka a matsayin personal life din Yaron, ko wannan operation Anaconda plan din yana cikin sojojin da suka kirkirota musamman yakin south south. Sannan asalin labarin daga bakinshi suka jiyo shi, haka yasa suka kara bincike aka tabbatar za a fita da mai ta teku. Shi yasa aka tura su.
"Ku kare kanku, idan kuka faɗa tarko!"
"Yes Sir!"
Commodore Magaji Abba Chindo, kiran wasu sojoji guda uku, ya umarce su da su je har gidan da ya dauko yarinyar nan, su ci uban Uwarsu, kada su d'aga mata kafa.

**
Unguwar hausawa.
Koda yake ana kiran unguwar ce da sunan unguwar hausawa, amma a zagaye yake da Musulmai da kiristoci, musamman inyamurai. Tun karfe shida na safe ya dace a ce an dawo da ita, amma shiru har karfe takwas.

"Ada wetin happen? I see you dey pass up and down, shebi your Ethiopia girl neva come back?" Inji wata Beyarabiya, cikin takaici da bakinciki Adda ta ce. "Bise kyale ni da yar iska haihuwar asara, me aka yi da haihuwar bakinciki, shad'ari ya haifa mana irin masifa, kaf cikin al'ummar fulani babu miyagun iri kamar anagamba." Ta faɗa tana watsa hannu. Fitowar wata budurwa daga wani daki tana yatsina fuska ta ce mata. "Addah hala irin masifa bata dawo ba ko? Kowa na fitowa bariki arziki ita wannan a barikin ma tsiya da masifa take kara janyowa kanta. Kuma wallahi sojan nan bai da mutumci, ba lallai ya saka condom ba, a tsarinshi baya saka condom. Shi yasa lokacin da ya tab'a daukar Ummi ta dawo tana ta mita, domin tace bata da infection dan shegiya ya zuba mata, mugu. Tow gashi ya dauki Zahrah."
Kwafa tayi tana faɗin."ai ni ban ga amfanin haihuwar Zahrah ba, shegiyar yarinya ta dauko bakin jinin Uwarta. Ke kan ai Munaisah kyanki jarinki gaki tabarkallah, ita waccan yar iskar."

Fitowar wasu yan mata da kayan barci, yasa tana kallonsu. "Zully kin tashi?" Dauke kai tayi kamar bata gansu ba, ta koma dakin ta dauko brush da marclean, ta kuma fitowa. Bakin magudanar ruwan ta tsuguna tana wanke bakinta. "Zulaihah hala laifin tura Zahrah kwanan waje ko?" Nan ma bata tanka mata ba. "Daurawa kai jaraba, wai tana jin haushin abin da ya faru ne?"
"Munaisah babu ruwanki da ni, domin zan ci mutuncin ki." Inji Zully din. Kumshe dariya tayi tana faɗin. "Bani na kar zomon ba, yau wata yarinya zata sha wutsiya gatar gato!" A fusace Zulaihah ta wuce bata kula su ba, sauran yan matan suna mata dariya, domin a duniya rayuwar Zulaihah idan za a ce ta bada shi domin ta kare Zahrah zata bada. Ta tsani irin rayuwar da mahaifiyar take daura yan mata a kai, suma dake son abin duniya da kwadayi yasa suna bada jikinsu me daraja, suna fadawa bariki.

Tashi Addah tayi ta nufi banɗaki ta kama ruwa, sannan ta fito domin ka'idar kiran wayar Mahaifin Zahrah karfe goma na safe, ji tayi kamar zuciyarta zata buga domin karfe goma saura. Wannan wacce irin masifa ce Zahra zata cillata cikinshi? Tunda take kawo yara babu wacce ta tab'a wuce shida na safe bata dawo gida ba, sai Zahrah. Abin karyawa suka yi baki daya taliya da mai da yaji, sai Zulaihah da ta fasa kwai da sadine ta soya da yar attarugu da tumatiri sai albasa, ta shiga daki ta ajiye musu tasan idan ba wani lalura ba, babu yadda zaayi Zahrah ta kai wannan lokacin, idanunta yana kan wayarta, duk wani motsin lokaci tafiya yake da sautin bugun zuciyarta.

A hankali ta kara rike wayar, goma tana cikawa wayar Addah tana kara. Jikinta na rawa ta fado dakin. "Zulaihah ban san me zan gayawa Shad'ari ba, don Allah taimaka ki mishi karya wallahi nayi danasanin turata."
Amsar wayar tayi cikin sanyin murya ta ce. "ina kwana Kawu?"
"Lafiya lau Zulaiha, ya kwananku da na Addah?"
"Lafiya lau Kawu!"
"Ina kawarki?"
"Baffa yau makaranta sun tura su, wani nazari sai nan da kwana uku zasu dawo in sha Allah."
"Tow Masha Allah, Ubangiji ya dawo da su lafiya, Zulaihah don Allah ki kula da Zahrah kin san yadda take bata ji, sai anyi da gaske." Murmushi tayi tana faɗin. "Kawu Indai akan gaskiya ne, ba zan gushe bata goyan baya ba, har sai na koma ga Allah."
"Allah ya muku albarka!"
"Amin Ya Allah, Kawu har yanzu babu labarin Ammynmu ne?" Shiru yayi kafin ya ce mata. "Na tafi har ye'ude ban samu wani labarinsu ba."
"Allah sarki Ubangiji ya bayyana ta!"
"Amin Ya Allah, ya Munaisah ita ko wayar ba zata yi da ni ba ne?"

"Bari na mika mata." Ta mike zuwa waje, ta mikawa Munaisah. "Baffanku!" Amsar wayar tayi ta saka a kunnenta. "Barka dai Baffa."

"Hmm! Ke Wato sai na nime arzikin magana dake, amma ina jin kina kiran Innarki ko?"

"Kayi hakuri Baffa!" Ta fada tana wani had'e rai, Indai zata yi waya da shi tow bata sake jiki tayi wayar kamar yadda take da innarta.....

#thedambuje

[2/16, 9:24 PM] Cutie cutie pie: *BAƘIN HAURE....□□*

{Greed for Money is the roots of all evils□}

Arewabooks:maidambu41

Wattpad:Mai_Dambu

Mallakar:Mai_Dambu

003

Zahrah

Lumshe idanuwa na nayi ina kallon dakin da nake, gari ya waye garai sake lumshe su nayi na kara tabbatar da inda nake, amma wani ikon Allah na kara fahimtar ashe ba lahira aka kai ni ba, a duniya nake, tashi na fara kokarin yi aka ce min. "Ke ki kula da ciwon jikinki mana." Kasake nayi jin mutum ce ke min magana ba daya daga cikin Mala'ikun da suka zare rayuwata ba, bani da karfi ko kaɗan don haka na ce mata. "Don Allah ban mutu ba ne?"

Juyowa tayi ta kalle ni,sannan ta ce min. "Kina da number yan uwanki?" Dafe goshina nayi ina tuna na bar wayata a dakin wancan dan iskan. "Baki ji ba ne?" Sake kallonta nayi na fara fada mata number Zully."Zero eight zero....."har karshen number, kiran layin matar tayi. Aka ce ana amfani da wayar. "Don Allah kira min wannan number." "Zero seven zero..." Lokacin da ta kira wayar ta shiga, an dauka sai dai ihun da ake yi yasa ta kura min idanu. "Ke ungo wayar kiji abinda yake faruwa." Ta mika min, ihu da kuka tare da jin alamar ana musu wani abu yasa na mike gabakidaya, nasan wasu zasu ce hala ban san halin da nake ciki ba ne?

Ganin na mike a hankali har na tsaya da kafaffuna, matar ta ce min. "Amma baki da hankali?" Murmushin wahala nayi domin ciwon kamar yanzu aka ji min, zafi da azaba sun ishe ni. "Eh ni mahaukaciya ce akan dangina!" Eh sune raunina, "ina zaki yanzu?" Matar ta tambaye ni, "zan tafi gida wani abu yana faruwa, idan naje in sha Allah zan dawo don Allah ki bar ni na fita."

"Zai shafi aikina ne!"ta faɗa tana kallon yadda damuwa ta bayyana ƙarara akan fuskata. Amsar wayar tayi ta koma gefe tayo kira, maganar da bai wuce second talatin ba, ta dawo ta mika min wayar tana faɗin. "Jira Doctor tazo."

"Ok" na fada ina kallon agogon ward din, wato wani ikon Allah jiran Doctor da nayi ji nake kamar rayuwata nake jiran yadda xa ayi da ita, domin ban san iya adadin bugun zuciyar da nake ji ba, can har na hakura zan mike, sai ga wata kyakkyawar matashiya ta d'andasa wanka kamar wata fure.

"Sannu yan mata ya jikin naki?" Ta tambaye ni,tana kai hannun ta saman rigata ta d'aga. "Pretty good!" Ta faɗa, "Sisi ta kira ni ta ce min,kina son zuwa gida."

"Eh!" Na faɗa ina kallon ƙasa, "ok wacce unguwa kenan?" Domin bata yi tsammanin ina jin Hausa ba, balle a kai ga wani yare. A'a tunaninta ai daga irin cotonou ko Togo, ko Mali,na fito ko irin yan ciranin Ethiopia nan, Yes haka skin dina yake kasancewar ni ba fara ba ce, amma ina da wani irin dogon fuska da siririn hanci, idanuna manya ne dara-dara.

Ni ba wata dogowa ba ce, domin yar siririya nake, sai dai fa ina da cikar halitta musamman kirji da kugu, a yanzu da nake shekaru sha shida a duniya, ina ji kamar na kama duk abinda ake bukata, sai dai halin irin na rayuwa yasa na faɗa ƙaddarar rayuwa.

"Wacce unguwa kike? Sannan me yasa zaki tafi yanzu bayan baki warke ba?" Kallonta nayi na ce mata. "Ina unguwar hausawa!" Na bata amsa cikin tararadin yadda zata

dauki unguwar da na fito. "Ke Bahaushiya ce?" Hadiya yawu nayi,tare da girgixa kai. Kallona tayi kafin ta ce min. "Fulani?" Da idanu na amsa mata, ina lumshe su, gyada kai tayi tana faɗin. "Jiya an kawo ki cikin mawuyacin hali, bamu jima da miki aiki ba, kice zaki tafi?"
"Dangina suna cikin wani yanayi!" Na fada kamar zan yi kuka nace mata. "Ni dai zan dawo kuma haka na gaya mata, don Allah ku bar ni naje naga halin da suke ciki."
Kallona tayi kafin ta ce da harshen Hausa, "kina son ciwonki kada ya warke ne?" Murmushi nayi kafin na ce mata. "Babu abin da xai samu ciwo na, kawai dai ina son ki kai ni na gansu, don Allah." Na fada mata da hausa. "shi kenan muje!" Ta fita zuwa waje can sai gata da kaya, ta mika min, haka na saka kayan na shiga bin bayanta a hankali, har na isa inda motarta take, wani soja ne ya bude min kofar ita kuma ta shiga baya, suka rufe min motar muka bar asibitin. "Amma me had'aki dashi?" "Wa kenan?" Juyawa tayi tana kallona. "Wanda ya kawo ki?" Hadiye yawu nayi, kafin na ce mata "babu" domin ban san yadda zan mata bayani ta fahimta ba. Har muka fita daga barrack din, ita kanta tunani take a ranta.
Yaushe Captain ya fara bin mata? Tasan a iya rayuwarta bata tab'a kama shi da mugun abu ba, kuma har yau babu wanda zai zo ya ce maka mace tana gabanshi.

A hankali ta maida kanta nazarin yadda ya ji mata ciwo, gabakidaya kanta ya daure ciwon yana bukatar nazari. Har muka bar barrack, hankalina baya jikina sai da naga mun dauki hanyar unguwar da muke zama, na ji kamar an kuma cilla ni cikin wata sabuwar bala'i "ya zanyi da addah idan ta san na dawo babu kudi sai ciwo."
Juyawa tayi tana kallona, ni a tunani na a zuciyata nayi maganar sai na fahimci ashe ba da zuciyata nayi ba, a zahiri nayi. "Zata dake ki ne?" Idanuna ne suka cika da kwalla na ce mata. "Idan duka ne da sauki, mahaifiyata ita ce zata sha zagi." Cikin yanayin dan son ta sha cikina ta ce. "Dama ba mahaifiyarki ba ce?"
Fatimah na hore ki, ki zama me takatsantsan ɗa abin da zai fito daga bakinki. Addah yar Uwata ce kada kuskurenta yasa ki saka duniya ta zargeta.
Hadiye maganar nayi kamar ban tab'a furta koda kalma daya ne ba, kaina a sunkuye muka isa kofar gidan da an yi bala'in cika. Kafin muyi parking motar sojoji ta bar unguwar tana kara da ihun a bata hanya, sai da suka wuce muka samu damar parking, a hankali mutanen suka ragu kowa ya kama gabanshi.
Hango Munaisah sun rufe Addah da mutane suke daukarta a waya, da sauri na fara kokarin bude motar, Doctor ta ce min. "Baki da lafiya fa, ki kula da lafiyarki mana."
Sauka nayi daga motar a hankali, bayan itama ta fito, ban tsaya jin abinda zata ce min ba, wallahi na zura da gudu."Addah" cikin wani irin yanayi me dauke da kallon kiyayya, tsana, takaici, bakinciki, Addah ke kallona."Zahra'u na gode da abinda kika saka aka min. Zahra'u saboda nace mu mori juna ki bada gishiri a baki manda shine zaki wulakanta ni? Zahra'u duk wani abinda nake bawa Ubanku da mishi kome nan nake sayarwa a bani kudi na tura mishi abinci, na bi maza a Saudiya don na ciyar da Ubanku. Duk yan uwanki suna kyautata min Zahrah kece kawai kika zaɓi kuntatta min. In sha Allah ki rubuta ki ajiye kamar yadda kika saka aka tozarta ni, wallahi sai na d'and'ana miki."

"Hajiya kafin ki fara shan alwashi yana da kyau, ki san me ya samu Zahran domin daga asibiti muke; taurin kai da tunda ta kira taji ihun ku, taki kwanciya a ka'idar aikin sai nan da gobe xata fara sauka a gado,amma ta tawo ganin halin da kuke ci!" Ta d'aga mata cikina, inda mutumin duhu ya caka min wuka. Takaici yasa Doctor ta koma motar ta ciro kudi a jakarta,ta kalle ni. "Gashi wannan kudinki ne,wannan kuma ƙatin shiga asibitin ne. Ina fatan zaki dawo a duba lafiyarki"
"Zan dawo"na fada mata, ina sunkuyar da kaina. Har ta juya zata tafi nace mata. "Baki gaya min sunanki ba" "Doctor Umaima Amin Minjibir." Daga haka ta juya zuwa motarsu, suka bar ni a tsaye. "Ke Zulaihah kamo hannunta ku shiga daga ciki, kafin matar nan ta dawo ta maida mata kudin,kin san halin zahararriyar kawarki "

Gabakidaya Addah ta manta da shegen dukar da aka mata, kun san wacece Addah? Addah ta musamman ce a duniyar kaunar kudi, Ya Allah ka mana tsari da irin soyayyar kudin Addah. A haka kuma duk duniya babu me moranta sama da Baffansu Ummi,baffan mu yana dai rike da dabbobinta ne domin babu yadda ya iya da jarabar Addah.

Idan nace zan fara baku labarin kauna da soyayyar da Allah ya daurama Addah kan kudi, sai ku ce karya nake domin haka ba zai faru ba. Addah saboda son kudi. Ta tafi har Saudiya tayi aikin tuwo tuwo.Addah ta zauna a garin lagos tayi harkar tuwo tuwo, kuma kada ku ce iya tuwo tuwon ne fa, A'a har da d'aga buje ana yi babu laifi. Jan hannuna yasa na dawo duniyar tunanin halin Addah, Matar nan kamar Ba ita aka daka ba. Haka muka shiga cikin gidan, Ummi tana gyara gidan.
"Shegiya kin zame mana bala'i da masifa, ban san wacce irin ƙaddara ce tasa adda."
"Ke kyaleta! Sannu Zahrah sannu yar nan, ke Zulaihah saka min ruwa na gasa jikina."
Ta zube kan taburma tana matsar kwalla, kafin na koma can gefe rike da bunch na yan dubu dubu har biyu. Hadiya yawu tayi ganin yadda nake rike dashi. Zulaihah har zata wuce, ta dawo ta amshi kudin ta mika mata ɗaya. "ai kowa yasan g**ndi kika sayar kika ciyar da Kawu shad'ari, duk cikin mu babu yarinyar da fita daya ta dawo miki da dubu dari biyu, sai yar baiwa me kafar sa'a don haka ga dubu dari nan ki warware gajiya, daga yau Kawu shad'ari kudin yar baiwa zai ci, muje Zahrah kici abinci mu koma asibiti. Ina rokon Allah kada yasa ki yi karkon kifi daga ruwa zuwa wuta. Duk me hankali ya ga ciwon nan yasan kin tsallake siraɗin rayuwa da mutuwa "
Da sauri Adda ta wawuri dubu darinta,tana washe baki. "Kema dai Zahra hala taurin kai kika mishi,ya burm.. ke daya waye ya turo sojoji suka min shegen duka?"
Dariya Zulaihah tayi ta ce "Ai kuwa gajarabul din da ya dauke ta mana ko Zahra?"
Bakina ya mutu murus Allah ya horewa Zulaihah baiwar predict duk abinda tayi hasashenshi sai ya tabbata haka.
Tsakin Munaisah muka ji, ta juya tana me faɗin. "A gama boye-boye sabo da kaza bai hana a yankata." Ta faɗa tana nufar dakin mu, haka muka bita muka bar Ummi a wurin Addah. Lokacin da muka shiga dakin. Zulaihah ta haɗa min tea, "Zahrah kin gudu a hannun gayen nan ko?"
"Eh zuzu!" Na fadi haka, ina kiranta da Zuzu saboda jin dadin sunan, Zulaihah ta girme ni, don kusan sa'ar Munaisah ce, a ƙalla zasu kai shekaru ashirin a duniya.

"Zahra'u! Ina kara baki shawara kada ki zama bolar da kowa zai zuba sharar shi akai."
Na gode na sha tea din kaɗan, sannan ta shirya ya kwashi kayan mu kala uku nata uku nawa uku. Muka fito tana rike da hannuna. Sai lokacin na ga jini yana zuba.
"Zuzu mutuwa zan yi?" Na tambayeta, Addah ta fito ta sha kwalliya kamar wata yar tsanar roba, domin bakin nan har da jan baki,ta kalle ni "za a koma asibitin ne?"
Gyada kai nayi, murmushi tayi sannan ta ce mana."tow ita Zulaihah da zata bi ki can, ta manta tana da kwastamomi ne?"
"Zan tura miki dubu talatin ta account ɗinki!" Kallonmu tayi kafin ta ce mana, "Anya Yaran nan baku cin junanku? Wannan shakuwar tayi yawa ku gaya min gaskiya me yasa kuke zartas da hukuncin junanku. Idan kuna cin juna ne na sani domin a bani kasona domin banga amfanin tara munafukai irinku, kuna cutata ba. "
"Yanzu addah don Allah wani yace miki, muna soyayyar jinsi ba zaki ji wani iri b?"wani tsalle tayi ta koma gefe can,"Kambu wallahi bani jin kome,kawai kudin daki zaki kara min na saka a muku shamaki da gulmar su Munaisah an kashe boss."

"Allah ya shirya ki Adda" inji Zulaihah muka fita, har waje ta biyo mu, muka tari taxi muka gaya mishi inda zai kai mu,kamar ba zai amince ba, sai kuma ya ce muje. Haka muka tafi har zuwa asibitin,kamar zan yi hauka domin kuwa ciwon ya taso ni a gaba. Haka muka isa har asibitin aka karbi katin, muka shiga.

Dr Umaima.

Tun dawowarsu bata wuce gida ba, domin yadda Zahrah ta arta aguje tasan sai an dawo da ita dole, don haka bata da wani aiki amma ta kasa tafiya, tana ji kamar akwai abinda take son ta sani dangane da yarinyar, tana asibitin har awa biyu. Aranta tana jin kamar ta tafi, amma ƙwaƙwalwarta na gaya mata zata zo, haka ta cigaba da tsayuwa har minti ashirin ya wuce idanunta yana kan wayar,minti takwas yazo zai wuce shima daidai babban hannu ya daura kan minti na tara, siririn hannu ya wuce kan taran kenan,taji dirin motarsu, ajiyar zuciya ta sauke tana tsaye idanunta na kan kofar.

..... Dakyar nake jan numfashi, domin zuwa yanzu na fahimci akwai dalilin da yasa jinin yake zuba, muna isa har bakin kofar Emergency,ya tsaya Zuzu ta fito da ni. Muka shiga cikin asibitin.
"Kun dawo?" Ta tambaye mu! "Eh Aunty, gashi jini yana ta zuba."
"Gudun da ta arta lokacin da muka isa ya haifar mata da zubda jinin" ta fada tana rike ni na kwanta, Zuzu ta fita tare da biyan mai motar kuɗinshi, ta dawo anan aka wuce wani daki dani, Zuzu tana zaune cikin tararradin mai zai faru.
***
Addah tana fita bata tsaya ko ina ba, sai gidan Malam Sammani wani dan arewa ne,da yake harkan malunta irin masu duban nan, kallonta yayi yana shafa gemunshi. "Zahra'u!" Ya kara zana sunanta a kasa, ya saki ƙasaitacciyar murmushi."yarinyar nan yar baiwa ce kamar yadda Yarki ta ce, tauraronta karfin tsiya ne da shi, domin ta gaji haka daga Uwarta,da kin barta da dan uwanki da ba karamin arziki zai yi ba, sai dai ƙaddarar da kika kirkira da hannunki ya shiga tsakaninku da arziki, sai dai kici a jikin yarsu. Wato yarinyar nan jiya tauraronta ya hadu da wani raunannen tauraro, kuma Qaddarar da ba a san me zata haifar ba gobe ta shata tsakaninsu. Ban san me zai faru gobe ba, amma tafiyar ƙaddara tana nan da riskanku baki ɗaya. Idan kina son zaman lafiya ki bi yarinyar nan zaki huta kowa zai huta, bayan ita babu wacce zata iya mallakar arziki domin duk inda ta shiga sai ta had'a arziki."

"Allah gafarta Malam, ina da mafarki akan Zulaihah ita fa?"
Share ƙasar yayi sannan ya rubuta sunan Zulaihah. Dariya yayi sannan ya ce mata. "kamar yadda baiwa take a gaban Uwar gijiyarta haka Yarki take a gabanta"
"Don Allah Malam duba min na sauran. "
Murmushi yayi ya ce mata. "Sunansu;"
"Munaisah!" Rubuta sunanta yayi yasannan ya kalli Addah. "Lallai kin hada masifar da ba zaki iya kashe ta ba, sai Allah babu kome a tare da ita sai bautar da zaku mata, amma.kuma zaki dan huta a jikinta kamar yadda kike hutawa a yanzu."
"Ummi fa?"
Rubuta itama sunanta yayi, sannan ya ce mata. "Ita wannan igiyar ruwa ce, duk inda ruwa ya jata bi zata yi. "
"Malam kace Zahrah zata...." Rubuta sunan Zahrah yayi ya cika tiren, yana murmushi ya ce mata. "Har ki mutu ba zaki daina cin arzikin ta ba"
"Malam kana nufin babu wanda zai."
Hannunshi ya kai kirjinshi, "na gama aikina indai ba so kike nai miki karya ba,kuma duk inda zaki je babu wanda zai gaya miki wani abun da ya wuce haka, idan aka gaya miki akasin haka karya aka miki wallahi."
Kudi ta ajiye mishi, ya girgiza kai ya ce mata."Ni yau bani bukatar kudi, can kasa nake son na rage gajiyata." Wani irin malolon bakinciki ne ya cika Addah, ta ce mishi "tow Malam" haka ta cire kayanta, suka kwanta a dan farin buzun malam na aiki, bayan ya rufe kofar, ai kuwa yazo bai wani mata wasa ko wani abu ba,. malam kamar jaki haka ya zo mata, yana sama da kasa akanta, surfeta yake yana zuba mata rashin mutunci, ta hanyar saduwa da ita kamar wata bebin roba, Addah ta ci azaba a hannun malam kamar ba gobe.
***
Operation Anaconda plan.

Suna isa bakin ruwa suka shiga cikin jirgin, kowa ya ajiye kayanshi ban da Captain da ya nufi inda matukar jirgin suke, ya fito da Map na inda zasu ya shimfida akan wani table.
"Likitan soja, Captain akan ruwa."
Murmushi yayi ya cigaba da warware taswirar, sannan ya fito ya sarawa Commodore Magaji Abba Chindo ya ce mishi. "Ko zaka zo ka duba taswirar!". Kafin ya rufe baki Magaji Abba Chindo ya kai mishi naushi, da sauri ya rike hannunshi.
"Please Sir kazo ka duba abinda na ce maka."
"Idan naki fa "
"Shi kenan!" Ya fada yana wucewa, "Guys idan Captain ya dake ni zan bishi sau da kafa, idan kuma na dake shi,kada na kuma ganinshi ya hauro kan ruwa sannan zai zama driver na."
"Commodore!!!!" Wasu daga cikin sojojin suka fara kiran sunayensu, wasu na cewa.
"Captain!!!"
"Look ni bana son faɗa!"
"Sai kayi sai kayi!!!"
Dama a cikin sojojin akwai waɗanda suke bayan Commodore, wasu kuma suna bayan Captain, na farko yana da matuƙar kamun kai,.yana da nutsuwa da sanin ya kamata, sannan duk inda suka shiga lokacin sallah yana yi zai gabatar da sallah.

Babu ruwanshi da hassada ko kyashi,gashi mutum ne mai yawan alkhairi da kyauta, bai da girman kai baki ɗaya, haka Allah yayi shi, abu daya mutane suka sani shi ne, akwai kauna da amana a tsakaninshi da duhu.
"Indai kai ba shege bane, ka zo ka gwada mana mazantakarka, matukar ba cin kanka kake a cikin duhun nan ba, ka zo nan, ka gaya mana shin hannunka domin aiki da sarrafa bindiga take zaune, idan kuma domin mulmula doguwar tsokar da take tsakanin cinyoyinka.."
Dariya aka kwashe ban da sauran sojojin da suke tare da Captain, suna masifar jin haushin Commodore,amma babu yadda suka iya, sai dai a wannan karon alamar dai maganar tayi tasiri.....
#thedambuje
[2/16, 9:24 PM] Cutie cutie pie: *BAƘIN HAURE....□□*

{Greed for Money is the roots of all evils□}
Arewabooks:maidambu41
Wattpad:Mai_Dambu
Mallakar:Mai_Dambu

ZINARIYAR MACE⚡
Wai shin 'yar'uwa menene matsalarki? zubewar nono, ko kuma rashin kwankwason juyawa a falo maigida ya shiririce ya manta da tibi da matan tictok, menene matsalarki ne? rashin ni'ima ko kuma mugun sanyin da ya yi miki katutu, shin rashin taushin fata ne ko kuma kuraje da tabbani, ko bala'in ramar da ta addabeki kuma babu rashin ci ba rashin sha a gidan auranki, gwaigwayewar gashi ce matsalarki ko kuma kaushi da faso na tafin kafa da bushewar fata, kina bukatar fatarki ta yi glowing kalarki ta fita kuraje su mutu, ko kuma kina bukatar azababbun turaruka da humra tare da turarukan wuta. Na san dai kuna da yawa matan da tumbi ya yi musu karan tsaye ina nufin ya katse muku hanzarin yi wa maigida gwalli da muskuce-muskuce a falo😀 Nesa fa ta zo kusa AL-KUTUBIYYA ISLAMIC MEDICINE sun tanadar muku da nau'in magungunan da suke magance kowace irin matsala da izinin Allah. Babban burinmu shine sha'ani na aure ya inganta a samu daidaito. Muna da.
Na gyaran nono.
Na sanyi.
Dilka tare da hadin sabulu.
Duk Wani nau'in maganin mata.

Humra turarukan wuta perfumes, original miski tahra 3in1, ciccibi budurwar kaza. Had'addun supplement irin wad'anda ba su da matsala. Maganin Sliming wato narka tumbi. Abubuwan da muke sayarwa suna da yawa, kuma babu asarar dukiya. Muna garin kano kuma muna tura kayanmu kowane gari fad'in Najeria da Nijar har ma da kasashemn ketare. Kai tsaye a tuntu'bemu ta lambobin wayarmu domin karin bayani.
08089965176
07084653262

004

Captain

Juyawa yayi ya kalli Magaji Abba Chindo da yake mishi dariya, idan ya sake suka yi faɗa. Tow yau ba zai iya samun nutsuwa ba, don haka ya saki dan ƙaramin murmushi ya ce mishi. "Sai a ka yi rashin dace, ni mata-maza, bana haɗa jikina da yan maza, musamman waɗanda basu dauki aikata sabo illa ba." Daga haka ya juya abinshi, shiru wurin ya ɗauka, abin ya bawa Magaji Abba Chindo dariya, amma da ya nutsu sai ya fahimci da gaske Captain magana ya gaya mishi. Mikewa yayi zuwa ciki jirgin don da suna daga waje ne.

"Kai magana ka gaya min?"

Murmushi Captain ya yi sannan ya ce mishi.

"Kaga ni bana son tashin hankali, kayi hakuri ba magana na gaya maka ba." Kurawa juna ido suka yi, sannan ya fauce Map din hannun Captain ya yaga gida biyu.

"Naga yadda...!" Kafin ya rufe baki Captain ya zabga mishi marin da sai da ya daina gani. D'ago shi yayi ya ce mishi. "Kada ka sake wani yaji wannan labarin domin zai maka dariya, kada ka kuma aikata abin da kayi. Ni idan kaci zarafina zan yafe maka. Amma idan ka taba aikina zan baka sakamakon da yafi haka. " Wato marin nan, ya shiga Magaji domin kuwa hakorin shi na wannan bangaren har yana girgiza.

Sauran matuka jirgin duk hankalinsu na kan aikinsu, babu ruwan su kuma haka da Captain yayi shi ne zaman lafiya, don haka, A hankali ya juya tare da fita daga dakin, Captain ya gyara takardan, bayan Mr Oke ya mika mishi salatep, ya gyara suna hira sama sama.

Lokacin sallah yana yi suka fita baki ɗaya, musamman Domin a yi sallah wanda Captain ne ya jasu, sannan aka ɗauko abinci da wasu daga cikin sojojin suka dafa, mika mishi aka yi ya kalli agogon ya ce musu. " Na koshi!" Haka suka kyale shi, ya tashi tare da ɗaukar abin hango wasu abubuwan, yana me duba gabansu.

Komawa ciki yayi ya dauki wata waya,ya shiga duba sakon.

Sir mutanen nan basa gudanar da kome sai dare yayi,hankalin kowa ya koma tsoron dare. Kada ku shigo da rana domin zasu gudu mai da wayar yayi ya ajiye, taya zai yi facing Commodore? Haka ya daure ya fita ya zauna a gabanshi.

"Yallabai!" Cikin wani irin yanayi Commodore yake kallon Captain kamar ya shake dan banza amma yanzu ya fahimci gayen ya wuce tunaninshi. Mari daya yayi mishi, hakorinshi yake girgiza ina kuma da sun daku, tow kuwa kareraya shi zai yi ya tara dan iska a gefe kenan? "Meye?" "Inda zamu shiga basa kome da rana, sai dare."

"Tow me kake so nayi?" Ya faɗa yana nad'e hannunshi a kirji. "Ina ga a tsaya nan, sai mu duba nisan kafar ruwan, idan nisan ba yawa sai muyi musu shigar dare."

"A matsayinka na wa?" A hankali yayi kasa da kanshi kafin ya ce. "A matsayina na soja, kuma shugaban rukunin sojojin da suke aikin sirri, mataimakin ka. Na bada shawara kuma na fita." Ya faɗa yana me mikewa daga gaban Magaji ya nufi dakin iko. Jikin Magaji ne yayi sanyi, kudirinshi shine a kashe Captain a wannan lokacin, kuma ba zai fasa ba.

Don haka ya mike tare da fito da sabon tsarin da ya sauya, a ka'idar zuwansu nan. Shi ne shi zai jagoranci wasu daga cikin Yaranshi su isa har inda ake zaton abin, amma son zuciya irin nashi, sai ya kalli Captain ya ce mishi. "Kai da team dinka zaku tafi inda ake badakalar, ni da team dina zamu zauna a nan. Domin ba za a rasa

wanda zai iya kawo farmaki ba, idan kuma ba a samu ba kunyi nasara, ga fireworks sai ku sanar da mu."
"Amma Sir wannan abin babu tsari, taya kana shugaban sojojin kuma kace Captain zai jagoranci wasu daga cikin mu, kuma mutumin da bai tab'a rike bindiga ba, aikinshi kawai sanin meke faruwa."
"Shi namiji ne, idan har ya cika namiji ya jagorancin tafiyar."
"Na amince " ya faɗa tare da ware wasu daga team ɗinshi. "Zamu tafi in sha Allah hakkina ne, na bawa rayuwarku kariya,ku yarda da ni in sha Allah zan mai daku cikin iyalanku lafiya."
"Mun amince " suka fada, sannan ya shiga musu bayani tare da tara su a cikin wurin tukin jirgin, yana nuna musu yadda tafiyar zata kasance.
***
Addah

Kallon Addah mutumin yayi ya ce mata. "Ki kula da zuciyarki kada ki aikata abin da zai dame ki, ita yarinyar babu ruwanta." Kasa magana tayi can ta daure ta ce mishi.
"Yanzu haka 'yata zata kasance? Babu wani cigaban rayuwa sai ta karuwanci? Karshenta."
"Ba farinciki da nutsuwa ake nima ba?" Ya tambayeta yana gyara zaman wandonshi, domin yana matukar jin dadi Adda tana cikin mata na musamman da yake mu'amala da su. Murmushi yayi yana faɗin, " A gaskiya bakya tsufa " dauke kai tayi ta gyara jikinta, sannan ta dauki jakarta ta bar dakin, tana fita waje ta sauke ajiyar zuciya, tana jin wata iriyar tsanar Zahra. Duk inda zata aiki akan zahrah sai ta bada kanta bata san me yasa haka ba, yarinyar ta shiga ruyuwarta ita da take tutiyar ta samu hannun jari, ashe bala'i ta daukowa kanta.

Hadiye bakinciki tayi ta shiga kasuwa tayi sayayya. Sannan ta dawo gida ta mikawa Ummi wata leda, ta ce mata. "Ki girka mata wake da hantar mu kai mata asibiti!" "Tow ai basu bamu kati ba" "eh idan kuka isa ku kira Zulaihah."
"Hmmm!" Inji Munaisah, ta cigaba da gyaran farcenta, domin tana son zuwa saloon a mata fixing farce. "ina son zuwa saloon dai, domin farce na da kaina yayi datti." Da Ace Munaisah ta san halin da Adda take ciki ba zata fara fadar ita zata saloon ba, dauke idanun tai kanta ta wuce ɗakinta. Sai da tayi wanka ta cire roban condom din mata ta wurga cikin masai din, sannan ta wanke gabanta tass. Sannan ta gyara ta fito, Adda ta san darajar gyaran jiki, shi yasa take gyara jikinta. Duk da abin da take yi be dace ba, amma kuma ita ta dauki haka a matsayin wata hanya ta samun kudi cikin sauki,

Aiki take amma a zahirin gaskiya gangan jikinta ke jagorantar aikin, amma zuciyarta da kwakwalwarta basa bata haɗin kai, baki daya ta kashe rayuwarta domin yau ta samu riba, tana son ace yau ta zama wata hamshakiya, amma wani ikon Allah rayuwarta da na Yarta ne a lalace, wanda take ganin ta maida ita baya an gaya mata ba zata iya kome da ƙaddarar ta ba, "hmmm!" Ta fada tana kallon tilin kayan da ta sauke daga wardrobe ɗinta, tana mamakin me yasa meta da wannan aikin? Lallai ya kamata ta mike wannan lamarin sai kace an saka mata hannu. Jin muryar yan matan da suke mata aikin abinci suka shigo gidan yasakata mikewa

"Ina Zahrah take?" Jin murya Shamsiyah yasata fitowa daga cikin ɗakinta tana kallonsu. "Tana asibiti ba lafiya." Daga haka ta nuna musu kome da kome da ta sayo, sannan ta wuce ɗakinta ta kwashe kayan. Wurin karfe daya na rana Zulaihah ta kirata. "Wai Addah ba za a kawo mana abinci ba ne?" Runtse idanuwan ta tayi kafin ta lailayo wata uwar ashar ta maka mata, "babban.....,,, ubannki! Ba za a kawo ba kina da abinda zaki fada ne? Shegiya mara mutunci."
"Addah dubu dari aka baƙi, idan ba zaki d'aga kafa ba, ki dawo min da kudin mu maza, dawo da saba'in xan baki talatin din."

Kamar ta fasa ihu tayi shiru, kafin ta ce mata. "Bana son iskanci, nace ba za a kawo muku ba ne? An jima za a kawo muku." Ta fada a fusace, "Adda ihu kike mana fa?" Inji Zulaihah. "Yanzu don Allah na ce muku ba zan kawo ba ne, ku yi hakuri me da me kuke bukata?"
"Yawwa a hada mana da kofi biyu, kayan tea flask da kuma special abinci dare da rana. A kula da mu kamar baki Hajiya Addah."
"Shi kenan za a kawo muku." Wannan shine asalin dole kanwar naki. Haka suka kashe wayar, kowa najin babu dad'i ita Addah tana ganin kamar Zulaihah bata kyauta mata, ita kuma Zulaihah tana haka ne domin huce takaicin Mahaifiyarta.
***
Zahrah
Ruwa aka sanya min, bayan an kara duba min ciwon, shi ne aka fito dani, yanzu dai sun saka min ruwa da wasu allurai. Ina jin wayar Zulaihah da Addah, a hankali barci yayi gaba da ni. Ban farka ba, sai wurin karfe uku, na samu Munaisah da Ummi suna hira sama-sama. Zulaihah bata dakin, kallonsu nayi kafin na ce musu. "Kunzo ne?" Domin ban kawo a raina zasu zo ba. Kallona suka yi kafin suka ce min. "Eh amma ke taya aka yi ana yin abun arziki ta kasa ke taya kika kare da gefen cikinki?" Shiru nayi ban ce musu kome ba, shigowar Zulaihah da Dr Umaima yasa ni kallonsu ina kakaro murmushi. Ganin su Ummi da Munaisah sai Dr ta kara yarda wani lokaci halittar kyau da hasken fata bala'i ne, domin kuwa Munaisah hancinta da huji, kunnenta kuwa har saman kunnen a makale suke da barima har da na gwal.
Sannan ta kara kallonsu ganin yadda suke wani, iyayi yasa ta sha jinin jikinta waɗannan yan matan sun fini wayewa da gogewa a bariki, ni din kamar sabuwar yankar rake ce, shi yasa har nake gadon asibiti tow ko da ta koma gida ta ji kaninta yana bata labarin ai gida gida, Magaji Abba Chindo ya sa aka yi ta niman wata yarinya da ya dauko daga cikin gari. Kallona tayi tana mamakin anya ba ni ba ce? Duba min ciwon tayi tana faɗin. "Kin yi sallah kuwa?" Girgiza kai nayi. "me yasa kike wasa da sallah.". Kura mata idanu nayi kafin na bude baki ta daura da cewa. "Sallah tana kare mutum daga aikata alfasha, idan har kika kiyayye sallah, a duniyar nan babu wanda ya isa ya cutar da ke, sai dai abin da Allah ya rubuta xai same ki."
"Na gode zan kula, bana wasa da sallah amma daga faruwar wannan al'amarin nayi wasa da sallah har subhi da zuhur sun wuce ni"
Murmushi tayi sannan ta juya tana kallon Zulaihah. "Idan kika hada mata tea, tayi sallah ko a zaune ne sai ta sha rabin kofi."
"Abinci fa, domin gashi an kawo." "Sai jibi saboda tumbin ta ya tabu, tasha tea din idan babu abinda ya faru, zata iya cin abincin."
"Shi kenan" ta faɗa tana hada tea din, sannan ta fita daga cikin ɗakin, haka Zulaihah ta rike ni har ban daki ta taimaka min nayi alola, sannan na dawo dakin na gabatar da subhi da zuhur, ina idarwa na amshi tea na sha, ciwon ciki ne ya sako ni gaba, kamar zan mutu kiranta Zuzu tayi suka shigo dakin. Wuce dani wurin scanning aka yi, aka min anan suka ga ɗinkin cikin bai yi da kyau ba, akwai buƙatar a sake min wani aikin yau. Alluran rage zafi tayi min, sannan suka wuce aka fara shirin, a lokacin Adda ta kira su Ummi tana faɗa akan me basu dawo ba, suka gaya mata ai aikin aka kuma shiga dani, babu shiri Addah ta nufo asibitin, domin abin ya bata tsoro kada garin niman duniyarta, na rasa rayuwata. Bata san amsar da zata bawa Shad'ari ba.

Haka kuwa ta iso a gigice, tana tsaye har aka fito dani. A galabaice jikinta yayi matukar sanyi, ita tsoro take ji kada na mutu, haka suka bi ni har dakina, "Likita ya aikin?" "In sha Allah an dace, dama na farko munyi shi tare da bin raunin ne, amma na yanzu mun yi shi ne da bin duk inda yake ciwon."
"Hmm! Kuma nawa ake bukata? Domin akwai kudi a hannunsu." Kura mata idanu Umaima tayi kafin ta ce mata. "Allah sarki, ai Captain ya biya kome babu abinda ake bukata duk kudin da za a cire a insurance ɗinshi za a cira."
"Kai madalla."

Murmushi Addah ta sake tana faɗin. "Don Allah ko zaki taya ni amsar kudin hannunsu, ki ce musu akwai wani abu da za a saya." "Hajiya anya kece kika haifi yaran nan?" "Kai haba daya Kyakyawar me dogon hanci da dogon gashi, ita ce na haifa. Ita kuma mara lafiyar da wancan me doguwar riga ruwan toka ubansu daya kanina ya haife su, ita kuma daya fara tas din can itama yar Kani nace, Zahrah ce ta dauki duhun fatar Uwarta ai kin gansu nan." Gaba Doctor Umaima tayi ta barta a nan tana surutu, haka kawai take jin Addah bata mata ba, Indai zaka kawo Yara ka daura su kan wani yanayi mara daɗi, meye ribarta? Itama Adda dakin da aka kwantar dani ta shigo, tana tsaye sai yamutsa fuska take tana faɗin. "Ita dai wannan shegiyar ta san hanyar b'adda kudi loko-loko, ban da iskanci da wulakancin taya zaki kare a gadon asibiti akan ciwon da bai taka kara ya karya ba, mtsew." Ta ja tsaki tana isa bakin gadon yarinyar nan yar bala'i, a ranta domin kuwa ta ga yadda ran kowa yake a b'ace idan ta cika mita kan yanayin da ake ciki.

"Tow ai ku muje ko, tunda an yi aikin a sa'a" ta fada tana barin dakin, haka suka bi bayanta ban da Zulaihah da take zaune, ta saka ni a gaba tana kuka. "Ya Allah kai ka jarabce mu Ubangiji ka tashi kafadar Zahrah." Ta cigaba da kukanta, har aka yi sallar la'asar tayi sannan ta koma ta zauna. Shigowa Dr Umaima tayi tana faɗin. "Kuka ya isa haka, ki ci abinci."

"Ba zan iya ci ba, bayan Zahrah tana kwance."

Shiru suka yi, sannan Dr ta ce mata. "Matar nan Mamarki ce?" Rintse idanunta tayi tana jin kamar an watsa mata ruwan zafi a jikinta, don dai Allah ya ƙaddara zata zo a tsagin addah ne amma da ba zata tab'a yarda a ce Addah mahaifiyarta ce ba.

"Eh Mamata ce."

"Allah sarki naga kuna kama sosai."

"Eh haka mutane ke faɗa muna kama da Adda, shi yasa duk lokacin da wani ya ganni sai ya tambayeta ko ya tambaye ni."

Daga haka tayi shiru itama Dr Umaima bata zake sai ta san kome akanta ba, amma zucuyarta ta kwadaitu da son sanin wacece Ni?

★★

Tarkon makiya

Bayan an yi sallar Isha, da ya jagorance su, yayi musu addu'a. Sannan ya mike tare da kallon sauran abokan shi da suke su bakwai ne, sauran kaso masu girman suna tare da Commodore Magaji Abba Chindo, murmushi yayi sannan ya dauko kayan aiki, yana kuma da kayan da zasu saka idan zasu faɗa cikin ruwa. "John ko zaka zauna anan ne naji kace matarka ta kusan haihuwa."

Daukar kayanshi yayi yana sakawa, "Cab ai nayi Imani da Allah, amma gara na mutu a filin yaki da ace ina nan, ina jiran dawowarku." Ya fada yana saka rigar ruwanshi domin ana iska don har tana kad'a jirgin ruwansu.

"Ammar kai ma ko zaka zauna ne, kace rabonka da Misau tun haihuwar Anam, saboda inda zamu mutanen suna dauke da miyagun makamai."

"Hmm! Fatana kada Kasata ta mance da 'ya ta."

"Kana nufin zaka bi ni kenan!" Haka yayi ta rokonsu da su hakura da bin shi, amma ina baki daya suka nace, sai sun bishi anan ne suke ta hira da zasu tafi wurin karfe tara na dare, ya dauke su zuwa wurin Commodore. "Zamu tafi Sir! Dayawa sun daura hakkin kula da rayuwarsu akanka da kuma ni, Sir sun yarda da kai ne suka gwammaci su zauna da kai, Sir hakkin mu ne mu kare kasarmu da mutanen da suke karkashin kulawarmu. Please Sir gasu nan"

Har ya gama maganar Magaji Abba Chindo,bai ce mishi cikanka ba domin kuwa baya fatan ya bude baki yayi magana, Babban burin shi Captain yana barin jirginsu yan tada kayar baya su yi musu daga-daga da namar su, shi yasa da ya ce ya tafi,ya fara bin sauran yana gaya musu ai fa Captain da suke ganin zasu bi, bai da lafiya da zaran an fara harbe-harbe cutarshi zata motsa. Muna cikin zamani ne da son kai yayi mana katutu, kowa son ranshi yake haka yasa baki daya suka janye bin bayan Captain.

Kuma an gayawa Captain amma kuma bai ce kome ba, domin bai dauki haka a matsayin wani abu me muhimmanci ba. Yasan Commodore Magaji Abba Chindo yana jin haushinsa, amma kuma bai kawo a ranshi kiyayyar zata girmama haka ba, sai dai ya ce Allah ya kyauta.
Haka suka bar wurin da jirgin yake da wasu kananun jiragen ruwan, masu colour din navy blue. Haka suka shiga tafiya daidai an fara ruwan sama me karfin gaske.
Haka suka yi ta tsala gudu, a nan Jirgin aikinsu, suna barin wurin aka shiga shagali da hidima, dama kafin dare sai da Commodore ya tura wasu matasan sojoji biyu suka kwasu musu yan mata, aka shiga shagali.
Haka yasa yaki barin Captain zama domin, yasan matuƙar yana nan ba zai bari ayi shagalin ba, asalin sun manta da aiki suka zo yi, haka yasa suka yi ta shagali ga shi ana ta ruwa kamar da bakin kwarya.
---- A bangaren Captain da mutanen shi, ba karamin gudu suke ba, kasancewar takun yana jan jirginsu, karshe shi ya amshi tukin, ya kalli John ya ce mishi. "Da matukar hatsari fadawarku ruwan nan, a daidai wannan lokacin don haka tunda ana ruwa ku kashe fitilar goshinku, zamu isa har jikin jirgin."
"Ok Sir" shi ya fara kashe wutar nashi sauran mutane bakwan suka kashe nasu.

A hankali suka yi ta tafiya, har suka isa wurin babban jirgin da yake dauke manya cantainers, zuwa kasashen waje. Tsayawa suka yi kusa da jirgin, sannan suka harba abin da zai rike su idan suka sauka daga cikin jirginsu. Hakance kuwa ta faru duk su bakwai suka shiga cikin ruwan bayan sun daure kugunsu da wata igiya, sannan suka fara hawa jikin jirgin har suka shiga saman jirgin.

Babu kowa, Captain shi ya musu jagora, har cikin jirgin inda ya fahimci za a fara kwasar man saura wani lokaci kadan, don haka suka samu maboya suka boye, tare da samun bayanai akan kari. Sun kai wurin karfe sha biyu kafin aka fara aikin kawo danyen man fetur din, don haka sai da suka samu damar musu kawanya, kafin suka bude wuta a sama, dole yan daban suka yarda makamansu, domin abin ya basu mamaki, "dama sojojin da aka kaiwa hari daban ne da waɗannan sojojin?" Inji Shugaban yan daban. "Captain ka ji sun kai hari jirginmu.....
Waye zai mutu? Waye zai rayu follow my golden Pen.
#Thedambuje
[2/16, 9:24 PM] Cutie cutie pie: *BAƘIN HAURE....□□*

{Greed for Money is the roots of all evils□}
Arewabooks:maidambu41
Wattpad:Mai_Dambu
Mallakar:Mai_Dambu

ZINARIYAR MACE⚡
Wai shin 'yar'uwa menene matsalarki? zubewar nono, ko kuma rashin kwankwason juyawa a falo maigida ya shiririce ya manta da tibi da matan tictok, menene matsalarki ne? rashin ni'ima ko kuma mugun sanyin da ya yi miki katutu, shin rashin taushin fata ne ko kuma kuraje da tabbani, ko bala'in ramar da ta addabeki kuma babu rashin ci ba rashin sha a gidan auranki, gwaigwayewar gashi ce matsalarki ko kuma kaushi da faso na tafin kafa da bushewar fata, kina bukatar fatarki ta yi glowing kalarki ta fita kuraje su mutu, ko kuma kina bukatar azababbun turaruka da humra tare da turarukan wuta. Na san dai kuna da yawa matan da tumbi ya yi musu karan tsaye ina nufin ya katse muku hanzarin yi wa maigida gwalli da muskuce-muskuce a falo😀 Nesa fa ta zo kusa AL-KUTUBIYYA ISLAMIC MEDICINE sun tanadar muku da nau'in magungunan da suke magance kowace irin matsala da izinin Allah. Babban burinmu shine sha'ani na aure ya inganta a samu daidaito. Muna da.
Na gyaran nono.
Na sanyi.

Dilka tare da hadin sabulu.
Duk Wani nau'in maganin mata.
Humra turarukan wuta perfumes, original miski tahra 3in1, ciccibi budurwar kaza. Had'addun supplement irin wad'anda ba su da matsala. Maganin Sliming wato narka tumbi. Abubuwan da muke sayarwa suna da yawa, kuma babu asarar dukiya. Muna garin kano kuma muna tura kayanmu kowane gari fad'in Najeria da Nijar har ma da kasashemn ketare. Kai tsaye a tuntu'bemu ta lambobin wayarmu domin karin bayani.
08089965176
07084653262

005

"Captain mai zamu yi?" Shiru yayi yana kallon yan tadda daya bayan daya. "Sir me zamu yi?" A hankali ya saka hannunshi ya ballo tear gas, tare cilla musu, sannan suka ƙare fuskokin su, ai kuwa sai ga hayaki fuuuuu, haka yasa shi shiga cikin hayakin tare da kama su sannan suka daure su baki daya, kafin ya mike yana faɗin. "John zaka tsaya anan, kai dasu Ammar, duk wanda ya motsa ku sakar miishi wuta ko waye shi?" "Ok Sir!" Sai da ya karkasa su sannan ya sauko ruwa ya nufi inda jirginsu yaƙe na aiki. Sosai yayi shirin tunkarar asalin jirginsu da aka kaiwa hari.

Koda ya isa ya samu babu kowa a cikin jirgin sai wasu mutane biyu, da suka jikata sosai. Durkusawa yayi a gabansu. "Me ya faru?" Cikin azaba da Harbin da aka mishi ya fara bashi labarin. "Muna cikin shagali bayan tafiyarku sai kawai muka kaji ƙaran harbi, ashe yan fashin tekun ne suka mana tarko." A hankali ya mike tsaye duk da ruwan da ake yi, dafe kanshi yayi ya koma cikin jirgin mutum daya ne a cikin matuƙan ya tsira shima yadda ya fada don ya shiga ban dakin kasa Allah ya kubutar dashi. "Yanzu ka juya da jirgin zuwa headquarter zan tawo da sauran mutanen." Ya fadi haka yana fita daga jirgin, a hannun dayan mutumin ya samu takarda. Amsa yayi yana dubawa,
Mun ji labarin baka tab'a fita operation ka fadi ba, so wannan karon ka zo ka amshi yan uwanka sannan ka sakar min mutane na, ko na kashe Commodore.
"Zaku wuce headquarter zan tawo da wancan jirgin." Ya fita da sauri ya koma asalin jirgin yan fashin tekun, tsoron shi daya kada suma tarko aka musu. Koda ya isa ya same su, ajiyar zuciya ya sauke sannan ya saka aka karkato kan jirgin, baki daya suka nufi headquarter ɗinsu,. Suna isa dama labarin ya isa an kaiwa jirginsu hari har an sace wasu sojojin. Yana isa da wadanda aka harba, asibiti aka wuce da su. Admiral da kanshi ya zo inda aka ajiye jirgin. A lokacin karfe biyu na dare, "Sir!" Ya sarawa Admiral. "Aiki yayi kyau, yanzu wani hali Magaji yake ciki tare da sauran abokan aikinku."
"Umarni nake jira mu sake sabon shiri." Captain ya faɗa yana sarawa. "Zan duba lamarin yau, amma tabbas dole a kai musu ɗauki." Mika mishi takardar da aka ajiye musu yayi. Shiru Admiral yayi yana kallon takardar. "zan tura yau kafin gobe zan nema maka _permission_ "
"Ok Sir!" Ya sara mishi, sannan suka bar wurin aka wuce da mutanen da suka kamo, lokacin da ya shiga barrack din baki daya labarin ya karad'e cikin barrack din, waɗanda mazajensu suke hannun hankalinsu ya tashi, waɗanda mazajensu suke asibiti, a daren wasu suka yi ta wucewa, su kuma suna tafiya a mota. "Yallabai wannan abin da ya faru, da damu zai faru Allah ya tsare mu." Gyada kai yayi yana kallon hanya, kofar gidanshi aka sauke shi, kasancewar shi ne babba a cikinsu. Sai da ya fito ya ce musu. "Kada ku manta ku kula da kanku. Idan sun gama zamu tafi gobe ko jibi."
"Ok Sir!" Sannan ya ce musu. "Ku kula da iyalinku." Ya wuce ciki da sauri, yana shiga ya sauke ajiyar zuciya bayan ya shiga da sallama, a ka'idar wannan operation din ba a fita da waya, daga nesa ya hango wayarshi yana haske, a matuƙar gajiye ya isa wurin. *Brother* ya gani baro-baro a saman screen din wayar, a hankali yayi picking yana sakawa wayar a kunnen shi. "Baka yi barci ba?"

"Taya zan yi barci bayan wurinka na zo."
"Ka koma, ina da abinda zan yi nan da kwana biyar."
"Ai na gama nawa kawai, ka shirya." Brother ya gaya mishi. Dafe goshi yayi yana sosawa ya ce mishi. "Ka koma inda ka fito, don Allah." "Babu inda zan tafi." Yana fadar haka ya kashe wayar. Zama yayi jikinshi da matukar damuwa.

Zahrah
Muna kwance muka ji kar'ar motar daukar marasa lafiya. Kafin wani lokaci asibitin ya cika da hayaniyar mutane. Har kusan karfe hudu na asuba, can sai ga Dr Umaima ita da wasu Nurses su uku. "Baku yi barci ba?" Girgza kai nayi nace mata. "Eh Aunty, amma lafiya?" "Sojojin mu ne suka hadu da tsautsayi, Sisi kira mana Captain aikin nan ba zan yi ni daya, sannan ki haɗa da Mrs Kayode hutun ya ƙare." A hankali ta tawo kaina. "Nasan kuna da hankali, please ku kula da kanku sannan kada ku ce wani abu."
Gyad'a kai nayi nace mata. "tow Aunty Umaimah." Fita suka yi, can kuwa muka kara jin hayaniyarsu ya karu, Zuzu kan duk abin da ake tana ta barci, sai da na gaji na tashi zaune ina yatsina fuska.
Suna fita basu wani ɗauki wani lokaci ba, suka yi ta kiran wayar likitocinsu.
Haka suka halarta kafin wani lokaci sun fara aiki, kafin karfe shida na safe, sun fito daga aikin. "Captain ko zaka kwanta ne?" Ta tambaye shi cikin kulawa, domin Allah ya jarabceta da kaunarshi, amma shi babu haka a ranshi. Gyada mata kai yayi, ko bude idanunshi baya iyawa balle yasan inda yake jefa kafarshi, haka ta juya itama ta bar sauran aikin a hannun Mrs Kayode ta tafi gida.
Dama mun yi da Zuzu karfe shida zata wuce ko shida saura domin tun fitar Dr Umaima, itama ta farka ta leko mana abinda yake faruwa. Har tayo saurayi a cikin sojojin. Shi yace zai kai ta gida, muna idar da sallar asuba, ya zo suka tafi ni wani barci me karfi ya dauke ni. Ko don mun raba dare bamu yi barci ba ne. Haka nayi ta barci kamar me, yana shigowa ko don ya gaji ne, kawai yana shigowa ya kwanta. Tuni barci yayi gaba da shi, duk da yana son yin sallar asuba, amma ina barci me nauyi yayi gaba da shi.
Wani ikon Allah dukkan mu biyu babu wanda ya fahimci halin da dayan mu yake ciki. Har wurin sha biyu lokacin Nurse tazo duba ni, anan ta same mu kwance ya tattara ni ya cusa cikin jikinshi ni kuma kamar mage na kwanta kwayam kamar mage, ko yanayin ba mamaki ko dumin da muka ji daga junanmu ya haifar mana da barci me nauyi, ganin haka ta juya tana me barin dakin, Dr Umaima ta kira ta gaya mata. Ai babu shiri sai gata a asibitin, tana isowa Zuzu tana isowa itama. Kallon juna suka yi, kafin Dr Umaima ta ɗan bata rai tana faɗin. "Ki jira ina zuwa."tana faɗin haka ta shigo, a hankali ta tashe shi, kaina yana kirjinshi, hannunshi dukkan biyu ya zagaye ni dasu. Sake tab'a shi tayi ya buɗe ido dakyar yana kallon ta. "Kafin ka dawo hankalinka ya kamata ka san inda kake." Kallonta yayi, sannan ya kalli inda nake kwance. Bai ga fuskata ba, amma baki daya yaji lissafinshi ya fara aiki kamar wanda ya aikata wani mugun aiki, ya ware manyan idanunshi ya kafeta da shi. "Su waye a waje?" Sanin ko ta fusata ba zai dame shi ba. Ta ce "babu sosai." A hankali ya zare jikinshi a nawa, kafin ya saka kafarshi cikin takalminshi, yana kallonta. "Baka duba ciwon ba, sau biyu aka yi aikin fa." Cikin kamewa da nuna kamar bai aikata kome ba, "Good!" Ya saka kai ya fita. "Karfe nawa?" Agogon hannunta ta kalla ta ce. "12:30" "innalillahi'wa'inna'ilaihi'raji'un! Ban yi sallah asuba ba." "Sai dai sallah safe." Inji Dr Umaima. Da dan sauri ya bar ward din, dama dabi'arshi ce matukar yayi aikin dare tow ba makawa sai ya shiga daki daya yayi barci, a gidanshi baya iya barci kwana yake yana mafarki.
Koda ya fita motarshi ya faɗa, da gudu yana shiga ya bata wuta, kan lokaci ya isa gidan, a kofar gidan ya taradda motar bmw, sai da ya tura motar gefen gidan,a kasar bishiyar lim, yayi parking da sauri ya fito tare da kallon inda motar take. Bai ga alamar da wani ba, haka ya wuce motar ba tare da ya kalli inda motar take ba, ya shiga kokarin buɗe kofar gidanshi, a hankali yaga kofar a buɗe yaƙe. "Emmanuel

yazo aiki kenan?" Ya tambayi kanshi,cikin gidan ya shiga tare zubawa wanda yake zaune idanuwa. Dauke wuta yayi tabbas a duniya an rena shi. Wucewa yayi a gaggauce ya nufi dakinshi. "Na ga kayan jini, na san baka fara kisan kai ba, balle na ce ka fara amma na wanke Yaronka bai sani ba, domin ya same ni a kofar inajiranka."

Bai ce mishi cikanka ba, ya wuce dakin yayi wanka da alola yazo ya gabatar da sallar asuba, sannan ya hada da zuhur. Shima bakon zuhur din yayi sannan ya wuce kitchen. Abinci ya dafa musu mai kyau sai kamshi yake, a hankali ya nufi falo da abincin, ya ajiye nashi sannan ya wuce da na Captain ɗin ya ajiye mishi a gabanshi. "Kaci nasan kana nan kana wasa da cikinka, ga aikinka aikin hatsari ne." "Me yasa baka jin magana?" Ya tambaye shi yana kallonshi. "Ni kuma? Ai idan akwai mara yafiya da rashin jin magana kai ne dai baka jin shi, kai a dadin ranka ne ka bar mahaifiyarmu tana kuka tana gayawa Allah yaushe zaka dawo gare ta? Ya Majeed duk abinda ya wuce ya wuce, a barshi ya wuce ban ga amfanin datse alaƙar da kayi ba."

"Aryan ka koma kace baka ganni ba."

"Zan koma amma ka sani na gama abin da ya kawo ni, gashi ka duba."

Ya ajiye mishi takardar izinin tafiya da Captain Majeed Mamman Ba'are, kuma Doctor a wani bangaren.

"Akan me zaka min haka?" "Muna da Kyakyawar alaƙar kasuwanci da kamfanonin mu da mahukuntan Nigeria, don haka kai tsaye daga sama na liko da kai kasa, don haka sun baka hutun wata guda."

"Kasan hatsarin da abokan aikina suke ciki?" Ya fada a fusace, "bai kai hatsarin da BA'ARE GOLDEN EMPIRES yake ciki ba, sai ka zab'a saura kwana uku zaben, su kuma abokanka, zai dauki sati kafin su fito domin sun bada zabin a sake musu kayansu ko su kashe su. Na gama hada maka kayanka." Ya fada yana ƙoƙarin barin dakin yana faɗin. "Akan shegen aikin da albashinsa bai wuce a sayawa karen gidan mu abinci ba, kazo zaka kare rayuwarka akanshi."

Shiru yayi yana kallon abincin, tabbas abubuwa dayawa sun faru. Amma kuma ba zai tab'a yarda ya rike musu kome ba, zai dawo bakin aikinshi. Kamshin abincin yasa shi jin wani irin yunwa, da sauri ya fara ci, shigowar Aryan Ba'are yasa shi d'ago kai yana kallon shi, zama yayi a gaban Aryan Mamman Ba'are, murmushi suka yiwa juna, zama yayi ya juye abincin kan na Captain Majeed, suka fara ci hawaye na zuba daga idanun Aryan Mamman Ba'are, diban abincin yayi a cokali ya mikawa Majeed din, amsa yayi yana kallon shi, "kayi hakuri saura kwana huɗu ne ba uku ba, na fahimci yadda kake son aikinka." "Ba kome." Ya diba shima ya bawa Aryan Mamman Ba'are, amsa yayi yana ci, d'aga kai Captain yayi yana maida kwallarshi. "Kayi hakuri!" "Ai ba fushi nake ba, kawai dukiyar wancan mutumin ne bana son alaƙa da shi, don Allah ka."

"Ba dukiyar shi bane yanzu, dukiyarmu ce wanda naka da kaki amfani da shi yafi karfin tunanin kowa. Duk hannun jarinka sun fi na kowa yawa,.kaga yawan kudinka."

A hankali ya bude baki zai magana Aryan Mamman Ba'are ya cusa mishi abincin a baki, dole ya ci. "Maganar aurenka ma Hajiya tana son lallai ka koma ayi maganar aurenka."

"Ni bana son." Tura mishi abincin yaƙe yana murmushi, karfi da yaji Aryan ya hana shi magana, kuma yayi shiru ya ci abincin tass, sannan ya bude mishi ruwa ya sha, sannan ya mike yana kallon shi. "Me ya faru? Naga jini a zanin gado da sauransu."

"Ba kome fa."

"Nasan baka fara bin mata ba, amma wannan sarkar fa." Shiru yayi yana kallon Aryan. "Ban san me ya faru ba, kawai dai."

"Amma kuma." Girgza kai yayi, Aryan ya san halin ba zai tab'a magana ba.

A hankali ya mike ya dauki wayarshi, ya kira Admiral. Sun jima suna magana, sannan ya koma cikin dakinshi can sai gashi dauke da kayan aiki. "Zan tafi kwana biyu in sha Allah zan yi."

"Nayi alkawarin maida mata kai gida, zan zauna har zuwa ranar."

"Shi kenan!" Ya faɗa ya fita daga cikin gidan.
Asibitin!
Wato yana tashi daga gadon, ina bude kanana idanuwa na da suke cike da barci. "tashi" inji Zuzu. "Ke wani irin dumi naji, shi yasa nayi ta barci." Murmushi tayi min sannan ta ce. "Zahrah kin san dumin da kika ji?" Girgiza kai nayi ina kallonta, dariya tayi min sannan ta ce min. "Dumin wani Kyakkyawan soja kika ji, ke dama ana samun Kyawawa ne a sojoji?" "Ke!" Na ware idanuna, ina shafa jikina. "Da fatan bai min kome ba?" Na fada ina zare idanu. "Namiji fa?" Gimtse fuska tayi tana hararata, "Sai hakuri domin ya b'arar miki da darajarki sai dai mu taru mu kwashe." "Ke Zulai!" Na san a duniya ta tsani na kirata da Zulai tun muna yara, don haka ina cewa zulai ta ce. "Zan ci mutuncinki banza babu abinda yayi miki."
"Allah ya huci zuciyarki." Daga haka na rufe bakina. Ban daki ta shiga ta haɗa min ruwan zafi,.na shiga na kama ruwa sannan na fito da alola.
Abin sallah ta shimfida min nayi sallar, asuba da zuhur ina istigfari,domin nayi laifi me girma na wasa da sallah, koda na idar addu'a nayi sosai sannan na tashi zuwa bakin gadon. A hankali nake jin wani irin kamshi yana tashi me matukar dad'i da sanyi, ware ido nayi ina kallon Zuzu. "Zuzu kamshi me nake ji?" Kamshi kuma?" Gyad'a kai nayi ina kallonta. Itama ni take kallo, dube dube muka shiga yi, a hankali Zuzu ta d'aga pillow da yake gadon, wani ƙaramin hanky ne yake wannan azabebben kamshi.
"Mtsew ji abin da yake kamshi." Na ja tsaki, ina kokarin gyara zama, fari ne kal a hankali na warware. Gefen zanen wani babban gida ne kamar masarauta gashi nan kamar castle. An rubuta BGE.
"Mene ne ma'anar wanan kalamar?" Na tambayi Zuzu. "Adda mai tuwo tuwo!" Ta fada min hankalinta kwance. "Amma dai ke dai anyi yar banzar Y'a."
"Tow shi kenan sunanshi Fadimah Zahrah Buba Shad'ari." "Bana son b.... uba." "Na waye? Nawa ko naki ko najin dadin bakinki?" Abinci ta saka min kaɗan, duk da dama aikin ai ba wani aiki na tashin hankali ba ne, a hankali nake kurbar shayi, ina kallonta. "Zuzu!" "Na'am!" Ta amsa tana kallona. "Kinyi alƙawari ba zamu tab'a cutar da juna ba?" Na mika mata hannuna, "Me yasa kika bukaci haka?" Ta tambaye ni, murmushi nayi ina kai abinci bakina, a hankali na d'ago kai ina kallonta. "Ban sani ba, amma kuma nasan dai wata rana zamu iya cin amanar juna."
Amsar kofin hannu na tayi da plate ɗin,ta ajiye, a duk lokacin da tayi haka nasan me take nufi. "kin san an min aiki." Na faɗa idanuna rau-rau. "Mtsew! Kin ci sa'ar ciwon jikinki da kin sha mamaki."

Dariya nayi mata, sannan na cigaba da karyawa ta, har na gama ta balla min maganin da na gani ta Ciro a lock din gadon ta mika min. Da ruwan tea na sha ina son tmbayarta Addah amma nasan halinta bai zama dole ta bani amsa ba.
"Ya Addah take?"
"Lafiya lau!" Kallon fuskarta nayi naga kamar a dakile. "Wani abu ya faru ne?" "A'a." Ta fada tana leka wayarta, kawai na sha jinin jikina haka kawai Zuzu ba zata sauya ba. Sai na share kawai ban ce mata kome ba.
Tuna abin da ya faru a komawarta gida yasa baki daya, ranta ya kara b'aci da maganar Zahrh
Lokacin da ta koma gida, ta samu Addah tayi bakon wani mutum, tunda ta gansu a dakin Addah tasan mutumin ba na alkhairi ba ne, duk da ba yau din ya fara zuwa ba, sai dai kuma zuwan shi na yau kamar niman shi aka yi, shi din d'an bori ne. Haka yayi ta tsalle yana ihu, kafin can ya fara gyatsa. Ya fashe da dariya, yana nuna Addah da hannu. "Tabbas baki da arziki a jikinta a yanzu, sai gaba zaki ci arzikinta sama da yadda kika zata. Kaddara ta hadata da shi, maza ki nisanta ta daga wannan duniyar zuwa wata duniyar, domin kuwa kika sake suka kuma haduwa ba zaki kara morarta ba har abada."

"Nazimu ya zanyi? Ita Zulaihah bata da gobe ne?" Ta faɗa a hankali. Gyatsa ya sake yana dariya. "Gobenta yana manne da yarinyar da take asibiti." A dame ta kalli Nazimu ta ce mishi. "sauran yan matan fa?" "Hmmmm! Itace inuwarsu."
"Babu yadda za ayi a mallake min ita?" Shafa gemunshi yayi ya ce mata."ba zan iya wannan aikin ba,lokaci na zuba da zaki amfana da rashin haka, idan aka mallaka miki ita ba zaki tab'a samun biyan bukata ba."
"Nazimu kace na dauketa daga nan?" Gyad'a kai yayi yana gyatsa. "In sha Allah wani sati zamu wuce Taraba!"
"Dakyau. Ki nisantatta da nan domin zai bincikota."yana gama fadar haka ya fara kwara amai, nan Addah ta fito ta gaya musu zasu tafi Taraba, shiru kowa yayi a cikinsu. "Addah kinsan muna zuwa za a fara maganar munki aure fa."
"Ba zamu wuce kwanaki uku ba, tunda zamu bi motar dauko shanu ne,iya kwanakin da zamu yi uku ne, idan kuma kuna son zama anan shi kenan "
"A'a zan tafi naga Yakumbo na kwana biyu ban ganta ba."inji Ummi,
"Nima zan je na ga Nenne na!.....
#Thedambuje
[2/16, 9:24 PM] Cutie cutie pie: *BAKIN HAURE....□□*

{Greed for Money is the roots of all evils□}
Arewabooks:maidambu41
Wattpad:Mai_Dambu
Mallakar:Mai_Dambu

ZINARIYAR MACE⚡
Wai shin 'yar'uwa menene matsalarki? zubewar nono, ko kuma rashin kwankwason juyawa a falo maigida ya shiririce ya manta da tibi da matan tictok, menene matsalarki ne? rashin ni'ima ko kuma mugun sanyin da ya yi miki katutu, shin rashin taushin fata ne ko kuma kuraje da tabbani, ko bala'in ramar da ta addabeki kuma babu rashin ci ba rashin sha a gidan auranki, gwaigwayewar gashi ce matsalarki ko kuma kaushi da faso na tafin kafa da bushewar fata, kina bukatar fatarki ta yi glowing kalarki ta fita kuraje su mutu, ko kuma kina bukatar azababbun turaruka da humra tare da turarukan wuta. Na san dai kuna da yawa matan da tumbi ya yi musu karan tsaye ina nufin ya katse muku hanzarin yi wa maigida gwalli da muskuce-muskuce a falo😀 Nesa fa ta zo kusa AL-KUTUBIYYA ISLAMIC MEDICINE sun tanadar muku da nau'in magungunan da suke magance kowace irin matsala da izinin Allah. Babban burinmu shine sha'ani na aure ya inganta a samu daidaito. Muna da.
Na gyaran nono.
Na sanyi.
Dilka tare da hadin sabulu.
Duk Wani nau'in maganin mata.
Humra turarukan wuta perfumes, original miski tahra 3in1, ciccibi budurwar kaza. Had'addun supplement irin wad'anda ba su da matsala. Maganin Sliming wato narka tumbi. Abubuwan da muke sayarwa suna da yawa, kuma babu asarar dukiya. Muna garin kano kuma muna tura kayanmu kowane gari fad'in Najeria da Nijar har ma da kasashemn ketare. Kai tsaye a tuntu'bemu ta lambobin wayarmu domin karin bayani.
08089965176
07084653262
006
Juyawa tayi ta kalli Zulaihah,kafin ta ce mata. "Baki da ra'ayi ne mu barki anan?" Murmushi tayi iyakarshi lebbenta. Ta ce mata. "Ina da ra'ayin idan na tafi nima ba zan dawo ba, aure zan yi domin na samu mijin aure " dariya Addah tayi sannan ta ce mata. "Ta yaro kyau take bata karko, Allah ya kai mu zulai." Har ta juya zata tafi ta ce mata. "Ki sani matukar muka tafi kika zauna a can, duniya sai ta san me kike aikatawa balle mijin da nake da yakinin shi kike hari." "Addah barazana kike min?" Itama ta mike tsaye, tana kallon Addah. "Kashedi nake miki, kuma idan na miki

barazanar ai ba laifi ba ne. Saboda ai da kome nawa kika kawo haka, sannan idan nace zan miki barazana ba laifi ba ne." sannan ta juya ga Ummi ta ce mata. "Ko nayi laifi a cikin wannan maganar?" Girgza mata kai suka yi, domin Allah ya zuba musu shakkar Addah idan ka cire Zulaihah, da sam bata shakkarta, ɗakinta ta koma ta kalli Nazimu. Kamar zata fashe da kuka. "Yarki bata da matsala, halayyarku ce da bambanci, ita ba zata iya abin da kike yi ba, domin tana da kirki da nutsuwa shi yasa halayyarsu da jininsu ya hadu da Yarinyar can, don haka ina baki shawara da kada ki sake, ki takura Yarki domin duniya ki sarara mata."

Gyad'a kai tayi tana faɗin. "Itama tana da farin jini fa." "Eh mana, amma kuma kila yawan takurar da kike mata zaisa ta iya rabuwa dake na har abada."

Dafe kirji tayi tare da cewa. "Don Annabi?" Wannan ne karon farko da Addah ta kira sunan Annabi Muhammad Sallallahu alaihi Wasallama,domin ba dabi'arta ba ne kiran sunan Allah. Yadda Nazimu yayi kasa da murya yasa ta nutsuwa tana sauraron shi, sannan can yana gamawa ya mike ya fita, Munaisah ta shiga dakin ta gyara, "Ya gaya min maganar chef yace wai yau ki saka wannan turaren zaki samu alkhairi sosai a wurin shi."

"Kai Addah ni ai mota nake son ya saya min." "Banza sakarya motar kaniya, idan kika samu kudi saniya zaki saya da shi a fara ajiye miki."

"Kuma haka yayi fa, Addah ya batun Zahrah?" Tsaki tayi tana tab'e baki, zata tafi can ta hadu da wancan dan iskan Yaron, su kare kalau ni ina zargin anya Yaron nan bai gama lalata Zahrah da take jin ba zata iya wani abu sai da shi ba." Addah ta faɗa tana kallon Munaisah, "Uban waye ya sani, shegiya munafika ni ban son tayi aure domin haka zai saka a samu a gaba da munki aure sai zaman bariki." Shiru Addah tayi tana kallon Munaisah ta sake murmushi ta ce mata. "Da ni kuke zancen, ki bar kome a hannu!"

Daidai shigowar Zulaiha. "Wa makaru wa makrallahi wallahu khairar makiri." Tana fadar haka Addah ta zuba mata idanu, "zan tafi asibiti."

"Allah ya tsare." Juyawa tayi ta fita, amma ranta soye yake...

"Ke tunanin me kike yi ne haka?" Tab'e baki tayi tana faɗin. "Babu kome!" Ta fada tana kallon wayar. Ba zan iya ganinta cikin wani yanayi na Kyaleta ba, don haka na ce mata. "Zuzuna gaya min!" A hankali ta d'ago kai tana kallona kafin hawaye ya zubo mata."Zahrah kin ji dadinki,tunda kike baki tab'a zina ba, sannan baki tab'a yarda kin lalata tarbiyyar da Kawu shad'ari ya miki ba, Zahrah wani sakayya zan bawa mijin da ya aure ni?" A hankali ta fashe da kuka, sosai tana yi tana karawa. "Kada ki manta Allah xai baki mijin da zai kauna ce ki a duk yadda kike, kin ga yanzu da kin yarda kin amince kin koma diplomar nan, ai da yanzu saura watanni zamu gama, na gaya miki ba zina yake bada abinci ba, a'a yarda da Allah, Zulaihah kin bi na Addah kina lalata gobenki, bayan su mazan abin da yake jikinki suke bi idan suka gama dake zasu gudu."

"Ya zanyi?" Ta fada cikin kuka, tana kara jin tsanar kanta. "Kiyi hakuri kawai." Na fada mata, a hankali ta warware min tafiyarmu taraba, amma kuma tana jin addah tana kulla min sharri. Murmushi nayi na ce mata. "duk abinda Addah zatayi, ba zata hana Allah ikon shi ba, don haka ta gama abin da zata yi saura ta barwa Allah ikonsa."

Daga haka muka cigaba da hirarmu.

**

Kwana biyu mai kyau aka yi ana bata kashi a tsakanin, Captain da yan tada kayar baya, kafin aka fitar da su Commodore Magaji Abba, wanda yaci bakar wahala. Sannan sojojin ruwa da na kasa suka kame sauran yan tawayen aka tafi da su, a daren ya dawo gida a gajiye anyi anyi ya tsaya a asibiti amma ina, domin shima akwai rauni a jikinshi, yana shiga ya samu Aryan yana kwance a falon. Wucewa dakinshi yayi ya nufi ban daki ya shiga cire kayanshi, yana gamawa ya ga inda aka harbe shi biyu saboda bullet proof da ya saka ne basu ji mishi rauni ba, wanka yayi ya fito ya sha magani, ya sauke salolin da yake kanshi. Sannan ya fito ya hada tea ya

sha, kafin ya dawo daki ya kashe wutar gidan baki daya, akwai yarda da Amana a tsakaninsu da duhu.

Karfe biyar na asuba ya farka, ya nufi ban daki yayi wanka da alola ya fito falon suka yi sallah,a lokacin an fara ruwan sama. Kitchen Aryan Mamman Ba'are ya wuce ya hada musu abin karyawa. "Kasan yau zamu bar garin nan." "Eh! Amma ai ana ruwa." Kallonshi Aryan yayi kafin ya ce mishi. "Zamu wuce Enugu a can muke da jirgi zuwa kano."

Haka ya zauna ya ci abinci, suna hira sama-sama. "Ya Amaan?" Tab'e baki yayi yana faɗin." Yana nan." Daga haka dukkansu babu wanda ya kara cewa Uffan. Har suka gama, Aryan ya shiga dakin Majeed yayi wanka ya shirya sannan ya zo ya kwashi kayansu, yafita da su. "kana nufin kwana biyu da kayi baka fita ko ina ba?" Tab'e baki yayi irin abin ya zame mishi jiki ya ce mishi. "Ina zan leka? Gari kullum ruwa, da nasan haka ne, ai da na tawo da Sanayah!" Shiru yayi yana kallon yadda yake shirya kome. Bayan ya gama shima ya koma ya shirya tsaf cikin Kananun kaya, suka rufe gidan bayan ya kwashe kayan abincin ya rubutawa Emmanuel, yayi amfani da shi. Sai da suka fara zuwa headquarter yayi sign sannan ya leka asibiti ya duba Magaji Abba Chindo, da yake zaune ana wanke mishi ciwon shi, zama yayi bayan an gama nurse din suka fita ya amshi sauran kayan aikin ya cigaba da gyara mishi ciwon. "Ba na son na kuma maimaita maka abin da ya wuce, amma zan gaya maka gaskiya yarinyar nan da ka saka a bi sawunta ni na taimaka mata, ba don kome ba sai don na kubutar da kai daga sharrin zina. Nasan kayi nisa amma ka gwada barin shi zaka fahimci abin da nake nufi. Ni zan wuce ƙasarmu, ka sani ba wai bamu da inda zan yi aiki ba ne, sai dai wannan karon idan na tafi ba zan dawo ba,na bar maka ƙasarku na koma aiki a babban headquarter Naval na French." Daga haka ya mike zai fita daga cikin dakin. " tow sai me? Bayan sai da na zama nakasashe zaka gaya min na daina zina? Sun kashe min gaba wadancan karnukan."

"Zina ya janyo maka haka." Daga haka ya juya ya fita, bai samu Dr Umaima ba, sako ya bar mata tare da tura mata kuɗi, sannan ya fita daga asibitin suka bar garin ma baki daya.

***

Ranar da na cika kwana shida, aka sallame, Doctor Umaima tazo tare da mika min jaka. "Gashi akwai ticket na jirgi zuwa Yola, daga can zaki samu motar taraba. Don Allah ki koma gaban Iyayenki ga wannan kuɗin inji Captain ya ce a baki kuma yana bada hakuri da abinda ya faru. Shima ba a son ranshi ba ne."

Murmushi na sakar mata, ina faɗin. "Duk wannan kuɗin?" "Akwai matsala ne?" Girgiza kai nayi, sannan na ce mata. "Ko zamu je banki a tura min kuɗin." "Wani bank ne?" "Ecow bank!" "Me yasa sai bank din?" Saboda idan na koma zan tafi niman Mamana ne ne a Kamaru.". "ok muje!" "Gaskiya kin yi dabara, yadda Adda ta shirya wulakanci tana ganin kudin nan zata raba ki da su."

Murmushi nayi na wuce muka fita, da taimakon Aunty Umaimah muka tura kudin account dina, sannan suka sa ni lallai sai na yi welcome back din layina. Bayan nayi na sayi wata yar ƙaramar wayar bani da buri akan babbar waya. Haka yasa nake rayuwata da yar karamar waya abina.

Lokacin da muka zo gida, na samu su Addah sun gama shirin tafiya. Koda na gaya musu ni jirgi zan bi sai suka yi shiru, Zulaihah itama ta kira wani sugar daddy dinta ya tura mata kudin ticket, sai gashi baki ɗaya sun biya har da Addah da Ummi. A daren muka bar garin fatakwal. Muka wuce garin Yola. Mun isa wurin ƙarfe daya na dare, don haka muka kwana a masallacin da yake cikin airport din, gari na wayewa muka fito tare shiga kasuwa muka yi sayayyar tsaraba, sannan muka dauki hanyar taraba.

A hankali muke tafiya, hankalina yana kan wayar hannuna, na turawa Sabiru sakon gamu nan muna hanya, amma shiru bai dawo min da ansa ba. "Ya dai

Zahrah?" Tsaki nayi ina yatsina fuska."Sabiru bai kira ni ba." Juyawa Addah tayi tana kallonmu, fuskarta dauke da murmushi. "Allah ya sa ba halin yan maza zai miki ba." Shiru nayi ban iya magana ba, amma tabbas akwai wani abu a kasa, haka kawai Sabiru baya kin daukar kirana ko sakona ya gani.
Wai ma kun san wacece Ni?
Fadimah Zahrah Buba Shad'ari, shine cikakken sunana. Mahaifina Bafulatanin taraba ne daga karamar hukumar Takum. Gari ne da ya hada makiyaya da manoma.
Alhaji Shu'aibu Jauro shine kakanmu dattijon arziki, mutumin kirki da babu biyun shi, Allah ya mishi rahama. Domin ya rasu tun ina da shekara shida a duniya, amma ba zan manta alkhairinshi ba.
Addah ita ce Babbar yarshi, kuma kangararriya mara jin magana. Wato ana cewa albasa batayi halin ruwa ba, hakan ce ta faru da Addah domin bata dauko halin iyayenta ba dukka biyu, sai Baffa'm wanda shine d'a na biyu da yake bin Addah, mutum ne me hakuri kawaici da Dattaku. Baffa'm yasan darajar kanshi da rayuwarshi. Mutum ne da yake da ilimin addini sosai, sai dai bai samu halin yin ilimin boko ba, sai ya saka a ranshi matukar yana raye Yaranshi sai sun yi karatun boko, wani abin haushi. Nenne Matarshi kuma uwargidansa, babu ruwan ta domin har wurin ardo ta kai Baffa'm don yace sai yaranshi sun yi boko.
Haka ya hakura dake yana tafiya da shanu cirani, musamman yankin Gyambu da yake da yalwataccen yanayi me kyau, yana zuwa yayi watanni sannan ya dawo da su. A irin wannan tafiyar ne ya hadu da Mamana domin tafiyar ta kaishi har kamaru, a can ya aurota ya kawota. Lokacin Munaisah tana da shekaru biyu a duniya.

Tunda Baffa'm ya auri Mamana, mutanen gidan suka sakata a gaba, wai ita Rumada ce wato bayin fulani, duk da kana ganin Mamana kasan yar babban gida ce, domin duk rugar mu babu macen da take sanye da zinari a kunne sai ita, sannan take gaya min ina Yarinya su Mahaifinsu kana cika shekaru goma a duniya kake fara zuwa aikin hajji, daga nan duk Shekara kana tafiya Umara. Wannan yasa duk yan gidansu suka je aikin Hajji.
Baffa Modibo shine ke bin Baffa'm, sai dai mutum ne mara kirki,haka yasa har da shi a cikin masu musgunawa Mamana. Haka tayi ta rayuwa a kuntacce, a lokacin da aka haife ni kuncin yayi yawa, domin a lokacin Addah sun dawo da Mijinta ya saketa, haka ta zo ta saka Mamana a gaba da fitina da tashin hankali. Har zuwa lokacin da ta samu wata kawarta ta kawo mata ziyara daga kano suka tafi tare da Addah, ashe tafiyarta Kano Saudiya ta tafi.

Wato mu yan gidanmu Allah ya zuba mana baiwar kyau, sai ma dai nice da nake da duhun fatar Mamana. Haka yasa yan gidanmu suke yawan min ba'a. Bayan tafiyar Addah Baban Zulaihah yaso ɗaukarta, amma Kakanmu Alhajijo yace ba zai dauketa ba, sai ta kai shekaru bakwai a duniya.
Haka muka taso da Zulaihah duk da ta girme.ni, haka Mamana ta haɗa mu ta riƙe. Tunda Addah tabar Nijeriya ta isa Saudiya, take tukaranci da rashin jin magna, har dai ta samu yadda take so.

A nan kuwa ba zance me ya faru ba, domin a lokacin ban wuce shekaru Biyar ba, aka nime Mamana aka rasa, sama da kasa ta b'ace, wannan al'amarin ya daki babana da Alhajijo a lokacin ya kwanta jinyar da tazama ajalin sa,, haka muka zama marayun dole ni da Zulaihah. A lokacin Baffa'm ya saka ni makaranta, kuma cikin ikon Allah sai Ubangiji ya min baiwa na daukar karatu, domin ina da shekarun goma a duniya na gama primary school. Na shiga secondry school, a gurin a saka sunana a registered din yan jss one aka saka a na yan jss two, haka Baffa ya cika musu kudi domin shi mutum ne mai son yaga kayi abinda yake so.
Ina da yayu maza biyu, Babangida da Habibu, sai Munaisah take bin Habibu. Sai ni nake bin Munaisah, sai Kuluwa take bina, sannan Dizah burin Baffa'm akan mu yayi yawa amma haka Nenne ta kashe mishi burin akan Yaranshi,ni ce kawai yake da iko

dani, shi yasa ina shiga jss3 a shekaru goma sha daya na kara riƙe wuta, koda muka shiga Ss1 bana wasa, ina shiga ss2 na nime Baffa'm ya biya min waec da neco, sanin ina kokari yasa shi biya min ikon Allah sai gashi da muka yi jarabawar naci, duk da bani da shekaru amma ina da dan tsawon kafa. Sannan ni siririya ce sosai. Kamar mamata haka nake.

A shekarar da na gama secondary Hajiya Addah ta dawo, ganin mu yasa ta fara shiri akanmu, sannan a gefe guda kuwa burinta ya kusan cika, don haka ta kwana biyu ta sayi shanu ta bawa baffanmu, ta koma ashe a Lagos take da aka kore hausawa masu tuwo-tuwo shi ne ta dawo fatakwal. Ganin mu kawai yasa tana komawa tayi gaggarumin shiri, tana zuwa ta dauko Ummi da Munaisah,suka zo watansu biyar suka dawo. Ni da Zulaihah da zasu koma aka tawo damu,a lokacin Baffa'm ya bani takarduna,nayi kokarin niman cigaba domin ta gaya mishi zan koma makaranta. Da muka zo kuwa kudin da ya bani taso kwacewa ni kuwa na ce ta mai dani gida baki ɗaya shekaruna sha huɗu, ina da wayewa ta ilimi,domin saura izu goma na sauke Kur'ani mai girma.

Wannan dalilin yasa addah nima min, diploma a bangaren ilimin lissafi, kuma dama Allah ya min baiwar iya lissafi. Har yan canji suna kirana na taya su aikin lissafi idan ban tafi makaranta ba, a hankali Addah tayi ta fito da asalin kalarta akan lallai mu bi maza, ni kuwa naki na sha duka da wahala, ga azabtarwa yunwa kada ku manta wannan shafa ce domin a gidan Ubana ma na horu da rashin abinci, Zulaihah ce aka samu kanta, domin ba zata iya jurewa ba, haka na samu number din baffa na gaya mishi, shi ne yasani na hada shi da wani iyamurin gefen gidan Addah yana turo min kuɗin makaranta da na abinci. Yayarshi ce babu yadda ya iya da ita idan yayi magana zata ce ya mata rashin kunya,haka yasa ya zuba mata ido. Kullum zai kira yaji ina nan ko na tafi, baya kira a wayata sai wayar addah.

Kudin da take samu a wurin su Ummi da Munaisah da Zulaihah,da shi take turawa gida ana saya mata dabbobi, gashi bata gajiya da kai karana na mata kaza nayi kaza. Ya kira ya min nasiha, domin ban tab'a boye mishi abinda take son nayi ba, shima kuma yace naji tsoron Allah yana gani na idan ni bana ganinshi.

Haka muka cigaba da rayuwa, gashi har na zama cikakkiyar budurwa, domin ban wuce shekaru goma sha shida ba, haka yasa maza rawar jiki a kaina, amma naki Ba su fuska, sai ranar da ƙaddara ta haɗa ni da mutumin nan da ya soka min wuka,koda yake shegen iyayi na ya kai ni. A daren da abin zai faru wannan sojan yazo wurin Tuwon mu ya matsawa Addah ta barshi ya dauke ni, amma taki domin ya tab'a daukar Ummi bayan ya kwana da ita ya mata dukar kawo wuka ya korota. Sai da ya zuba mata kudi, sannan ta barni muka tafi, daga na bishi na amso kudi ya tafi da ni.

Koda ya kawo ni, da farko bai nuna damuwa akan yana son wani abu ba, sai da na je na kwanta ina nazarin yadda zan fita ya shigo min tsirara, ai kuwa garin na kwaci kaina na bude mishi wani abu can, ai kuwa ya fadi can, da haka na gudu, daga nan na hadu da Aminin duhu.

..... Biyar na yamma muka isa taraba, daga nan kuma muka dauki shatar mota har har zuwa Takum kai ba zan fadi yadda farinciki yake wanze akan fuskar mu ba, amma tabbas mun yi kewar garin mu, ai kuwa bamu isa ba, sai dare shima ba cikin gari ya shigo damu ba.
"Driver ai da ka kaimu sai mu kara maka kuɗi."
"Gaskiya Hajiya ba zan iya barin takum ba, ina ma zaku?"
"Jenuwa" shiru yayi kafin ya ce mana.."zaku ƙara min dubu ashirin?"
"Eh zamu kara maka!"inji Zulaihah domin ta kagu ta isa gidan. Gyara tsayuwa yayi ya ce mana."tow muje!" Haka ya cigaba da tukin har muka isa garin mu, dake shigar dare muka yi, har kofar gida ya kai mu ya sauke mu, sannan ya juya abinshi....

#thedambuje
[2/16, 9:24 PM] Cutie cutie pie: *BAƘIN HAURE....□□*

{Greed for Money is the roots of all evils□}
Arewabooks:maidambu41
Wattpad:Mai_Dambu
Mallakar:Mai_Dambu
007

Tunda muka sauke kayanmu naji bakiɗaya wani irin sanyi ya lullube ni, sanyin dadi domin babu inda ya fi mahaifarka, haka na karewa garin kallo cikin wani irin tsananin so da kauna. Buga kofar rugar mu muka yi muryoyin mu na tashin sallama, Baffan Ummi ya fara fitowa yana faɗin. "Ikon Allah Hajiya Addah kece a garin mu a daren nan?"
"Eh Modibo gani nan jenuwa babu shiri. Bari mu shiga mu huta."
"A'a bari a taso Lantana ta dama muku fura." "Barshi Modibo bari mu huta haka." "Tow madalla, ku huta lafiya." Ya juya zuwa bangarensu, mu kuwa ni da Zuzu tsohon dakin Mamana muka shige domin dama babu kome sai tsohon gadonta da tarkacen da ake zubawa a dakin, haka muka kwana a gajiye, dake Allah ya taimaka duk mun yi kasaru a Yola sallah Magariba ma sai da muka yi a hanya. Wani abu da ya dame ni, shine na kasa barci haka nayi ta juyi har asuba ta gabato, daga nan na tashi nayi sallar Isha da na asuba, sai lokacin barci me nauyi ya ɗauke ni.

Cikin wani irin yanayi mara daɗi, nake barcin nan, make min cinya aka yi na bude idanuna. "Ya?" "Kawu na kiranmu." "Karfe nawa yanzu?" "Tara da rabi." Tashi nayi ta mika min kofi da dafafen madara."sha ki hada da magani sai mu tafi." Yatsina fuska nayi domin bana son shan madara, haka Allah yayi ni bana son madara idan ba dole ba, haka kuwa na sha, ina tsaki sannan na mike muka fito zuwa dakin Baffa'm, bayan na sha kayan sanyi. Koda muka isa yana bakin kofarshi yana zuba ma Yaran Baffa Modibo shayinsa. D'ago kai yayi ya kalle ni sannan ya saki murmushi, yana faɗin . "Innawuro sai yanzu kika farka?" "Eh Baffa." "Zulaihah kema shigo." Haka muka shiga dakinshi, zama muka yi ga dadi da dumi. "Kun iso lafiya?" "Alhamdulillahi, mun same muku lafiya?" "Masha Allah, Alhamdulillahi. Ya jikin naki?" Sai a lokacin fuskarshi ta sauya kaɗan. Zuba min Idanu yayi kafin ya gyara zama ya kira sunana. "Fadimah Zahrah!" Gabana ne ya fadi, na kalle shi kafin nayi kasa da kaina. "Na'am!" "Idan aure kike so, me yasa baki gaya min ba?" Girgiza kai nayi, a hankali ya shiga min nasiha, Baffa'm yana da matukar hakuri da sanyin hali, haka yasa ba zaka tab'a jin shi yana faɗa da wani ba. Sai da ya gama ya zuba mana idanu yana son jin me zamu ce. "Kawu shad'ari!" Kallon Zulaihah yayi zata magana na rike hannunta. "Meye kike son hana ni magana?" "Ya wuce, a barshi ya wuce har gaban Ubangiji ya wuce." "Kawu laifi ne don ta kare kanta daga dattin zina? Yar uwarka azzaluma ce, bata da imani."
"Kuyi hakuri nasan Allah yana tare da ku, kuma me yasa baku gaya min zaku zo ba? Garin jenuwa babu lafiya, ai da ban barku kunzo ba. Muma zaman dar-dar muke."
"Lafiya kawu?"
"Lafiyar kenan, sai dai wasu daga cikin yan uwa Makiyaya kuma abin da na fahimta baƘin haure aka samu suka shiga gonar mutanen suka musu barna sannan suka kashe musu mutane kusan goma. Haɗe da yiwa matansu fyade, tun ranar juma'a suke son daukar fansa, hukumar tsaro suka shiga cikin lamarin, yanzu haka babu dad'i garin baki daya, shi yasa nake son idan da hali gobe ku bar garin nan."
"Baffa'm na dawo kenan fa." Kura min idanu yayi na wasu dakikai kafin ya ce min. "Kiyi hakuri ki koma can, idan kin samu miji maza ki kirani ki gaya min."
"Baffa'm Sabiru fa?" Kaina a sunkuye."Allah bai nufa shi ne abokin rayuwarki ba, yayi aure suna jalingo da Matarshi da yake yana aiki a can." Wani irin sanyi ya shige ni daga waje har cikin jikina, na hadiye wani irin yawu me daci. "Baffa." Kura min idanu

yayi sannan ya ce min. " Allah yana sane dake, ga wannan takardun, ki tabbatar kin nime Mahaifiyarki, domin duk inda take tana cike da kewarki."
"Baffa'm me yasa ka bani?" Na tambaye shi lokacin wani irin sanyi da zazzaɓin sun rufe ni. "Akwai rayuwa akwai mutuwa idan na kasance araye zan tayaki nimanta, idan muka bana raye zaki tsayawa kanki, Zulaihah ku rike amanar juna,kada ku sake wani abu ya raba tsakaninku, ita duniyar ba kome sai rud'i da karya, ba kome zaka bashi damar fushi ba, na horeku da zumunci, kuma duk abinda Addah zata muku, kada ku sake ku yi fushi Allah yana tare da masu hakuri." Nasihar Baffa'm yake mana, sai da ya gama sannan ya shiga tsokanarmu. "Kun tuna kuna yara kuke damben wace ce zata sha furar Alhajijo." Ya dauki wani allon karfe, ya shiga rubutu yana kallona. "wannan zamanin dole ka nimawa kanka mafita, idan ba haka ba, sharrin zamani sai ya hada da zuri'arka." "Haka ne Kawu " murmushi yayi sannan ya cigaba da rubutun,yana jan mu da hira har ya gama ya wanke a kwanon shan, ya dauko wani saiwa ya jefa yana faɗin. "ku dai rike gaskiya da Amana, ban da cuta da cinAmana, zalunci bai da tsawo domin idan alkadarin ya karye sai an tozarta."
"Haka ne!" Suka ci gaba da hirarsu da Zalaihah ina jin su, har ya gama.ya bawa kowacce ta sha. "Idan kun fita ku bawa Ummi da Munaisah, su sha." "In sha Allah!" Muka fada, "Baffa'm rubutun me ka bamu?" Murmushi yayi ya ce min. "Tsarin jiki ne?" Gyada kai nayi, har zan fita ya ce min. "Innawuro!" Juyawa nayi, "zo nan!" Komawa nayi na zauna, bude wani ƙunshin takarda yayi ya mika min. "Ina ta ajiyewa kafin aurenki, ki saka a wannan abin me kama da lalita, wata rana zai miki amfani kada yunwa ko talauci ya sa ki.aikata Zina don Allah ki rufa min asiri kinji. Duk inda zaki kada ki zauna babu sana'a wannan gwal ce na Mahaifiyarki."gyad'a Kai nayi, a hankali na mike ina mishi godiya, har zan fita ya mika min wasu leda. "Shi wannan abubuwan masu mahimmanci ne, na yaran Harirah ne nasan..." Burr muka ga shigowar Nenne, fisge ledar tayi, "wato ga yar so, ni kuma nawa yaran da baka so su mutu da bakinciki da yunwa bani. Ai keda ganin uwarki sai a lahira."
"Harirah kenan. Allah ya bamu sa'a." Daga haka na fita na barsu, tana saukewa Baffa'm tijara. Ni kan cikin gidan na nufa duk da wani irin zazzaɓin da nake ji, bai hanani zuwa sassan Baffa Modibo na gaishe su ba,har dama-dama Yakumbo bata da matsala, sai Amaryarta ce ma Bama shiri. Yakumbo wacce sunanta Sarai tana da yara hudu, Shu'aibu shine babba yana yola a can yake karatu shine yaron da ya fita Zakka a bangaren Baffa Modibo. Sai Jamilu yana nan domin yayi aure yana garin takum, sai Sa'idu kafin Ummi.
Amaryar Baffa Modibo kuwa, tana da Yara kusan shida duk maza ne, sannan irin haihuwar nan na kunika. Yaran kamar kwarkwata.
Aminu shine babba, sai Zakaria, Amadu, Adamu, Abdullahi, Abubakar dan karaminsu, wucewa dakin mu nayi na kwanta, ina ganin Zuzu tana dafa mana abinci,domin doya ce take dafawa zata mana miyar kwai. Zulaihah akwai kokari domin duk inda zata, tafi da gidanka take yi, har indomie tazo mana da shi, ga kifin gwangwani irin me Mai din nan. Tana gama dafa doyar take bani labarin yadda tayi da ruwan rubutu,ta ce min. "ke nabasu suka ki sha, ai kuwa na sha rabi na bar miki rabi."
Ni dai bance mata kala ba, na cigaba da kwanciyar da nake, domin idan na bude baki zan yi magana kuka ne zai kwace min. Haka na dauki lalita ta, ina kallo. "Zahrah ya dai?" Idanuwa na da suka cika da kwalla na kalleta."Ashe Sabiru yayi aure bai gaya min ba?" "Mtsew sai kace autan maza." A hankali na fashe da kuka, ina jin wani irin abu yana taso min, kamar kukan nan saka ni ake yi, har sai da nayi na gaji, tana kallona taci abinci ta koshi, ta mike ta daura ruwan zafi, ta fita tayi wanka sannan ta shirya zuwa gidan Babanta, koda ta je can faɗa yayi mata me yasa zata zo, gari ba lafiya. Hakuri ta bashi tare da mishi zancen ta hadu da wani tana son ta turo shi,ta kira saurayin ta hada su, sukayi magana ta roki Babanta kada ya bari Addah ta sani. Ya mata alƙawarin ba zata sani ba.

***

Karfe biyar ina wurin dabobbi, ina taya Baffa'm tatsar madara. Wayarshi tayi ƙara dauka yayi yana me sallama. " Alhaji Abubakar ko?" "Eh ni ne?" "Okay ko zaka fita kai da wani naka, domin mun samu labarin za a."
"Anan aka haife mu, anan muka girma bamu da inda yafi nan, sai dai mu mutu, Yallabai mun gaya musu, bamu ne muka musu barna ba, taya zamu cigaba da amsar laifin da bana mu ba, a matsayinku na jami'an tsaro hakkinku ne kula da rayuka da dukiyoyin mu."
"Shi kenan, kada kace ban sanar maka ba, na gaya maka gaskiya kuma ba a bamu umarnin kare kowa ba, don Allah ka fita daga cikin Jenuwa."
"Shi kenan!" Baffa'm ya faɗa yana kallona, taya zai fara. Haka ya wuce ni ya saka aka kira mishi sauran mutanen rugar ya gaya musu abin da yaƙe faruwa. Shiru suka yi kafin aka samu wasu tsagera suka kama dariya."Baffayo kana nufin Mu bar rugarmu saboda kada mu mutu? Kusan kai ma kana da shanun nan,don haka babu inda zamu ai wannan maganar karya ce wallahi babu wani! Harin da za a kawo mana, da alamu tsufa ya fara kama baffayo." Kiri-kiri matasan nan suka ƙaryata shi, haka yasa shi komawa gida da tarin takaici da bakinciki.

Koda ya dawo ana kiraye-kirayaen sallar Magariba, a masallaci ma yayi magana dayawa suka karya tashi sai yayi shiru, koda ya dawo bayan isha muna cin abincin, ya shalenta abin yake faruwa a cikin gidan, Babangida ya ce mishi. "Baffa taya zasu kiraka su gaya maka, kawai dai wannan zance ne. "Bai fito ya ƙaryata baffa ba, amma maganarshi sak ce da ta sauran mutanen, ban san me yasa ba ko don a gabana aka yi wayar sai naji zuciyata tayi sanyi, kuma wani irin tsoro da fargaba, ya shige ni Zulaihah ma ta shiga haɗa duk wani abu me muhimmanci akan mu bar garin cikin daren nan, amma wani abin mamaki kana naka, Allah yana nashi, wurin karfe tara na dare, muka dinga jin ƙarar harbe-harbe, hankalin Baffanmu ya tashi, yana shigowa dakinmu ya ce min.."taso Fadimah." Tashi nayi a rikice ya cewa Zulaihah. "Kema tawo!" Dakinshi ya wuce damu," kada ku sake ku fito matukar bani na bude muku kofar ba, da izinin Allah babu abinda zai faru." Ashe ya tafi har dakin Nenne ya kwaso yaranshi, Yar matan nan tace ta adana Yaranta, domin mugun nufinsa ya janyo wannan tashin hankalin,da bai fada ba ai da babu abinda zai faru. Bai mata magana ba ya dawo duk inda ya nime su bude kofar ya kwaso yaran sunki,.haka yasa shi dawowa ya dauki addarshi ya tsaya a kofar gidanmu.
Ban tab'a shiga tashin hankali irin na yau ba,domin kuwa kana d'aga kai zaka ga yadda garin yayi jajjur da wuta da hayaki. Baka jin kome sai karar bindigu da kukan dabbobi.

Ban san me yasa idan wani abu ya faru mutane ke huce takaicinsu akan shanu ba, shanu suna da daraja a rayuwar Bafulatani, domin zai iya hakura da rayuwarshi akan dabbarshi, amma mutane basu ganewa. A cikin yan dakikai nayi wannan nazarin, "Tau!" Muka ji kar'ar harbi kamar a cikin gidan anan aka yi,kuma babu karya a cikin gidan aka yi. "Malam Buba yau addarka ba zata amfane ka, da kome ba, domin kafin ka kai sara mun tashe ka aiki." Jijjiga kofar nayi ina hango Baffa'm a kwance, domin sun haska mishi katon torchlight dinsu mai shegen haske, Baffa'm a kwance jini na zuba ta gefen cikinshi.

"Kai ku shiga ku fito mana da yaran da suke cikin gidan, matan ku ware mana manya da kanana, mazan a musu yankan raggo a gaban Malam Buba da yace basu ne suka mana barna ba." Inji mutumin, "tow;" dakyar Baffa'm ya mike yana rike kafar mutumin. "Don Allah dan ladi kada ka cutar dasu, wallahi bamu bane. Akan me zamu cutar da zaman da muka yi na amana da ku?" Shure Baffa'm suka yi tare da take mishi wurin ciwon, suna murtsukawa. Haka suka fito da kowa na gidan, har da Baffa Modibo. Babangida da Habibu. Sa'idu da su Aminu. Dukar kofar da nayi yaja hankalinsu ba zan iya ganin wannan cin mutuncin ba, gara na mutu da Mahaifina. "Aiho boye wasu kuka yi?" Ya dokawa Baffa'm gindin bindigarshi akan ciwon, "ku balla kofar ku fito da su." Haka suka nufi kofar da gudu Baffa'm ya tashi yana me tare kofar. "Ku min kome na yarda, don Allah ku kyale mata da yaran basu yi kome ba."

Rufe shi da duka suka yi, tare da janshi daga kofar dakin suka ɓalle kofar, tare da finciko mu. Suka yi waje damu. Ganin suna dukar Baffa'm babu me cetonshi na nufe shi, tare da fara ture su, haka aka fisgo ni suka bugani da kasa, tashi nayi da rarrafe kafin na isa sun mishi wani irin duka tare da cin zarafinshi suka tube mishi suturarshi. Rike gashin kaina mutumin yayi yana dariya. "Ke me baba ko? Maza jeki, Malam Buba idan kana son mu kyaleka dole sai ka amince kayi tarayya da Yaranka mata. Su kuma Yara mazan su kwanta da iyayensu Mata ko kuma mu,mu kwanta da su."
Suka fada suna dariya irin abin ya musu dad'i. "Ku kashe ni ba zan iya ba, ba zan iya kallon wannan kazantar ba." "Ashe? Tow kai daure min hannun mazan a musu yankan raggo su kuma matan ku ware min yan matan manya kuma su raba su." Har zuwa wannan lokacin yana rike da gashin kaina. "Dan Ladi kada kayi abin da zai dame ka, don Allah kada kaci zarafin Musulunci mana, addinin Kirista bai baka damar cin zarafin mata da yara ba." Amma mutanen nan suna dariya suka d'ago Babangida. "Kaje ka kwanta da uwarka kacita kamar yadda namiji yake cin Matarshi a gadon auren, kada ka biyewa Ubanku ba zai tab'a barin ku tsira ba, kana gamawa ga kofa ka fita ba zamu tab'a ka ba." Kusan yadda dan Adam yake da buri, kuma a ran Babangida gani yake idan ya aikata haka zasu barshi ya rayu, Baffa'm yasan yaudara ce kawai. Rike hannun Babangida yayi ya ce mishi. "Idan ka sake ka aikata haka, zasu kashe ka Allah ya saka hijabi a tsakaninku har abada ba zasu kasance a shimfidarka ba, Mahaifiyarka da yan uwanka, haramtattu ne a gare ka. Don haka kada ..." Dauke kan Babangida suka yi da harbi, sai gashi a jikin Baffa'm. Wani irin ajiyar zuciya Baffa'm ya sauke ya ce musu."Gara ku kashe mu da ku kasance kuna saka mu,aikata barna."

Wurgar da ni Mutumin yayi na na rarrafa wurin Baffa'm, na mika mishi kayanshi. Ina durkushe a gabanshi. "In sha Allah duk tsanani yana tare da sauki, kada wani abu ya baƙi tsoro gwagwarmayar...." Sake mishi harbi suka yi a gadon bayanshi. Ya fadi a jikina. "Kada tsoron mutuwa yasa ki ki tserewa da zaki rayu. Kiyi iya yinki Allah yana tare da mai gaskiya da takawa." Wani Harbin suka yi mishi sai da jin ya wanke min fuska. Har lokacin bai cika ba, babban burin shi yaga mun tsira ba tare da sun ci zarafin mu ba.

Janyo shi suka yi, akan idanuna kamar wata gaula ina kallonsu, suka shiga bude mishi wuta har sai da ya daina shure shure yana kalmar shahada, ban san ya aka yi ba amma ihu da karar harbe-harbe nake ji amma ban san me yake faruwa ba..haka suka yi ta bin Yaran nan suna harbinsu har da Baffa Modibo, akan idanun Nenne suka kashe mata Yaranta maza biyu, Yakumbo Sa'idu, Amaryar Baffa Modibo kuwa a wurin ta samu tab'in hankali domin kuwa ganin jinin yaranta yasa ta kama dariya. Bayan sun kashe mazan baki ɗaya, haka suka yi ta bin iyayenmu mata suna kwanciya dasu, ko nace Fyade. Hawwa'u da Hadiza kan, ko taron da mazan suka musu ne, amma ban san kome ba, sai da naji an rufe mu da duka ni da zalaihah. Ni dai naji kamar an suka min wani abu ban kuma sanin kome ba.
Bayan sun gama ta'aadacinsu, suka sakawa gidan wuta, kafin wani lokaci rugar mu ta zama makabarta domin babu inda babu gawarwaki. Sannan yadda suka tozarta mu haka suka bar mu a wulakance. Bayan tafiyarsu Addah da duk rashin imaninta yau sai da tayi kuka, Ita ta tashi da gudu tana shiga dakinta ta Ciro kaya tana daukar zanuwa da zanin gado, ita da Yakumbo. Dukkan iyayen nan kana ganin yadda suke abu kasan karfin zuciiya ne domin Nenne da suka mata wulakancin bata iya tashi ba, haka aka yi ta lullube gawarwakin da sauran mu, ita kan Amaryar Baffa Modibo, bayan sun gama mata fyaden, kasheta suka yi sannan suka barta a wurin. Zama Addah tayi a gaban gawar kannenta ta fashe da kuka. Sai lokacin kuka ya zo mata, har gari ya waye sai lokacin yan agajin gaggawa suka kawo mana taimakon gaggawa. Aka wuce damu asibiti sai dai kuma babu gado domin kuwa asibitin cike yake.

Wani abin da nake son ku sani, Taraba tana kudu da kasar Kamaru, sannan koda aka bamu taimakon babu wani abu, tura mu camp na yan gudun hijira aka yi, muna zuwa can,aka ce babu wuri dole aka hada mu da hukumar gudun hijira aka mana takardu aka wuce da mu Kamaru....
This is the beginning.....300₦..
#thedambuje
[2/16, 9:24 PM] Cutie cutie pie: *BAƘIN HAURE....□□*

{Greed for Money is the roots of all evils□}
Arewabooks:maidambu41
Wattpad:Mai_Dambu
Mallakar:Mai_Dambu

Wato jiya an yi kuka, hmm ayi hakuri na kara bada hakuri. Abin labarin a sannu 😍 wannan naku ne masu bibiyata. Allah ya saka da alkhairi 😍❤□□ na ji dadin comments dinku na jiya ya tashi kaina su Auntys and mommies har da niman kari □😹 Na gode sosai

008
Saboda azabar ciwo da muke fama da shi, bama fahimtar juna ko me yake faruwa, iyayen mu mata kawai zaka kalla ka fahimci suna cikin wani yanayi amma gudun kada su sare a gaban idanuwan Yaransu yasa suke fakar idanunmu suna kuka. A haka muka isa har Kamaru tafiyar kwana biyu,
Adamawan Kamaru aka kai mu, anan babban camp na yan gudun hijira yaƙe. Sai da muka je asalin headquarter aka mana takardu, sannan aka wuce da mu asibitin da yaƙe asalin garin, anan aka shiga bamu taimakon gaggawa.

****
Niamey: Niger republic

Ranar zaben.
Wato wannan ranar abu biyu za a gabatar na farko yadda suka shirya idan har suka fi su Aryan Mamman Ba'are yawan vote. To zasu amshe BA'ARE GOLDEN EMPIRES daga hannunsu Hajiya da Yaranta, na farko kenan, na biyu zasu sayarwa mutanen kasashen waje, sannan su zare hannun jarin Hajiya da Yaranta.
Sai dai wannan lokacin al'amarin daga ita har Yaranta sun sadakar musamman da suka ga Aryan Mamman Ba'are ya dawo babu Majeed, sai jikinta yayi sanyi a matsayinta na Uwa ya zata yi? Hawaye ne ya zubo mata tana kallon Aryan Mamman Ba'are.
Tasowa yayi ya mika mata hanky yana faɗin. "Kukan me kike yi?" "Na hango faduwarmu ne, burinsu idan muka fadi hatta gidan BA'ARE housing estate zamu bari, duk wani abu da ya shafi BA'ARE zamu bari." Dariya yayi yana faɗin."haka muke so sannan a wannan karon za a sake gwanjon kome har da estate kenan?" Ya fada yana mikewa daga inda ya zauna ya koma wurin shi, masu hannun jari da matsayi a board din kamfanonin BA'ARE mineral oil and gas, amma babban al'amarin da wannan rikicin yana kan GOLDEN EMPIRES ne.
Hajiya Nana ita ce a sawun gaba, sai Hajiya Tani da d'anta Sajjid Mamman Ba'are, sai Hajiya Rabi Mamman Ba'are, sai Hajiya Fauziya Mamman Ba'are, can sai ga Hajiya Harirah Mamman Ba'are, dukkansu da yaransu mata da maza.

Dukkansu nan babu wacce za a nuna mata takarda ta karanta, kawai kishin jahilci ake yi, Hajiya Sa'adatu Mamman Ba'are, ita ce Hajiya mahaifiyarsu Captain. Kuma ita ce Amaryar Alhaji Mamman Ba'are,sannan ita ce take da Yara maza uku cif. Su Majeed suna da yayu mata manya, amma kusan da yake akwai kishi da hauka yasa kowa yake rayuwarsa a inda yaƙe.

Idan ka cire Hajiya Harirah da take da abin bata yarda ta kashe kanta da kishi ba, domin sai da ta nime ilimi, saboda ta fahimci wani abu da sauran suka gaza fahimta.
Can Alhaji Haladu Abdul Majid Ba'are sai
Alhaji Kamilu Abdul Majid ba'are, kafin Hajiya Hadiza Abdul Majid ba'are.
A bangaren Hajiya Sa'adatu Mamman Ba'are, Akwai Amaan Mamman Ba'are, sai Aryan Mamman Ba'are, sai Jamilah Mamman Ba'are, sai Aneesah ita ce auta.

A hankali wurin yayi ta cika, kuma a wannan zaman babu bare amma kuma wani abin mamaki shine zuwan wasu daga cikin turawa da yan siyasar da Sajjid Mamman Ba'are ya gayyato, ya tashi ya taro su. Har wurin Nana suka gaishe ta. Kafin suka gaida kowa sannan suka koma wurin zamansu, Abdul Majid dan Hadiza Abdul Majid ba'are, ya mike tare da nufar wurin Hajiya suka gaisa. "Hajiya Abdul Jeed ba zai zo bane?" Idanunta da suka cika da kwalla ta ce mishi. "Ban sani ba, na dai tura Aryan bai ce min kome ba."
"Lallai Jeed dole ya bayyana anan. Domin an shirya makirci na bala'in fitar hankali."
Duk wahala da ta sha, da iya azabar da ta sha, wai karshe abin da ta samu shine ya tsonewa kowa ido. Suna da nasu amma ita nata da na Yaranta ya tsone musu ido. Hajiya Hadiza Ba'are watsawa danta Abdul Majid harara tayi, ita kan bata san wani irin d'a ta haifa ba, ko a gidan Ubansu haka yake makalewa ya'yan kishiyoyinta yana basu kulawa kamar wani son shi suke.
Komawa wurin zamanshi yayi yaki yarda ya kalli Hajiyarsu, da Nanah kakarsu kenan. Kanshi yana can bakin kofar aka fara taron tare da zab'en ra'ayi akan matsayin BA'ARE GOLDEN EMPIRES. Abin dai ba a cewa kome.

Haka aka fara voting, jikin Yaran Hajiya yayi sanyi ban da Amaan Mamman Ba'are, dan shi dama yasan haka zata faru, kuma shi yana tare da su, babu me kaso mafi girma da yawa a kamfanonin kamar Majid, don haka gara ayi uwar watsi kowa ya rasa, Aryan Mamman Ba'are kuwa ko a jikinshi domin bai tashi ya kada kuri'ar shi ba, kallon shi Alkalin yayi ya ce mishi. "Malam Aryan Mamman Ba'are, shin baka ga kowa ya kada kuri'a ba ne?" D'ago kai yayi yana yak'e ya ce mishi. "Alkali kayi shiru yanzu zan kundume wasar domin uban gayya ya bayyana." Ya cigaba da danna wayarshi alamar game yake yi, "Malam Aryan kuri'arka ake jira fa." "Ba iya nawa ba, har da na wancan da yake tsaye a bakin kofar." Ya nuna musu Majid Mamman Ba'are sanye da kayan turang. Shadda ce skyblue, yasha babban riga da takalmi halfcover, kanshi sanye da rawani ya rufe fuskarshi da ita, yadda yake tafiya kasan cikakken jarumi ne. Mikewa Aryan Mamman Ba'are yayi ya tafi can bayan kujerar da aka ware babba kuma an lullube shi da mayafi, Hajiya ya dace ta zauna a wurin amma saboda fitina ta hakura, sai gashi Aryan ya janye lulluben da aka mata, sannan ya jata baya, Majid Mamman Ba'are ya isa wurin y zauna, dukkansu sai da suka mike tsaye. Yadda ya zauna sai da ya jingina da kujerar sannan ya aza kafa d'aya kan ɗaya, ya janye mayafin da yake fuskarshi. Yana bin ilahirin mutanen wurin da rikitaccen Idanuwan shi me dauke da wutar takaici da b'acin rai. "Amma taya dan iskan Yaron nan ya dawo?" Cikin kwafa Hajiya Tani tayi magana tana kallon Majid da ya daura daya kan ɗaya, yana sakin wani murmushi yana kallon Aryan da ya koma wurinshi da zama. "Alkali Bismillah!" Inji Aryan ya faɗa yana murmushi. "Tow Malam Aryan kuri'arka da ta Abdul Majid Mamman Ba'are ya rage, akan sikeli" hannu ya kai aljuhun rigar shi ya Ciro wasu zinarai manya guda uku, sai na shi daya yana zuwa ya saka nashi, yana kallon kowa a wurin sannan ya saka daya na Majid Mamman Ba'are, tuni hannun ya rinjayi daya hannun cikin tsokana da niman magana ya ce. "Alkali idan na saka sauran biyu ina cewa Ba zaku ce nayi son kai ba?"
"Baka da matsala Malam Aryan" cikin wani irin juyi ya ajiye dayan, sai ga shi bakidaya ya rinjaye gefen. Kafin d'aga dayan sama ya ce musu. "Kun ganshi nan kuri'ar Majid Mamman Ba'are na karshe kenan!" Ya ajiye . Shiru wurin ya ɗauka. Babu wanda ya kawo Majid zai bayyana, balle a kawo zancen kuri'arshi, sannan babu wanda ya kawo wannan al'amarin haka shi daya kuri'arshi daya ta mutane goma ce

ukun baki daya ta mutane talatin ne, domin kuwa asalin zinarin na Alhaji Mamman Ba'are ne, da kanshi ya ajiye wasiyya har kotu aka kai banki aka ajiye, asalima ba a kasar ya ajiye ba. Sai aka zo rabon gado aka gani. Ya narka ta zuwa na Majid Mamman Ba'are kuma ya saka sunanshi a jikin zinarin.

"Kuri'ar Hajiya Sa'adatu da Yaranta sune masu rinjaye, sannan suna da damar fadin yadda suke so ayi da BA'ARE GOLDEN EMPIRES."

A hankali Aryan ya mike ya ce. "Alkali dama ai idan aka yi rinjaye a kan mu gwanjon kamfanin za ayi ko?" Kallon Alhaji Haladu Ba'are da Sajjid Mamman Ba'are alkali yayi, suma kura mishi idanu suka yi.

"Alkali ni nake magana ba Sajjid tani ba, ba Haladu Ba'are ba, Aryan Mamman Ba'are yake magana."

"Eh Malam Aryan."

"Kawai a saka a kasuwa!" Ya fada yana me komawa wurin zamanshi ya daura daya bisa ɗaya.

Ajiyar zuciya Alkali yayi ya fara karanto ka'idodin sayar da kayan.

"Doka ta farko waɗanda suka fadi basu da hurumi akan kamfanin dole suyi hakuri da duk abin da zasu ji ko zasu gani. Doka ta biyu idan aka sayar ga duk wanda ya saya hurumin shine cire sunayen wasu da baya ra'ayi a board meeting, doka ta uku iya waɗanda suka saya suke da ikon tafiyar da kamfanonin baki ɗaya."

Wannan shine shirinsu idan Majid Mamman Ba'are bai zo ba,tow abin da za ayi kenan. Mikewa Aryan Mamman Ba'are yayi ya mikawa alkali kudin da aka sakawa kamfanonin. Hajiya tasan ba wayonta bane, ba Kuma iyawarta ba ne kawai wata falala ce daga rabbul alamin, ya bata yara maza biyu masu matuƙar zuciya da son cigaban juna. D'aga takardar kudin alkali yayi, nokewa kowa yayi babu wanda yayi kuskuren tashi domin kuwa basu da kwatar kudin da aka nima balle rabi. Haka yasa Majid Mamman Ba'are mika hannu. "Na saya!" Shine dama me hannun jarin da ya wuce misali. Yana fadar haka ya mike, tare da barin taron. "Alkali kaji ya saya, ko akwai wanda zai ja ne?"

"Babu Malam Aryan!" A hankali ya taka gaban kujerar Hajiya Tani ya zuba mata ido. "kun shirya wasa, ba tare da kun san waye dan wasan ba, ya dawo har na tsawon lokacin da ya dibawa kanshi."

Daga nan ya nufi wurin Hajiya ya daukar mata jaka, suka nufi hanya Jamilah da Aneesah suna biye da su. Lokacin da Amaan ya isa wurin Nanah kasa magana yayi. "Munafiki ba kace mana Aryan bai same shi ba? Ko dama munafurci ne yasa kazo don kasan sirrinmu!"

"Nana!" Alhaji Haladu ya kira sunanta, "shima bai san kome ba, babu babban shaidanin kamar Aryan yaron nan "

"Wai ku yaushe zaku daina faɗa akan abin da ba naku ba? Dukiyar nan da bakin Ya Mamman ya mallakawa Sa'adatu da Yaranta, musamman Majid don Allah ku kyale su mana."

"Ai kai ban san wani irin haihuwa nayi ba, baki daya baka da kishi da kishin yan uwanka, ban da jaraba irin ta Mamman ai shi kenan."

Hajiya Tani bata ce kome ba, domin dama ba zata tab'a cewa ba, amma zuwan Abdul Majid Mamman Ba'are ya kashe mata kasuwa, domin duk burinta ya lalace. Juyawa tayi ta futa bata musu magana ba, ta nufi hanyar waje ita da d'anta. "Hajiya!" Hannu ta d'aga mishi. A waje suka same su, musamman Aryan."Hajjaju! Ki kara shiri da kyau."

"Kana wasa da rayuwarka." Inji Sajjid Mamman Ba'are. Ai kamar jira ake Sajjid ya fadi haka sai ga Press sun shiga daukar hotonshi a bakin kofar kamfanin. "Taron da aka shirya domin ruguza kamfanonin BA'ARE, ya tashi cikin wani irin juyin juya halin, domin kuwa ana cigaba da taron Majid Mamman Ba'are ya bayyana sannan ya saye kamfanin da kaso daya na cikin dukiyar shi, abin da ba a saba gani ba domin duk taron da ake Majid bai tab'a halartar taron ba, amma wannan karon ya tawo cikin ban mamaki " can wani dan jaridar ya amsa da cewa. "A wani abin da ba a san mafarin

shi ba, Sajjid Dan wurin Hajiya Tani da ta likawa Marigayi Mamman Ba'are, yayiwa Aryan Mamman Ba'are barazana da rayuwarshi."

Jikin Hajiya Tani ne ya dauki rawa, ta juya tana kallon Sajjid da ake ta daukar shi, da sauri ta fada cikin Motarsu, suna shiga ta juya a fusace . "Ina ruwanka da shi? Idan ma wani abu ya maka sai ka yi shiru meye na tanka mishi? Ga ka nan kato amma tunaninka na Yara ne, bakasan ka girme shi ba ne? Amma ya iya nutsuwa ya shirya kome cikin dadin rai. Ka koya daga gare shi."
Rintsa idanun yayi yana jin kamar ya fita ta rufe su da duka. "Kai mishi barazana da rayuwarshi? Kasan ko ciwon kai yayi kai ne, idan mun koma gida kayi gaggawar kiran yan jarida ka wanke kanka."
"In sha Allah "
"Na gaya maka, hatta tari idan kayi duniya zata fassara shi da wata manufa ce, baka gane ba, kana kokarin lalata min shiri na."

Hajiya da Yaranta baki daya wucewa gida suka yi, Majid da daman ya rigasu barin wurin taron, sun same shi a dakin shi na Asali , yana kwance. Dakin duhu kamar kullum. "me yasa kake son zama cikin duhu?" Tashi yayi zaune yana kunna wutar da yake gefen gadonshi. "Hajiya ina jin dadin haka ne, domin yana tuno min da wasu abubuwan da suka wuce."
Murmushi tayi tana kallonshi ya kara girma, ya nutsu ba kamar lokacin baya ba. Ya zama cikakken namiji me cikar halitta, sadauki da duk inda ake nimanshi ya kai. "Abdul Majid maganar aure fa?" Gabanshi ne ya fadi, ya kurawa ƙasa idanu. Akwai wani abu da yake rufewa a zuciyarshi baya jin zai iya aure. "Hajiya!" Ya kira sunanta muryar shi tana rawa. "Hajiya auren nan dole ne?"
"Dole ne Majid! Dole kayi aure domin haka ne zai saka ka kara zama cikakken mutum ka zama magidanci."
"Hajiya."
"Akwai yar kawata babanta abokin cinikin mu ne, kaje an jima da yamma ka ganta."
"Hajiya!" "Bana son musu, ai na maka adalci rabonka da kasar nan." Mikewa tayi tare da fita daga dakin. Sai da ta isa bakin kofar ta juya ta ce mishi. "Ka fahimci gatar da zan maka amma ban maka dole ba." Gyada kai yayi yana jin kamar ya fasa ihu.

Hajiya tana fita falon ta Salamatu me aikinta tace "Hajiya akwai baki a falon kasa ." Kura mata idanuwa tayi ta ce mata. "Su waye?" Cikin girmamawa ta ce mata. Hajiya Nana da Hajiya Hadiza!" "Muje!" Tsayawa Salamatu tayi Hajiya ta shiga gaba, har falon kasa suna zuwa suka same su a hakimce. Niman wuri tayi ta zauna tana gaishe su. "Ina Abdul din yake?" Inji Hajiya Nana. "Yana sama!" Kwafa tayi ta ce mata. "Wato har ya kai da ya mai da mutane yan iska ko? Sai yazo gari ya ki zuwa gaishe da Hajiya." Murmushi Hajiya tay ta ce musu. "Na ga dai Abdul Majid Mamman Ba'are, d'ana ne kin manta ne Hajiya Hadiza? Da kika ce Yaransu Hajiya Rabi da Fauziya sune Yaranki, Yaran da suka fito daga jikina Yayan bariki ne, yanzu kuma da wacce kuke tafe?"
Kurawa Hajiya idanu suka yi, Nana ta ce. "Bana son munafurci, kiyiwa jikana magana yazo har gida ya..."
"Tunda kika kasa hakuri kika zo takalata da faɗa, kin san dai baki isa na zo har gidanki ba." Ya fada yana gyara hannun rigarshi. Kallonshi tayi wannan yaro yana bata tsoro har cikin ruhinta. Hadiye yawu tayi tana kauda kanta domin tana matuƙar tsoronshi. Zama yayi ya kalli Hajiya Hadiza ya ce mata Mama Barka dai."
Tab'e baki tayi ta ce mishi. "Barka."
"Yanzu Alhaji sai kazo garin nan baka zo ka duba ni ba.? Fisabilillahi." Ta fada kamar zata fashe da kuka.....

#thedambuje
[2/16, 9:24 PM] Cutie cutie pie: *BAƘIN HAURE....□□*

{Greed for Money is the roots of all evils}
Arewabooks:maidambu41
Wattpad:Mai_Dambu
Mallakar:Mai_Dambu
009

Tamke fuska yayi yana kallonta, domin ba zai tab'a mantawa da izayar da matar nan ta bashi ba, cikin muryar shi mara daɗi ya ce mata. "Nana kin ajiye ni ne da zan zo na duba ki?" Shiru tayi tana kallonshi kamar zata mutu, idan ta ga yana nuna mata kiyayya haka. "Alhaji ina laifin Nana don ta damu da kai?" Mikewa yayi bai basu amsa ba, musamman ita Hajiya Hadiza da ya tsani ta mishi magana.

"Kyale shi ai Uwarshi tana gani yake wulakantani." Murmushi Hajiya tayi tana faɗin. "kin sha gaya min idan kina magana da ahalinki na daina shiga cikin maganar, kuskure ne don na zab'i yin shiru akan na magantu?"

Cikin borin kunya ta ce mata. "Hmmm! Haka dai kika ce, amma ni yaushe na ce ki daina shiga cikin ahalina. Yanzu dai nazo ne maganar kamfanonin nan, da fatan dai ba za a cire min hannun jarina ba ko?"

"Ni babu ruwana ki same shi." "Tow ta nan kika bullo min Sa'adatu?" A gajiye da halin Nana Hajiya ta ce mata. "Nana meye nawa a cikin wannan lamarin? Yaran nan jikokin ki ne, sannan kuma."

"Kawai dai ki ce mana Yaranki sun fi karfinki, amma taya akan wannan yar maganar zaki ce wai babu ruwanki salon munafurci da nunawa kamar ba ruwanki." Inji Hadiza Abdul Majid ba'are, "Hadiza kin ga babu ruwanki da sha'aninmu, tsakanin Nana da Jikokin ta gata ga su ina ruwana?"

Ta fada tana kallonsu, kwana biyu da suka wuce har cikin gidan suka biyo ta suka ci mata mutunci har da mata gorin a caca aka aurota, haka duk bai isa ba Nana ta gaya mata cewa ta zuba idanu tayi kallo hatta wannan gidan da take ciki sai ta fice daga cikinshi, sai gashi Allah ya raba gardama ya kawo mata shi cikin sauki, don haka ba zata lamunci rainin hankali ba. "Hmm! Nana tashi muje!" Inji Hadiza, haka suka fito a harabar gidan suka same su, a ran Hajiya Hadiza ta ce. *Shaidanun biyu* kallon Nana Aryan yayi, ita hankalinta yana kan hannun Captain yana goge wata sabuwar bindiga. "Captain ni dai ka nima min lasisin rike bindiga!" "Munafiki algungumi uban me zaka yi da bindiga?" Juyawa yayi ya kalli Nana. "Hajjaju laifin me na miki? Uwar Mamman Ba'are!" Ya tambaye ta, yana wasa da katon lion dog ɗinshi. "Uwarka Sa'adatu gata can a sama." Juyawa yayi ya sumbaci hannun shi ya wurga mata. "Ta iya haihuwa tunda ta haifi Abdul Majid Mamman Ba'are, ta haifi Aryan Mamman Ba'are ba, Uwar Jamilah da Aneesah, Babar Amaan Mamman Ba'are, akwai saura ne?" Ya tambaye ta, cike da takaici ta ce mishi. "munafikin banza." "Da nayi miki me?" "Kai dai wutarka dabance." Sam baya son hayaniya, don haka ya d'anna kunamar ya sake harbi a iska, shiru wurin ya dauka. Musamman Hajiya Nana da ta ji kamar zuciyarta ya harba, kafin su farga daga ita har yarta sun gudu baka ganin alamarsu, sojojin da aka bawa Captain ɗin suka shigo a guje. "Sir!" Murmushi yayi ya musu alamar su tafi da hannunshi.

Kar'ar harbin Majid Mamman Ba'are, ya karad'e ilahirin gidan baki daya, wanda yasa kowa ya sha jinin jikinshi, lallai Majid ya iso, Gidan Alhaji Kamilu Abdul Majid ba'are, kuwa tab'e baki yayi ya ce. "Kowa ya sayi rariya yasan zata yi yoyo, ai na gaya musu, babu ruwansu da Yaran Sa'adatu amma suka ki, gashi nan sun takalo mana jaraba." Ya fada yana shan tea a hankali, "ni kuwa sai nake ganin kamar da gayya aka takalota."

Kallon Matarshi yayi, kafin ya ce mata. "eh da gayya ce mana, tayi abu ko Yaranta suyi su zama masu laifi ake so." "Amma me yasa suke haka ne?" "Saboda dukiyar Mamman ya raba biyu ya basu rabi, rabi aka yi rabon gado da ita."

"Allah ya kyauta!"

"Kin yi waya da Maisarah?" "Eh mun yi waya, amma tace min idan suka samu hutu zata zo." Shiru yayi yana kara jin ba dad'i. Kowa a duniya yana farinciki da nutsuwa idan yana tare da ahalinshi, amma shi a nashi ɓangaren dole ya hakura da Maisarah ta koma wurin dangin Mamanta da suke labenon, tunda a can ya auro ta,kuma ba karamin son Yaransu suke ba. Sai dai tun bayan Mutuwar Mamman Ba'are yarinyar taki zama a wurinshi. "Ina Jamal?" " Ya tafi wurin kallo!."

Gidan Hajiya Tani.

Cikin matsanancin b'acin rai take kallon Sajjid Mamman Ba'are, "kasan yadda na ɓata lokaci akan ka samu damar shiga cikin dukiyar Mamman Ba'are?" Girgiza kai yayi yana durkushe a gabanta. "Kiyi hakuri Hajiya!" "Idan ka kuma bani hakuri sai na tsine maka." Ta fada ranta yana suya, "sai da na gaya maka ba zan dauki kuskure ba, kace babu matsala Amaan zai bamu hadin kai, amma sai gashi daga kai har shi kun fad'i." Kasa magana yayi domin yana matukar tsoron kada yayi magana ta tsine mishi.

"Yanzu kana da hanyar da zaka iya dawo min da asarar da nayi?" Girgiza kai yayi, tayi kwafa sannan tacigaba da cewa. "Dake kai lissafinka baya ja, shine ka bude shegen bakinka zaka mishi barazana da rayuwarshi!" "Na tuba Hajiya!" Ɗaukar glass cup tayi ta jefe shi sai da ya tasa mishi goshi, jini ya shiga zuba a Kyakyawar fuskarshi.

"Ka sake bani hakuri sai na illataka!" Jini da yake zuba yasa shi rike wurin. "Ɓace min da gani." Mikewa yayi ya nufi dakinshi,ya shiga kallon kanshi a mirror din dakinshi. Wayarshi ce tayi ƙara. Dauka yayi ya ce. "Na'am!" Cizon fatar bakinshi yayi ya ce. "Ban san asara ba, kayan nan Libya zaa shiga da su, ka gayawa Guru ya binciko min duk inda Jaguwa yake a tsakanin sahara da dazuzzukar Kamaru da Nijeriya, idan kuka sake na fita farauta ba zai muku kyau ba." Ya kashe wayar yana me jifa da ita, asara biyu yayi yau baki daya bai tab'a shiga damuwa irin ta yau ba, ban daki ya wuce ya wanke fuskarshi da jikinshi, sannan ya bude first aid kit ya gyara goshinsa. Yana gamawa ya fito yana tsane jikinshi, ya ji harbin bindigar Majid. Datse fatar bakinshi yayi da hakorinshi sai da ya fara jini.

Ya sake bakinshi a hankali, yana jin Idanunshi yana cika da kwalla. Idan yana raye sai ya ga bayan Majid, ya raya a ranshi yana me kara tabbatarwa kanshi, sannan ya shirya cikin kananun kaya, ya dauki madubi ya saka domin ta rufe mishi inda aka jefe shi. A falon ya sami Hajiya Fauziya, tana kasa da murya ta ce. "Wato ban san yadda aka yi wancan dan iskan Yaron ya dawo ba, amma tabbas ita Uwarshi abin ya mata dad'i." "Zan fita." Dauke kai tayi tana faɗin. "Hm!" Daga haka ta juya ga Hajiya Fauziya. "Me kika ce?" Cikin tuntuben harshe ta ce mata. "Naga alamar babu nasara." A fusace Hajiya Tani ta watsa mata harara. "Kika ce me?" Hadiye yawu tayi ta ce mata. "Dama nace wannan karon mun fadi ya zamu yi?" Tab'e baki tayi tana faɗin. "Ya kuwa zamu yi? Ku je kuyi shawarar makomarku bamu ba."

A zunkud'e tace mata. "Ban gane ba?" Gyara zama Hajiya Tani tayi ta ce mata. "Dama da an samu nasara kamar yadda na gaya miki, kina da kaso saba'in cikin dari, ni zan tashi da talatin kuma gashi ya dawo." Cikin tsannanin takaici Hajiya Fauziya ta sauke kanta kasa, "Ban san ta inda aka samu matsalar nan ba, amma tabbas akwai wani abu."

"Idan ma akwai ya dace ki sani kece me yara mata baki daya, gara Rabi tana da Lukman, Harirah tana da Sharif ke fa? Babu ko daya sai Yara mata, kuma kin san koda yau gwanjon kayan ba'are aka yi kasonku bai wuce kason Aryan ba, kai ina ba ma zai kai kason Aryan ba. Duk da yadda muka yi dake na cewa zaki tsayawa Sajjid a wurin sai gashi har aka tashi baki yi kome ba, yanzu zaki zo kice min wani abu." Tana gama fadar haka, ta mike tana me barin Hajiya Fauziya a wurin. A hankali ta fita ta bar gidan, tana me jin takaici me yasa Majid ya dawo daidai wannan lokacin.

Alhaji Haladu.

Tunda ya shiga yake safa da marwa, kana ganinshi kasan lissafi ya kwace masa. Matarshi kuma me bashi shawara ta musamman ta zauna tana kallonshi. "Abban Afiyyah ban ga dalilin d'aga hankalin nan naka ba, ai ja da baya sai raggo, taya zamu zuba idanu Sa'adatu ta ci bulus bayan ka manta a caca aka ciyo ta."

Cikin takaici ya zuba mata idanu, ya ce mata "taya zan manta bayan dan uwana ya ciyo ta ne a caca,a lokacin da yake ƙishirwar d'a namiji a lokacin ya saka kudinshi aka ci kawunta."
Murmushi tayi tana kara jin haka shine abinda take bukata,bata kaunar Sa'adatu ta cigaba, amma dole haka zata hakura.
Shigowar Hajiya Fauziya kamar an watsota daga sama, yasa baki dayansu suka razana. "Ke lafiya?" "Ina lafiya kuwa." Ta fada tana gyara zama, "ya zamu yi Haladu?"
Gyara zama yayi ya ce mata. "ya kuwa zamu ban da mu nime wata hanyar?"
"Kamar ya wata hanyar?"
Gyara zama yayi yana faɗin. "Dole zamu marawa Tani baya, sai mu san me za ayi kuma."
"Kana ganin marawa Tani baya shine mafita?" Inji Hajiya Turai Matarshi. "Eh mana shine mafita, domin ita ba zata watsar da ra'ayinmu ba"
Dariya tayi tana faɗin. "Lallai fa, tow Tani itama hanyar niman shiga take kan dukiyar Yaran Sa'adatu, idan kuka mara mata baya zata iya juya muku baya, idan kuka nime naku na kanku kowa zai kasance a ankare. "
Shiru suka yi kafin kuma suka ce mata. "Bamu fahimci inda kika dosa ba?" A hankali ta gyara zamanta ta warware musu fahimtarta, sannan ta kara musu kwarin gwiwa da cewa dole su kasance masu mika kai domin idan baka iya kama barawo ba tow shi zai kama ka."
Nan suka yi na'am da shawara ta, har Hajiya Fauziya ta fita, Hajiya Turai ta cewa Mijinta. "Bari na gaya maka gaskiya, matar nan munafuka ce ka sani nima kuma na sani, so abin da zan gaya maka. Zata tafi wurin Hajiya Tani da zancen nan, kai ka fara kiran tani ka gaya mata abin da ka yanke. Sai na gaya maka yadda zamu yi"
Ai kuwa kamar yadda ta fada haka ya kira Tani, ya gaya mata kome da kuma yankar bayan da Hajiya Fauziya ta mata, sannan suka dauki laifin kacokan suka daura mata, ita ce ta kawo musu zancen a shiga malamai. Jin shi Hajiya Tani take, sai da ya gama ta ce mishi. "Zan duba al'amarin"
Ta kashe wayar, murmushi Hajiya Turai tayi ta ce mishi. "Ka shirya zuwa bayan Magariba ka tafi gidan Hajiya Sa'adatu ka yi sulhu da ita. Idan ta lalace maka anan a can zaka fita"
Kurawa Matarshi idanu yayi tunda yake bai tab'a zata shaidaniya ce har haka ba. Take ya sake murmushi yana faɗin. "Lallai Hajiya ke duniya ce."

Murmushi tayi tana faɗin "taya ba zan kasance haka ba, ina tare da dai ga makiya sun rufa maka baya ta ko ina, ai lahu a gare ni na tsaya maka, don haka kada ka ji kome mijina."
***
Wurin karfe biyar na yamma Hajiya Sa'adatu tana kan abin sallah, tana lazimi Nabeeha matar Aryan ta shigo hannunta dauke da katon tire, bayan ta Aryan ne dauke da Kwando, "Assalamu alaikum Barka da maraice Hajajju." Sallamewa tayi tana kallonsu fuskarta dauke da murmushi ta ce musu. "Amin wa'alaikumus Salam, barkanku mutanen kirki." Gyara zama tayi tana faɗin. "Nawa ne ko na Hammanku?"
Dariya sukayi. "Hajiya naki da nashi ne, muka ce bari a kawo mishi, duk da ban gaya mata da wuri ba." " Hajiya kinji ba yaki gaya min zai tawo da hamma kawai sai gashi nan yazo da zancen akwai bako." Nabeeha ta faɗa tana tura baki. "Baka kyauta ba, maza jeka dakinshi ka taso min shi."
"Tow Hajiya." Haka ya fita zuwa dakin Majid din da yake kwance, ya lullube kanshi da mayafi, dakin ya bada wani irin duhu. Kunna wutar dakin Aryan yayi, ya hango shi zaune ya jingina da allon gadon. Amma kanshi a lullube yake. "Baka da lafiya ne?"
Janye lulluben yayi yana kallon Aryan. Dauke kai yayi yana me sake lullube kanshi. "Kazo falon Hajiya da yake sama Please."
"Me zan yi?" A yanayin rayuwarshi matukar ba'a wurin aiki ba,baka tab'a ganin fara'arshi, tashi yayi ya sauka daga gadon ya nufi ban daki. Sai da ya gama uzurinshi

ya fito ya saka hula a kanshi ya fita. Zuwa falon hajiya domin sun fito daga ɗakinta, yana shiga ya same su a kan kafet sun baza abinci. "Matar Aryan ce ta maka abinci."

"Nagode sosai!" Ya fada yana gyara zamanshi a kafet ɗin, Aryan ya zuba mishi yana jan shi da hira. "Amma shirun da Hajiya Tani tayi babu magana a kasa?" "Allah yana sane kuma yafi mu sanin abinda yake zukatansu."

Inji Hajiya, tana cin abincin itama don ta lura Majid yaki cin ko loma daya ne, har yau yana shakkar cin abincin kowa, domin rufawa rayuwarshi asiri yasa ban da girkin Hajiya kai ko tea bai yadda ya ci wani abu daga wani wurin ba. Shi yasa a duniyarshi yake shakkar kaidin mace. Saboda kaf duniya babu wanda yasan cewa sanadin jinyar Mahaifinsu guba ce. A hankali ya tura abincin yana murmushi. "Bana son abincin da aka saka citta da tarfarnuwa, domin ina da allergy."

Sanin ba zai ci bane Aryan yayi maza y kare dan uwanshi. "Wayyo kayi hakuri, na manta na gayawa pretty baka cin citta da tarfarnuwa." Murmushi yayi ya mike, karshe abincin da bai ci ba kenan. Kuma ai Hajiya tasan ba zai ci ba. Ita tana ganin har yau Majid bai warke ba, pretend yake kamar mai lafiya amma a zahirin gaskiya bai da lafiya. Shi yasa take son yayi aure ko zai samu wacce zata jure matsalarshi,

"Kiyi hakuri haka yake, baya cin citta da tarfarnuwa ne, tun yana Yaro." Itama Hajiya ta fadi haka, shi kuwa gogan naku yana shiga dakin drower yaja ya Ciro kudi me yawan gaske, ya fito daga dakinshi kenan suka hadu da Amaan Mamman Ba'are,. Kallon kallo suka yiwa juna kafin kowa ya kame kanshi, akwai wannan rigimar na sako da sako, amma ita Hajiya bata taɓa kawowa al'amarin zai lalace har girman yaranta ba, a zahirin gaskiya tsanar da Amaan yakewa Majid tayi yawa da har sai da kowa yayi magana. Wani irin tsana ce irin na matukar na samu dama sai naga bayanka. Amma a bangaren Majid babu wannan tsanar kawai shi mutum ne da yasan ciwon kanshi da darajar kanshi,. Sannan bai kullaci Amaan har haka ba. Kamar yadda shi ya kullace shi, reni ne baya so kuma ya fahimci Amaan yana da reni da son abin duniya.

Kiyayyar tasu ta faro ne daga lokacin da Alhaji Mamman Ba'are, ya bar wasiyya akan cirewa kuri'arshi ya gadarwa Majid, sannan ko a halin jinya yadda Alhaji Mamman Ba'are yake ta rokon a nimo mishi Majid ya roke shi gafara kada ya mutu da hakkinshi ya kara tunzura dayawan mutanen dake jikinshi, bawan Allah nan har ya mutu da rokon a kira mishi Majid, don Allah ya yafe mishi.

Duk da akwai hakkin iyaye akan Yaransu, haka akwai hakkin Yara akan iyayensu, wannan al'amarin ya tab'a zuciyar kowa na jikin Mamman Ba'are musamman Hajiya Nana wacce idan taji yana cewa Majid ba zaka zo ba, Majid kana ina ne? Majid zan mutu ban ga fuskarka ba. Majid nasan na cuce ka, Majid kazo. Shi yasa bayan kome da ya warewa Majid, akwai wasu takardun da ya bawa abokinshi. Wanda babu wanda ya sani daga Hajiya sai Abokinshi Alhaji Abubakar Abzin, shima shahararren dan kasuwa ne da yake garin marad'i, kuma wani ikon Allah Alhaji Abubakar Abzin bai tab'a takowa zuwa Niamey ba, idan abubuwa suka shiga gaban Hajiya wurinshi take zuwa. Yanzu ma tunaninta kafin hutun Majid ya ƙare zata kai shi garin marad'i, su gana.

Wannan shine shirinta.

Sai da Majid ya jira Amaan ya shiga dakin, sannan shima ya shiga ya mikawa Hajiya kudin tare da mata magana da idanu, ta bawa Nabeeha. "Barka Hammayo." Inji Salaha matar Amaan, "Barka!" Ya fada a hankali, idan baka saka kunne ba, ba zaka ji me yace ba. Shigowar yara uku suna ihu, yasa shi juyawa. Sai wani guda daya da yake bakin kofar shiga falon Hajiya. "Appa kaga Shuraim ya dake mu ko?" Yaran suka nufi wurin Amaan, mikewa Amaan yayi tare da nufar Shuraim ɗin. Shima Aryan har zai mike Majid ya kalle shi, a fusace ya koma ya zauna yana kwafa. "Kai wato munafurcin da ka gada daga wurin wancan dan iskan Yaron shine zaka fara." Ya rike kunnen Yaron. Amadadin yaron ya fasa ihu, sai ga Amaan yana fasa ihu, babu wanda ya san me ya faru, sai yaron ne kawai ya san me ya faru. Daukarshi Majid yayi suka

fita. "Daada taka mishi kafa kayi ko?" Ya rad'a mishi a kunne. "A'a" "Daada Allah yana kona me karya inji Ummina." Dakinshi ya shiga da shi, ya Ciro katon kwalin chocolate, ya mika mishi sannan ya kara dauko dayar ya ce mishi. "muje!" Haka ya riko hannunshi har falon Hajiya suka koma, zama yayi ya kira sauran Yaran, Yaran Amaan dake duk mata ne, tasowa suka yi duk da harara su da Amaan yake, haka suka tawo wurin Majid ya ajiye su a gefensu. Sannna ya mikawa yar karamar yar Aryan hannu da sauri ta taso. Ya ajiye ta" Kai Ayyan ka sammata a naka, Anum da Widad zan basu anan."
"A baco na Yaya!" Injin yarinyar. "Bushrah!" Babanta ya daka mata tsawa. D'ago kai Majid yayi ya watsa mishi harara. "Tow shi kenan tunda baki son na Yaya Anum a san mata?" Gyada kai tayi, ya bude musu kwalin ya ciro chocolate din ta ce mishi. "Dada a bacon na Anunu." Ta maida hannunta baya. Hajiya kuwa me zata yi ban da dariya ta ce mishi. " Ai yadda ka bawa sa'anta kwali itama haka zaka dauko mata kwali domin bata yarda a raba kansu da yan uwanta."
"Uwata taso muje." Ya dauki su Anum ya zaunar dasu a saman kujerar ya dauki Bushrah har dakinshi ya dauko mata nata, tun da ya bata, ta fara bashi labarin da Allah ya gani bai fahimci Yaren ba, har suka isa falon, bashi labarin take.
"Ja'ira mara kunya, dole ki bashi labari anya takwara haka zamu yi dake."
"Jiya babu luwana dake, ban baki cokulet dina ba " ta zauna ta yaga kwalin. Ya zube dukka. "Dada ashe min!" Wato ya kwashe mata, "abawa jiya." Ai kuwa Hajiya ta wafta ta ce. "Sai dai kada abawa gobe, amma jiya kan zan sha."
Haka aka yi ta hira har wani lokaci kafin lokacin magariba tayi duk suka tashi zuwa Masallaci..
Sansanin gudun hijira

#thedambuje
[2/16, 9:24 PM] Cutie cutie pie: *BAKIN HAURE....□□*

{Greed for Money is the roots of all evils□}
Arewabooks:maidambu41
Wattpad:Mai_Dambu
Mallakar:Mai_Dambu
010
Sansanin Yan gudun hijira
Adamawan Kamaru.

Abu na farko da muka fara fuskanta a camp din, shine rashin matsuguni da kuma kayan amfani, wai a haka dai an kawo mu nan saboda akwai inda zamu zauna, sai dai tunda aka yasar damu a asibitin wanda ba laifi an gwada mana kulawa da duk wani abun da ya dace, sai dai kuma babu wanda ya kuma zuwa da zancen ga yadda zamu yi, kwanan mu goma duk da haka mun samu lafiya daidai gwargwado. Idan ka cire Nenne da Yakumbo lantana da kullum jininsu yake hawa. Ita kan Yakumbo idan ta zauna sai ajiyar zuciya tana kiran sunan Sa'idu. "Ayya ayya akan idanuna suka kashe min shi. Ko tausayin rai basu ji ba, suka kashe min Abubakar yaron da bai gama koshi da nono ba." Sai ta fashe da kuka, ita kan Nenne bata hummm bata hmmm, hasalima tsayuwa mai kyau bata iyawa, domin a bakin Munaisah nake ji wai an mata ɗinki ciki da waje, sakamakon yadda suka mata kaca-kaca. Ashe wani lokacin kuka ma rahama ce, har yau ina son nayi kuka amma ko da wasa ban zubda hawaye ba, sai dai idan na tuna mutuwar Baffa'm sai naji har zuciyata tana wani irin bugawa, can kuma naji kirjina yana min ciwo, dole sai na kwanta. Lokacin da likita yazo na gaya mishi, kura min idanu yayi kafin ya ce min.
"Kina son ki mutu ne da kuruciyarki? Me yasa kike tuna abin da ya faru?" Sunkuyar da kai nayi, ina wasa da yatsun hannuna. "Zan bada test a miki, kada ki sake na ga wani abu domin zan na miki allura kullum."

Murmushi nayi nace mishi. "Ni." "Ke ke! Meye?" "Ina son nayi kuka ne?" Kura min idanu yayi kafin ya ce min. "shi kuka yana zuwa ne idan lokacin bukatar shi yazo, lokaci na zuwa zaki yi kuka kin ji." Gyada mishi kai nayi, ina faɗin. "Nagode!" "Ba kome yar fillo!" Daga haka na fito daga office din, na fita daga cikin asibitin can harabar asibitin na nufa na tsaya ina shakar kamshin ƙasa, domin ina son na samu nutsuwa. Idan nace ina jin dadin rayuwa nayi karya, ko dariyar da nake a dole nake yin shi ba wai yana kaiwa zuciyata ba ne. "Nan kika fito?" Juyawa nayi na kalli Addah ko daga ina take oho. "Hmm!" Nace mata, gyara tsayuwa tayi domin itama har yanzu bata gama jin dadin jikinta ba. "Zahra babu wani abu ne, kin ga saboda Lantana da Matar Babanki anki sallamar mu, balle har mu samu damar barin asibitin nan."

Shiru nayi ina nazarin wace irin zuciya ce da Addah haka. "Naji Zulaihah tana cewa akwai wani abu a wurinki." Sai lokacin na samu zarafin mata magana. "Zuzu ba zata gaya miki akwai wani abu a hannuna ba, sai dai idan Munaisah ta gaya miki." Na fadi haka ina kallonta, sai kuma ta fara kame-kame. "Yauwa ashe." "Addah don Allah bana son damuwa, ki je kice ta baki kudin ki kyale ni."

"Hmmm! Ai kin san dai zuzunki ba zata tab'a bani wani abu ba." Ta fada tana hararata, na ga karfin hali a wurin Adda. Haka ta taso ni a gaba, har dakin da aka kwantar damu, na nufi wurin Zuzu nace mata. "Bani jakar nan" a hankali ta d'ago kai ta kalle ni, bari na gaya muku wani abu dukar da aka mana ya haifarwa Zuzu rashin ji da kunnenta daya. Bata ji sosai sai ka mata magana da karfi, ni kuma bana son na sabar mata da yawan magana da karfi. "Me zaki yi da shi?" Ta tambaye ni, tana kallon Addah da ta haɗe rai ita kada ma ta sakata a cikin lissafin ita ta turo ni. Itama kuwa Zuzun tawa haɗe rai tayi ta ce da ƙarfi. "Ban san inda yake ba." Tunda ta fadi haka nasan wallahi ba zata bada ba, kuma duk abin da za ayi sai dai ayi amma ba zata tab'a bada jakar ba. "Ai kin ga irinta, waye ya gaya miki ana mu'amala da irin Zulaihah da tana da jin ta ma ya aka kare balle ta rasa jin." Juyawa nayi na kalli Munaisah tana matsa kafar Nenne, Ummi tana kwance gefen Yakumbo. Ni daya ce bani da uwa anan, ita me uwar ma bata samu tausayi da jin kai ba. "Addah lalurar Zuzu ba siya tayi ba, sannan likitocin kwakwala da kunne sun ce zata dawo da jin ta kamar baya, matukar tana amsar magani, me yasa kike mata gorin ji? Idan tausayi da jin kai bai shiga tsakaninku ba, Addah kada tsangwama da hantara ya shiga tsakaninku domin wata rana ita ce zata tsaya miki."

Daga haka na koma wurin Munaisah na ce mata. "Ya jikin Nenne?" Idanunta da suka yi bullu-bullu sakamakon kukan da take yi ta ce min. "Jikin Nenne kara zafi yake, gashi yau bakiɗaya bata ko magana." Wani irin tausayi ne ya cika min zuciya, na ce mata. " Bari na je na ga Dr Moses!" Haka na fita, a hanya na hadu da Nurse rabeka, "yar fillo ina zaki?" "Yawwa Aunty Nurse zo ki duba min Mamanmu." Ba musu ta bi bayana har dakin mu, tana shiga ta fara dubata da sauransu. Kallona tayi ta ce min. "Yar fillo bari na kira Dr Moses!" Haka kuwa ta fita can sai ga su tare da wasu likitoci biyu, haka suka dubata sannan suka saka Nurse Rabeka da Nurse Ali suka dauketa a keken marasa lafiya aka fita da ita, haka muka bi bayansu. Har wani wuri can da aka rubuta ICU da manyan harufa. A wurin muka tsaya aka shiga da ita, tunda muka tsaya a wurin Munaisah ta fashe da kuka, kuka take tana faɗin."me yasa? Me yasa sai mu? An kashe mana iyayenmu, anci zarafin mu da iyayenmu, an kona mana dukiyarmu da muhallinmu me yasa gwamnati ta zama makauniya?" Rungumeta nayi, ina buga bayanta. "Zahrah Nenne kawai ta rage min sai ke, Zahrah idan wani abu ya samu Nenne ba zan tab'a yafewa Gwamnatin Nigeria ba, ko ina ka shiga kome mugun aikin da aka yi, zaka ji ance Fulani me yasa aka tsane mu? Kowa yasan bafulani daga kiwo sai sayar da madara yake, amma a yau duk wani aikin ta'addanci zaki ji sunan bafulani ni ne, me yasa Zahrah me muka yi? Zahrah bamu da yanci anan mu da bakin haure daya ne, babu tausayi, babu tausassawa, babu." Rufe mata baki nayi. "Kowane bawa da yadda rayuwa take zuwa mishi, idan muka kalli yadda tazo mana, sai mu amshe ta da hannu bibbiyu, kada mu zama masu son rai, shi Ubangiji bai tab'a jarabtar bawa akan baya sonshi ba, yana jarabtarshi ne gwargwadon karfin imaninshi. Ki cigaba da addu'a Allah ya bata lafiya.". Wato ko

Munaisah yar gata ce, tunda ga Mahaifiyarta a raye, ni fa? Gani a kasar su mahaifiyata, amma ban san ta inda zan fara nemanta ba. Haka na hadiyi tawa damuwar, domin ba lokacin bayyana tawa bace, haka na cigaba da zama da ita, domin Addah bata biyo mu ba, Zulaihah kuwa bata iya tafiya saboda kafarta da aka mata dauri. Ta samu tsagewar kashi, muna zaune a wurin har suka fito, mikewa nayi na nufe su. "Ya jikin Mamanmu?" "Da sauki!" Dr Moses ya faɗa, yana kallon yadda muke raba idanu. "zamu iya ganinta?" Girgiza min kai yayi yana faɗin. "tana ƙarƙashin kulawar computer ne." Sabon kuka Munaisah ta fashe da shi, tana rike kirjinta. "Wayyo Allah na, Wayyo Allah Nennena. Don Allah ku barni na ganta." Girgiza kai yayi yana faɗin. "zaku kanta amma ba yanzu ba, sai ko zuwa gobe."

Rufe bakina nayi, cikin rudani ina kallonshi. Ita kuwa Munaisah kuka take me tab'a rai, baki ɗaya na rasa ina zan saka kaina. "Yar fillo kada ki damu fa, zata ji sauki kawai an dora ta akan kulawar computer ne, ki cewa Fulani ta daina kuka haka. Nenne zata ji sauki." Gyada kai nayi, ina kallon Munaisah, haka suka tafi suka bar mu a wurin.

Dakyar naja ta muka koma dakinmu, sallah muka yi. Abincin da ake rabawa na asibitin aka kawo mana, ban iya cin ko loma daya ba, haka Munaisah itama bata iya ci ba. Muna idar da sallar Isha, na mike xan fita Munaisah ma ta biyo ni haka Zulaihah ma ta ce mana. "Ku jira ni." Ummi da take jikin Yakumbo ta ce mana. "Zahrah akwai maganar da Yakumbo tace zata gaya miki don Allah." Kallonsu Zuzu nayi nace musu. "Kuje ina zuwa." Zuwa nayi na zauna a gefen Yakumbo. "Gani Yakumbo!"
"Zahra'u!" "Na'am!" Ga Ummi nan na baki amanarta. Ta shiga lallubar hannuna, kallon Ummi nayi da ta dauke kai, tana share hawayen da yake zuba mata. "Sis yaushe yakumbo ta daina gani." Murmushin karfin hali tayi ta ce min. "Zahra'u, don Allah ki taimaka min ki maida Ummi Yola wurin Dan Malam, ina tsoron kada na mutu rayuwar Ummi ta lalace." Wato sai na rasa ya zan kwatanta halin da nake ciki, shin zan fadi ne na mutu ko kuma zan fita ne nace a bude zuciyata a ciro min shi a rage damuwar mutane da yake cike a bar min tawa. Ajiyar zuciya na sauke sannan na rike hannunta. "In sha Allah, zan cika alkawarin da na daukar miki." Itama rike hannuna tayi da kyau ta ce min "Ki yafewa Nenne, don Allah ki yafe mana, don Allah ki yafe mana ko zamu samu rahamar Allah." A wannan lokacin ina son nayi kuka ko zan rage nauyin da yake zuciyata, amma ina zuciyata sai kara zafi take tana kara taurarewa, ina ga ba mamaki an sauya min zuciyata daga tsoka zuwa dutse. A hankali na zubawa Yakumbo idanu. "Duk abinda ya wuce ya wuce abar shi har a wurin Ubangiji ya wuce."

Na fada ina kokarin barin dakin, "Kina nufin kin yafe mana?" "Har a gaban Ubangiji bana fatar haka ya tsayar damu a kan wannan abin, na yafe maku." "Ki bari na gaya miki abin da muka aikata mana!" Juyawa nayi na koma wurinta, na saka hannu na rufe mata bakinta. "Nace na yafe, kuma ko kin gaya min ba zai sauya kome ba, sai ma lalata kome da zai yi. Ina fatan nima Ubangiji ya yafe min laifin da nayi mishi ya rufa min asiri, ba ya tona min ba. Yakumbo abar maganar Allah ya baku lafiya."

Rike hannuna tayi tana faɗin. "Lallai Allah ya albarkaci rayuwar Aminatu a duk inda take, ta haifi daya tamkar da dubu. Zahra'u Alfarma daya zaki min, ina son na mutu a wurin dan Malam." Kallonsu nayi kafin nace mata. "Yakumbo in sha Allah za a maidake wurinshi." Daga haka na fita, ICU na nufa, a hanya na tsaya tare da jingina da bango,na rasa me ke min dadi, sai da nayi nazari kafin na wuce wurin su Zuzu. "Sai yanzu?" "Eh!" Na fada ina me zama a gefen Munaisah. "Zuzu Yakumbo tana son komawa gida, ko muma mu koma ne?" Gyada kai tayi kafin ta ce min. "idan mun koma wurin waye zamu zauna?"
"Wurin Ya Dan Malam mana!" Na fada mata, ina kallon reaction ɗinta. "Hmm! Shima nima yake, ba laifi idan kin saka su Yakumbo a motar, amma har ga Allah na yafe Nigeria, domin nasan sun kashe min har mahaifina." Ta fada tana kallon kofar icu ɗin. Kaina a kasa ban kuma magana ba, har dare ya fara yi na riko hannun Munaisah. "Sister taso muje." "A haka xan bar Nenne a nan? Idan wani abu ya same ta fa."

Girgiza kai nayi sannan na riko hannunta, "Muje babu abinda zai faru, in sha Allah." Daga haka muka juya zuwa dakin mu, dukkansu sun kwanta nice kawai nake zaune, ga Addah da bata zama haka kawai ta tsiro da yawo, ina zaune a wurin har wani lokaci na tashi na shiga ban daki nayi alola na fito na shimfida dan kwallin kaina na fara sallah.

Sallar nafilla nayi ta jerawa, ina rokon Allah ya yafewa iyayenmu da suka rigamu zuwa gareshi, ya musu rahama. Ni kuma Allah ya bayyana min mahaifiyata. Su Nenne kuma Allah ya basu lafiya. Haka na cigaba da sallah har wurin karfe biyu, a lokacin Addah ta shigo. Gadonta ta nufa ta kwanta. "Addah ke daya ce me lafiya a tsakaninsu Yakumbo, amma Addah kin ki bamu lokacinki sai ki tafi yawo ba zaki dawo ba, sai dare ya raba."

"Tow Zahrah sai ki rufe ni da duka, dake an ce miki yawon banza nake tafiya ba."

Ban kara ce mata uffan ba, ina jin Zuzu tana kwafa, idan na fahimta idanunta biyu. Kawai ba zata yi magana ba ne, haka na kwana, kusan kamar nurse domin ina jikin Munaisah ina kula da Yakumbo. Wannan al'amarin ba karamin tab'a rayuwata da lafiyata yake ba, da gari ya waye bayan mun yi sallar asuba, sai ga wasu mutane uku, biyu maza daya mace. "Zamu mai daku sansanin gudun hijira ne, domin mun samu labarin yadda wasunku suke fita yawon dare." Dukkanmu Addah muka zubawa idanu. Matar nan tayi mirsisi da idanunta, ta nuna ni. "Ga yar iskar da take bin maza, nayi fadar nayi maganar na gaji." Wato wani irin razana muka shiga, domin babu wanda ya kawo Addah zata iya min sharri, ni kuwa banyi mamaki ba, domin fiye da haka idan akace zata min wallahi zan yarda, matukar Hajiya Addah ce kaɗan da aikinta, amma kuma abin da tab'a rai.

"Tow koma waye, zamu tafi da ku." "Addah ki fara gina wutarki kafin ki tafi lahira." Inji Zuzu, sake bude baki tayi zata kara magana. Na rufe mata baki saboda ko Munaisah da muke tare itama bata ce kome ba, hakan yasa na gane ni ce bare a cikinsu, dukkansu abu daya ne. Haka na shiga haɗa kayanmu. "Muna jiranku."

"Ranki shi dade, akwai yar Uwata da bata da lafiya an kaita ICU ko zan zauna a jikinta?"

"Ba zaki zauna a jikin kowa ba, domin kuwa kika zauna a nan ba jinyar zaki yi ba, yawonki zaki shiga yi." Inji Zuzu. Haka suka fita, ko ya aka yi sai ga Nurse Ali da Rabeka. "Yar fillo, ga wannan katin yanzu na amsa miki keda yar Uwarki. Koda zaku fito daga camp zuwa nan tow ku tabbatar kun rike wannan katin, sannan Fulani zata tsaya tunda Mamarta ce, ke idan an jima yayi sai kizo ki canjeta. inji Doctor Moses."

Ba alfahari ba, haduwa da mutanen kwarai a jinina yake, duk inda na shiga sai na hadu da mutanen arziki, haka muka fito baki ɗaya, a lokacin da zamu bar Asibitin Dr Moses yaga Yakumbo ya dubata da kyau, sannan ya bamu magani akan muna bata idan ya kare muzo da ita taga likita. Gyada mishi kai nayi, muka tafi inda Nenne take, dake zamu bar Munaisah a wurin. Rike hannunta nayi. "Don Allah ki kula kin ji." Gyada min kai tayi, ban san wani irin zuciya nake da shi ba, ni fa bana iya rike ka idan kayi min, ina ji a raina babu amfanin rike mutum araina domin haka ba zai amfane ni da kome ba, sai ciwon rai.

Ni kuma bana son hassada da kyashi ya shiga, zuciyata saboda kai.

Haka muka isa camp din, cikin wani irin yanayi, muna isa Office din shugaban da yake kula da camp din aka kai mu, aka saka sunanmu, da inda muka fito da dalilin fitowarmu. Ana gamawa muka fito daga office din, Mutanen da suka kawo mu, suka raka mu har wani tanti, shiga muka yi baki dayanmu. Ba laifi cikin a rufe yake kasar kuma an lailaye shi da leda, alamar waɗanda suka zauna a cikin tantin suna da tsafta. Zubewa muka yi, daya matar ta ce min. "Fillo zamu je ki fara dauko muku kayan shimfidarku." Gyada kai nayi, muka fita da ita,haka nayi ta jido kayanmu. Har da kayan Abincin. Cikin sakin fuska matar ta ce min. "Akwai kayan abinci ku nawa ne?" "Mu bakwai ne." Na fada a sanyayye. "To shi kenan kai kayan ki dawo."

"Amma me yasa za a bamu danyen abinci?" Murmushi tayi tace min. "Danyen abinci shine zamu iya baku, idan muka ce dafaffe ne, a wurin bayarwa aka fara dambe sai an zubda abinciin baki daya."
"Subhanalillahi!" Na fada ina ɗaukar katifa da ta daura min, har tantin mu ga nisa. Ina kaiwa na kuma juyowa zan koma muka hadu da wata yarinya. Itama budurwa ce. "Barka mai kyau!"
Murmushi nayi mata sannan na ce mata. "Ai kema mai kyau ce." Juya idanu tayi, "Hmm!" Ai ban tsaya bin nata ba, na wuce abina domin ina da abin yi. Tass na kwaso kayan har da kayan abinci, ina tsaye ina haki Zuzu ta ce min. "Yanzu ya zamu yi idan aka fara ruwan sama?" Juyawa nayi na kalleta. "Kamar ya?" "Wurin girki. "Ok na fahimta. Kamar an wurgo ta,ta shigo cikin ba sallama. "Batun girki kuke? Akwai inda ake sayar da itaccen da gawayi, har gas akwai me sayarwa." Ta fada tana rangwad'i da yauki. Da fulatanci Zuzu ta ce min "Zahra a ina kuka kwaso mana Zee yauki?"
"Ande!" Ita kuwa sai yauki take, wato ko Allah ya shirya zuzu. "Dukkanku masu kyau ne, wow." "Yanzu ya zamu yi kenan mu sayi gawayi kawai domin zai fi gas din nan, ko?" Na tambayi Zuzu. "Tow ya zamu yi da kudin nan na naija ne da" "ai duk suna amsa, kasancewar garin nan yana kusa da boda, zaku iya sayayyarku da shima."
"Mun gode amma meye sunanki?" ."Aina'u suna na!" Gyada kai mukayi, muna kallonta kafin Zuzu ta ce . "Kina da kyau!" Ai kuwa kamar an kunna radiyo, ta fara zuba. "Zahra'u dauke kawarki ta rakaki, ku nimo mana abinda zamu ci bamu isa da surutun ta ba." Inji Addah ta faɗa da fulatanci, haka na jata muka tafi har inda zamu sayi kome,, dake a cikin kayan da aka bamu har da kayan miyar gwangwani kifin gwangwani, da sauran tarkacen irinsu garin kunu, shinkafar ci da ta tuwo garin madara, burabisko, mangyad'a da man ja, magi ma ban tab'a ganin irinshi ba, sai a wurinsu, haka muka siya har da tukunyar hannu da kwanuka. Anan wurin take cewa. "idan ba zaku yi amfani da kayanku ba, ku bamu zamu baku kuɗi." Murmushi nayi mata nace mata. "Bamu koshin da zamu sayar da abinci ba, ki jira idan mun koshi zamu kawo mu sayar."
.....
08130269641
Mai_Dambu
[2/16, 9:24 PM] Cutie cutie pie: *BAKIN HAURE....□□*

{Greed for Money is the roots of all evils□}
Arewabooks:maidambu41
Wattpad:Mai_Dambu
Mallakar:Mai_Dambu
011
Bige hannuna Aina'u tayi cikin rangwad'a ta ce min. "Ba a fadar haka, Uwar mugu bata lamuntar cika baki" sannan ta kalli matar cikin fara'a ta ce mata. "Uwar mugu muna neman yafiyarki domin bakuwa ce daga Nijeriya bata san kome akan gurin nan ba." Murmushi matar tayi tana kallona cikin wani irin kallo kafin ta juya ga Aina'u tana murmushi ta ce mata. "Ya sunanta?" Cikin kad'adi irin na wanda ya saba ta ce mata. "Zahra!" Rike baki Uwar mugu tayi tana cewa. "Mai Babbar suna kenan, kun ga uwata takaina, maza ku je babu komai ai Uwata ce bata laifi."
Aina'u kamar ta zube kasa, tayi ta godiya har da cewa. "In sha Allah zaki same ta mai biyayya." Idanunta kyam a kaina, ni kuwa ko dar ban ji ba, domin matar asalima kawai bata kwanta min a rai ba, haka muka bar wurin ko inda take ban kuma kalla ba, babbar mace ce amma yanayinta zaka kalla kasan bata da mutunci. "Amma matar nan bata da mutunci ko?" Da sauri Aina'u ta rufe min baki, ta juya tana kara gaida matar, wacce da na juya na kalleta ni take kallo."Uwar mugu bata da matsala, kuma bata da abokin tarayya a cikin sansanin gudun hijirar nan, mace ce da tasan kan duniya idan taso zata iya janyowa a Kore ki, ko kuma a kwace muku kayan abinci. Tana da Yaro ɗaya baya cikin sansanin nan, yana tafiya farauta ne, sai dare ya ke

shigowa. Matar tana da matuƙar hatsari idan ka nuna mata kai ma dan duniya ne, idan kuma ka bita a hankali zata iya sakawa kowa ya kaunace ka, idan ka nuna mata baka da mutunci zata iya sakawa a tsane ka. Uwar mugu mace ce da take hada mutum da mutane masu arziki na wajen nan. Nima ba karamin arziki na samu a ta sanadinta ba."

Ware idanu nayi na kalli Aina'u, "yanzu Aina'u harkokin bin maza ta dauraki a kai?" Murmushi tayi irin bai dame ta ba, ta ce min. "Kai ji wata magana sai kace wani saɓo nayi, ai wannan rayuwar idan baka iya d'aga kafa ba, ba zaka huta ba, abincin da aka baku kin zata zai kai wata ne? Bari ki ji, daga zarar kun kai sati biyu nan ne idanku zai raina fata." Baki daya naji hankalina ya tashi, bamu rabu da bukar ba an haifi Habu, wato mun yi gudun gara mun tadda zago. Ban kuma magana ba, haka dai na barta tayi ta surutu domin ban san me take fada ba, haka muka isa, na ajiye kayan na shiga daki na samu wata mata suna ta hira. "Laaa Mamata itama tazo kenan." Ta shigo, "Tumba!" Ta kira sunanta. "Na'am Aina'u." Zama tayi a jikinta tana murmushi. "Kin samu kawa daga zuwa kenan?" Mamar ta tambayeta. Juya idanu tayi tana faɗin. "Eh Tumba." "Dama Yarki ce?" Gyara zama tayi tana murmushi ta ce mata. "Y'ata ce, na tafi Saudiya na barta ina dawowa rikicin boko haram ya koro mu nan Kamaru." Shiru tayi kanta na kasa kafin ta ce. "Sai da muka yi kwana talatin a hannun Yan boko haram, suna gana mana azaba, ga cin zarafi da fyade." Ta rungume Aina'u, itama yarinyar k'amk'ame Mamarta tayi, alamar har yau idan suka tuno abin yana musu zafi da ciwo. "Sun ci zarafinmu." Mikewa nayi na fita waje, kallon sama nayi domin bana son hawayen da ya taru a idanuwa na su zubo. "ku shiga da kayan ciki domin za a sace." D'ago kai nayi muka yi ido biyu da shi. Security ne domin naga sanye yaƙe da Uniform. "Tow!" Nace mishi. Na shiga da kayan cikin tantin mu, "Aina'u a ina zan samo ruwa?" Mikewa zumbur tayi tana faɗin. "Muje!" Ta dauki daya daga cikin langar da ta sani na saya. Muka fito ban ga mutumin ba, haka muka ratsa ta dakinsu, da mutane a ciki. Guga ta dauka, dakin ban da warin sigari baka jin kome. Kafin ta dauki gugar daya daga cikin mazan dakin ya fisgota. Tana dariya ta ce mishi. "Meye haka, Faruq?" Da sauri nayi baya, na tsaya a waje, ina jin mazan dakin suna ta dariya, har da ita ganin xata bata min lokaci na juya na bar wurin, haka kawai naji jikina yana bani kamar ana bina, juyawa nayi naga mutumin dazun ne. Mutanen da na gani a dakin suma irin kayan jikinsu ɗaya, tsayawa nayi naga ko zai wuce, abin mamaki sai naga ya tsaya. A hankali wani sabon tsoro ya kamani na juya . "Me kake so?" ."raka ki kawai zan yi, don naga kina da nutsuwa. " Ya tawo ya amshi bokitin hannuna, yayi gaba ina bayanshi, har bakin inda zamu d'ibi ruwan.

Kallona yayi ya ce min."Idan muka karasa wurin zaki iya ganin maza suna wanka, zaki iya ganin su babu kaya?" Sunkuyar da kai nayi na juya bayana, ilahirin jikina rawa yake, "bana fatan kara ganin wani babu kaya" na juya kamar zan fashe da kuka. Abin da ya faru yana dawo min, a hankali naji kirjina yana min ciwo, ban san tafiyarshi ba, sai ga shi nan dauke da bokitin da jarkar ruwan, haka muka tawo, ina share hawayen da yake zuba min. "Idan zaki dauki shawarata, ki hakura da tarayya da yarinyar nan, sannan idan dare yayi ki kula da kanki da yan uwanki."
"Wani abu yana faruwa ne?" Murmushi yayi irin wanda yafi kuka ciwo, ya ce min."ki kula da kanki." Sai lokacin na hango Aina'u tana rungume da wani mutumin. Tana hango ni ta ture shi, ta iso wurina. "Balali meye haɗinka da Kawata?" Bai tanka mata ba, ya saka ni gaba muka wuce ta, shiru tayi har taga wucewar mu, sannan ta biyo mu, a bakin kofar tantin mu, muka hadu da Zuzu ta fito da wutar tana gani na, ta ce. "Zahra'u hala kin mai damu kazar turawa zaki saka mana wuta a daki?" Murmushi nayi nace mata. "matar Babban sakataren gwamnati yi hakuri bari na mai da shi waje, kada ki narke domin da kitse aka yi ki " na ajiye ruwan ina kallonshi. "Na gode Yayana " na fadi haka ina jin kwalla yana cika min idanu. "Ni ne da godiya, amma bana son yaya nan". Zuba ruwa a tunkuyar zuzu tayi, tana faɗin. "Love at first sight!" "Yes haka ne, yar uwa." Ita kan aikinta ta cigaba da yi, dakyar na sallame shi ya tafi.

Yana tafiya Aina'u tana zuwa. "Zahrah kin ga mutumin nan dan iska ne, kada ki bashi fuska." Kallonta nayi na wasu dakikai, kafin na ce mata. "Na gode." Tow me zance mata? Ni dai nasan idan karuwanci bai zama abincina ba, ba zai tab'a zame min guba ba, tunda mutanen da suke zagaye da ni kusan ƙaddararsu ta haɗa da wannan sana'ar.

Ganin naki kulata, ta ja ta zauna domin na fahimci abincin take bukata, don haka Zuzu tayi uwa tayi makarbiya, ta tsaya kan abincin, ganin nima bani da katabus akan abincin ta koma tantinsu, domin yadda Zuzu ta haɗe rai ko ni a dakile take amsa min magana, don haka tana gama abincin, ta zuba kwanon asibiti sannan ta zuba mana a wani kwano, muka hadu har da Addah muka ci. Alhamdulillahi ba laifi mun tashi komad'a, sallah muka yi, sannan na shirya tare da kwanon abincin ni da Zuzu muka nufi Asibitin, ba a hana mu fita ba, amma sai da muka bi kofar uwar mugu, haka Balali ya gaya min ya ce na gaya mata zamu tafi asibiti. Lokacin da muka isa tantinta wanda yafi na kowa kyau, domin kamar gida yake, buga mata kofa muka yi, ta ce. "Waye?" "Zahra'u ce." "Shigo abinki!" Bude kofar nayi na tura kaina da sallama, dakin sai warin wiwi yake, durkusawa nayi na ce mata. "zamu tafi duba Mamana a asibiti ni sai gobe zan dawo, yayata zata dawo da yar Uwata."

"Ai naji labarin Yadikonki ce, mahaifiyarki yar kasar nan ce, baki son a nima miki ita ne?" Idanuna ne suka cika da kwalla muryata a sanyayye na ce mata. "ba a bukata, waɗanda suke wani hali nake son su samu lafiya tukun nan."

"Sai kin dawo, ga abinci ko zaki ci." Da sauri na ce mata. "A'a na gode!" Na mike na fito, Zuzu da Balali suna waje, ina fitowa ya kalle ni. " Me yasa kace mu gaya mata?" "Domin ina son ki samu kusanci da ita, yadda babu me iya tunkararki da mugun nufi, idan har kika iya kiyaye abin da bata so, cinnaka bai isa ya cijeki bata saka an ga bayanshi ba."

"Amma ya naji ɗakinta yana warin wiwi?" Murmushi yayi yana faɗin, "muje zaki fahimci wani abu nan gaba." Da muka fito mun haɗu da wasu zafafan motoci guda biyar, mutanen da suke jikin motar dauke suke da manyan bindigu. "Tambayarki ga amsarta." Shiru nayi ban san dame zan lissafa abinda nake son ganewa ba, haka muka isa bakin hanya ya saka mu a mota, ya dawo. "Zahrah bayan tafiyarki diban ruwa, matar nan dai Addah ta bata labarin mu, sannan ta amince zata shiga sana'arta."

"Yanzu don Allah ita Addah meye abin burgewa a wannan sana'ar? Gaskiya gara na mutu da nayi wannan sana'ar." Murmushin takaici tayi ta ce mata. "gara ke, kina da taurin kai, ni Addah tana cewa zata tsine min nake amincewa. Ki godewa Allah babu wani mai mugun nufi a rayuwarki." Ta fada tana kuka, rike hannunta nayi ina faɗin. "Ya isa haka!" Itama rike hannuna tayi tana wani irin kuka, wanda na fahimci ba kukan abin da yake faruwa damu ba ne, akwai wani abu a ranta. "Zahra'u Alfarma nake nima daya tal?" Rike hannunta nayi, hannuna ta ja cikin rigarta, ta daura a saman cikinta. A razane na cire hannun ina toshe baki. "Idan ya rayu, zan so ki rike a matsayin naki don Allah bana son ya bata min gobe na. Idan na mutu ki rike shi har abada." Wani irin rawa jikina ya dauka, ban taɓa kawowa a raina haka zai faru da Zuzu ba, "Me yasa kika bukaci haka?" "Babu wanda ya sani sai ke, don Allah." A daidai isar mu asibitin, sauka nayi na bashi canjin da Balali ya bamu. Koda muka isa asibitin Munaisah tayi kuka har ta godewa Allah. Tana ganinmu ta faɗa jikina, tana kuka tana faɗin. "tun tafiyarku sai tashi abin yake ana ta niman wanda zai nimo ki, tana son ganinki." Bubbuga bayanta nayi, na ce mata. "Ya isa!" Dakyar ta daina kuka na ajiye mata abinci, ta fara ci zata cire hannu na cigaba da bata, tana ci tana kallona. "Kiyi hakuri.!" Ta ce min, ni na saba da wannan kalmar bata wani hana ni sakat, haka ta ci abincin sosai, sannan na tafi inda zan sauya kayana, na nufi dakin da Yadikko take, an zuba mata na'ura kanta da kirjinta. Ina zuwa na rike hannunta. Kafin na shafa kanta bude idanu tayi tana kallona. Hawaye ne yake zuba mata, ta rike hannuna da babu kome. Ina murmushin karfin hali nace mata. "In sha Allah zaki tashi kin ji Nenne na, zaki tashi da kafarki da karfinki."

Kallona kawai take har na wani lokaci, kafin Munaisah da Zuzu suka shigo. Kallonmu tayi tana kallonmu bakidaya, "bari na rakasu," na janye rikon da tayi min, na tafi na rakasu. "Balali yana jiranku zai kai ku har har tantin in sha Allah."

"Tow shi kenan!" Haka suka hau mota na dawo dakin Nenne, ina rike da hannunta, tunda ta bude idanu ta ganni, ta lumshe idanunta, wato ko? Wannan yanayin Allah kadai yake da ikon jarabtarka a zauna lafiya. Nenne tana cikin wani irin yanayi, domin kuwa tasan kai ne akanta amma babu bakin magana. Can kuma zuzu ta fado min a rai. *Yaushe tayi cikin?* Wannan shi ne tambayar da nayiwa kaina, kuma nasan bani da me bani amsar sai ita, haka yasa nayi shiru, ina nazarin wannan al'amarin da tashin hankali yaƙe. Kwana nayi a zaune ban rintsa ba, ina sakawa da kwancewa, sannan Zuzu ta bani abin cikinta. Ashe Uwa tana kyauta da d'anta tun kafin ya shaki iskar Yanci? Amma me yasa Zuzu tayi haka? Me yasa tayi shiru bata fada ba? Ko tana tsoron kada Addah ta ce ta zubar ne?[1] tunda haka ya tab'a faruwa da Shamsiyah tasa dole sai da ta zubar da cikin hankalinta ya kwanta. Ajiyar zuciya na sauke idan har Addah zata iya sakawa a zubda na bare tabbas zama bai kama ni ba, dole mu bawa cikin kariya. Ajiyar zuciya na sauke ina jin kamar na sauke rabin damuwar da yake damuna. Kiran sallah ya fahimtar dani ashe kwana zaune nayi.
Haka na fito zuwa Masallaci, acan nayi sallar asuba, sannan na koma ciki.

Karfe tara da rabi, sai ga likitocin da suke dubata. Suka gama dubata sannan suka fito babu wanda ya ce min kome, bayan tafiyarsu ne Zuzu ta kawo mana abincin,"Ina Munaisah? Kina fama da kanki zaki zo nan?" Murmushi tayi tace min. "Kuma sai na zauna kowa yasan ina da Yaron ciki?" Gyara zama nayi na fara cin abincin da kunun da ta kawo min. Ina sha ina kallonta, "Zahrah don Allah bar kallona haka." Sai na dauke kai kamar ban ji me ta ce ba, na cigaba da cin abincin na. "me yasa baki gaya min kina da ciki ba?" "Saboda kin koya min kome ya same ni, na adana shi sirrina ne ba na kowa da kowa ba, har kwanan gobe baki gaya min yadda aka yi kika samu yankar cikin ba, amma na tayaki boye mutumin da kuka kwanta gado daya a asibiti. Addah tasan da wannan zancen ai sunanki." Murmushi nayi ina kallonta. "Zuzu kenan, kina tsammanin wani hujja ce don na ki gaya miki yadda aka yi na yanke a cikina? Ban sanshi ba, ban san yadda aka yi ya taimaka min ba, ban kuma San me yasa ya yanke ni ba, abu daya na sani Allah ya kubutar da ni daga hannun Azzalumi ne ya wurga ni rayuwarshi. Haka ya ishe ki ko kina buƙatar wani karin bayanin?"

"Shi mutumin da ya kwanta dake a dakin asibiti fa?" Kura mata idanu nayi, baki daya sai naji abincin ya fita kaina. Na rufe a hankali nace mata. "Ki raya duk abinda yake ranki haka shine daidai." Na fada mata ina murmushin takaici. Mikewa nayi ina karkade hannuna. "Zahra'u kina boye min abubuwa dayawa, sai dai nice uwar baki uwar magana, nayi ta gaya miki sirrina." "Me kike so nayi miki? Ni nasan ban boye miki kome ba, kuma iya gaskiyar kenan na gaya miki me kike so bayan haka?" Shiru tayi tana kallona, kafin tayi kasa da murya ta ce min. "Ina wannan lokacin da muka hadu da wani dan Yola ya zo seminar?" Gyad'a mata kai nayi, a ranar da ya zo cin tuwo ya roke ni na bishi, koda muka je bai yarda mun wuce masaukinshi ba, tambaya ta yayi asibiti muka je, a daren ya kai ni wurin likita aka duba lafiyata, da nashi domin yace baya son yayi mu'amala da macen da take dauke da wata lalura shi asalima Haihuwa yake nima, Allah ya bai bashi ba. Kuma yana da mata huɗu babu wacce Allah ya nufeta da haihuwa. Bayan an gama mana ne muka wuce masauki, kusan dukkan kwanakin da muka yi da shi. Ba zan iya mantawa ba, duk da sabon Allah ne amma kuma abubuwan da suka faru ba masu mantawa bane, bayan ya gama kwanakin shi zai tafi ne ya bani number shi akan idan wani abu ya taso na gaya mishi sannan ya roke ni da cewa kada na bi wani namiji na tsawon wata uku. Ban tab'a haduwa da wanda yake zuba min kuɗi kamar hauka irinshi ba, haka nayi ta bawa Addah kudi ina tafiya na kwana a hotel gudun kada tace na bi wani namijin, wata biyu da tafiyarshi ne na fahimci ina da ciki, na tura mishi sakon da kwanaki da test da aka min, kin san wani ikon Allah sakon ya same shi dai-dai zai bar kasa ne,

amma a ranar ya turo min kuɗi da duk wani abun bikata, ya kuma roke ni naje gida na gayawa Baffa zai zo niman aurena. Tun lokacin na rasa yadda zan gayawa Addah, har cikin ya shiga wata hudu,ina boye mata kwatsam sai ga abin da ya faru nan muka tawo jenuwa, ashe Allah bai nufa zamu sake ganawa da shi ba ne." Ta fada cikin wani irin kuka, kasa magana nayi ina kallonta, kafin na d'ago kai....

#Thedambuje
[2/16, 9:24 PM] Cutie cutie pie: *BAƘIN HAURE....□□*

{Greed for Money is the roots of all evils□}
Arewabooks:maidambu41
Wattpad:Mai_Dambu
Mallakar:Mai_Dambu
012

Wani lokaci kana iya ganin abu amma don a zauna lafiya zaka iya makancesa sai a zauna lafiya, ba tare da an cutar da juna ba. Kusan hakan ne ya faru idan da ace na d'ago kai na kalli abinda Addah take min sai nace hakkina ya kama Zuzu amma idan na duba yadda itama zuzun Addah ba kyaleta tayi ba, sai naga ashe ba kome bane don tayi min wani abin, tunda 'yar da ta haifa ma bata kyale ba. Irinsu Addah a cikin al'umma masifa ce matukar zaka nemo kudi tow bata da matsala da kai, kaunarta da kudi yasa bata jin ko dar, zata iya aikata kome matukar zata samu kuɗi, babu abinda ya dame ta. "Kin yi shiru!" Ta faɗa tana share kwallar da yake zubo mata. "Tow Zully me zance? Ina ga a gayawa Addah maganar cikin ki, domin bana son na samu matsala da Addah."

Mikewa tayi kamar maganar da nayi ya bata haushi, ta juya zata bar wurin na sha gabanta."Ban fadi haka saboda na b'ata miki rai ba, amma idan kin ji haushi kiyi hakuri kin ji " hawaye ne ya zubo mata, tana min wani irin kallo me cike da tausayi, tsarguwa nayi na juya baya. "Zan mutu ne?"
"Ki min alƙawarin ba zaki barshi yayi maraici ba." Rufe mata baki nayi ina faɗin. "Kina saka zuciyata wani irin bugawa, don Allah ki rufa min asiri, bani da kowa sai ke." Cire hannuna tayi ta daura bisa cikin ta ce min. "Sai wannan kina da wannan, in sha Allah zan zauna a gefenki." Komawa muka yi wurin zaman muka zauna. "Me yasa ranar da Baffa zai baki addu'a baki gaya mishi ba?" Hawaye ya zubo mata, ta share tana faɗin. "idan na gaya mishi zai tsani yar uwarshi a tsarina bana son a tsane ta da wuri, na fison sai na mutu za a tsane..." Rufe mata baki nayi ina faɗin. "Duk lalacewarta mahaifiyarki ce, kada don abin da take yasa zaki so duniya ta zage ta, kiyi hakuri wata rana sai labari."
Kamar zata ce wani abu sai kuma tayi shiru, "kin ci abinci ma kuwa?" "Na koshi!" "A'a Maman Unborn zauna kici idan bai isheki ba, a karo miki." "Ni fruit nake so." Shafa fuskata nayi, sannan na juya na fita kasancewar gari ne masu yalwar ya'yan itace, ban sha wuya ba asalima ina zuwa wurin na samu Doctor Andrew zai saya sai ya biya mana kudin, duk da ban so ba, amma haka na amsa ina mishi godiya, na kawo mata, yadda take yasa na zuba mata idanu. Da alamu ranta yana son ya'yan itacen domin yadda take ci kamar tana ci da wani. Murmushi nayi nace mata. "My heart yana son abincin da kike ci." Girgza kai tayi tana faɗin. "Mace ce!" "Are you sure?" Gyad'a kai tayi tana faɗin. "Na rasa ma me zance, ke bakya tsoron wani abu ya faru ne?" Dariya nayi tare da mika na ce mata. "Bana tsoron kome, yaushe Munaisah zata zo, barci nake ji bakidaya jikina ciwo yaƙe."

"Zata zo maybe sai yamma!" Numfashi na sauke, tare da cewa. "Ai kuwa da ta min bidi'a domin wallahi barci nake ji." Karbar zancen tayi tana faɗin. "Eh tow Allah yasa ta zo ɗin." Haka muka cigaba da zama har rana tayi, hakura da abincin da ta kawo min nayi na barta ta ci, dama kuma Zuzu bata da ciki ma, ci gareta kamar gara balle kuma an samu kari, haka yasa nake yawan kallonta domin burge ni take, muna zaune

sai ga Nurse Ali da takeaway, ya mika min yana faɗin. "InJi Doctor Moses." "Kace mishi Allah ya saka da alkhairi."

"Zai ji!" Ya zubawa Zuzu idanu, kafin ya ce mata. "Me yasa baki fara awo ba?" Dauke kai tayi tana faɗin. "Bana bukata." Mai da hankalin shi kaina yayi ya ce min. "Ki mata magana wallahi bata kula da kanta balle cikin jikinta. Na tsani taurin kai idan ma baki son cikin waye ya aike ki wurin uban cikin?" Yadda yake masifa sai duk muka zuba mishi idanu, can na harbo jirgin shi.

"Tow kayi hakuri!" Kura mata idanu yayi, yaga ta dauke takeaway da ya kawo tana ci, juyawa yayi ya bar wurin. "Dan iska da kugu kamar na sauro, ya wani tsaya kamar ubana yana min masifa, bai san takaicin da yake bani ba, wai ya tsaya sai masifa yake daga ganin shi nan ba wani kuzari ne da shi ba, a gado." Rufe mata baki nayi ina faɗin. "Don Allah ban da yasasshiyar magana domin ina da ajiya a jikinki." Ture hannuna tayi. "bana son bu....." Maza na danne bakin. "Tarbiyya daga ciki ake farawa, yanzu ne lokacin da zaki fara dora mishi tarbiyyar da kike so, don Allah ban da zagi ko fushi."

Kura min idanu tayi, "yanzu duk abin da nayi sai ya ɗauka?"

"In sha Allah!"

"Tow ya zan yi?"

"Ki yawaita ambaton Allah da azkar, yawan addu'a zai taimaka wurin haihuwar salihar mace." "Ban sani ba ko zamu gana da Babyn don Allah kada ki bari addah ta rab'e ta. Domin kuwa tana rab'arta yarinyar zata tashi a matsayin karuwa." Ta fada idanunta jawur.

***

Sansanin Yan gudun hijira.

Kallon Addah Uwar mugu tayi, tana kara kallon sauran yan matan. Murmushi tayi ta ce musu. "Ni Zahrah nake so, domin har na gayawa mutane na samun sabuwar yankan rake." Gyara zama Addah tayi tana kallon Uwar mugu, cikin tsananin takaici ta ce mata. "Yarinyata Zulaihah zata iya abin da kike so." Girgiza kai tayi tana faɗin. "Dukkansu sun san maza, sana'ata akwai hatsari ina son yarinyar da maza basu bude mata idanu da kofa ba ne, don haka." "Idan ma sayar Zulaihah zaki yi zan sayar miki da ita." A razane su Ummi da Munaisah suka kalli Addah. Baki sake tare da son tabbatarwa shin Addah ce ko ba ita ba ce. "zan sayar miki da ita, suma ki ɗauke su a aikin." Hadiye yawu Ummi tayi tana faɗin. "A'a ni dai na tuba." Zabga mata mari Addah tayi sai da ta durkushe. "Idan har zan sayar da diyar cikina dan Ubanki gaya min me zan yi da ku? Don haka babu fashi."

"Ni dai na amince."

Kallonsu Uwar mugu tayi ta ce mata. "Tow kada ku damu, ku koma an jima za a azo a duba lafiyarku,domin sana'ar mu bama son kasada a cikinta. Sannan daga nan.har sauran iyakokin mutanen mu ne, kuma a cikin gidan nan kowa na wane, naji kince kin tuba ko?" Ta nuna Ummi, sannan ta saki murmushi, "ba zan miki dole sai kin shiga ba, amma mahaifiyarki ko kuma shi kenan."

Jikin Ummi ne ya dauki wani irin rawa, tare da zubewa a wurin tana me rarrafawa har gaban Uwar mugu. "Na amince, don Allah kada wani abu ya same ta." Ta fada tana kuka. Shigowar da aka yi yasa duk suka mike banda Ummi da take durkushe tana kuka, "Hajajju a ina kika samo flowers masu kyau haka!" Ya fada yana gyara zaman facemask din fuskarshi.

"Sannu da zuwa ranka shi dade." Sannan ta juya tana kallon Addah . "Ke ki tafi ki bar su." Juyawa Addah tayi, ta bar su a wurin. "Hajajju a taimaka min nayi wanka, ina son tausa."

"An gama!" Ta kalli Munaisah domin ta lura Allah ya daura mata itama son abin duniya. "Ki shige cikin dakin nan akwai duk abin da ake bukata ban da musu." Gyada kai tayi tana faɗin. "Tow!" "Ke !" Ya kira ta, tashi tayi ya kalli Uwar mugu da take tsaye. "Bana son naga kyawawan mata na kuka, Hajajju ki ce tayi shiru.". "kinji kiyi shiru" dunkule hannun yayi yana bubbaga kafadarshi. "Kafata ciwo yake min, ko zaki

min tausa." Kallon Uwar mugu da take tsaye tayi ta mata alama, da sauri ta mike ta nufi kafadarshi. "Yallabai da akwai wani abu ne?"
"Dilla ya arce da kayan dawa." Ya fada yana daura kafarshi a saman stool din da ta ajiye mishi. "Garin k'ak'a naga dai har da Giwaye a dawa."
"Ambaliyar ruwa aka yi, kusan kowa yasan yadda ruwan yayi barna ba kowa yake iya tsira zuwa tudu ba."
"Amma kuwa dilla har ya manta yadda kura ta kawo mishi cabka ya tsere."
"Magana ake miki ta ambaliyar ruwa." "Eh kuma haka ne, gaskiya ba kowa yake tsira daga ambaliyar ruwa ba, sai wanda Allah ya so ceta." Kallonta yayi yana kara nazarin yadda take tsaye, "duk wani sansani nasan inda yake zuwa, amma ban same shi ba. Hajajju kece kawai nasan akwai alaƙar wasa da dariya a tsakaninku." Wani ware idanu tayi tana dafe kirji. "Na shiga uku." Ta zube a kan gwiwarta. "Don Allah ka rufa min asiri." Lumshe gajiyayyun idanunshi yayi yana kara jin wani irin gajiya me tattare da kasala cikin wani yanayi me dauke da sanyi ya ce mata. "Na gaya miki, ta inda aka hau ta nan za a sauka matukar nayi idanu biyu da shi, tow lahira zata yi bako." Ya fada daidai fitowar Munaisah daga dakin. "An gama hada maka ruwan."
Inji Uwar Mugu, "Hmm! Ina aina'u?" "Bata san zaka zo ba" ta bashi amsa muryarta na rawa, mikewa yayi a hankali yana kallon Yan matan ya ce musu. "Su waɗan nan daga ina suke?"
"Hmmm! Yan gudun hijira ne!" "Yayi kyau, amma ina da rani ga damina ya gangamo ban san yadda zan yi ba, domin ina tsoron kada kwarin wake su bata min ruwa."
"Hmmm! Ina ga matukar sanyi da tsawa bazasu b'ata maka ba, mai zai hana ayi aurensu zuwa bad'i da damina sai a haife su."
"Hajjaju ba zai sai bad'i da damina ba. A k'ak'ar bana ma matukar yan matan nan suna da hankali sai mu game da su."
"Mai zai hana? Kyawawan mata ai abin so ne."
"Eh amma ba dukkansu ba, akwai wacce kai kanka kasan ba a yi ta don tsalle ba, anyi ta ne domin adana a cikin gida. Idan na wannan tabbas daukar ta zan yi na kaita wata duniyar ta rayu domin ni da Yarana." Cikin murmushi ta ce mishi. "Akwai irin flower da na ajiye maka, amma nasan zaka bukata ka je kayi wanka."
Mikewa yayi yana tangad'i. Har dakin yana rike da hannunsu har bandakin, hawaye ke zuba daga idanun Ummi domin ita bata ga wani cigaba daga wannan kazamar rayuwar ba, haka suka mishi wanka tsaf sannan suka dauki towel da suka ga a cikin wardrobe.
"Ku nawa ne kuka zo sansanin nan? Ba a min karya." Ya faɗa yana kallon Ummi da take share hawayenta, a hankali ta bashi labarin su nawa ne. "Ina sauran yan matan?" "Suna asibiti." Ta bashi amsa tana share hawayen. "Dukkanku karuwa kenan?" Girgiza kai tayi ta ce. "A'a iyayen mu ba karuwa ba ne, Yayar mahaifinmu ce, sai Zahrah itama bata taɓa yadda da kowa ba. Bata son sana'ar."
Murmushi yayi yana kallon yadda take kuka, "Gaya min yanzu mene yasa kike kuka?" "Mahaifiyata ba lafiya, sannan ta ce kada na kara aikata wani abu. Wallahi na tuba."
Ta fada tana zubewa akan gwiwarta. Shiru yayi sannan ya ce mata. "Yanzu ita Mamanki tana nan kenan?" Ya kalli Munaisah da take tsaye. "Eh!" Mikewa yayi, cikakken namiji me Kyakyawar sura, ya dauki mayafinshi ya lullube mata kai, ya kalle ta sosai. "Kina ji na!" Ya faɗa yana kallon Munaisah. "Kada naji ko na gani, domin idan aka ci amanata ina iya kashe mutum. Da munafuki gara barawo." Ya fada mata yana tab'a kanta," jeki babu wanda zai dakatar dake." Da sauri ta juya zata fita, ya ce mata. "baki ji ba, ki nutsu sosai." Gyada kai tayi tana fita, a hankali ya budewa Munaisah hannu."ke ina Mamanki." "Tana asibiti da Zahrah da Zulaihah." Shafa bayanta yayi ya ce mata. "Me yasa baki je ba." Sake shiga jikinshi tayi tana k'amk'ame shi, domin tun wanda aka mata a rikicin jenuwa bata kara hada hanya da namiji ba, amma ganin Bako yasa baki daya tana jin kamar ta cinye shi.
"Kina nan mahaifiyarki tana tare da yar uwarki!" A hankali take lasar kirjinshi zuwa wuyarshi. "Ina girmama uwa me yasa?"

Bakinta ta kai habbarshi, tana wani lasar bakin kamar ta samu alewa, a hankali ya kunce towel din kugunshi ya d'auketa suka faɗa gadon, gefen gadon ya kai hannunshi ya ciro golden ring a cikin aljuhun wandonshi. Yana romancing da ita yana kara saka kayanshi, yana gama sakawa cak ya d'auketa ya dora ta, bisa bishiyar dogon Yaronshi.

Hannunshi dukkan biyu a kirjinta, ita kuwa sai aikin gaske take, ko tunawa da abinda ya faru bata yi ba, damuwarta kawai taji namiji a jikinta. Shi kuwa sai da ya kure mata lissafi domin ya jima shima bai hadu da Shaidaniyar yarinya irinta ba, don haka sun jima suna cinye juna.
---A lokacin da Ummi tazo fita kallonta uwar mugu tayi,tana son tayi magana amma sai tayi shiru, har ta bar wurin Uwar mugun ta wuce tantinsu, da sauri sauri. Tana isa ta cusa kai kenan, idanunta ya sauka akan Addah zata shake mata uwa, da wani karfi ta bangaje Addah ta fadi can. Ta shiga dukarta kamar Allah ya aikota.

Dake yarinya ce kuma da sauran kuruciya a tare da ita, da kuma a fusace take da Addah haka ta rufe idanunta tayi ta dukar Addah. Ganin da gaske zata kashe ta yasa ta saka ihu da kururuwa tana niman ceto. Amma ina zuciyar Ummi ta kai iya wuya, domin ta gama sarewa matukar basu nan Addah kashe mata uwa zata yi, tunda ta iya sayar da Yarta Uban waye ba zata kawar don cimma manufarta ba, Ihun Addah yasa mutane suka farga aka kawo mata dauki. "Ke ba Babarki ba ce!" Aka shiga d'aga ta dakyar. "Da wannan ta haife ni gara ban zo duniya ba, in sha Allah Addah mushe sai yafi ki daraja." Ta fada tana kuka me ciwo, ta d'ago kai tana kallon yadda kowa yake bata laifi. "Wannan da haihuwarki gara b'arinki, sam baki cancanci zama uwa ba, Allah ya isa tsakanina da ke, Addah In sha Allah lahiranki sai tafi duniyarki muni." Ta fada cikin kuka domin bata san wani level zata ajiye Addah ba, domin matar bata buƙatar addu'a sai Addu'ar iftila'i da masifa da jafa'i. Sai da Uwar Mugu ta shigo ta zubawa Addah idanu. Kafin ta ce. "Me ya had'aki da ita?"
"Eyeee! Hmm kawai don."
"Karya take zuwa nayi ma same ta, zata kashe min Yakumbo." Harara Uwar mugu ta watsa mata tana faɗin. "Ka da na kuma jin makamancin haka."
"Naji Hajiya haka ba zai kuma faruwa ba," inji Addah da kumburaren bakinta, kallon Ummi tayi ta ce mata. "Kema wannan ya zama na karshe ki kula da Mamanki. A wannan duniyar mutane na iya kome saboda kuɗi kiyi tunani dakyau...
#money
#evilalive
#trueordare
#mai_dambuje
[2/16, 9:24 PM] Cutie cutie pie: *BAƘIN HAURE....□□*

{Greed for Money is the roots of all evils□}
Arewabooks:maidambu41
Wattpad:Mai_Dambu
Mallakar:Mai_Dambu

Ni ban san me Adda tayi aka tsane ba, salon ku saka mata ido da baki ta lalace 😹😫□□□ da alamu Adda tana girgiza ku😹 mutuniyar kirki saura ku ji ban dadi 😫😹□

_____
```Assalamu alaikum barkanmu da warhaka da fatan kuna cikin koshin lafiya, karku manta da wannan Kamfani mai albarka mai kawo muku kayan bukata cikin sauki da Aminci da Inganci.
Wato TA RASULU MULTIPURPOSE. YA SAKE DAWO MUKU DA KAYAN NAN MASU ARMASHI DA DANDANON KOWACCE MACE TAURARUWA CE.

_____
```

MARKADADDIYAR GYAD'A
HADADDEN KAYAN SHAYI
GARIN KOSAI NA TAFI DA GIDANKA.
GARIN TUWO
GARIN KUNU YAR ASALI
CURRY ME DADI
SPICES
TYME
YAJIN DADDAWA ME KYAU
GARIN DAN WAKE
JAN YAJI MAI DAD'I...

_____
BUGU DA KARI MUN TANADAR MUKU DA KAYAN FITAR SALLAH DA NA SHAGALIN SUNA DA BUKUKUWA.
ATAMFOFI, LESHINA, MATERIAL, SHADODDI, YADUDDUKA NA MAZA DA NA MATA, JAKKUNA DA TAKALMA.
WANI ABIN SAI KUN ZO TA RASULU MULTIPURPOSE DOMIN KASHE KWARKWATAN IDANU.
ZAKU IYA TUNTUƁARMU A WADANNAN NUMBOBIN.. 08086639163 - 09030168590....
MUNA DAKON SAYAN DAI-DAI KO SARI.....```

013

"Babu abin da kudi basu saka mutum ya aikata, rayuwar mahaifiyarki ko kuma ki wayi gari babu labarinta shine gaskiyar da zan gaya miki." Daga haka ta juya ga Addah, "Ba kowa yake da hakurin da zai ga kina shirin lalata mishi goben shi ya iya hakuri ba, don haka sai a kula." Daga haka ta fice a dakin, ita kuma Ummi ta koma gaban Mamanta, tana shafa fuskarta hawaye na zuba mata, a duniya idan akwai abin da ta tsana shi ne ka tab'a mata Yakumbo, haka yasa ta kece da kuka me ban tausayi, gani take kamar duk abin da ya faru Addah ce sababi domin da bata yi shawarar kawo Zahrah Taraba ba, da basu faɗa wannan bala'in ba, bakiɗaya ta tattara laifin kacokan ta aza bisa kan Addah, tsanarta da wani sabon kiyayyar Addah take ji, a hankali ta juya tana kallon Addah kafin ta ce mata. "In sha Allah sai na gayawa Zulaihah kin sayar da ita, sannan abinda baki sani ba, Zulaihah ciki ne da ita, don haka ki saka a ranki bakin ciki da goyon shege yana wuyarki. Mu dai duk lalacewar da muka yi bamu daukowa iyayenmu shege ba, kinci ribar bariki da hujja." Ta fada tana sakin wata dariya me daukar hankali ta cigaba da cewa. "Ni dake shege ka fasa, idan baki ga bayana ba, ni sai naga naki wallahil azim ki ajiye a ranki daga yau na fara farautar rayuwarki. Ba iya ke ba, hatta ta Zulaihah sai na saka ta tsane ki sama da yadda kike tsammani."

Cikin da Ummi ta faɗa mata, bai bata mamaki ba. Kamar yadda take ji take gani zata rasa Zulaihah. Murmushi tayi ta ce mata. "Ai ciki na san da shi, sai me? Kuma ki saka a ranki cikin ya kusan b'arewa matukar ina raye. Na gama magana sayar da ita zan yi idan ma suna sonta da cikin jikinta shi kenan, idan har zan sayar da d'iyar cikina Wacece ke da bazan iya cusawa a tashin hankali ba? bakya gaba na domin ina da abin da ya fiki daraja." Shigowar Munaisah ta kura musu idanu, "ba sai kin zuga Zulaihah ba, Addah sayar da ita kika yi ra?" Ta tambayi Addah dafe da goshinta, "Addah na zata duk abin da zamu yi miki akan kuɗi iyalinmu da mu kanmu mun tsira." Dariya Ummi tayi, ta ce mata. "Baki san wani abu ba, tow ina kallon lokacin da Addah ta danne Nenne har dai da ta shiga wannan halin."

Cakume wuyar Ummi Addah tayi. "Munafiki algunguma me nayi miki?" "Addah ba zamu kara miki biyayya ba ne, na gaya miki kuma sai na rabaki da duk me shirin yimiki biyayya." Ummi ta faɗa tana dariya. "Domin idan ta kashe iyayenmu,

bamu da kowa bayan ita, zata saka mu lallai mu amshi ƙaddarar da bata rubuce cikin littafin mu, wallahi ina gaya miki sai na ga bayanki"
"Ummi kina tsammanin don kin gaya min Addah tayi yunkurin kashe Nenne zan yi mamaki ne? A wannan takin ni kaina na samu damar zan kawar da Nenne domin matukar tana raye ba zan samu yadda nake so ba, don haka ki ajiye a ranki mutuwarta shi ne tashina."

Wani abu ne ya tsaya a ran Ummi wato, ita ta ma lura duk wanda ya zauna da Addah sai ya zama mara mutunci, fisabilillahi uwar da ta haife ka, zaka nuna bata da amfani a rayuwarka. Komawa jikin Yakumbo tayi, tana jin kamar ta goyata su gudu, domin kuwa tana hango rashin imaninsu kada ta matsa jikin Mamanta a kashe mata uwa. Tana jin yadda suke shewa da ihu, kudi suke kirgawa tun daga lokacin bata tashi a gaban Yakumbo ba, sai da taji sallamar Zalaihah. Sai lokacin kunya ta kamata, tabbas bata kyauta ba amma kuma babu wanda zai so a tab'a mishi uwa. Abin da ya fara fitowa bakin Zulaihah shi ne. "Addah hatsari kika yi ne?" Ta tambayi Addah hankalinta a tashe. Kallon Ummi Addah tayi, ta fashe da kuka tana nuna Ummi. "Ban gane ba, kina nuna Ummi gware kuka yi da ita?" Girgza kai tayi ta fara magana. "Kashi ta bani." Juyawa Zulaihah tayi ta kalli Ummi, bata ce mata kome ba, ta wuce ta zauna tana nishi. "Ashe dama zulai har zaki yi ciki ba zaki gaya min ba?" Da sauri ta kalli Ummi, eh Ummi tasan da cikin, kallon Addah tayi kafin ta ce mata. "Ina son cikina ne, domin ba don naci abinci na same shi ba, domin ina son Ubangiji ya gafarta min ta sanadin cikin."
"Shi yasa Uwar da ta haife ki, ta sayar da ke ba." Inji Ummi, sannan ta cigaba daga inda take cewa. "Babu wanda zai yarda yana ji yana gani don biyan bukatar wani a kashe mishi Uwa, kama wannan tsohuwar kilakin nayi zata kashe min mahaifiya, kuskure ne don na kare rayuwar Mahaifiyata? Nayi laifi kenan?" Girgza mata kai Zulaihah tayi, tana jin zuciyarta kamar zata buga, ta kalli Addah . Gyara zama Ummin ta kara yi ta ce mata. "Ta sayar da ke. Idan kina da yadda zaki yi kafin su bukaci ɗaukarki da cikin jikinki sai ki sani." Daga haka ta mike ta suri gwangwani. "Zan tafi sallah ga Yakumbo, idan wani abu ya same ta, Addah ce." Daga haka ta fita daga tantin, Zuzu kan bata ce kome ba,.domin kuwa tasan idan tayi magana ba mamaki zucuyarta ta buga, haka ta zauna shiru har Ummi ta dawo. "Ki duba tana raye?" Zuzu ta tambayeta.b'ata Yakumbo Ummi tayi ta cewa Zuzu. "Eh tana raye." A hankali ta juya ta fara sallah, tana idarwa ta fara addu'a a lokacin Munaisah da Addah suka fice a dakin, ita kuwa ta cigaba da musu munanan addu'a da tsinuwa. Duk wanda ya jefa rayuwarta cikin hatsari.

"Ya isa haka, kada garin fushi ki jefa rayuwarmu cikin tsinuwa. Tunda Yakumbo tana raye, ki saka idanu akanta. Kuskure daya kika min, na bayyana zancen cikin jikina ko Zahra sai yau na gaya mata. Addah kuwa ba zan yi mamaki ba, idan ta nuna bata san da zancen cikin ba, ai ba laifi ba ne, to amma kada ki kara min haka." Itama Ummin cikin kuka ta ce mata. "Wallahi na gaji ne da halin Addah, a can idan ta ce ta dauki nauyin mu da na iyayenmu ba laifi amma a wannan lokacin da muke, cikin tsaka me wuya ta ce zata saka mu, karuwanci ai babu kanta sannan haka bai ishe ta ba, sai da na kamata zata kashe min Uwa, gaya min Zalaihah me ya dace nayi?"
"Kare mahaifiyarki;" inji Zuzu, "Gaya min ta ina nayi kuskure? Akan addah wani irin bala'in rayuwa ne ban gani ba? Kafin na waye a harkan sai da aka zubda min ciki sau uku, ya take son nayi? A haka ta haɗa ni da mutumin da ya goga min infection da kyar na rabu da ciwon. Haka kawai sai ta nime kashe min uwa? Duk abin da nayi fama da shi addah bata bani kudin magani ba, ni daya nayi fama da kaina.

Allah ba zai tab'a barin addah ba, domin daga duniya zata ga sakamakon abinda ta aikata. Wallahi nayi dasananin abin da na aikata, Zuzu akan idonku aka keta alfarmar Mahaifiyata, aka keta nawa maza sun fi shida akan Yakumbo, Zuzu Gaya min har zan ji wani d'a namiji ya burge ni? Gaya min anya akwai adalci a cikin wannan yanayin?

Mahaifiyata fa suka lalatawa farinciki bayan sun kashe kannena da mahaifina da kowa nawa.

Zuzu me Addah take so nayi? Bayan na gama ganin masifa da idanuna zata bukaci na kara hada shimfida da wani d'a namiji, tsoro nake ji Zuzu ina tsoron Allah kada ya kona ni." Rungume juna suka yi. "Babu wanda zai kuma saka ki dole, koda bana nan kada ki gayawa Zahrah kome ki barta ta fahimci abinda ya faru da kanta, kada ki gaya mata don Allah."
"Wallahi ba zan iya ba, matukar na ganta cikin wani yanayi zan gaya mata. Amma zuzu me yasa kike gaya min haka?" Murmushi tayi tace mata. "Ba kome kawai dai na gaya miki ne kada ki gaya mata kome."
Suna zaune addah suka shigo da kayan ciye-ciye, itama Zuzu ledar da tazo da shi, ta bude suka ci abincin da Ummi. Sai da ta gama cin abincin, ta kalli Munaisah. "Ita baiwarki da kika bari a can Asibitin me kike nufi?" Kallon Addah tayi, tana son tayi magana amma ganin har lokacin Zuzu bata yi magana ba, yasa Addah kasa da kanta. "Zaki tashi ko sai naci Bu..... Ubanki." Inji Zuzu tana mikewa. "Doluwa jaka!" Mikewa Munaisah tayi kamar zata mutu, ta dauki kayanta. Itama zuzun ta mike tana bayan Munaisah, tana kare mata zagin kare dangi, har asibitin don masifa Zuzu ta kawo ta, ina zaune kamar wata mara galihu, sai ga su nan mikewa nayi ina kallon yadda Munaisah take share kwalla. Domin a duke zasu daku da Zuzu, amma kuma Zuzu irin mutanan ne masu matukar kwarjini domin yar bala'i ce.
"Meye na kuka?" "Rabu da shegiya ba zata zo ba, wai har tana kuka yar iska Uwarki ce, ba Uwarta ba."
Girgiza kai nayi na cewa Zuzu. "Tunda bata son zama ta koma, ke mu kwana dake." "Wallahi ba zata koma ba, idan ta koma ma wurin wani shegen zata kwana." Sake baki nayi ina kallonta, "wurin wani shegen zata kwana?" "Wallahi na rantse miki da Allah, kwana zata yi a wani wurin."
Mikewa nayi ina karkad'e jikina na ce mata. "Ok sai ki zauna. Ai kin san yadda ake kome ke muje!" Daga haka muka bar asibitin, raina yana b'aci. "Kin san Ummi da Addah sunyi faɗa?" "Ina zan sani, tunda ina asibiti."
Murmushi tayi tace min. "Hmmm! Allah abin tsoro rayuwa abin tsoro, yau wai Ummi ce take gaya min Addah ta sakata aiakata abubuwa masu kazanta, yanzu ta tuba ta bi Allah ba zata kuma bin maza ba, asalima tsoron mazan take "
"Alhamdulillahi Allah ya amshi addu'ata, akanta kenan, tunda gashi nan tana faɗin ta tuba."
Murmushin karfin hali tayi ta fara bani labarin yadda aka yi, ware idanu nayi ina mamakin yadda ta iya dauke kai kamar babu abinda ya faru. "Me yasa baki damu ba?" "Kawai ba zan tab'a damuwa ba, domin kare rayuwar Mahaifiyarta tayi, kuma ko kashe addah tayi bata da wani hukuncin." "Amma!" Rike hannuna tayi tana faɗin. "Addah tayi kurakurai, kada haka ya zama abin da zaki bi bayanta, barta da halinta bata ga kome ba." Ta fada tana sauke ajiyar zuciya.

Ban san me yasa haka yake faruwa ba, amma nasan Addah tana da kaso mafi girma na lalacewar rayuwar Ummi, lokacin da muka isa da Balali muka haɗu tunda ya ganni yake murna, sama sama na gaishe su, muka wuce koda muka isa kallona Ummi tayi ta ce mana."me yasa kuka bar ta a can Asibitin?." "Mahaifiyarta ce duk abinda ta gadama tayi, rayuwar Nenne yana hannunta, ta ce ko ta samu damar kawar da ita, zata yi ga damar nan na bata na dauko Zahrah da ta tare mata damar." Inji Zuzu tana dafa kafadana. "Ban gane ba?" "Ba zaki gane ba." Hadiye yawu nayi wato idan na fahimta akwai abin da ake boye min, kura musu idanu nayi da na fahimci basu son na fahimci kome, sai na zauna ina faɗin . "Yau baku mana abinci ba ne?"
"Tun tafiyarki jiya babu wanda ya kara abinci sai Zuzu." Inji Ummi, mikewa nayi na dauki sauran kayan abincin, na fara kokarin daurawa, sai ga Uwar Mugu da wasu matasa uku, kallonta nayi kafin na mike ina son nayi magana. "Ina Munaisah?" Tana asibiti wurin Mamarta. "Me yasa bata zo ta gaya min ba?" Daga ciki zuzu ta leko tana

faɗin. "Bata zo ba, domin can ya dace da ita ba nan ba." "Ke waye ya saka ki?" Daya saurayin zai shiga cikin tantin na tare shi, "wai meye haka ne?" Na tambaye ta. "Kyale su ku tawo da Aina'u " haka suka wuce ina kallonsu, juyowa Uwar mugu tayi tana kallona, fuskarta a sake. Ta bar wurin a can kuwa tana shiga dakinta, ta ce . "Yallabai yarinyar tana asibiti wurin jinyar Mamarta, amma na saka a kawo min Aina'u."

Gyad'a kai yayi yana kallon wayar hannunshi. "Me yasa bata gaya min Uwarta bata da lafiya ba?" "Afwa Yallabai."

Haka aka tawo da Aina'u da ta cab'a kwalliya kamar zata wurin gasar kyau.

★★★

Niamey. Niger republic

Familyn BA'ARE

Alhaji Muhammad Dan Ba'are, su ɗin dangi suke da Ibrahim Khalil Dan Ba'are (na cikin Bororoji) kakansu daya, kasancewar sun jima da barin agadaz, haka yasa su sai suke amfani da Ba'are zalla, yayin da Khalil yake amfani da Dan Ba'are.(zaku iya bincikar Bororoji duk da ban fito da nasabarsu ba, amma labarin BAƘIN HAURE da Bororoji yana da nasaba da juna)

Alhaji Muhammad Dan Ba'are, ya baro gida agadaz domin karatun addinin Muslunci, ba don kome ba sai don yadda Mahaifinsu yake fifita wasu ɓangaren na gidan da su, shine d'a na farko a gidan, sai Alhaji Ibrahim Dan Ba'are d'a na biyu, sai Hajiya Latifa, Mahaifiyar Mohan.

Kasancewar su dakinsu Ibrahim sun maida hankalinsu akan karatun boko, yayinda Mamman Ba'are yaki boko ko kadan, haka yasa shi ganin ai ana fifita yaran dakinsu Ibrahim, mahaifiyasu an maida ta kamar saniyar ware. Dalilin haka ya bar gida, ya tafi karatu a can ya hadu da wani abokanshi. Suka wuce kasar mali.

A can suka shiga harkar hako ma'adinai, har na tsawon shekaru biyu, ana haka wata rana, kasa ta rubta musu sai da suka kwashe wata goma sha huɗu, kafin aka fito dasu, a kasar nan shi daya ya rayu sun kai su goma sha takwas da suka shiga amma shi daya ya rayu, a lokacin da aka kai labarin Mutuwarshi, Nana sai da ta kwanta jinya da tsanar kishiyarta Hajiya Balaraba, da ganin kamar ita ta mata hanyar da d'anta ya mutu, gaba da kiyayya me zafi suka kara ruruwa a Familyn Dan Ba'are dalilin da yasa suka bar garin agadaz kenan.

Shi kuma a can ya rayu cikin amincin Allah, domin a tsawon watanni nan. A ramin nan da suke hako kuza, a nan yayi katarin haduwa da dutsen zinari, haka yayi ta hak'a, bai fasa ba Abinci sai beraye su yake kamawa ya buga gwal da kuza, wuta ta kama, ya gasa beran da ya kama. Ruwa yana samun shi ne ta wata jijiyar bishiya da ta ratsa karkashin kasa.

Haka yayi ta rayuwa, kwatsam sai ga shi ana tono, inda cikin hukuncin Allah aka tono da shi, ya tara dukiya me yawan gaske sannan aka fito dashi. Wannan abin ya bawa kowa mamaki, asibiti aka wuce da shi yayi sati biyu aka sallame shi, tare da kayanshi baki daya da ya hako a rami.

Aka dawo da shi Nijar, Aka karrama shi gwamnati ta bashi babban gida da fili anan Niamey. Sannan gwamnatin ƙasar ta nemi ya sayar mata da abinda ya zo da su, ya sayar da kadan domin ya gina dukiyarshi saboda kusan rayuwarshi ya saka a hatsari ya samo dukiyar nan.

Kad'an da ya sayar din nan, da ita ya cigaba da gina katafaren kamfanin zinari, har ya kuma haɗa gwiwa da kasar Mali ana shigo mishi da zinari, a lokacin bai wani karatun boko ba, amma kuma ya san kan lissafin kome, sai da ya samu shekaru uku da dawowarsa ya tafi ya nimo Danginshi. Ganinshi cikin wadata da nutsuwa yasa suka ta murna, har agadaz ya je domin an san ya mutu dole yaje ya nuna kanshi dan su san yana raye.

Yana zuwa Kanin mahaifiyar shi ya bashi auren Yarshi, Rabi duk da bai so ba amma haka ya amshi auren, domin yana niman macen da tayi karatun boko wacce zai ciccibeta ya dorata akan dukiyarsu, haka aka sha biki.

Tana shiga a burin shi tana fara haihuwar namiji, zai gina rayuwar yaron ta hanyar bashi ilimi me yawa da zai rike dukiyarsu. Sai dai kash tana fara haihuwa ta haifi mace, haka ya kara auro Fauziya itama tana shigowa mata ta fara haifa masa, haka ya hakura ya cigaba da kula da yaran da basu ilimi sai dai iyayen basu wani damu da ilimin ba, ana haka ya hadu da Harirah yar secondry haka yayi ta mata hidima, har ta gama itama dai ba wani abin kuzo ku gani ta yi ba,haka ya aureta.

Alhaji Mamman Ba'are, yana da wata dabi'a ita ce cacca, dake yana yawan shiga libya, a nan ya haɗu da Alhaji Nasiru Wodabbe shima rikakken dan cacca ne.

"Yau gidan nan yayi baki,ga Alhaji Nasiru Wodabbe gefe guda Alhaji Mamman Ba'are, yau wasan sai tafi koda yaushe armashi da karsashi" domin kowa yasan kowannensu gwani ne a harkar cacca.
"Idan nayi nasara akanka Ba'are me zaka bani?" Murmushi Mamman Ba'are yayi ya ce mishi. "Wodabbe idan kayi nasara a kaina, ka kwashe kome har da kayan jikina. Idan nayi nasara akanka kuwa zan bika har garin na dauke shanayenka!"

"Na yarda!" Inji Nasiru Wodabbe, shima kuma Mamman Ba'are ya ce mishi."na amince."
Aka shiga buga cacca kamar da wasa, Nasiru Wodabbe ya shiga nasara akan Mamman Ba'are, har dai da ya cinye shi kome hatta wandon jikinshi sai da ya saka a cacca. "Mamman Ba'are kwashe kayanka, idan ka haifu namiji ka saka kamfaninka " kurawa Alhaji Nasiru Wodabbe idanu yayi, kamar ya zagi Uwarshi. "Zan saka amma ka sani idan nayi nasara ba zan maka da wasa ba."

"Na amince," saka kamfanin yayi cikin murna da kwarewa Nasiru Wodabbe ya fara buga wasa, tun a zagaye na farko ya fahimci kamfanin Ba'are GOLDEN EMPIRES ba sa'ar sa bane, domin a wasan farko Ba'are ya dawo da kayanshi wasa na biyu ya dawo da kome hatta zobensa na azurfa sai da ya dawo da ita. Murmushin yaƙe yayi suka cigaba da wasa, aka cinye kome cikin takaici ya ce mishi. "Na saka yar Yayana Sa'adatu."
Shiru Mamman Ba'are yayi yana kallon Nasiru Wodabbe,"Me yasa baka saka yarka ba sai yar dan uwanka." "Da ina da Y'ar
ba zan saka Sa'adatu ba, domin darajarta tafi karfin dan cacca irinka,na gaya maka."
Tab'e baki Mamman Ba'are yayi yana dariya,"bari na gaya maka ko gwal ce da kanta, bata fi karfin dan cacca irina ba sai ma tausayinta da naji da ta samu Baffa irinka."
Cikin fushi Nasiru Wodabbe ya kara buga wasan hannunshi, cikin rashin sa'a ya fadi Mamman Ba'are yana bugawa sai gashi yayi Nasara, "Na sameta kana da wani abu da zaka fanshe ta?" Idanunshi ne ya kad'a jajjur. "Kai tsinanne yarinyar da babu ruwanta, yarinyar da gwamnati dauki nauyinta saboda kasancewarta hazika, me ilimin addini da na boko, shine zaka samu a banza ba zan baka ita ba, ni na sakata a cacca amma ka fara ketare ni kafin ka isa gare ta."
"Ba zan ketare ka ba, yadda ka saka ta a cacca haka zaka bani ita har da kome nata." Shi kanshi Alhaji Mamman Ba'are, bai tab'a zatan Allah zai bashi irin macen da yake so ba, sai da ya buga kamfanin shi na gwal a cacan sai gashi Allah ya bashi ita a lokacin da bai zata ba.

Kafin wani lokaci rikici ya barke a tsakaninsu, sai ga manyan maza da bawa hammata iska, dakyar aka raba su domin har jami'an tsaro sun shiga lamarin, Alhaji

Mamman Ba'are da yaga samu zai ga rashi ya daka tsalle ya ce ai ta zama tashi tunda wasa aka buga, wasa gaske dai yaki karbar kome ita Sa'a kawai yake so. Ganin haka yasa Alhaji Nasiru Wodabbe ya amince da shawarar da aka bashi a office din yan sanda aka daura auren Sa'adatu Aliyu Wodabbe da Alhaji Mamman Ba'are, a Office din yan sanda, da sadakinta aka bashi yana ji yana gani Alhaji Mamman Ba'are ya wuce tare da ɗaukar yan rakiya har gidan Nasiru Wodabbe, ganin kamar Mamman Ba'are bai da hankali yasa shi isa gidan kafin su isa, yana shiga kamar wanda aka wurgo shi, dama a Libya yake da zama da Matarshi da yar rokonshi. Sakamakon wani karamin abin da bai kai ya kawo ba, ya baro kasarshi.

"Sa'ade ki yafe min, na miki rashin adalci. Kiyi hakuri in sha Allah gobe zaki yi dariya." Ya fada yana dauke kanshi ya kalli Matarshi, Raliyah. "shiryata za a zo ɗaukarta na aurar da ita " "ka me?" Ta tambaye shi jikinta yana rawa. "Eh na gaya miki na aurar da ita, ina ga ai da Hausa na fada ba larabci ko fillanci ba."
"Amma me yasa? Kasan Lamido yana can yana jiranta."
"Haka Allah ya nufa ita ba matar shi ba ce." Ya dawo kan Sa'aden ya riko hannunta. "Kinsan ba zan tab'a cutar dake ba ko?" Gyada kai tayi kanta a sunkuye. "Tow kiyi hakuri kin ji." Ya fada yana Hadiye kukan da ya zo mishi, haka ya hada har da kome nata, ya tsaya Raliya ta shiryata.....
(Hmmmmmmmm ku bi alkalamin ƙaddara)
#Mai_Dambu
[2/16, 9:24 PM] Cutie cutie pie: *BAƘIN HAURE....□□*

{Greed for Money is the roots of all evils□}
Arewabooks:maidambu41
Wattpad:Mai_Dambu
Mallakar:Mai_Dambu

Assalamu alaikum barkanmu da warhaka da fatan kuna cikin koshin lafiya, karku manta da wannan Kamfani mai albarka mai kawo muku kayan bukata cikin sauki da Aminci da Inganci.
Wato TA RASULU MULTIPURPOSE. YA SAKE DAWO MUKU DA KAYAN NAN MASU ARMASHI DA DANDANON KOWACCE MACE TAURARUWA CE.

_____
MARKADADDIYAR GYAD'A
HADADDEN KAYAN SHAYI
GARIN KOSAI NA TAFI DA GIDANKA.
GARIN TUWO
GARIN KUNU YAR ASALI
CURRY ME DADI
SPICES
TYME
YAJIN DADDAWA ME KYAU
GARIN DAN WAKE
JAN YAJI MAI DAD'I...

_____
BUGU DA KARI MUN TANADAR MUKU DA KAYAN FITAR SALLAH DA NA SHAGALIN SUNA DA BUKUKUWA.
ATAMFOFI, LESHINA, MATERIAL, SHADODDI, YADUDDUKA NA MAZA DA NA MATA, JAKKUNA DA TAKALMA.
WANI ABIN SAI KUN ZO TA RASULU MULTIPURPOSE DOMIN KASHE KWARKWATAN IDANU.
ZAKU IYA TUNTUƁARMU A WADANNAN NUMBOBIN.. 08086639163 - 09030168590....
MUNA DAKON SAYAN DAI-DAI KO SARI.....

014
Tana fito da ita ya kalli yarinyar, kafin ya riko hannunta har waje. Ya ja Alhaji Mamman Ba'are gefe. "Gata nan, ka da ka duba lalacewar da nayi ka hukunta ta da shi, wallahi billahil azim mahaifinta shahararren Malami ne kuma attajiri ne, soyayyar da take min tun tana yarinya yasa ni tawowa da ita yawon bariki, Sa'adatu bata rasa kome ba, hatta abinda zata ci Ubanta ya tanada mata, wallahi rashin ji ya sani fitowa da ita, Ba'are don Allah kada ka cutar da ita babu ruwanta."

Duk da zuciyarshi ta motsa akan yadda ya mishi da farko amma kuma yadda yake gaya mishi inda yarinyar ta fito sai yake ganin kamar bai mata adalci ba, amma halin Nasiru Wodabbe yasa shi jin ko kad'an baya tausayin yarinyar domin baki daya bata wuce shekaru goma sha shida ba, haka ya kad'e babbar rigarshi ya ce mishi. "Nasiha kake min ko me? Ka sani babu abinda ya dame ni, daga yau har zuwa ranar da zan gama amfani da ita a caca na ciyo ta."

"Na roke ka kada ka cutar da ita, don Allah. Ita bata maka kome ba ni nayi laifi." Ya fada yana niman durkusa mishi. "Abbati kada ka durkusa mishi, Indai akaina ne wallahi bana tsoron duk abinda zai faru kuma bana fatan naga hawayenka. Duk abinda kayi a kaina Abbati daya ne, ba zaka tab'a cutar dani ba." Cikin wani irin tashin hankali ya riko hannunta. "Ba zaki fahimci me na aikata ba, sai dai duk rintsi kada ki manta da Allah." "Ke muje, na gaji da wannan wasan kwaikwayon naku, sai kace uban wani ne yasaka shi saka ki a caca." Haka Alhaji Mamman Ba'are ya sako ta a gaba har inda motarshi take. A lokacin yana da wani aboki wanda suka taso tun suna agadaz daga baya shi da iyayenshi suka koma marad'i da zama. Wato Alhaji Abubakar Abzin.

Duk da shi yayi karatun boko, can marad'i yayi tunanin kai Sa'adatu domin a can zata fi sakewa. Haka kuwa ya faru domin daga Libya kai tsaye marad'i ya wuce da ita, a lokacin da Alhaji Abubakar Abzin ya ganshi da ita, ya sha mamaki amma sai ya nuna ba wani abu bane, domin yasan kulafuncin niman haihuwar d'a Namiji da yake, bai kai burin shi na niman mace mai ilimi ba, sai gashi ya samo yarinya karama me ilimi da nutsuwa.

Bayan sun kebe da Alhaji Mamman ya labarta mishi duk abinda ya faru. Sannan ya mika mishi takardunta, ya duba sosai ya ce mishi. "Kai ne dan boko, duba min ta ina yarinyar nan zata tayani rike kamfani na?" Ya tambaye shi yana leken takardar.
Gyaran murya yayi kafin ya ce mishi. "Yarinyar bata da matsalar kome, sai dai tana da fahimta ta bangaren kimiyya, idan da a zabinta zaka tambaya ba zai wuce ta ce zata karanci likitanci ko unguwarzoma. "

"Tow ina niman wanda zai rike min kamfani ina zan barta ta tafi asibiti, duba dai da kyau." Ture takardar Alhaji Abubakar Abzin yayi ya ce mishi. "Maganar gaskiya, idan har kana son ta zama yadda kake so, dole sai ka nisantatta da wannan rayuwar, ka kaita wani wurin ta rayu tayi karatu. Domin idan tana cikin matanka da danginka kishi da damuwa ba zai barta ba, sannan ita ce karama kowa zai zo mata da fitina da baƙin kishi. Don Allah ka nisantatta da gidanka ban ce kada ka kaita ba, zaka iya kaita amma kuma dole ka rabata da su. Domin kuwa matuƙar tana cikinsu ba zata yi karatun ba, kuma ba zata baka abin da kake so ba, karshe ta haifa maka yaran da kake so babu ilimin da kake bukata, zaɓi yana gare ka." Ya faɗa mishi yana gyara zaman shi, ajiyar zuciya ya sauke kafin ya ce mishi. "Kana nufin na dauketa daga cikin gidan kenan?"
"Duk yadda yayi maka."
"Shi kenan zan d'auketa amma ina zan kaita?"
"Nigeria, kano idan ka kaita can in sha Allah zata dawo maka da abinda baka zata ba."

Shiru yayi kafin ya sauke ajiyar zuciya, "ya zan yi da Nana?" Shiru Alhaji Abubakar Abzin yayi kafin ya ce mishi. "Nana ka ɗauke kai akan wani abun da take amma batun yarinyar nan ka tsaya kai da fata ka bata ilimi idan ba haka ba, gidanka duk jahilai za a ayi ta haifa maka. Karshe ga hanyar da za a ci abinci amma kuma babu damar cin abinci, sai dai a kashe kamfanin a zauna a haka. Amma a ƙalla aka samu mace daya da maza biyu zasu jagoranci kome da yardar Allah."

"Shi kenan in sha Allah haka za ayi." Ba don Allah ya bashi aboki na gari ba, tabbas Alhaji Mamman ba'are haka zai kaita cikin iyalinshi babu wani tsari ko plan. Sannan Alhaji Abubakar Abzin ya kara mishi kwarin gwiwa na ya tsaya akanta kai da fata, domin yasan Mahaifiyarshi ba karamar shu'umar mace ba ce, idan bata son mutum. Sannan yana son yadda yarinyar take da nutsuwa koda Allah zai bata haihuwa da Alhaji Mamman Ba'are, ya kasance Yaran sun fita daban.

A wannan takin Amaryar Alhaji Mamman Ba'are ita ce mace mara yara dayawa, amma daga Rabi har Fauziya, a ƙalla suna da yara kowaccen su shida zuwa bakwai , domin gidan gasar haihuwa ake kamar yadda suke hango iyakar kokarin mijinsu.

Sannan Nana ta kara musu zafin kishinsu, ta hanyar gasa musu magana da cewa "Ni duk macen da bata haifa min jika namiji ba, ai tayi a banza tunda mace bata gadon arziki." Wannan ya kara musu kwarin gwiwa daukar ciki suna haihuwar yara rututu, don ma Uban yana tsaye akan Yaran. A gefe guda ga kannenshi da suke hararar dukiyar, wanda ya sani sarai kawai dauke kai yake akan su, fatanshi kada ya bar duniya bai samu wanda zai rike kamfanin ba.

Haka ya tawo Niamey da Sa'adatu. Asalin Bafulatana, kana ganinta kasan Bafulatana ce kasancewarta doguwa sirirya. Ga kyau ga farar fata gata da wata irin kunya da kamun kai. Haka yasa Alhaji Mamman Ba'are, kware mata daga yan kwanakin da suka yi a hanya, ya fahimci yarinyar mace ce guda, haka yasa yayi ta nan nan da ita har suka iso gida.

Sannan itama bata takura kanta ba, tunda tasan ba zata iya sauya ƙaddarar da ta same ta ba. Haka suka isa kantamemen gidan alfarma. Wanda ya gaji da haduwa kamar ba gobe, suka shiga cikin gidan motar tayi parking ya fito itama ta fito. Cikin gidan ya nufa da ita, tana baya yana gaba duk inda ya wuce gaisuwa ake mika mishi har ya nufi falon Nana, zama yayi a saman daya daga cikin kujerun falorn, ita kuma Sa'aden ta zauna a kasa, kanta a kasa. "Ka dawo Mai Babban suna, ya hanya ya kasuwar?"

"Alhamdulillahi! Kasuwa tayi albarka tunda har da mata na samu." Ya fada yana dauke kai yana kallon Sa'adatu. Kalman Alhaji Abubakar Abzin yana dawowa mishi. "Don Allah kada ka zubar mata da mutunci ta hanyar gayawa mutanen gidanka a caca ka samo ta."

"Ban gane ba?" Ta tambaye shi.da alamar bata ganen ba, gyara zama yayi ya gaya mata kome amma ya roketa da don Allah kada sauran matanshi su sani, Sa'adatu a caca ya samota. Kuskuren shi kenan bayan Alhaji Abubakar Abzin ya roke shi, shi kuma yana tunanin Nana Uwa ce da zata iya rufa mishi asiri, sai dai yayi kuskuren domin Nana bata cikin irin wadannan iyayen.

Kiri-kiri ta shafawa idanunta toka, ta shiga bala'i da hayagagga. Akan me zai auro mata mugun iri, maza ya fice mata da ita daga gida, kada bala'i ya fado musu cikin dukiyarshi mai tsafta.

Fadar Nana da ihunta yasa matan gidan sanin Alhaji Mamman Ba'are ya karo aure kuma matar Nana bata yi na'am da ita ba. Haka sukayi ta bala'i a gidan, ya wuce da Sa'adatu bangarenshi, ya zuba mata idanu.

"Kiyi hakuri laifina ne, da ban gaya mata ba da haka bai faru ba." Dake tana da hakuri haka ta sunkuyar da kai ta ce mishi. "Ba kome Uwa ce bata laifi." Wannan abin da tayi ya kara mishi kaunarta da bai san lokacin da ya faɗa ba,

Haka zaman gidan ya kasance, idan ta fita tsakar gida, Hajiya Rabi da Yaranta su rufeta da duka, koda kasheta zasu yi idan Nana ta fito cewa take. "shegiya jinin

matsiyata, Ubanta da tsiya ya masa katutu a caca ya sakata. Ku kashe banza da haihuwar su gara mutuwarsu."

Harirah wacce ta kasance itama yar babban gida ce, sannan Yayanta babban lauya ne, yasa take iya shiga fadar Sa'adatu, sau biyu tana kwatarta a hannun Hajiya Rabi da Yaranta. Sun mata dukar kawo wuka, ta suma ta ce musu. "Wallahi idan yarinyar nan ta mutu sai na gayawa Yayana ya nima mata hakkinta kuma daurin rai da rai za a muku kun san dokar Nijar ai." Jin haka yasa suka rage dukanta, aMma hantara da wulakanci ayi abinci a hanata. Karshe ma sai wanda yaran suka jagwalgwala shi za su bata, ga bakar magana idan ta bukaci wani abu.

Shi Alhaji Mamman Ba'are bai san me ke faruwa ba, domin bata tab'a gaya mishi halin da take ciki ba, amma kuma tana matukar cutuwa, sai Harirah ce ta gaya mishi abin da suke mata, ta ce mishi. "Idan baka yarda ba, ka tafi ka dawo idanunka ya gane maka, nima don ina gidan ne aka rage dukanta amma matukar bana gidan tow sai abin da ya karu "
Haka ya kwana cikin mamaki, domin koda ya tambaye ta, shiru tayi mishi kanta sunkuye tana wasa da yatsunta. Washe gari da safe, suka fita daga shi har Harirah.

Lokacin har Sa'adatu ta fito tana share gidan, Yar Hajiya Rabi Babban wacce bata wuce shekaru goma ba, ta zo wucewa ita Sa'adatu bata sani ba, ta zuba mata shara. Ai kuwa yarinyar ta daddage ta zuba mata dundu a baya, tana ihu. ""Mama Mama kin ga wannan matsiyaciyar da aka auro a caca ta zuba min shara ta b'ata min safa ta." Dama Hajiya rabi tana cike da ita Harirah ta hana a casata, sai gata ta fito da wani murtikekken bulala. Ta rufe Sa'adatu da duka, tana yi yaranta suna yi. Fitowa Hajiya Fauziya tayi tana faɗin. "Shegiya sai kace Mayya idan an gama dukarki wanke -wanke na yana jiranki." Tasan ana dukarta ne babu halin amsa mata, haka ta shige kitchen ta dibo ruwan zafi zata watsa mata sai ga Alhaji Mamman Ba'are da Harirah. "Ka gani ba? Ruwan zafi zata watsa mata bayan sun gama dukarta. Alhaji kaji tsoron Allah Ubangiji ba zai barka ba, kasan zaka kawo ta cikin masifa ka auro ta ka mai da ita wurin danginta."
"Rabi da Fauziya. Na baku nan da minti ashirin ku bar min gidana, idan kuwa na dawo na.same ku wallahi sai na sake ku.". Ya nufi Sa'adatu ya dauketa suka nufi ciki. Goge mata fuska yayi yana son yayi Magana amma ya kasa magana. "Shirya mu bar ƙasar."
"Ina zaka kai ni? Wurin Abbati? Ko wurin Baffana?" Ta tambaye shi cikin kuka. "Wani wuri da zaki rayu babu faɗa babu tsangwama."
"Tow."
Haka ta shirya kayanta sannan suka fito a lokacin Nana ta fito tana kallonshi. "Ban gane ba, ina zaka kaita?"
"Idan Uwar da ta haife ni, ta gaza taimaka min waye zai taimaka min? Nana ke kika basu damar cutar min da Mata? Nana gani na da kika yi a raye yasa kike cutar da abinda nake so? Nana zan nisantatta da ku ne domin Harirah ta gayawa dan uwanta na auro mace na kawo Matana suna son kashe ta, kotu zata turo min sammaci sai ki san abin da zaki ce musu."daga haka ya riko hannun Sa'adatu suka bar gidan, Marad'i ya wuce da ita suka kwana biyu, a wannan kwana biyun ne, ya mai da ita cikakkiyar mace, cikin alfahari da samun mace irinta, dama an gama.mata kome na makarantar, da shi da Alhaji Abubakar Abzin suka tawo da lta garin kano, inda ya tsaya sai da yaga ta fara karatu. Don kusan watan shi biyu
kafin ya fara shirin dawowa nijar ya rike hannunta.
"Kinsan dalili na na kawo ki nan, kin san kudirina na kawo ki nan. Don Allah kiyi karatu sosai, kiyi abin da ya kawo ki zan na zuwa lokaci zuwa lokaci ina duba ki."
Gyada kai tayi, Washi gari motar shi tazo ta dauke shi, haka ya barta cikin kewa da rashin sabo, ta fara karatu a BUK, a tsangayar tattalin arzikin kasa da kasuwanci. Yarinya me kwazo da hazaka.

Wata ukun farko da fara karatun, kaf tsangayar suka san tana ja,. Ai kuwa shima Alhaji Mamman Ba'are da suka zo da Alhaji Abubakar Abzin, ya ga sakamakon da ta fara samu ya fahimci yarinyar guruwa ce, domin samun irinta a cikin Yaranka ba karamin arziki ba ne.

Haka yayi ta dora Alhaji Mamman Ba'are a kan hanya, yadda zai na kyautatta mata. Har ta samu shekara daya a lokacin ne ta samu cikin Abdul Majid. Cikin tsananin zafin laulayi haka ta haɗa karatu da laulayi tana tsoron kada ta samu matsala ya ce tana wasa, a lokacin ta shiga aji biyu. Haka yazo ya samu tana fama da laulayi ga shi suna tsakiyar semester, kanta yayi zafi duk da wannan yanayin bai gaza gaya mata kudirinshi ba, har ya gama kwanakinshi zai tafi ya ce mata. "Idan mace kika haife zan barki ki kara haifar daya, su zama biyu kema ki samu abokan hira, don Allah ya azurtani da Yara mata sun kai goma sha bakwai ga na cikinki ga na cikin Rabi da Fauziya. Don haka kina haifan biyu zan kai ki a cire mahaifar ki huta kinji."

Gyada mishi kai tayi tana jin duk abinda ya ce, domin ita ba zata tab'a bijire mishi ba, shi din kamar waliyi ne a gare ta, haka yasa ta ke daukar duk wani abin da ya ce da muhimmanci. A hankali ya shafa kanta yana rungumeta. Abu daya yasa yake sonta, ilimi da kokarinta. Kuma yaranta zasu banbanta da Yaransu rabi haka yasa yake kara jin dadin ganinta tana kara mishi biyayya.

**

Ya dawo da su Hajiya Rabi, suka nime saka Harirah gaba, danginta suka ce basu san da zancen ba, kada su fara saka yarsu a gaba ba yarda zasu yi ba. Haka ba karamin ja mata mutunci yayi ba. Bayan shekara daya ne Alhaji Nasiru Wodabbe da Mahaifin ta suka zo mata da kayan aurenta, kayan alfarma na yar gata, da wasu daga cikin yan uwan Mamanta,. Dake Alhaji Mamman Ba'are har kasarsu ya tafi ya je suka ganshi ya tabbatar musu tana lafiya, sai gashi sun kawo mata kayan aurenta da duk abinda ake na al'adar kasar nijar. Shima ganin ya auri yar babban gida, basu bar kasar ba, sai da ya ajiye musu kayan auren da ake a cikin kayan har da zinari babba tukwaicin budurcinta.....

#past
#entangled
#revals
#lovers
#Dambuje😸
[2/16, 9:24 PM] Cutie cutie pie: *BAƘIN HAURE....□□*

{Greed for Money is the roots of all evils□}
Arewabooks:maidambu41
Wattpad:Mai_Dambu
Mallakar:Mai_Dambu

□ Wai page biyu kuke so, Yasin kuyi maneji mana😸 masoyan Addaririya

Assalamu alaikum barkanmu da warhaka da fatan kuna cikin koshin lafiya, karku manta da wannan Kamfani mai albarka mai kawo muku kayan bukata cikin sauki da Aminci da Inganci.
Wato TA RASULU MULTIPURPOSE. YA SAKE DAWO MUKU DA KAYAN NAN MASU ARMASHI DA DANDANON KOWACCE MACE TAURARUWA CE.

_____
MARKADADDIYAR GYAD'A
HADADDEN KAYAN SHAYI
GARIN KOSAI NA TAFI DA GIDANKA.
GARIN TUWO
GARIN KUNU YAR ASALI
CURRY ME DADI

SPICES
TYME
YAJIN DADDAWA ME KYAU
GARIN DAN WAKE
JAN YAJI MAI DAD'I...

BUGU DA KARI MUN TANADAR MUKU DA KAYAN FITAR SALLAH DA NA SHAGALIN SUNA DA BUKUKUWA.
ATAMFOFI, LESHINA, MATERIAL, SHADODDI, YADUDDUKA NA MAZA DA NA MATA, JAKKUNA DA TAKALMA.
WANI ABIN SAI KUN ZO TA RASULU MULTIPURPOSE DOMIN KASHE KWARKWATAN IDANU.
ZAKU IYA TUNTUƁARMU A WADANNAN NUMBOBIN.. 08086639163 - 09030168590....
MUNA DAKON SAYAN DAI-DAI KO SARI.....

015

A bangaren Nana ta dai sassauta kiyayyar ta ne don, iyayen Sa'adatu babu wanda ya isa ya kawo musu raini sannan daga mazan dangin har matan kana ganinsu kaga wadanda suka san ciwon kansu, ga wanka da matan suka yi na arziki zaka fahimci sun tashi cikin arziki da wadata domin gwala-gwalan da sukayi kwalliya da su, bayan tafiyarsu ne ya fara ginin part din Sa'adatu ya zuba mata kome nata, da zai tafi wurinta ya dauko mata yan kunnenta babban set da karami ya kai mata,

A lokacin da laulayi nata yayi sauki kenan, haka ta rike shi da daraja, bai gayawa kowa Sa'adatu tana da ciki ba, amma yadda yake lissafin zata haihu bayan sun gama jarabawa zai kaita wurin danginta ta zauna sai tayi arba'in ya dawo da ita. Haka kuwa aka yi domin suna gama jarabawa, ya zo ya zauna ko zata haihu amma ina shiru haka.yasa shi daukarta suka tafi kasar Iyayenta. Lokacin da ta ganta a cikin danginta. Ranar kwana tayi tana kuka tana jin wani irin son danginta..ga iyayenta ga Abbati sai shiga da fita yake yana kawo mata abinci da ta ce tana so.

Shi kanshi Alhaji Mamman Ba'are sai da yaji wani iri domin kuwa yarinyar ba tsarar shi ba ce, don Abbati ya nuna mishi wanda aka so ta aura, yaro ne Matashi amma haka ƙaddara da rabo ya shiga tsakani. Ranar da suka isa a daren ranar ta haifi d'anta namiji, babu wanda yasan tana nakuda, tsabar kunya da wauta.

Yafendo mahaifiyarta tana dakin Mallam mahaifinsu, suna sallar nafilla da mallam wanda suke kiran shi Babaji, taji kukan jariri, bata yarda kunnenta ya jiyo mata ba, sai can ta kara jin kukan. Ai sallama tayi ta nufi dakin ta, anan ta samu Sa'adatu da Kanwarta Kabo, an rasa wanda zai yi wani abu, sun saka Baby a gaba. Dariya abin ya bata ta ce. "Danejo jaririn kuka kasa a gaba. Keda kabo shine baku fita kun kira Sumai ba?" Tana jingine da gadon, tana sauke ajiyar zuciya. Bata ce kome ba, itama Yafendo fita tayi ta kira Sumai, Uwargidanta kenan, ita tazo ta gyara Babyn tsaf, ta wanke Sa'adatu a lokacin, sannan suka saka turaren wuta, domin ita Sumai fulanin chad ce, tana harkar turaren wuta. Kafin wani lokaci gidan ya cika da kamshi, Sa'adatu ana kiranta danejo, Babaji yana kiranta da Hajiya. Kasancewar sunan Mahaifiyarshi ce kuma Hajiyar ce da gasken gaske.

Da asuba aka gayawa Alhaji Mamman Ba'are, Hajiya ta haihu.don da fari bai fahimci wacece Hajiya ba, sai da Alhaji Nasiru Wodabbe ya zauna ya mishi bayani, sai ya gane ya kuma ce musu. "In sha Allah Hajiyarta za a kirata.". Haka ya fita Masallaci, ya shiga gidan don ance mishi ta haihu amma basu gaya mishi me ta haifa ba, sai da ya shiga Sumai take murmushin farinciki ta ce mishi. "An samu da namiji, ango ba cefane." Zubewa yayi a kasa ya zuba sujudul shukur, kafin ya fashe da kuka, aka mika mishi Yaron, jikinshi yana rawa ya fito da yaron har gaban Babaji, ya ce mishi."ka saka mishi sunanka." Murmushi Babaji yayi ya amshi yaron ya mishi huɗuba, a madadin yasaka mishi Aliyu, sai ya saka mishi Abdul Majid. Ya mika mishi.

"Gashi nan Abdul Majid, kukan ya isa haka. In sha Allah zai zame maka fitila a duk wani Mabudin alkhairinka." "Mallam baka saka sunanka ba?" Ya faɗa hawaye na zuba mishi. "Suna na ba shine mai muhimmanci ba, sunan da zai zame mishi alkhairi ake bukata."

Malam yaji dadin wannan kara da Alhaji Mamman Ba'are ya mishi, shi kan kuka yake tayi, don gani yake kamar ba dan shi bane, har asibiti aka kai Yaron aka duba lafiyarshi. Sannan suka dawo kwanan shi biyar ya dawo Nijar ya gayawa Nana ai Sa'adatu ta haihu, bata wani damu can ba, sai da ya ce mata namiji ta haifa shine bayan suna suka je ita da Hadiza da Harirah. Ba karamar hidima aka musu ba, duk iskancin Nana da wulakanci sai da ta rena kanta, domin tazo inda ake magana ta arziki wato kudi kumbar susa. Domin su suka je Barka, sai gashi sun dawo da kayan arziki niki-niki. Madadin haka ya janyowa Sa'adatu farinjini sai tsanarta ya kara cika zuciyar Hadiza da Nana, ita kan Harirah tun farkon ganin Sa'adatu da hakorin hajji jikinta ya bata daga babban gida ta fito, shi yasa bata wani takurawa kanta wurin kishi me zafi ba.

Watansu guda suka dawo kano da kaya niki -niki, suka cigaba da zuwa makaranta. Da dattijuwar da tazo da ita daga garinsu me suna Inno, ita tayi ta renon Abdul Majid har suka yi arba'in da wasu satika sannan Inno ta koma ita kuma ta cigaba da karatunta, sai da suka yi wata hudu sannan suka tafi marad'i, kwanansu uku suka wuce Niamey. Wayyo rawar kai a gurin Alhaji Mamman Ba'are ba acewa kome, haka tayi musu sati Uku. Don zasu koma makaranta kuma har cikin azumi suna karatu. Haka da zata dawo Alhaji Mamman Ba'are yayi ta mata hidima.

Har suka dawo, kaunar da yake nuna musu ya janyo mata bakin jini, haka suka yi ta jigilar karatu ga danginta daga garinsu ana yawan mata aike, lokacin da Abdul Majid ya cika shekaru biyu, suka tafi Umara da shi, Abbati ya biya mata da Abdul Majid. Lokacin sun samu hutu koda suka dawo, Nijar suka sauka a can ta huta domin lokacin zata shiga aji hudu ne, ga zata tafi IT, wannan zuwan ta fahimci kamar bayan son ganinta har ta gama hutun zata koma, ya zo domin sau biyu suka hadu, da zata koma ya mata kome, ya ce kada ta kuma zuwa Nijar.

Tunda ta dawo bai kuma waiwayonta ba, Allah ya so Abbati baya wasa da zuwa ganinta duk bayan wata uku, bata taɓa gaya mishi tana cikin matsi ba, ba kayan abinci shima Abbati idan yace zai zo Mahaifinta zai cika mota da kayan abinci akawo mata . Sannan Yafendo tana turo mata da kayan sayarwa turaren wuta da wasu abubuwan da babu anan, haka yasa ta samu damar tsayawa da kafarta.

A can Nijar kuwa, Alhaji Mamman ne ya hadu da wata mata sun haɗu tun a lokacin zuwan shi Mali, sun dan tab'a soyayya sai gashi ta kuma dawowa rayuwarshi,. Bayan da ta fahimci ta kare mata, tun da suka hadu ta kara jan ra'ayinshi suka fara soyayyar bariki, kuma dama can yar barikin ce shima ba zai ce ba yar barikin bace domin bai san.yadda aka yi ya fada tarkonta ba.

Tunda ta dawo rayuwarsa tayi bincike a cikin matansa wacece yafi so, a binciken ta gano Sa'adatu da danta. Anan ta fara shige da fice, sai da ta cire mishi su a ranshi, sannan ta aza mishi kiyayyar Abdul Majid, idan ya ga yaron kamar zai kashe shi. Don haka yace kada ta kuma zuwa gare shi, don yaron.

----- Bayan ta gama IT, ta koma makaranta Allah ya taimaka akwai kudi a hannunta dasu ta biya kudin makaranta, ta cigaba da karatu, suna cikin karshen zangon da zasu gama makaranta, yazo a lokacin Abdul Majid bai wuce shakara biyu da rabi ba. Da murnar yaron ya tawo gare shi, Alhaji Mamman yasa kafa yayi kwallo da Yaron, tana wanka ta ji ihun Abdul Majid, da sauri ta fito daga ban daki, ganin Alhaji Mamman Ba'are ya rufe yaron da duka, yasa ta isa wurin ta dauke shi, tana faɗin. "Yaron da babu ruwanshi me yayi da zafi?" Kame gashin kanta yayi ya rufeta da duka, har da kwallo da ita, wulakancin da yayi mata Allah kaɗai ya sani, ya kuma jan ta har cikin ɗakin, haka Abdul Majid ya tafi bakin kofar yana buga kofar yana kiran sunanta "Hajiya!" Yana buga kofar, Alhaji Mamman Ba'are kuwa, ya kwana biyu bai

tab'ata ba, haka yayi ta sukuwa akanta kamar ya samu jaka. Yana gamawa ya tashi yayi wanka ya gyara jikinshi, ya saka aka sauke musu abincin yayi tafiyarshi,

Bai kara waiwayarta ba, sai bayan sun gama exam ana batun zuwa bautar ƙasa, ya samu tana fama da laulayi, lissafi yayi kafin ya sakata gaba suka je asibiti aka duba lafiyarta, sannan suka dawo ya kuma rufe Majid da duka, ya kara saka mata doka. Tana gama bautar ƙasa Masters zata wuce. Haka yasa suka zama kamar bayi, a wannan zuwan da yayi har da Hajiya Tani da ya mai da ita yar gida. Amma idanuna Harirah yana kanta, domin bata yarda da ita ba, koda tayi magana akan hakan sai da suka kwashi yan kallo. Tana ji tana gani Tani ta samu damar k'amk'ame kome a cikin gidan.

Wato tani wata irin Shaidaniyar mace ce, da ta gallabi kanta da duk wanda yake kusa da ita. Musamman ta kananaye kowa har da kannenshi da Nana, babu wanda ya isa ya d'aga mata murya. Domin idan kayi magana Alhaji Mamman Ba'are zai ce ka fita ka bar mishi gida, haka yasa kowa ya sha jinin jikinshi. Kowa ya rufawa kansa asiri, kuma ai wargi wuri yake samu. Akwai wani lokaci da Hajiya Rabi ta rufe ta da duka, ai kuwa Alhaji Mamman Ba'are yana shigowa ya samu Tani a inda Hajiya Rabi ta dake ta, babu bin ba'asi ya rufe Hajiya Rabi da duka, sannan ya kwaso mata kaya ya watsa a waje, da guzirin sakinta.

Wannan abin ya tashi hankalin mutanen gidan, domin saura igiya daya a tsakaninsu, haka sai da aka yi da gaske ya dawo da ita, ya kuma kafa mata doka, tun daga ranar Tani take zuba mulki kuma babu wanda ya isa magana, sannan itama Tani tasan cewa yana biye mata amma mafi yawan hirarsu zai sako sunan Sa'adatu. Hankalinta a tashe ta nufi wurin Malaminta ya rufe mishi baki da zuciyarshi.
***
A Kano tayi bautar ƙasa, kasancewar Abbati yazo, tana gamawa ta wuce kasarsu a can ta haifi Amaan aka turawa Alhaji Mamman Ba'are sakon haihuwarta, dake a can kamfanin labarin ya same shi, Kuma dayake aikin bai shafi jaririn ba cikin farinciki ya tsayar da dan aiken ya bashi sako ya kai musu, amma shi dai bai taka har can ba, har tayi arba'in ta koma Kano. Dan abin da taxo da shi suka cigaba da rayuwa, bai kuma zuwa ba sai da Amaan ya cika wata takwas, ya turo Alhaji Abubakar Abzin, ya kara biya mata masters ta cigaba da karatu, haka tayi ta fama da Yara biyu ga karatu, koda Alhaji Abubakar Abzin bai zo ba, akwai mutumin da yake kawo mata sako.

Lokacin Abdul Majid yana da shekara uku da rabi, Amaan yana da shekara daya da rabi, domin har ta yaye shi. Sai ga Alhaji Mamman Ba'are da Tani dauke da d'anta karami da ta haifa bata jima ba, kuma abin mamaki shi kanshi Alhaji Mamman Ba'are ya kasa cewa kome akan dan na farko shi bai ce dansa ba ne, sannan kuma bai ki yaron ba, a wannan zuwa da yayi, rayuwar Abdul ta fara fuskantar matsala, abin da ya kawo haka, shine tunda suka zo gidan suka saka shi a gaba da duka, na safe daban na rana daban, idan suka mishi wannan dukar, zasu saka shi a daki a rufe shi, a manta da shi ita kanta Sa'adatu bata da ikon ciro shi, idan ta ciro shi kuwa Tani ta sakata a gaba da masifa sai kace ita ta haife ta, idan Alhaji Mamman Ba'are ya dawo kuma ta gaya mishi ya rufe ta da duka, ita uwar a wahale yaron a wahale.

A hankali Abdul Majid ya zama kamar dolo matukar Alhaji da Tani suna gidan zai na wani irin sizing kamar zai suma. Tsoro da firgici na Uban ya kara cika zuciyar Yaron, satin su hudu suka bar gidan, shine ya dawo daidai amma kuma sai ya xama ko sauti yaji mai karfi, zai zabura yana niman inda zai boye kanshi. Gashi zama da mutane bai saka ta saki jiki da kowa ba, haka yasa bata mu'amala da kowa.

Wani zuwan Mahaifinta taron Malamai na Afirka, yazo ya ganshi bai tsaya ba, ya dauke shi zuwa gidan Sheikh Muhammad Taj Kalarawi, ya ajiye mishi Yaron yana

faɗin. " Malam Muhammad ka kalli yaron nan kamar akwai sihiri ko?" "Ikon Allah yanzu dan wannan yaron aka yiwa asiri haka?" Murmushi Sheik Aliyu Wodabbe yayi ya dauki Yaron. "Idan anyi ne don a ga bayan shi, in sha Allah ba zasu ga bayan shi ba. Sai ya zame musu gaggarabadau.." ya dauke yaron yana murmushi, "Alaraini kayi hakuri kada ka mai da musu sharrinsu."

"Ni ban musu ba, kuma ba zasu min na kyale ba. Kasan waye ni kuma kasan daga ƙabilar fulanin da na fito, wallahi ba zan bari ba." "Don darajar Ubangiji kayi hakuri amma shi ka tsare shi." Huci yake kafin ya sab'a yaron zai fita Sheikh Muhammad Taj Kalarawi, ya ce mishi. "Kawo shi!" Mikamai yaron yayi, sannan ya tafi ya koma wurin Sa'adatu. Ya tambaye ta meke faruwa da Yaron, amma bata ce kome ba sai kuka. Haka yasa shi fahimtar tana da damuwa amma ba zata fada ba, sati biyu ya yi a garin tare da tsayawa akan Yaron.

Wannan zuwan ya zame musu alkhairi, domin kuwa har makaranta aka saka yaron, bayan tafiyarshi Alhaji Mamman yazo da Tani. Hmmm ganin yaron yana makaranta da nutsuwa. Hankalinta ya tashi a wannan lokacin da ta saka mishi kahon zuka, domin kuwa duka take mishi wani lokaci idan zai tafi makarantar domin har gida ake zuwa daukar shi, amma zata hana a kai shi, duk da Sa'adatu tana son mata magana tsoron abinda zai je ya dawo yasa take rintsa idanunta.

Bata taɓa hanawa ba, sai sau daya tana laulayin cikin Aryan da aka zo za a dauke shi, Tani ta hana. Kasa hakuri tayi ta ce mata. "Gaskiya ba zai yiwu ba, ya tafi makaranta domin ba zai zama ya rasa nutsuwa ba, a gida bai huta ba sannan a can inda zai huta kice ba zashi ba, wannan ba yi bane ." Ta kamo danta ta fi da shi. Tana komawa cikin gidan Tani ta saka sakatar gidan zata rufeta da duka, ita dai bata san me ya faru ba, sai dai kawai an balle kofar gidan ne aka d'aga daga kan Tani da ta suma.

Koda Alhaji Mamman Ba'are ya zo don yaji labarin abinda ya faru, shima tsorata yayi da Yanayin Sa'ade, don haka ya tattara kayan Tani da d'anta. Bai kuma takowa gidan ba, har ta haifi Aryan ita da kanta tayi mishi huɗuba. Haka tayi ta rayuwa can wurin danginta kamar sun manta da ita, haka shima bangaren mijinta ya manta da ita, sai da ta kai dole ta cire Abdul Majid a makaranta. Dake makarantar Sheikh Muhammad Taj Kalarawi ne,. Ya daina ganin yaron domin Allah ya daura mishi son Abdul din, wani ikon Allah sai kamar an dakatar da shi da zuwa duba su. Haka ya watsar da tunaninsu.. yara uku babu abin da zasu ci, don haka kawai ta fita ta fara aikatau, tana wanke-wanke da abinci, a bakin titi, karshe ma karatun da take ne ya tsaya, akwai wani karamci da kanawa suke dashi, kasancewarta bakuwa kuma daliba, ganin bata zuwa aka tashi wasu daga cikin dalibai suka nimo labarinta, haka yasa makarantar B.U.K suka dauki nauyin sauran lokacin da ya rage mata, wannan karamcin da suka. Mata yasa bata iya mantawa da su ba, sannan daliban tsangayar suka hada mata kudi ta kama sana'a a cikin gidan, ba sai ta fita ba.

A bangaren yaranta ta saka su a wata makarantar gwamnati. Haka suka ta rayuwa da dadi ba dad'i. Har suka gama ta cigaba da xama a Kano, a hankali ta rungume Yaranta, ta cigaba da sana'a idan suka cinye jarin, sai ta nemi aikatau a gidan mutane.

Abdul Majid tun yana primary yake da kokari, sai dai daga lokacin da aka mishi tsawa, zai birkice ya koma kamar dolo, haka yasa wani lokaci yake hakura da makarantar ya zauna a gida.

Akwai gidan da take aiki, Yaron gidan ya nimeta da lalata, ita kanta bata sani ba. Sai da ta ganta a Office din yan sanda, an rufeta, tayi tayi ta musu bayani amma ina sharri aka mata, haka ta bar Yaranta a gida ,babu kowa sai Allah, tayi kuka tayi bakinciki har cewa take ita da ganin wannan rayuwar da mutuwa tayi ya fi mata, akan wannan rayuwar domin tana cikin tasku. Tun safe da Yaran suka karya har rana

bata dawo ba, har dare babu labarinta, haka Abdul Majid yake goyan Aryan idan ya gaji ya sauke shi. Kwana suka yi babu kowa a gidan sunyi kuka har sun yi shiru. Washi gari da safe suka tashi babu Mamansu. Har rana bata dawo ba, dalilin da yasa Abdul Majid ya fita bakin shagon unguwar kenan ya sato bread,. Babu wanda ya lura da halin da suke ciki.

Haka aka rufe shi da duka yana rungume da bread din, yaki sakewa sai dukan shi ake yi, makocin sune ya ga ana ta dukar shi, shine ya karbe shi. An farfasa mishi jiki. Mutumin da yake lura da shige da ficen su, yaga yau bai ga Mamansu ba. "Abdul Ina Mamanku?" Yana sheshekar kuka ya ce bata dawo ba, har lokacin yana rungume da bread din,. "Me yasa ka daukar musu bread." "Aryan da Amaan yunwa suke ji Hajiya bata dawo ba." Jikin mutanen da suka dake shi ne yayi sanyi. "Nawa ne kudin bread din?"
"Dari ce!" Biyan kudin yayi ya saka yaron a gaba har gida, "ina mamarku take aiki?"
"Ta can ne?"
"Tow ka jira ni ina zuwa." "Tow!" Gidan shi ya koma ya amso musu kunu da dumammen tuwo, ya kawo musu Aryan da Amaan suka ci sai da suka kusan cinyewa sannan suka koshi, Aryan ya koma ya kwanta sannan Abdul Majid yaci kadan ya bar musu, yadda Mamansu take yi ta ci kadan ta bar musu sauran....
~~~~~~~~~~~~~~
```Shahararu goma aduniyan kayan mata wato m zee kamshi kayan mata kenan inakuke matan kwairai manyan Mata fah bamuna mataba Mata masu aji Wanda tasan kanta agidan mijinta kozokuyi gyara masu kyau da inganci Wanda zaisa oga nishadi yasashi farinciki atare dake kayanmu wane yaro sai uban yaro kinsha zumar makalemata dare daya wanka goma wanan set ne na kayan kwairai akwai fati budurwa mumuna da aeki Dan miyau malaka to shu,Umar Zuma zumar kiba gari kiba Zuma me lakani ningi tsumin lahaula hadin miski ba ahira dawando garin me kabara kasa ruwa sama ruwa wanan magani ba ,a magana magani sanyi mekyu maza da Mata ci da kaza ci da cicibin vlp yan shila ci da kifi nama kayan sakiba na gida danawaje munadakaya kala kala fani kamshi munada shu uwar humra namu ba irin nasubane akwai turare 24 hr turare kabasa Dana gida masu Dadi gakyau ga kamshi 08063845136```

#Mai_Dambuje.
[2/17, 5:06 PM] Cutie cutie pie: *BAKꞋIN HAURE....□□*

{Greed for Money is the roots of all evils□}
Arewabooks:maidambu41
Wattpad:Mai_Dambu
Mallakar:Mai_Dambu
016
Mutumin nan bai yi kasa a gwiwa wurin neman Mutanen unguwar tare da mai unguwa, ya zauna a tsakiyarsu ya ce musu. "Akwai matar nan yar kasar Nijar, tow gaskiya a da ina ganin mijinta yana zuwa, amma a yanzu an dauki shekara biyu ban ga mijin yazo ba, sanan ita kuma tana yawan fita aikatau domin ina yawan ganinta ta fita da sassafe ta dawo da la'asar lis, tow kada na kaiku da nisa Matar nan dai jiya bata kwana a gida ba, sannan ku yi nazarin idan mune ya zamu ji? Sannan yarinya ce domin bata kai talatin ba, don Allah ku duba lamarin."
"Hmmm! Waye ya sani ko yawon bin maza ta tafi." Inji wani mutum a wurin, tsawa limamin unguwar yayi mishi. "Mene ne hujjarka?" Sunkuyar da kai yayi, kafin liman ya ce. "A yanzu muje gidan, ko akwai yaron da zai fada mana inda take zuwa aiki." Haka suka mike bakiɗayansu, suka tafi har gidan, sun samu Aryan yayi kashi ya b'ata jikinshi. Haka Mutumin farko ya kira Matarshi ta wanke su, sannan ta dauko musu kayan Yaranta, suka kasa sannan ta riko hannun Abdul Majid suka fito. "Abdul
~~~~~~~~~~~~~~

Majid!" "Hmmm!" Ya fada yana komawa gefe, domin har yau yana fama da rashin sakewa. "Kasan gidan da Mamanku take zuwa aiki?" Gyada kai yayi. "Ok Maman Luba tafi da sauran, bari ya kai mu inda take zuwa aiki."

Haka suka saka Abdul Majid a gaba, har gidan dake tana zuwa da shi yana taimaka mata da Aryan yana wasa da shi, koda suka zo gidan babu wanda ya yarda yayi musu maganar Sa'adatu, sannan babu wanda ya kula su, sai da yan unguwar suke gayawa musu ai tun jiya da hantsi yan sanda suka tafi da ita office dinsu.

Ba karamin kaduwa suka yi ba, domin kuwa har an rasa me magana, haka suka mai da Abdul gida, sannan wasu suka wuce kasuwa, wasu kuma suka hakura da kasuwa suka nufi Office din yan sanda nimanta. Musamman Baban Luba mutumin nan yayi halacci musamman da yake makocinta, haka suka yi ta yawo kafin Allah ya gajarce musu wahala, suka same ta goshin Magariba a wani Office din yan sanda.

A lokacin da suka je a bada belinta, kin sauraronsu aka yi, da suka nace aka kawo laifin da ake tuhumarta da shi na sata da yunkurin kisan kai. Shiru kowa yayi kafin, suka roki a basu ita tana da Yara kanana. Amma aka hana su, sai dai sun fito da ita, suka ga ko tsayuwa bata iyawa ga yunwa ga tashin hankali, haka Baban Luba ya tafi ya sayo mata tuwo hannu baka hannu kwarya haka take cin abincin.

Tana ci a lokacin hankalinta ya dawo jikinta, duk yadda suka so jin me ya faru, kunya da zurfin ciki ya hanata magana. Haka suka maida ita hankalin kowa ya tashi, sai da aka mai data ta zauna tayi ta kuka tana jin me yasa ta kasa magana. Haka ta kwana kuka.

Washi gari..

Gidan mutumin da take aiki suka je, dakyar da sannu sannu aka bawa mutumin hakuri sannan ya janye karar domin yace kotu ce zata raba su da ita, daga taimako zata kashe musu d'a da sata. Su dai tunda aka janye karar, suka yi godiya suka bar gidan. A can office din yan sanda, aka bada belinta, aka dawo da ita gida, Baban Luba shi ya fita can sai gashi da kayan abinci, ya kawo mata da dafaffen har da Yaranta. "Idan kina da matsala ki yi magana da Maman Luba, Allah ya tsare na gaba."

"Allah ya biya maka bukatarka na alkhairi, na gode." Ta fada tana kuka, haka ya bar gidan, sai da tayi wanka tare da sauke sallolin danke kanta, ta samu wuri ta zauna ta sakawa yaran abinci, suka ci banda Abdul Majid da yake manne a jikinta, yana kallon yadda take sharar kwalla. "Hajiya kici abinci man." Ya faɗa kamar zai fashe da kuka. "Na koshi Alhaji!" Ganin taki ci yasa shima yaki ci. Yadda ta ga rana haka ta ga dare, Washi gari ta tafi har gidan Baban Luba tayi godiya, sannan ta ce mishi. "Ina son zan fita da yaran, ga gidan."

Kafin Baban Luba yayi magana Maman Luba ta yi maza ta karɓe zancen. "Ina zaki kuma?" "Ina son zuwa nijar ne, shine nake son fita muyi Bara ko za a samu kudin mota." Ta fada cikin matsanancin kunya, "Bara?" Suka hada baki, "ki je gida ki shirya gobe in sha Allah sai ku tafi, yau zan samu abokina Hamisu bazabarme na gaya mishi akwai fasinjar marad'i ko?" Gyada kai tayi, ya jinjjina kai ta koma gida, haka ta dawo gida, bayan fitar shi ta koma gidan ta cewa Maman Luba."idan kina da aiki kawo na rage miki."

"A'a Maman Abdul barshi." "Don Allah kawo ko wanki ne." Haka matar ta fito da wankin. Kafin azahar ta gama wanki, kuma kayan sun fita tass, ta shanya mata sannan ta basu abinci suka dawo gida, ita kan Maman Luba wani irin son Sa'adatu take, shi yasa take tsananin tausayinta. Tasan yarinya ce. Da dare Luba ta kawo musu abinci har gida, washe gari da sassafe makocinsu ya sakata a gaba, bayan ya gayawa me unguwa da liman, aka kaita tasha sannan suka bata guzuri me yawa, ta baro Kano zuwa marad'i. A lokacin da ta isa ta samu Alhaji Abubakar Abzin, baya gari a gidan ta zauna na tsawon sati daya, kafin ya dawo. Duk da tazo wurin shi da damuwa amma kuma tana ganinshi sai ta kasa fadar kome, ta koma kuka. Yana rike da hannun Abdul Majid, yake tambayarshi sai ya kalli Mamansu kafin yake magana,

amma yaki fadar abin da ya faru. "Hajiya baki ce kome ba, sai kuka." Girgiza kai kawai tayi. Haka ya mike ya ce ta koma can wurin uwargidansa tunda dama a can ta sauka, Mutumin kirki, Washi gari ya tashi wani yaron shi ya je har Kano aka duba mutumin da ake bashi aika ya kai mata, ashe ya rasu, sannan dan aikan ya tafi har unguwarsu, anan yaji labarin abin da ya faru, kwana biyu tsakani sai gashi nan ya dawo da bayani, Alhaji Abubakar Abzin ya yi shiru. Sannan ya kira ta. "Me ya faru har aka rufe ki na tsawon kwana biyu?" Kanta a sunkuye ta ce mishi. "Babu kome Abba." Don a haife ya haifeta.

"Shi kenan, amma Mamman yana zuwa?" Hawaye ne suka zubo mata, ta girgiza kai. "Shi kenan." Haka ya fita a ranar ya bar marad'i, wato koda ya isa Niamey. Faɗa suka shiga yi shida Alhaji Mamman kamar zasu yi doke-doke, kafin suka dawo Alhaji Abubakar Abzin ya gaya mishi halin da iyalinshi suke ciki. "fisabilillahi yara maza har uku fa, gasu nan duk da rashin kulawa amma yaran sun samu tarbiyya kaji tsoron Allah kafin ya tsayar da kai."
"Naji zan zo amma gaskiya Ya fada kuma sai yayi shiru, kafin yayi kwafa. Kwanan Alhaji Abubakar Abzin daya, suka juyo tare. Cikin farinciki yaran suka ga Babansu, sai dai Majid ya koma jikin Hajiya ya lafe, saboda kallon tsanar da Alhaji Mamman yake mishi.

Tambayoyi har da takardun ta, duk ta bashi sannan ya kalleta cikin isa ya ce mata. "gobe zaki koma Kano, ki sani ban baki damar kiyi karatu don jin dadinki ba, ban tara dukiya don yaranki su ji dadi ba, na tara su ne, don amfanin gobensu. Dole ki jajirce ki kuma koyi boye damuwarki, sannan kiyi hakuri da abinda kike da shi. Wannan shine abin da zan gaya miki ".
"Mun gode sosai hakan ma" ta faɗa muryarta a raunane. "Kada ki kuma kawo karana." "Allah ya huci zuciyarka, in sha Allah haka ba zai kuma faruwa ba."
Haka ya kwashi Amaan da Aryan, ya tafi da su yawo, sai dare ya dawo dasu. Duk abinda ya kawo musu haka yace kada ya bawa Abdul, amma abin ka da Uwa. Sai da sauran suka yi barci ta tashe shi ta bashi ya ci, sannan ya kwanta. Tausayin Abdul take ji, gani take kamar tana da laifi wurin duk abinda ya same shi. A hankali take shafa kanshi har barci ya dauke shi, tana zaune a wurin Alhaji Abubakar ya shigo ya cewa Matarshi ta turata wurin Mijinta, haka ta shirya ta tafi, za a iya cewa wannan karon rabo ya kawo ta, domin kuwa washi gari ya juya ya koma ya bar kome nasu a hannun Alhaji Abubakar Abzin. Ita kuwa a ranar ta dawo kano da tsaraba me yawan gaske. Ta kaiwa gidansu Baban Luba, sannan ta kai na gidan Mai unguwa da Liman, don sune iyayenta.

Bayan tafiyarta da binciken da Alhaji Abubakar Abzin yayi, ya ji gaskiyar abinda ya faru. Ai kuwa ya maka mutumin da yasa aka rufeta a kotu, rikici babba aka yi ta yi kamar me, sai da dattawan unguwarsu suka saka baki, haka ya sama mata yanci, suna dawowa ranar Monday aka zo aka kwashe Abdul da Amaan suka tafi makaranta. Ba laifi zuwa yanzu ta samu dan nutsuwa, tana dan sana'a kuma abincinsu yana nan.
***
A can kuwa Tani tana zuba mulkinta yadda take so, bata yarda ta kuma cewa tana son zuwa ganin halin da Sa'adatu take ciki ba, domin tsoron abinda ya faru kada ya kuma faruwa, haka ta zauna tana zuba musu isa da mallaka.

Sannan a gefe guda ta mallake Nana sai yadda tayi da ita, kuma bata da katabus sai Abinda Tani ta ce, ana haka ta saka Alhaji Mamman a gaba ya saka mata danta Sajjid a makaranta tare da gaya mishi duk abinda yake so Sajjid zai mishi, ba sai ya damu da Abdul ba, fatanta kawai ya saka Sajjid a cikin Yaranshi. Amma mutumin nan yaki kula zancen. Idan ta dauko zancen zai ce mata yaji kawai don ta rabu dashi amma a ranshi baya jin zai yarda ya amshi Sajjid domin ba jininshi ba ne.

Haka tayi ta kokarin lallai sai yaron, ya zama wani abu kai babu wanda ya isa yayi mishi fada balle tsawa. Ga rashin kunya da fitsara.
****
Tunda suka dawo ta fara laulayin cikin Jamilah don ma babu wani wahala, amma kuma tana yawan kwanciya. Saidai da sauki,haka taci gaba da rayuwa har Allah ya sauketa lafiya, ta samu yarta mace, Kyakyawa da ita, haka yasa ta saka sunan Yafendo Jamilah.

A lokacin ba laifi abinci da sakon yana samunta, haka tayi ta renon Jamila, amma ta turawa Alhaji Abubakar Abzin sakon ta haihu, shi kuma ya turawa Alhaji Mamman Ba'are, bai bi ta kanta ba, sai bayan shekaru biyu, rabon Anisah ya kaishi Kano, a lokacin Abdul Majid ya kusan gama primary, a wannan zuwan da yayi ne. Ya kama yaron ya mishi mugun dukar da ya suma saboda kawai an kawo kararshi wai ya dauki kudin wani me shago, ya mishi wannan dukar, ya tura shi gidan horar da kangararun Yara,. Wani abin tashin hankali ya dauke Hajiya da sauran Yaran suka koma Niamey. Suka bar Abdul Majid, da yayi fama da jinya ga cutarwar yan gidan, duk wanda ya fika ƙarfi zai zalunce ka, sannan yara ne masu banbancin hali, har da marasa jin magana masu luwadi, sai dai tunda suka barshi Hajiya ta bar amanarshi a hannun Maman Luba. Tana can amma addu'arta bai daina sauka a kanshi ba,

Sai da ya kwashe shekaru goma har ya zama kaman dan gida, anan ya gama primary school da secondry school, yayi jarabawar shiga jami'a, ƙoƙarinshi yasa shi samu tallafin karatu a wurin gwamnatin Kano, anan ya tsaya ya karanci bangaren likitanci, tsawon wannan lokacin, Hajiya tana marad'i, tunda Alhaji Mamman ya zubasu yayi tafiyarshi, Alhaji Abubakar Abzin shine kome nasu, har ta haihu.

Dukkan Yaran sun san Majid amma Anisah bata san shi ba, sai labarinshi. Zamanshi a gidan horan Yara, ya kara maida shi wani irin mutum mai murdadden hali, sannan baya hmm baya Humm. Dole yasa yake zama a cikin aji, amma baya son hayaniyar mutane ko kaɗan. Idan dare yayi kuwa baya barci domin idan ya fara barci zai ta mafarkin Babansu yana dukar Hajiya. Haka xai bude idanu, sau biyu yana faduwa a aji, a duk ranar da yayi mafarkin tow zai fadi ya suma sai washe gari don bai samun isasshen barci.

Ganin haka zai shafi karatunsa, yasa shi fara ganin likitan kwakwalwa, aka fara duba shi, domin har dawanau aka tura shi. Lokacin da suka samu hutu, ya shirya ya tafi marad'i da tambaya da kwatance yaje gidan Alhaji Abubakar Abzin, Aryan yana kofar gidansu na maradin ya hango Abdul ba zai manta da shi ba, da gudu ya tafi ya rungume shi." Hammayo;" murmushi yayi ya kara rike shi suka nufi cikin gidan, ya kawo musu tsarabar Kano. Hajiya da ta ganshi, juya baya tayi tana kuka. Murmushi yayi bai ce mata kome ba. Ya zauna kanshi a sunkuye. Haka ta shiga daki Jamilah ta fito ta ce. "Hammayo kai ne" ta zauna a kusa dashi tana washe baki . "Yafendo kin zama yan mata " "sai buhun rashin mutunci." "Hammayo kaga Hamma Aryan ko?" Tashi yayi ya shiga dakin Hajiya, ya same ta a can kuryar dakin tana kuka. Zama yayi gabanta. "Hajiya ko daidai da rana daya ban manta daku ba."
"Amma ai na manta da kai!" "Hajiya nasha mafarkin kina sallah kina min addu'a da wannan na yarda a zuciyarki ina tare dake."
"Alhaji baka yi fushi ba?" Girgiza kai yayi yana murmushi. "Hajiya kina karkashin mijinki, a kaina ba zaki kashe auren da na bude idanu na gani ba." Hawaye ne ya zubo mata danta dan kimanin shekaru goma sha takwas. "Gobe zamu je Niamey."
"Hmm! Allah ya kai mu!" Ya fada.
Haka ya fita ta kawo mishi abinci, kannen suka zagaye shi, suna bashi labari can sai ga Anisah ta shigo tana kuka."Hajiya!" "Na'am Auta."
"Hajiya Hamma Amaan ya kwace sauran canjin."

"Allah ya shirya min ku baki daya." Ta amshi sakon, ta ajiye a kitchen. "Hajiya Ina hamma Aryan?" "Suna cikin daki Hammayonku ya dawo." Da sauri ta shiga Dakin, ta d'aga labule. Kura mishi idanu tayi idanunta cike da kwalla. "Hammayo!' bude mata hannu yayi, da sauri ta isa gareshi tana kuka. "Hammayo ban sanka ba, amma Hamma Aryan kullum sai ya bani labarinka." Murmushi yayi yana kallon Aryan. "Ya ce miki ina sat.." rufe mishi baki Aryan yayi. "Alkhairi nake gaya mata, yarinya ce bata san sharri ba please."
"Hamma Amaan yake gaya min wai sat..." Rufe mata baki Jamilah tayi. "Ke dai akwai bakin allatsine, idan kika bi na wancan sakaran sai an daure ki igiya tayi saura."

Domin daga Jamilah har Aryan basu shiri da Amaan,.kamar wuta da auduga. Mikewa yayi suka tafi masallaci, suna dawowa suka samu Hajiya tana kokarin tuka tuwo.. "Hajiya bani na miki?" "Yau.girkin maza zamu ci?" Ta tambaye shi, "zamana a gidan Horon kangararrun Yara, yasa na rike bangaren girki har gasar girki muke " ya faɗa a sanyayye, Duk da cikin raha yake maganar amma fuskarshi bata nuna haka ba, yanayinshi babu yabo babu fallasa, suna zaune ya tuke tuwon ya kwashe tas, yana gamawa wata mata ta shigo kawo kar'ar Amaan. "Maman Jamilah ina jin kunyarki, ki jawa danki kunne wallahi ya fita harkata da yarinya ta."
"Kiyi hakuri;" shine abinda Hajiya ta faɗa, sannan matar ta fita tana zage-zage. Can kafin magariba sai ga Amaan, ya shigo yana zage zage da rashin kunya. Kallon Abdul yayi ya ce mishi. "Barawo ka dawo ne?" "Hammayo muje masallaci!" Inji Aryan, domin a cike yake da Amaan babu ranar da zata waye ba a kawo ƙarar shi ba, "Kai dan shegiya da kai nayi?" Wani irin mari Abdul ya kifa mishi, a wurin ya zube yana nishi, "kayi yadda kake so, idan kaso ka fadi abinda yayi maka. Amma ka sake ka zagi wani cikinsu sai na cire ma hakori."
"Hajiya kina ganin barawon danki zai kashe ni." Alola yayi ta wuce daki, shima ya wuce dakin. A masallaci Aryan yake bashi labarin abinda yake faruwa, sannan wani abin tashin hankalin shine duk bayan wata biyu Hajiya xata kwashe su har Niamey, su je can ayi ta wulakanta su ana ganawa Hajiya azaba da masifa.

Lashe baki yayi yana jin daci a ranshi, haka sukayi sallah sai bayan Isha suka dawo, tun a kofar gidan suke jin muryar Jamilah, Hajiya tana gefe bata yi magana ba ta xuba musu idanu Amaan sai dukanta yake. A fusace Aryan ya nufi Amaan Majid ya rike shi, "sake ta!" "Idan naki fa?" "Aryan wuce da hajiya ɗakinta!" Ai dama ganin hajiya a wurin zai saka ya kyale shi, sai gashi cikin fushi ya kai mishi wani irin duka a kafa, dauke wuta yayi wato Majid zama gidan horon nan ya koyar da shi mugunta sala sala. Targad'a shi yayi ya ce mishi. "Kafin ka warke ka fara fita zaka fahimci muhimmancinsu, idan ma baka horu ba, akwai hanya dayawa da zaka nutsu."
Haka ya wuce da ita daki, yana faɗin. "Kin mishi rashin kunya ne?" "A'a Hammayo, kiranta yayi tana sallah shine tana idarwa ta fita ya kama dukanta da hajiya tai magana yace babu ruwanta."
Cizon fatar bakinshi yayi yana jin tafasa a ranshi, a daren Aryan ya gyara dakinsu, da Inda Hammayo zai kwana. Haka suka kwana suna hira, sai asuba suka yi barci.. wurin karfe goma motar kai su Niamey tazo, suka tafi sai cika Amaan yake yana batsewa. Har suka isa gidan, wanda daga kofar gidan zaka fahimci ana sha'ani ne.

Lokacin da suka isa gidan, ba laifi ana ta hada-hada, falon Alhaji Mamman suka nufa suka gaishe shi sama sama ya amsa. "Kai me yasa meka?"
"Ba Barawon can bane ya dawo ya targad'a min kafa ba."
"Waye barawo!"
"Abdul Majid!" Wanda ya shigo falon, mikewa Alhaji Mamman yayi ya ce. "Sa'a me yasa kika kawo min shi gidana!" Juyawa yayi ya bar falon. Ai kuwa garin bashi hakuri ya rufeta da duka, har waje. Wannan abin ko a jikin Amaan domin shi gani yake Hajiya ta rabasu da jin dadin gidan Ubansu ta kawo su wata duniya suna wahala. Shi yasa duk abinda Alhaji Mamman zai mata baya tausayinta ko kaɗan.

Da gudu Anisah ta fita waje, "Hammayo kazo Alhaji xai kashe Hajiya." Sun saba duk lokacin suka zo haka xai mata duka a gaban jama'a. Amma na yau ya wuce tunaninsu domin biki ake yi a gidan, kuma ga mutane babu wanda ya damu sai ma tsayawa da suka yi suna kallon abin. Haka ya ratsa taron ya shiga. Ya rike hannun Alhaji Mamman Ba'are da yake zuba mata duka. "Ya isa haka!" D'ago kai yayi yana mamakin waye ya isa ya dakatar dashi daga dukar Sa'adatu. "Ya isa haka Alhaji Mamman Ba'are!" Ya sake hannun shi yana kallon cikin idanunshi. "ya isa haka nace!" Ya fada yana me dago kai yana kallon Hajiya Nana. " Na rantse da Allah,duk ranar da danki ya kuma d'aga hannu ya tab'a min Uwa, sai na hauro sama na bugaki da kasa daga saman zan wurgo ki billahi azim, Uwa bata fi Uwa ba duk sunansu Uwa." Ya faɗa yana d'ago Hajiya. ""Kai waye ya baka damar shigo mana gida?" Inji Sajjid Mamman Ba'are, cikin wani irin fushi, ya juya ga Sajjid wanda ganin idanun Abdul ya bashi tsoro. Kwayar idanunshi a fusace yake fushinsa daga zuciya take kunno kai ga idanunshi, kamilalliyar fuskar shi bata nuna fushin ba..

"Kace me?"

Hadiye yawu yayi, ya juya ga Alhaji Mamman Ba'are zai magana Hajiya ta ce mishi. "Kul ka kara magana!" "Hajiya idan ya kuma dukanki sai kashe shi, Nana kin ji me nace." Ya fada da karfi, juyo shi hajiya tayi ta watsa mishi mari, ta kuma marin shi. Jikinshi ya hau cira kamar zai tashi sama. "Ban doraka akan haka ba,me yasa zaka min haka?" Inji Hajiyar tana kuka."Mahaifinka ne me yasa zaka mishi haka a gaban jama'a?" Zube gwiwarta tayi ta ja hannun Majid din, sai yaki. "Ki cewa danki ya fita na tsame shi cikin zuri'ata."

"Haka yayi ai dama kafin yau ni ba danka bane."

"Ba zai fita ba, rashin kunyar da yayi sai Uwarshi ta biya akan idanunshi." Jin Nana tana saukowa. A fusace yayi kanta tare da tsare ta da idanunsa masu Bala'in ban tsoro. Da gudu Hajiya ta rufe shi da duka, "ka bar tashin hankalin nan, ka koma inda ka fito na roke ka, don Allah na roke ka ka tafi ka yi nisa da mu na yafe maka zuwan."

Juyawa yayi zai tafi Nana ta dauki sandarta ta shiga bugawa Hajiya, "Hammayo tana dukan Hajiya" bai ce kome ba, ya nufi falon Alhaji Mamman ya ce mishi. "Ka fita ka jawa Mamarka kunne ko na kona gidan nan baki ɗaya wallahi billahi azim." Ya fada a haukace, zuwa yanzu shi kanshi Alhaji Mamman Ba'are tsoron Majid ya darsu a zuciyarshi. Ganin yadda ya fita da gudu, inda motar gidan take ya nufa, ya cire rigarshi ya bude wurin tanki, ya saka rigar sai da ya jike da fetur, ya Ciro yana watsawa a kan kome na gidan, "Hajiya kyale ta don Allah." Alhaji Mamman Ba'are ya fada, sannan ta tsaya tana hakki. "Me yasa ka dakatar dani?"

"Saboda d'anta zai aikata kome don mahaifiyarshi."

"Kenan idan aka dake ta zai dau mataki?"

"Zai aikata kome.ma". Ya faɗa yana kallon yadda Majid din ya d'ago Hajiya suka dauki kayansu, suka nufi gidan. " Ita da Yaranta su zauna a gidan shi ya bar magana gidan mu!" Inji Nana domin ta shirya sai Hajiya ta biya abinda Abdul Majid ya aikata musu.

Suna da kudi suna da karfi, Majid ba xai zubda musu kimarsu ba. Don haka suka hana Hajiya tafiya, suka sakata a gaba. Shima Majid din kin tafiya yayi yana tsaye a kofar gidan, yana jiran ganin ko Aryan ne, suna can Alhaji Mamman yasa Hajiya a gaba da cin mutuncin, har aka gama bikin cikin kuka take, karshe ma turawa maradi yayi aka rufe gidan wai kada Majid ya tafi can ya zauna.

Shi kuwa rubuta wasika yayi ya bada aka kaiwa Hajiya da ban hakuri,

Bayan tafiyarshi da wata biyu, Alhaji Mamman ya yanke mata rabin wahala ya sakata a gaba ta fara zuwa aikin kamfaninshi. Da iliminta da kokarinta ta fara aiki inda ta fahimci wasu na azurta kansu da dukiyarshi, don haka ta fara aikin binciken anan ta gano har da hannun Alhaji Haladu da Kamilu. Ta mika mishi duk wani abinda ta

tattara, sannan ya ce mata. "Ki saka Yaranki a gaba su koma makaranta, naji ance wancan dan mahaukaciyar, likitanci yake karantawa. Tow sai ya cigaba amma ya sani ko ya gama karatun anan zai yi aiki xa a fara gina mishi asibiti."
Zuwa yanzu baya shakkar mutuwa dama abinda yake so ya samu, Yaran hajiya zasu iya tsaya mata, duk da yasan yayi kuskure amma a yanzu yana da damar barin mata kome domin shima yanzu ya san girma ya cimma shi.
Majid da y koma sai da yayi jinya, a haka yake karatu, bayan wata uku aka kawo shi har marad'i, don bai san waye akanshi ba, abu daya yake faɗa sai na kashe ka idan ka tab'a min Mamata. Hajiya bata iya ganinshi a wannan halin ba, kamar an mata bushara ta wuce da shi wurin danginta,. A can ya zauna har ya samu lafiya sannan aka yi cuku-cuku ya dawo nan da karatu, amma abin ya zame mishi cutar damuwa dan mental health ɗinshi ya tabu, don ma Kakanshi yana tsaye akanshi da sauran dangin Mamarshi haka yasa shi ya boye yadda yake shan wahala, ya cigaba da karatunshi....
Bayan shekaru bakwai.....
#Dambuje
[2/18, 11:33 AM] Cutie cutie pie: *BAKꞮN HAURE....□□*

{Greed for Money is the roots of all evils□}
Arewabooks:maidambu41
Wattpad:Mai_Dambu
Mallakar:Mai_Dambu
017
Bayan shekaru bakwai.
Duk da wannan shekarun zaka dauka Hajiya ta huta daga jidalin dangin Alhaji Mamman Ba'are, amma ina domin bala'in ya kara hauhawa ne bayan Alhaji Mamman Ba'are ya nad'ata sabuwar shugabar kamfanin ya sauke wanda yake kai ya dorata, ai kuwa sai gashi fitina ta kunno kai, daga kamfanin har gida bata da sukuni.

A lokacin ko barci neman gagararta yake, wata irin wahala take sha da kamfanin Mamman Ba'are, gashi yadda ta tsaya ba ƙaramin bunƙasa kamfanin tayi ba, domin idan har kana son gane yadda kamfanin ya cigaba tow ka shiga office dinta, ita da Aryan suke tsara duk wani cigaba dake Allah ya taimaka shi mutum ne mai kwazo kamar Abdul sai gashi ya hada karatu da aikin da yake taya mahaifiyarshi, duk da wannan jigilar bai hana idan ta koma Nana ta sauko ta shiga gaya mata magana marasa dadi ba, ana cewa idan duka yayi yawa na kai ake karewa tow ita Hajiya baki daya da ta ko ina kare dukan take, sannan Yaranta tsayawa tayi akansu, domin idan ba haka tayi ba Yaran so ake a lalata mata rayuwarsu.
A cikin shekaru bakwai din nan, suka tafi bikin gama makarantar Abdul Majid, wanda kana ganinshi kaga babban mutum, sai dai har yau yana nan babu sakewa kamar baya, ga shi nan dai amma yanayinshi zai nuna maka yadda yake jin babu dad'i a cikin mutane. Haka aka gama a hanyarsu ta komawa gida ne, Hajiya ta amshi takardarshi. "First class, Alhaji ka fito da shi amma baka farinciki." Yake yayi ya ce mata. "Ya Amaan yake?" Ajiyar zuciya tayi tana kallon Aryan da Jamilah da kowannensu yayi tsaki. "Yana lafiya." Ta fada tana son ta manta da abinda Amaan din yake mata. "Hammayo yaushe zaka dawo gida?" Shafa kan Anisah yayi yana faɗin. "Zan dawo." "Ka dawo ko Hamma Amaan zai daina saka Hajiya magana, shi ba karatun ba, shi ba aiki yake ba. Sai dai kullum a bashi kuɗi. Hajiya tayi magana har ta gaji "
Bai ce mata kome ba, shi dai ba zai je Nijar ba, wallahi ko a kai za a kai shi ba zai je ba. "Hmm tayi hakuri ta cigaba da addu'a."
"Ba zaka dawo gida ba!" Shiru yayi bai ce mata kome ba, zata kuma Magana Aryan ya ce mata. "Nisah ya isa haka, Hammayo ya gaji." Ya faɗa yana kallon Abdul Majid din, dake su sun iya turanci duk haka suka juya harshen turanci. A hankali Aryan yake tambayarshi me yasa ba zai dawo gida ba.

"Kawai ba kome, zan tafi karatun sanin makaman aiki a Nijeriya ne "
"Amma.". "bana son hayaniya don Allah." Hajiya tasan halin Yaranta, kowa da irin nashi hakurin, amma hakurin Majid daban ne, haka fushinsa daban ne kuma zai iya hakura da kome musamman idan akwai wulakanci da cin mutuncin. Haka suka iso gida, Innarsu kanwar Hajiya wato Kabo wacce aurenta ya mutu take gida dauke da karamar yarta mai suna Zaytoonah. Yarinyar suna shiri sosai da shi, yana shiga ta tare shi da kyaututtuka masu yawan gaske. Tana murmushi ta ce mishi." Hammana ina tayaka murnar kammala karatun ka!"
Amsa yayi yana faɗin. "Na gode dear!" Daga haka suka wuce ta tsaya tana kallon Aryan da yake mata dariya. "Hamma Aryan dariyarka kamar gwalo kake min"
"Tow Allah ya baƙi hakuri, ina Nabeeha?" Murmushi tayi ta ce mishi. "Ka bani cin hanci dai na kira maka ita."
"Ok idan na shawo miki kan shi fa?" Murmushi tayi ta ce mishi. "Karya kenan domin kuwa zuciyarshi da kiyayya ta ginu, duk macen da zata samu damar kutsa kai cikin zuciyarshi mace mai Sa'a ce, mu shiga ciki zankirata."
Shi kan Aryan tausayinta yake ji, duk da ba bata wuce sha uku ba, yarinyar tana da hankali da nutsuwa, kuma kowa yana musu kwadayin zama ma'aurata, domin ahalin Sheikh Aliyu Wodabbe, suna da nutsuwa da hankali uwa uba Ilimi idan Yaro yayi magana ba zaka dauka shi yayi ba, domin an samar mishi nutsuwa tuntuni.
 Bayan isha Nabeeha tazo suka sha hira, sannan ya rakata bangarensu, waye zai ce wannan haɗin bai mishi ba? Ai babu kaf gidan domin soyayyar da sukewa Sa'a na musamman ne, shi yasa suka dorawa Abdul Majid wata irin kauna.
Bayan sati suka koma Nijar, suka cigaba da abinda yake gabansu. Shi kuma Abdul ya gama abinda zai yi ya dawo Nijeriya domin a can Nsukka yayi course ɗin shi na likitanci, wani ikon Allah sai gashi ya dace. Ana yaye shi aka tura shi asibitin Malam Aminu Kano, anan ya fara Internship ɗinshi. Yana tsaka da aikin ne aka fara diban sojojin sama. Yayi join amma suka ki amsarshi. Saboda wasu takardun shi, sau uku yana gwadawa amma baya samu karshe sai suka makale a bayan matsalarshi na cewa idan ya shiga damuwa zai iya kawo musu matsala a yanayin mental health din shi. Haka ya hakura da sojan sama, yayi apply na kasa shima ya makara, haka ya hakura wata shekara kamar wanda aka ingiza shi ya cika sojan ruwa, wani ikon Allah yana tura takadunshi, suka yi approved.

Amma a lokacin suka bukaci suga iyayenshi, kamar ba zai je Nijar ba. Amma haka ya tafi wurin Alhaji Abubakar Abzin, ya gaya mishi. Shiru yayi sannan ya ce mishi. "Dole Mamman ya tsaya maka." "A'a ni bana bukatar taimakon shi, kawai kai ai ka wadatar."
"A'a dole ya ga matsayin da ka taka, duk da nasan wata rana haka zai faru dole a bashi matsayinshi na uba."
 Haka Alhaji Abubakar Abzin ya tawo har Niamey, ya gayawa Alhaji Mamman Ba'are abinda yake faruwa. "Amma har na kusan gama.aikin asibitin yaron nan zai dauko wani zance?" Ya fada a harzuke, wai ma girma ya cimma shi. "Baka da iko akan karatun shi, lokacin da nake gaya maka ka janyo danka a jiki ki kayi, yanzu kuwa ya tsaya da kafaffunshi kace ya dawo jikinka, shi wancan da kake hidima dashi har yau babu cigaba jikinka ne?" Shiru yayi, Alhaji Abubakar Abzin ya mishi tass, haka yasa bayan kwanaki ya tawo har kano shi da Hajiya, duk yadda Hajiya taso ta janyo ra'ayinshi ya dawo ga asibiti ki yayi ya ce mata. "Babu dukiyata a cikin asibitin, ni nawa zan nima don Allah ki kyale ni na cika mafarkina." Alhaji Mamman Ba'are yana jin shi, amma bai ce kome ba dukiyarshi ce wato Majid yake kyama? Wani irin kuskure yayi ne haka? Lallai Majid shine magajin GOLDEN EMPIRES, shi daya zai rike da zuciya daya domin babu buri ko kwadayi a ranshi.
"Zan biya ka miliyan goma duk wata kazo ka taya mahaifiyarka aiki." Juyawa yayi ya kalli Alhaji Mamman Ba'are, ya saki murmushi ya ce mishi. "A'a bana bukata na gode."

"Abdul Majid ka manta da kome, ka dawo zan bar maka kamfanin BA'ARE GOLDEN EMPIRES " juyar da kai yayi yana murmushi. "Da kake gabar mutuwa ko? Hmmm wallahi idan na cire ahalina mahaifiyata da yan uwana har duniya ta nad'e bana fatan had'a alaka da dukiyarka, rayuwarka ka saka ka nimo dukiyarka nima rayuwata zan saka na nimo tawa. Hajiya ki gayawa Mijinki ya daina shiga rayuwata." Daga haka ya mike, ya nufi can wurin da aka saka water dispenser, ya dibi ruwan ya sha, sannan akan lokacin aka ce su shiga, koda suka shiga cikin dakin. Suka tattauna a lokacin da ake gaya musu sharudan aikin da sauransu, sannan sunan da yake jikin takardunshi yasa masu daukar sojoji a matakin farko yasa yake son ganin da gaske ne shi ɗin, family mahukuntan kasar nijar ne. Takaici yasa Majid cewa. "Sir ban nemi aiki a matsayin dan Mamman Ba'are ba, na nima ne a matsayina na dan Nijeriya kuma farar hula, bani da alaka da nijar." Juyawa hajiya tayi ta rufe mishi baki. "Me yasa baka jin magana ne?" Kwafa yayi cikin fushi ya ce. "Na fasa aikin ma." Ya juya zai fita, Alhaji Mamman Ba'are ya ce mishi. "Asibiti ko kamfani ina zaka yi aiki da su." A fusace ya juya zai magana Hajiya ta tsinke shi da mari, rike kunci yayi yana kallonta. "Wannan rayuwarka ce, va zan maka dole ka san daidai ba, amma ba zan matsa maka kayi aiki a ko daya daga cikin kamfanin Ba'are ba, ka tsaya akan ra'ayinka anji kai jinin ba'are ne, so what? Duniyarka zaka gina sai kayi fushi da damarka? Waye kai? Oya wuce kayi sign kai ba bawa bane, mutum ne mai ra'ayin kanshi don haka ka tafi aikinka Allah ya baka sa'a."

Haka yasa shi amsar kome cikin dadin rai, Hajiya tana tare da shi bayan sun fito, Alhaji Mamman Ba'are ya ce mata. "kin nuna min bani da iko da d'ana kenan?" "Me yasa lokacin da yake bukatarka baka damu da shi ba? Sai yanzu da kasan iya shi zai iya rike sauran abubuwanka. Nima ajiye maka aikinka zan yi na gaji zan koma wurin dangina."

A matukar tsorace yake kallonta, bayan Majid ya fito. "Kina nufin zaki juya min baya kenan?" "Hajiya muje!" Uffan bata ce mishi ba, haka suka tafi gidan da yake haya shi kuma Alhaji Mamman Ba'are ya wuce hotel, tunda ya isa can ya fadi rike da gefen kirjinshi, a kayanshi aka samu passport dinshi da hoton Majid da wasu abubuwan, haka aka wuce da shi asibiti. Sannan a nan suka shiga niman Abdul Majid a cikin asibitin, dakyar duka samo shi, koda ya zo kanshi bai wani girgiza ba, kawai dai ya tsaya duba wasu daga cikin tests din da aka bashi, anan suka yi magana da daya daga cikin likitocin. Ya ce mishi."Doctor kasan ya auna arziki?" Sosa kanshi yayi yana kallon Likita. "Ban gane ba?" "Hmm guba ne a cikin jininshi, wanda yayi yawan da." "Bar zancen haka, Allah ya bashi lafiya." Daga haka yaki yarda ya amince da sauran bayanan amma tabbas yasan abin da Alhaji Mamman Ba'are ya shuka shi ne zai girba. Ya je har gidan shi ya tawo da Hajiya ko ita bai yarda ya gaya mata ba, sai a bakin likitan taji. Wani irin tsoro ya cika mata zuciya. Tow Yaranta da suke can waye zai kare mata su. "kina tunanin su Anisah da Jamilah ko? Ai su ba za a musu kome ba, koda za'a yi sai don a kuntatta miki ta hanyar niman wani abu, amma ba wai don tab'a ki ba." Kwanan shi uku aka sallame shi, suka wuce nijar.

Tunda suka koma jikin Alhaji Mamman Ba'are ya ki,asalima jinya ya kwanta inda aka kwantar da shi asibitin da ya ginawa Majid a can yake kwance. A hankali jinya tayi jinya domin ya kai sama da shekaru biyu a kwance, har wannan lokacin bakin shi bai daina kiran Majid ba, yazo ya yafe mishi. Dakyar Hajiya ta samo shi A Lagos yazo ya ganshi a ranar da yazo yake gayawa Lauyan shi. "Kuri'ata na barwa Abdul Majid Mamman Ba'are, akwai wasu kamfanoni na guda uku da asibiti duk da sunan Majid Mamman Ba'are na ajiye su, lauya ka rubuta a matsayin wasiyyar da na bari, Abdul Majid Mamman Ba'are, ka yafe min." Dauke kai yayi yana latsa wayarshi ya ce mishi. "ai ban kullace ka ba, don haka Allah ya baka lafiya " daga wannan ranar Majid ya bar Nijar dama kwana uku aka bashi, ya bar musu kome nasu kai ko ruwan gidansu baya sha, sannan ya gayawa Hajiya matukar ba ita zata yi girki ba, kada ta sake Yaran su ci abinci daga wani waje don kashe su za ayi.

Daga lagos tura shi cotonou aka yi, a lokacin jikin Alhaji Mamman Ba'are ya kara rikicewa sannan ana ta nimanshi, a lokacin yana can teku Hajiya tayi sintiri ya kai sau uku. Babu labarinshi. Bata jima da dawowa ba, Allah ya amshi rayuwar Alhaji Mamman Ba'are, ya rasu ya bar wani irin tukekken rikici, domin bayan rasuwarsa, yan uwanshi da Hajiya Tani suka ce da kason su a cikin dukiyarshi.. sannan wasu suna jin haushin Majid domin gani suke saboda son da Alhaji Mamman Ba'are yake mishi ya mutu domin an ki fadar asalin abin da ya kashe Mamman Ba'are.

Ana cikin wannan tashin hankalin har aka kai shi makwancinsa ana rikici. Bayan anyi Addu'ar bakwai sannan aka fara batun gado, domin sai da aka kira Alhaji Abubakar Abzin, sannan aka fara rabon matanshi da suka mishi takaba aka ware musu nasu, sannan aka koma kan Yaranshi mata da maza aka raba, wasa wasa sai ga Hajiya ta tashi da wani irin kaso saboda ita Yaranta maza ne, sai Hajiya Rabi da itama ta samu ba laifi amma ina gani ake kamar da gayya aka tulawa Hajiya Sa'adatu.

A hankali Lauya ya fitar da kuri'ar kowa ya bashi, da sunanshi sannan ya cire na Alhaji Mamman Ba'are ya ajiye a gabansu. Wannan na Abdul Majid Mamman Abdul Majid ba'are ne, har aka gama raba kome ba a kira sunan Tani ba, nan tayi tsalle ta ce musu. "Shi Sajjid bai da kaso ne?" "Saurin me kike? Akwai kamfanin da take shigo da man fetur kasar nan, ita ce Alhaji Mamman ba'are ya bashi gashi nan." Ya tura mata. "Ban gane ba asibiti da mattan man fetur da ya gina fa?"
"Mallakar Majid Mamman Ba'are ne?" Sakin baki tayi tana kallon kowa. "Sajjid shima fa jinin shi ne." "Ta ina ya zama jininsa? Mamman Ba'are yana da yara talatin da biyar, biyar din kai sune Yaran Sa'adatu, sauran ashirin Yaran, Rabi, Fauziya, Harirah. Yaran rabi goma sha daya, Hajiya Fauziya goma sha biyu, ashirin da uku sun tafi, Yaran Harirah bakwai da dan karami auta. Lissafi ya fito?"
"Eh!"
"Tow bamu ji labarin ya kuma aure ba, domin ko Sa'adatu da ya aureta ya faɗa ke kuma a ina kuka yi auren?"
"Bai gaya muku Ni dadiron shi ba ne?"
"Eh koma meye Muslunci ba zata bawa danki gadon shi ba, domin duk wanda suka ci gado ya halatta a gare su."
"Ban gane ba?"
"Su aure ya basu uba, ke kuma dadiro kuka yi aka same shi, ba dan shi ba ne danki ne ke ɗaya "
Wani irin abu taji ya dake ta, tun daga ranar ta hana kanta sukuni ta saka masifa da bala'i a ranta, ta hada kai da wannan ta hada kai da wannan burinsu ace za a sake raba gadon, sannan har bincikan jini sai da taso a ciro gawar Alhaji Mamman Ba'are ayi domin a halatta Sajjid Mamman Ba'are akan dan shi ne Amma abu yaci tura. Don haka ta samu mutanen gidan ta basu shawarar saka hannun jari a kamfanin idan kudinsu yafi na Hajiya da Yaranta yawa, sai su kwace kamfanin. Haka aka yi har Nana da take kan gangara ta zuba hannun jarinta.dukda dai tsufa ba shine mutuwa ba.

Dake ana bada na Abdul Majid Hajiya ta zuba nashi bakiɗaya, sannan kamfanin sa biyu ana aiki ana tura kuɗin, asibiti ma haka, duk bayan wata sai ayi rigima a board meeting. Dakyar ake shayo kan rigimar, bayan shekara daya da rasuwa Alhaji Mamman Ba'are Aryan yayi aure ya auro Nabeeha, aka sha biki a lokacin Nana ta ce kada Hajiya ta kuma shiga harkar jikokinta har ta yanke hukunci bata gaya mata ba, ita da aka ciyo a caca. Dake sun san Aryan bai da kunya, tass yaje har sama wurin Nana yace mata. "Hammayo bai wurgo ki ba, wallahi kika kuma shiga harkarmu sai na turo ki daga sama." Ya janyota har bakin matakalar. "Sake ni mara mutunci, idan kace na fita Harkar uwarka zan fita ba sai ka kashe ni ba." Tun daga lokacin suka samu salama.
***

Bayan shekaru biyu da rasuwar Alhaji Mamman Ba'are, kamar wanda aka mishi kiranye, kuma ai kusan haka ne domin Hajiya ta hana idanunta barci akan Yaranta. Addu'a ba dare ba rana ga kome ta samu amma kuma kan Yaranta a watse, sannan a wannan lokacin ita ce me yara kanana, sannan tana cikin wani irin tashin hankali Sajjid ya saka Anisah a gaba. Ta rasa me yake nufi da ita, tayi mishi magana ya ce ta sa a dakatar da shi, da ta gayawa Amaan budar bakinshi ya ce mata. "Hajiya ki saka idanu akan Yaranki mata, kada kina can kina niman kudi da barci wasu su lalata musu rayuwa " sai da ta shiga tsakaninsu domin dambe suka so yi da Aryan abin ya mishi ciwo.

Wata laraba kwatsam sai ga Majid, lokacin Sajjid ya biyo Anisah wacce ta fito wanka daga ita sai towel, tana ihun niman ceto sai dariya ake mata, shi kuma da abokanshi sai ihu suke. Ranar da kayan shi na aiki ya shigo yaga yadda Sajjid yake kokarin jan towel din. Jan get din gidan yayi ya rufe, sannan ya dauki wani dutse ya jefi Sajjid din sai da ya fadi can gefe. Juyawa tayi ta hango Hammayo, da gudu ta rike towel din ta nufe shi. Rungumeta yayi yana faɗin. "ya isa haka." Ya janye ta, tare da cire rigar jikinshi na kakin soja ya saka mata.

"Wuce part din Hajiya!" A tsorace ta wuce, wato ba zaka san soja wala imani ba, sai da bawan Allah nan ya rufe idanu yayi ta zane su da duk abinda ya zo hannunshi. Ya kwabe Sajjid zigidir ya mishi dukar kawo wuka, Hajiya Tani zubewa tayi tana faɗin. "Idan ka kyale shi wallahi ba zai kuma kulata ba."

"Tani ni bana son ya daina kulata, don Allah ya kulata ni zan kula da lamarinshi."

"Nana ki bashi hakuri don Allah ya yafe mishi ba zai kuma ba." Wato dukar da Majid yayiwa Sajjid yasa baki daya kowa ya shafawa kanshi ruwan sanyi, domin Hajiya ta haifi zaki, shima kuma Sajjid ko ba a ce mishi ya fita harkarta ba, ba zai kuma shiga harkar nata ba. Don haka ya rufawa kanshi asiri bayan ya kyale shi, ya koma part dinsu, ya same ta ta saka kaya. Tana takure a wuri guda sai kuka take. "Me yasa baki tafi makaranta ba?"

"Bani da lafiya ne!"

"Kina da saurayi?" Gyada kai tayi, "Jamilah fa?" Tana da shi." "Kice mishi yazo ya samu Alhaji ayi magana" domin bai san Alhaji ya rasu ba, kuka ta kara sosai sannan ta gaya masa Alhaji ya rasu ana niman shekaru uku kenan. Jikin shi yayi sanyi. Amma kuma sai bai nuna ba, sakata yayi a gaba suka tafi kamfanin, a can suka bude farinciki, bai gayawa Hajiya kome ba domin ya gargad'eta kada ta faɗa.

Daga kamfani gida suka dawo da ake gaya masa abubuwan da aka bar mishi. "Ni dai na yafe dukiyar Mamman Ba'are"

"Baka isa ba!" Haka suka dawo gidan. Kallon gidan yayi sannan ya cewa Aryan. "Gidan a warewa kowa wurinshi baka san me wani yake yi ba haka zai saka kowa ya zauna lafiya babu saka ido ko cin zarafi. A cikin dukiyar da ya bari a ware part din hajiya a zagaye shi ina son ayi aikin nan da kwanaki arba'in."

"Tow ina Hajiyar zata?"

"Zata wuce garinsu, hutu na samu na wata biyu, don haka tafiya zamu yi sannan ka samu me niman Jamilah da Aneesah, su nufi Agadaz, su nime aurensu."

A gaban Hajiya aka yi kome, wani abu da Hajiya tayi ta karawa kanta kima shine, dangin Alhaji Mamman Ba'are, bata yarda ta ki su ba, binsu take har inda suke take takai har Hajiya Latifah mahaifiyar Mohan(Bororoji) tana zumunci da ita, sannan yana zuwa wurin Hajiya Umamata mahaifiyar Khalil Dan Ba'are,. Haka yasa suka tura su wurin Ibrahim Dan Ba'are, mahaifin Khalil Dan Ba'are.

Bayan masu niman auren sun gabatar da kome daga can, Aka kira Aryan aka gaya mishi an kai har da sadaki, ya ce tow ya gayawa Abdul Majid. Daga nan garinsu Hajiya. Basu bi tanka Amaan ba, suka yi tafiyarsu domin Hajiya ta gaya mishi, ya ce ba zai je ko ina ba, wato Amaan shine matsalar dakin Hajiya munafiki. Duk da uzurin da Hajiya take mishi baya gani.

Watan su daya da rabi suka dawo an gama gyaran gidan har an zuba kome na gidan, daga cikin gidan zaka shiga asalin cikin gidan baki daya, shi dai Majid ya ware layinsu baki ɗaya don abin da yake faruwa babu wanda ya shiga musu. Bai bar kasar ba sai da aka yi bikin kannenshi, sannan ya saka Aryan ya dawo da Matarshi kusa da Hajiya inda shima ya cire flat me kyau aka mata, suka zauna lokacin tana goyan d'anta Abdul.

Tunda ya bar kasar bai kuma waiwayonta ba, tsawon shekaru shida. A wannan shekarun babu ranar da Hajiya ba zata tafi niman shi ba, ko tasa a nima mata shi ba, sai gashi wannan karon Aryan ya dauko mata shi a kai.

Wannan shine labarin Hajiya da Yaranta.

Mu dawo labari.

Sansanin Yan gudun hijira..

Wato kun san meke faruwa a cikin sansanin gudun hijirar da muke kuwa? Hmmm wato wani murdadden al'amari ne, adamawan Kamaru tana iyaka da Nijeriya da nijar ta yamma, sannan ana smuggling na kwayoyi safara da yara da mata, wasu ana tura su cikin kamarun, wasu kuma a tura kasashen Afrika da turai.

Sannan babban wani abun mamaki ta hannun Uwar mugu ake wannan aikin, sannan asalin miyagun kwayoyi da makamai, ana shigowa da sune ta nan ana shiga da shi Nijeriya da nijar.

---- Kwana muka yi muna hira da Zuzu da Ummi Addah bata dawo ba, sai wurin asuba ta dawo tana kuka wiwi. "Addah lafiya!"shigowa da Munaisah aka ayi dakin kamar bata da lafiya ko taci duka. "Allah yayiwa Nenne rasuwa?" Tashi zaune mukayi. Murmushi Ummi tayi ta ce mata. "Hankalinku ya kwanta "

"Me kike nufi? Babu kowa a wurinta sai Munaisah naje domin na tayata zama ne!"

"Ya isa Addah" inji Zuzu, wallahi duk sun saka ni cikin duhu. "ina gawar?" "Tana can ana mata sutura" nida Zuzu muka fita, Ummi ta kalli Munaisah ta ce mata. "Daga nan karatun daya ce har birnin lantsandaal, kin biyewa Addah kun kashe Mahaifiyarki, ki rubuta ki ajiye. Addah sai ta ci amanarki wallahi kuwa sai ta saka ki kuka lokacin babu Zahra da zuzu, matukar zata sayar da Yarta ke din banza ce ba zata iya miki butulci ba. Na tausaya miki matuka gayya."

Tun bayan an yi jana'izar aka kaita makwancinta, da zamu koma Balali ya kirani ya ce min."don Allah ina son magana dake."

"Ok me ya faru?"

"Ki saka idanu akan matar da take dakinku da ita wancan me cikin." Hadiye yawu nayi, na ce mishi. "Lafiya kace haka?"

"Kiyi hakuri anan sansanin tunda wancan gayen yazo tow wallahi numfashin ki ma da zai saya tow tabbas zai saya ya samu kuɗi."

"Me zan iya yi?" D'ago kai yayi ya ce min. "Jeki zan baki sako!"

Haka na juya na tafi sai lokacin na lura ashe Uwar mugu ya gani. A hankali muka hadu da ita ta ce min. " Me yake gaya miki?" Murmushi nayi nace mata. "Ta'aziya yake min."

"Bayan nan bai ce wani abu?" Girgiza kai nayi nace mata. "Haba bai ce kome ba!"

"Zahra'u kenan! Mu shiga ki karya." Girgiza mata kai nayi ina faɗin. "A'a na koshi."

"Muje mana, ko an gaya miki wani abu ne?" Ganin tana son daura zarginta akan Balali yasa ni binta har dakinta, muka zauna ta shiga zuba min abinci da kayan ciye-ciye. Duk abinda ta zuba min sai da na raba biyu tana kallona, tana gamawa na ce mata. "Muci tare."

"Kin xata zan saka miki guba ce?" Girgiza kai nayi nace mata."ko daya kawai muci tare wannan zan kaiwa Zuzuna."

"Tow muci" haka muka ci tare da ita, sannan na mike ta kara min abincin. "Kina da wani irin kyau, kiyi amfani da kyan nan mana." Girgiza kai nayi nace mata. "ai kyauwa na muni ne ga wancan abin"
"Kina son zuzu ko????????? "
 □□Me ya kawo irin wannan tambayar... Jama'a me uwar Mugu take nufi.
#Thedambuje
[2/19, 12:21 PM] Cutie cutie pie: *BAKIN HAURE....□□*

{Greed for Money is the roots of all evils□}
Arewabooks:maidambu41
Wattpad:Mai_Dambu
Mallakar:Mai_Dambu

Assalamu alaikum barkanmu da warhaka da fatan kuna cikin koshin lafiya, karku manta da wannan Kamfani mai albarka mai kawo muku kayan bukata cikin sauki da Aminci da Inganci.
Wato TA RASULU MULTIPURPOSE. YA SAKE DAWO MUKU DA KAYAN NAN MASU ARMASHI DA DANDANON KOWACCE MACE TAURARUWA CE.

_____
MARKADADDIYAR GYAD'A
HADADDEN KAYAN SHAYI
GARIN KOSAI NA TAFI DA GIDANKA.
GARIN TUWO
GARIN KUNU YAR ASALI
CURRY ME DADI
SPICES
TYME
YAJIN DADDAWA ME KYAU
GARIN DAN WAKE
JAN YAJI MAI DAD'I...

_____
BUGU DA KARI MUN TANADAR MUKU DA KAYAN FITAR SALLAH DA NA SHAGALIN SUNA DA BUKUKUWA.
ATAMFOFI, LESHINA, MATERIAL, SHADODDI, YADUDDUKA NA MAZA DA NA MATA, JAKKUNA DA TAKALMA.
WANI ABIN SAI KUN ZO TA RASULU MULTIPURPOSE DOMIN KASHE KWARKWATAN IDANU.
ZAKU IYA TUNTUBARMU A WADANNAN NUMBOBIN.. 08086639163 - 09030168590....
MUNA DAKON SAYAN DAI-DAI KO SARI.....

018
"Na'am me kike ce?" Na kalleta cikin son fahimtar me take nufi, murmushi tayi tana kallona. "Kawai naga yadda kike damuwa da ita ce ko mahaifiyarta bata damu da ita haka ba, kin ga wannan wuri da kike kowa ta kanshi yake, ki ajiye wata Zuzu ki kama Harkar gabanki yafi miki."
"Ban damu da ko waye bai damu da zuzu ba, amma ni a raina na damu da zuzu. Sannan ba zan dauki wani ya dora ni akan hanyar da ba zata bulle min ba,, idan Addah ta gadama ta kula da rayuwar Yarta idan bata gadama ba, ta barta tai yadda take so. Ke da ita baku isa tilasta ni yin abin da ban shirya ba, idan kuma kina ganin zaki iya Bismillah. Har karshen rayuwata ba zan daina tsayawa a bayan zuzu ba kin ji na gaya miki sai ki san nayi." Daga haka na juya tare da barin mata dakin ko abincin ban dauka ba.
"Abincin da kika bar min fa?" Ban juyo ba, na ce mata. "Kece idan baki ci ba zaki mutu, ni kuwa ko banci ba zan rayu matukar Allah shine rayayyen nan da baya mutuwa."

Sannan na sa kai zan fita, ta kuma ce min. "Kada ki d'aga kafarki domin zan iya aikata kome." Juyawa nayi na kalle ta dariya nayi nace mata. "Ni ban san tsoro ba, ki gaya min taya zan san tsoro bayan akan idona aka kashe min dangina? Gaya min tsawarki bai wuce haushin dan kwaikwayo ba. Ni gurnanin fitar rai naji kin ga kenan babu abin da zai bani tsoro bayan nasan ina raye ne ko na mutu don Allah, ko a kashe ni don niman duniya." Daga haka na bar mata gidan, Yana kwance yana jin duk abinda suke fada, a ina aka samu yarinya me zuciya haka, Aina'u ya kalla da take ta sharar bacci, ya mike zaune yana mika, kirjinshi cike da gargasa ya dauki dogon wandonshi ya saka. Ya fito inda Uwar mugu take zaune tana mamakin maganganun Zahrah. " A ina kika samo jar wuya haka?" "Yan gudun hijira ne da suka taso daga Nijeriya, za akai su sansanin gudun hijirar hadin gwiwa da na Nijeriya yaranmu suka karkato mana da su nan, Yaran jiya da ka gani duk daga can suke."

Shafa kanshi yayi yana faɗin. "Yarinyar ta iya jefa citta a bakin mutane, ban tab'a jin yarinyar da ta gaya miki gaskiya haka ba." Sosa kanta tayi tana murmushi ta ce mishi. "Eh ai bata da kunya ko kaɗan. Haka yar Ubanta take fama da ita, taurin kai ne da ita kamar arnan dutse."

"Nawa aka samu domin ina son wucewa da shi kafin lokaci ya kure min." Sunkuyar da kai tayi tana faɗin. "Ba a wani samu dayawa ba, amma zaka iya zuwa wurin ajiyar zaka ga iya wanda muka samu." Gyada kai yayi yana faɗin. "Duk bayan wata shida nake zuwa amma ace iya wanda na samu kenan? Babu waɗanda suke jinya ne?" Kasa tayi da murya tana faɗin. "Allah ya baka hakuri, akwai Aina'u anan!" Shiru yayi kafin ya ce mata. "A nemo min nan da sati xan wuce na gaya miki."

"In sha Allah, amma akwai yaron nan Balali da Dilla ya kawo mana shi, yana son ballo mana ruwa."

"Ki saka a kawo min shi naji hujjarshi na lalata min dagiya ta."

"Yarinyar da ta fita suna tare."

"Nace a dauko min shi, ita kuma a tadata tabar min daki kafin fushina ya sauka har kanta." Da sauri ta nufi dakin ta tada ta, suka fito domin idan ya fadi haka rashin Imanin shi ya motsa kenan. Tana fita ta nufi kofar da su Balali suke aiki, ta ce. "Ku rufe kofar nan." " Tow!" A take suka rufe ta ce musu."ku kama min dan iskan cen ku kaiwa yallabai."

Bai gudu ba, ya tsaya suka kama shi har gidanta, ajiye shi aka yi gaban shi. Kanshi a sunkuye. "Kai me ya haɗaka da yan matan da suke wannan sansanin?"

"Ayi hakuri yallabai ba zan sake ba." "Hmmmm ba zaka sake kula su ba ko ba zaka sake wani abu ya fita daga bakin ka ba." "Dukka biyu yallabai." Gyada kai yayi yana faɗin. "Idanuna yana kanka, nan da sati biyu zan bar nan ka sake wani abu ya faru." Wata ƙatuwar wuka ya ciro, yana wasa da ita kafin ya ce mishi. "Da shi zan kashe ka."

"In sha Allah, ba zaka kara kama ni da wani laifi ba."

Haka ya bada hakuri sannan aka kyale shi, wani abin mamaki murmushi mutumin yayi bayan ya fita. "Me yasa baka kashe shi ba?" "Akwai abin da na karanta shi me dabi'ar Dilla ne bada hakuri akan kuskure wanda ya aikata da wanda bai aikata ba, wannan yaron dila ne. Kin san dai wannan wurin an gina shine da ra'ayin mutane mabanbanta, shi kin san aikinshi da abinda yake so, ni kin san aikina da abinda nake so, idan na ce zan kashe shi. Zan lalata goma daya bata gyaru ba, madadin na kama shi sai nayi rashin sa'a.

Dilla baya shan ruwa haka kawai sai da wutsiyar shi, idan har zai ajiye wani abu nashi tow duk yadda akayi ina iya jiyo kamshinsa domin yana nan kaɗan damu."

"Kana nufin yana kusa kenan?"

"Kin san waye Dilla?" Girgiza kai tayi ya ce mata. "Dilla ita ce dabbar da bata kwana a ko ina sai a tsakiyar busashen ganye, domin ko fara ne ya fada kan ganyen zata farka, Dilla bata kamuwa ta dadi sai da tarko. Don haka maharba basu iya kamata sai sun saka mata tarko."

"Tarko kuma?"

"Eh tarko ita ba a kamata da nama, ko abinci duk abinda tasan baya samuwa a daji bata cin shi, tarkon dilla na musamman ne domin raga ake watsa mata."

"Na gamsu Yallabai, amma taya zamu iya kama shi?" "Ai shi baya buƙatar tarko."."ban fahimta ba?" Mikewa yayi ya nufi dakin, ya watsa ruwa ya fito yana me zama ya ci abinci, bai kara magana ba kuma ita Uwar mugu tana son jin shirin Yallabai akan Dilla ne, tasan su basa shiri amma kuma bata zata al'amarin zai kai har haka ba.

Lokacin da na iso tantin mu, tsayawa nayi a waje ina jin shewar Munaisah da Addah, d'aga labulen nayi muka yi ido biyu da ita, gimtse dariyar tayi tana faɗin. "Allah sarki Nennena." " Ba sai kin yi min wasan kwaikwayo ba!" Na fada ina kallonta, shiru tayi tana kallona. "Wacce ta tsare miki gaba ta tafi, sai me? Daga nan sai ki daura daga inda aka tsaya." Na fahimci abu daya, daga Addah har Munaisah babu ruwansu matukar kudi zai zo musu wallahi zasu bada kome suka mallaka, kai hatta rayuwarsu da zasu iya sallama ta, tow kuwa zasu samu kudi da ita.

Sannan wani abin mamaki shine kudin nan gashi nan amma ban san me suke da su ba, zuzu tana kwance nace mata. "Yan mata kina jin yunwa ko?" "Jiranki nake ai ki zo kaina, Zahra'u yunwa nake ji." Mikewa nayi na hada wuta, sannan na yan yanka kayan miya, na soya shi sama sama."

"Zahra'u a saka kifi!" Duba wurin kayan nayi naga babu kifi."Zuzu bari na amso mana kifin!" Na karbi jakar kudina na dauki abinda nake da bukata, na fito waje. Gidan Uwar mugu na nufa, har na isa ban hadu da kowa ba, sannan kowani tanti shiru ya dauka, buga kofar nayi, ta bude. "Zahra'u me ya dawo dake?" "Kifi nazo saya." " Kin ga kuwa jiya da daddare Addah ta kawo min shi na bata kuɗi!"

"Ta kyautawa kanta!" Na mika mata kudin iya wanda nake so, ina jin Muryar shi me cike da Amo ya ce mata. "A maida mata wanda aka kawo a sayar a hada mata da kayan abincin."

"An gama Yallabai!"

"Kuma kada ki sake ki kara amsar kayan kowa inji ni!".

"Tow yallabai, maza ki mishi godiya." Ta ce min, "iya na kudina nazo saya." Na fada ina juya fuskata. "Ba zaki mishi godiya ba!" "Ni ba rokonshi nayi ba, shi yayi niyya kuma nace bana so dole ne?" Na fada Ina kallonta. "Yallabai!" "Bata abin da take so!"

Ya fada yana me juyowa yana kallona, nima kallonshi nayi na dauke kaina. Ban san yadda zan muku bayanin yadda yake ba, amma Kyakyawa ne dai-dai misali, sannan yana da sura irinta sadaukan maza. Amma abu daya da kwakwalwata taki mantawa shine yanayin surar Aminin duhu, har yau ina jin haka a raina. Domin kirjinshi a wani murde yake, tsokokin da suka cika kwanjin shi kadai abin burgewa ne. Dafe kaina nayi sakamakon jin kaina yana wani irin kuwwa. Sai yau na tuna da shi sosai, duk da zuciyata bata samu zarafin hasasho min shi ba, sai yau. "Baki da lafiya ne?" D'ago kai nayi na kalle shi, kafin na dauke kai ina amsar kayan hannunshi. "Mai kyau!" Ya faɗa kamar rad'a.

Juyawa nayi na bar wurin, ko ina da kyau Allah ya min tsari da hada shirgi da wannan abin kamar dodo. "Amma kada ki sake fitowa, domin tsarina ne." Shiru nayi ban ce kome ba, domin kuwa ba zan iya cewa komen ba, don naga yadda sansanin yayi kamar an yi shara. Haka yana nufin yana da karfin faɗa aji, ina isa tantin mu na ce musu. "Ashe yau ba a fita?" Sai lokacin Addah ta ce min. "Eh an gaya min jiya doka ce idan yana nan ba a fita." "Kuma Adda sai kika barta ta fita?" Zuzu ta mike dakyar cikin takaici. "Waye ya sani ko an shirya haka ne don a dauke Zahra din tunda yanzu anyi walkiya kowa yasan kowa."

"Allah ya tsare mana ita." Inji Zuzu, ina ga cikin nan ya karawa Zuzu masifa, domin faɗa tayi ta cigaba da yi, tana hararar Addah. "Na gaya miki ban da fada." "Ke kyale ni nayi magana, me aka yi aka yi son zuciya."

"Tow Allah ya baki hakuri!" Daga haka na tafasa mana taliyar da miya, na zubama kowa zan zauna uwar mugu ta shigo ita da Balali. Ajiye mana kayan yayi ya juya ya fita. "Daga yau kada wani ya kara kawo mana kayan Abincinsa."
"Hmmmm!"
"Inji yallabai ne, ba inji ba!"
"Tow ai bin na gaba bin Allah, ina zamu samu wannan kayan dadin naga har da madara."
"Na Zahra'u ce, ba na ku bane."
"Ikon Allah Zahrah an fara dan waken zaga ye ne?" "Ita ba haka take ba, domin har yau bata dagula kuruciyarta da sabon Allah ba " inji Ummi tana tattara kayan, wato na fahimci a dakinmu akwai wani irin yaƙi dake tsakanin Ummi da Addah, tsakanin Adda da Zuzu, sai suka saka ni a tsakiya, duk yadda aka kawo min duka zasu kare min, "kinji dadi Zahra sai ki saka idanu akan yan uwanki. Domin kada su kawo mana hayaniya."
Ta fada tana kallon Zuzu da Ummi da Munaisah da addah, ban san me yasa take yawan gaya min haka ba. "Na yarda da yan uwana, don haka ba zan sakawa kowa idanu ba. Kawai duk abinda kika ga ya faru tun can rubutacciyar al'amari ne."
"Gaskiya kan!" Inji Addah tana kasa da kanta, domin wani lokaci idan addah tayi wani abu yadda kasan mutuniyar kirki. Fita tayi ta barmu a wurin, na zauna naci abinci nima,

Haka muka ci muka koshi,bamu fita ba sai can yamma da aka ce mana zamu iya fita wanka, Zuzu da Ummi da Addah suka tafi, ya rage daga ni sai Munaisah, yadda bata ce min kome ba nima kuma ban saka ran xan yi mata magana ba, yadda take rayuwarta cikin nutsuwarta ba zaka ce uwarta ta mutu a ranar ba, domin ta warware kamar ba ita ba. Lashe bakina nayi ina gyarawa Yakumbo kwanciyar ta.
"Zahra'u!" Na juya a hankali ina kallonta. A hankali ta matso kusa dani. "Don Allah idan kin samu damar fita daga nan, ki nemi wannan number please Zahrah." Cike da Mamaki nake kallonta. "Murmushi tayi tana faɗin. "Zan fita mana, zan tafi nesa dake idan ina ganinki zan iya aikata mugun abu akan ki. A wannan wurin ba uwa ba d'a, kowa ta kanshi yake kuma zaka iya aikata kome saboda kuɗi. Fatana daya ki fita daga nan sansanin domin ba sansani ba ne, wuri ne na biyan buƙatar kai."

Baki daya sai ta kara min rud'ani, sama da wanda nake ciki ina muka kawo kanmu? Ina muke raye? "Munaisah me yasa ba zaki min bayani a nutse na fahimta ba?"
"Idan na miki ma ba zaki gane ba!" Muna zaune a wurin har su Addah suka dawo, Nima da ita muka fita, muka je wurin wankan, baki daya sai na kasa wanka na saba sai dare nake wanka,.don haka na juya ina faɗin. "Ke bani iya wanka sai dare yayi."
"Tow ai shikenan, ki je abinki." Haka na dawo na barta a hanya na hadu da Aina'u.
"Naji ance yallabai ya tura miki da abinci, tow wallahi na rantse da Allah ba zan dauka ba, itama wancan me kama da zabiyar sai naci B... Ubanta, domin ba zata kwace min masoyi ba, shegu Mayun kudi. Ki saka idanu ki ga abinda zai faru."
Rab'ewa nayi na wuce ina xan iya da haushin ta, don haka na koma tanti na kwanta. "Baki yi wankan ba!" "Wurin cike yake da mutane ba zan iya wanka a gabansu ba."
"Kuma dai!" Inji Addah.
Haka na kwanta muka yi ta hira har lokacin sallah yayi, sai lokacin Munaisah ta dawo. Kusan ma rikota akayi . "Me ya faru?" "Ita da Aina'u suka yi faɗa suka fada wuri me zurfi, ita kan ba a same ta ba. Sai Munaisah aka samu." Hadiye yawu nayi cike da tsoro domin nasan karshen mu yazo. Ihun Tumba muka ji tana faɗin. "Wayyo Allah na, kun kashe min fitilar dake haska min gabana wayyo Allah ka dawo min da Yarinya ta. Me tayi muku." Yadda take ihu yasa kowa jikinshi yayi sanyi.

"Me ya haɗa ku?" Kuka ta saka tana faɗin. "Ita ta tura ni wurin zurfi, kuma wallahi ban san cewa idan muka fada ba zata iya fitowa ba. Wallahi ban kashe ta ba"

"Hakkin uwa wasa ne?"
"Ummi ki daina kawo maganar Nennena a cikin wannan yanayin, don Allah."
Bakiɗaya sai na rasa bakin magana, d'ago kai nayi naga Addah tana murmushi, ban san me take nufi ba, amma tabbas murmushin mugunta ce zallah.
"Addah me akayi kike murmushi?" Na tambaye ta, ganin yadda ta firgita. Sauran ma duk suka zuba mata idanu ta ce mana. "Ni kuma? Akan me zan yi farin ciki da abinda ya faru." Bata rufe baki ba, sai ga wasu manyan karti, sun zo sun ɗauki Munaisah. "Wallahi bani na kashe ta ba." Haka suka tafi da ita, wurin Uwar mugu na tafi ina.buga mata kofa dakyar ta bude, zubewa nayi akan gwiwata. "Na yarda ki saka ni na aikata kome don Allah ban da Munaisah. " Na fada cikin matsanancin damuwa da tashin hankalin. Ƙarar fitar wasu manyan motoci irin na gidan yari Uwar mugu ta ce min. "Ai na gaya miki, ki kula da danginki. Me kike so ki sani? Ta amshi kudinta ta kuma kai inda ya dace, idan da rabo zaku ƙara ganawa, don sun tafi da yallabai."
"Sun tafi kin ga motar da ta fita sune, ba yau yaso tafiya ba, amma saboda samun dami akala yasa shi tafiya. Ki kula da mai cikin nan, domin idanun Addah kada ya tsaya akanta." Ji nayi kamar an hura min wuta a kirjina, dakyar na mike na nufi tantin mu, ina shiga na zube a wurin suma nayi mutuwa nayi Allah masani.

Ni dai gani nan domin sai da gari yayi haske na farka, a hankali na tashi zaune babu sallar Magariba da Isha, ga ta asuban ban samu ba. Tashi zaune nayi ina kallon dakin, Zuzu ce zaune sai Ummi da take jikin Yakumbo, tashi nayi da gaske na kalli wurin Munaisah babu ita babu labarinta.
"Bata dawo ba ko?"
"Kiyi sallah ki ci abinci, babu abinda yasan inda aka kaita addah ma tun jiya ta fita bata dawo ba." Inji Zuzu.
"Zuzu ki kula da Addah."
Mika min ruwa tayi, na fita nayi alola na dawo nayi salolin da suke kaina. "Ina son nayi kuka Zuzu." "Ai kuka rahama ce idan kin samu kiyi Zahra'una."
Kasa magana nayi ina kallon yadda kome ya lalace mana, "zuzu cikinki wata shida ko?" Juyawa tayi ta kalle ni, sannan ta gyada kai tana ajiye min abinci. "Ga kunu nan ki sha."
Wasa wasa tafiya da Munaisah ya xama.kamar tarihi domin babu ita babu labarinta babu labarin b'atar Aina'u abin da ya kusan tab'a kan Tumba kenan,. Addah kuwa facaka take da kudi son ranta.
A hankali lokaci yayi ta tafiya sama da yadda ba'a tunani, wata biyu kenan da tafiya da da Munaisah tana raye kuwa? Ta mutu ne?Allah shi kadai ya barwa kasan sani.
Muna cikin wata na biyu cib da tafiyarsu, haihuwa ta tasowa Zuzu da yamma haka aka nufi asibitin da yaƙe cikin sansanin, da ni da Addah haka muka isa asibitin da ita, tun yamma take abu ɗaya. Ina jin muryarta har na daina jin muryarta. Hankalina ya tashi domin uwar mugu tazo har sau biyu ana faɗin bata haihu ba. Sai yanzu naji ban yarda da kowa ba har Addah itama ban yarda da ita ba, ina tsaye Balali yazo ya ke tambayata. "Ya take?". "Alhamdulillahi tana ciki." Shiru yayi kafin ya ce min. "ban san waye ya dace ki taimakawa ba, uwar ko jaririn tana haihuwa zan muku wani abu da zaku bar nan ku tafi can ku rayu nan ba zasu barku ba. Yawan abincin da kuke ci yawan rayuwarku da kuke wasa dasu hatta kanki kada ki yarda da shi."".....

Shahararu goma aduniyan kayan mata wato m zee kamshi kayan mata kenan inakuke matan kwairai manyan Mata fah bamuna mataba Mata masu aji Wanda tasan kanta agidan mijinta kozokuyi gyara masu kyau da inganci Wanda zaisa oga nishadi yasashi farinciki atare dake kayanmu wane yaro sai uban yaro kinsha zumar makalemata dare daya wanka goma wanan set ne na kayan kwairai akwai fati budurwa mumuna da aeki Dan miyau malaka to shu,Umar Zuma zumar kiba gari kiba Zuma me lakani ningi tsumin lahaula hadin miski ba ahira dawando garin me kabara kasa ruwa sama ruwa wanan magani ba ,a magana magani sanyi mekyu

maza da Mata ci da kaza ci da cicibin vlp yan shila ci da kifi nama kayan sakiba na gida danawaje munadakaya kala kala fani kamshi munada shu uwar humra namu ba irin nasubane akwai turare 24 hr turare kabasa Dana gida masu Dadi gakyau ga kamshi 08063845136
(Wash na gaji wallahi!)
#thedambuje
[2/20, 4:26 PM] Cutie cutie pie: *BAƘIN HAURE....□□*

{Greed for Money is the roots of all evils□} Arewabooks:maidambu41
Wattpad:Mai_Dambu
Mallakar:Mai_Dambu

Assalamu alaikum barkanmu da warhaka da fatan kuna cikin koshin lafiya, karku manta da wannan Kamfani mai albarka mai kawo muku kayan bukata cikin sauki da Aminci da Inganci.
Wato TA RASULU MULTIPURPOSE. YA SAKE DAWO MUKU DA KAYAN NAN MASU ARMASHI DA DANDANON KOWACCE MACE TAURARUWA CE.

_____
MARKADADDIYAR GYAD'A
HADADDEN KAYAN SHAYI
GARIN KOSAI NA TAFI DA GIDANKA.
GARIN TUWO
GARIN KUNU YAR ASALI
CURRY ME DADI
SPICES
TYME
YAJIN DADDAWA ME KYAU
GARIN DAN WAKE
JAN YAJI MAI DAD'I...

_____
BUGU DA KARI MUN TANADAR MUKU DA KAYAN FITAR SALLAH DA NA SHAGALIN SUNA DA BUKUKUWA.
ATAMFOFI, LESHINA, MATERIAL, SHADODDI, YADUDDUKA NA MAZA DA NA MATA, JAKKUNA DA TAKALMA.
WANI ABIN SAI KUN ZO TA RASULU MULTIPURPOSE DOMIN KASHE KWARKWATAN IDANU.
ZAKU IYA TUNTUƁARMU A WADANNAN NUMBOBIN.. 08086639163 - 09030168590....
MUNA DAKON SAYAN DAI-DAI KO SARI.....
019
Wani lokaci kana son ace farin ciki da nutsuwa sun wanzu a bisa fuskarka. Sai dai ƙuma bai zama dole sai haka ya faru ba, matuƙar zaka yi fafutukar rayuwa da mutuwa tow dole kayi adabo da dariya sai dai wani sauyin idan tazo maka babu yadda ka iya

Cikin farinciki muka shiga rige-rigen shiga dakin, ana shiryata. "Ku bamu waje!" Malaman jinya suka ce. "A'a Zahra'u zo nan!" Yadda tayi kiran suna na yasa na isa wurinta, "dauke ta!" "Wai macen ce da gaske!" Na fada cikin zumud'i ban lura da halin da take ciki ba. "Mace ce Zahra'u, kada ki manta da alƙawarin mu." Ta faɗa hawaye na zubo mata. "Zuzu kada ki fadi haka, ai alƙawari gaskiya ce ba zan tab'a barin amanar da na dauka ba" kallon juna muka yi, naga zufa na karyo mata, "Zuzu kina lafiya!" Kallon Addah tayi tana murmushi. "Ki ajiye a ranki ko inuwar Y'ata kika rab'a sai bala'i da masifa sun zagaye ki." Juyawa nayi ina kallon Addah da babu wani ko dar a fuskarta sai murmushi. "Allah ya baki lafiya Zulai!" Yunkurin tashi take amma ta kasa, haka ta kalle ni hawaye na zuba mata ta ce min . "Ki bar sansanin nan, don Allah ko don abin da na haifa ki tafi wani wurin ki rayu don Allah."

Hadiye yawun bakina nayi ina kallonta, "Maman Baby ina zan tafi?"
"Ki je ko ina kawai ki tafi inda zata rayu don Allah, idan ba haka ba ita da Ummi kasa ku zasu yi a tire." Juyawa nayi ina kallon Addah jikina kamar mazari. "Ko da yake ba zaki gane illar da matar nan tayi ba ko? Tow shi kenan don Allah ki tafi kada ki ajiye Babyn tafi da ita ki kawo min ruwan zafi."
"Ba zaku bani Babyn ba?" Addah ta tambaye mu, kamar zata yi kuka ta ce mana. "Kuna zargina tun ba yau ba. Ni fa na haife ki, na dauki renon cikinki amma bakya raga min." "Zahra'u ajiye min Babyn nan a kusa dani, ki taimaka min na tashi zaune."haka na saka mata babyn a gefenta na d'aga ta zaune tana kallon Addah ba zan iya gane kallon kiyayya ce ko tausayi ba, amma tabbas kallon yana da nasaba da b'acin rai. "Dauki yar ki tafi ina jiranki yunwa nake ji " wannan shine karon farko da Zulaihah ta nime na basu wuri a tarihin rayauwarmu da ita, duk abinda zata fada ko tayi kai tsaye take yi a gabana. Ina fita ta ce mata. "Me kike so bayan rayuwata" zama tayi tana washe mata baki. "Ki bani rikon Yarki ba zan neman kudi da ita ba." Murmushi tayi tana kallon Addah. "Ko jikina kunne ne ba zan yarda ba, na haramta miki ita koda."

"Zulaihah kenan, idan na gayawa Zahra ce kin ta bata maganin zubar ruwan nono ya zaku kwashe? Ko na gaya mata cewa da bariki zaki shiga niman kudi ya zata ɗauka?" Wani irin rawa jikin Zulaihah ya ɗauka, tana kallon addah hawaye na zuba mata. "Addah me yasa zaki min haka? Me yasa karfi da yaji kike son lalata rayuwar Zahrah? Meye tayi miki? Na zata idan wani zai dauko wuka domin ya kashe zahran ke me kare ta ne ashe ke ce kike dab'a mata wuka ta baya me yasa sai ita? Gaskiya Allah ba zai barki ba, hakkin mu ya ishe ki duniya da lahira." "Yarki zaki bani!" "Har abada ba zan baki Y'ata ba, Zahra ce zata riketa. Na san Ummi zata gaya mata gaskiya amma na fi son koda zata tsane ni ke ta fara tsanarki na har abada."
"Ai kuwa zata bani ita domin na sayar da ita, kamar yadda na sayar da ke har mahaifanki domin kada ki sake haihuwa."
"Addaaaah" ta kira sunan da karfi, "me na miki?" "Baki min kome ba, Yarki zaki bani."
"Kin dauki kasonki Yarinya ko bayan raina ne diyar Zahra ce, don haka duk abinda zaki yi kiyi." Tafa hannunta tayi, sai ga wasu kartin maza sun shigo, haka suka kama Zuzu suka mata allura sannan suka kyaleta. A hankali ta kalli Addah, "da ke da Ummi kun sayar da Munaisah, bayan kun kashe Nenne. Yau ni kika sayar Addah matukar na rayu wallahi sai na farauce ki kamar yadda mafarauci ke farautar dabba." Harshen ta ne yayi mata nauyi daga nan bata kara magana ba, tana kallo suka rufa mata farin mayafi.

Lokacin da na isa tantin mu, dauke da Babyn sai da Ummi ta mike tana leka yarinyar.
"Yarinya tafi Zuzu kyau!"
"Wallahi kuwa!" Na fada, ina mika mata babyn. "Ummi Khair!" D'ago kai tayi tana kallona. Idanunmu ya haɗe da juna. "Me kuke aikatawa da Addah?" Murmushi tayi a hankali ta juya min baya, tana fadin. "Addah dai ni ina yi ne domin kare rayuwar mahaifiyata, duk lokacin da zata dauka zan so ta rayu koda ba zata yi magana ba, ba zata motsa ba ina son mahaifiyata."
"Ina kuka kai Munaisah?"
"Munaisah ta fiki gata, ta tafi inda zata samu nutsuwa ne, matukar tana tare da ke zata iya daukar zugar Addah ta kashe ki."
"Ummi ban gane ba?"
"Ba zaki gane ba, amma anan inda muke rayuwa ba zata yiwu ba sai da cin amana, sai da zalunci, sai da cutarwa ko ita Zuzu ai ta cutar dake ta hanyar da ba zaki tab'a yafe mata ba. Shi yasa don ki yafe mata idan kika samu labarin ta baki yarta ba zaki ji labarin nan kusa ba, kina da sauran lokaci ki je ki ji daga bakinta me ta aikata miki, Mother Teresa!" Ta fada tana mika min babyn, sake rungumar Babyn nayi zan fita. "Zuciyarki tana da kyau sosai Zahrah, kina da adalci sosai shi yasa ba zan iya cutar dake ba, amma kowa kika ga baki ganshi ba adalci yayiwa kanshi domin akan kuɗi

zasu aikata kome infact har dani zan iya kome abu daya yasa na kasa cutar dake Yakumbo", ta kalleta tana murmushi. "Amma idan ta nice yadda ake bani kudi domin na sayar da kowa kina nufin ba zan iya ba ne? Yakumbo ta yarda da cewa wata rana ke haske ce ga rayuwata."

Kunsan me ake kira da gudun ceton rai? Shi nake son nayi ko zan cimma manufarsu a kaina, don haka na sa kai na fita da gudu domin titsiye Zuzu ta gaya min wacce irin cutarwa tayi min, gabana faduwa yake ina ji kamar ana mai dani baya, duk yunkurin gudun da nake hakan amma ina kome ya lalace daga lokacin da na bar Zuzu. Koda na isa na samu an fito da gawarta ne. Haki nake ina kallon Addah kafin na kalli gawar zuzu. Da sauri na nufi kan gawar, rike ni Addah tayi tare da faɗin. "Mutane nawa ne kike son su mutu domin ki? Me yasa lallai sai kowa ya sadaukar da rayuwarshi domin ki? Me yasa lallai sai kowa ya rasa ranshi dominki? Zahra'u na rasa Y'ata dominki don haka ki bani jikata."
Kasa magana nayi ina jin jikina yana rawa.

"Ad.....!" "Dan uwana ya rasa rayuwarshi domin ke? Na rasa zuri'ata domin ke? Na rasa kowa don ke. Anya Zahrah ke mutum ce? Yanzu ma na rasa Zulaihah saboda ke." Kai na ne ya fara sarawa a hankali na isa gaban Zulaihah. "Ki tashi ki gaya mata ba don ni kika mutu ba, gaya mata ban san kome akan kowa ba. Me yasa?" Na fada da karfi, "Me yasa na zama masifa ga ahalina?" Na fada da karfi ban san yadda aka yi ba, kuka ne ya kwace min kuka nake wanda tunda nake a rayuwata ban tab'a jin shi ba. Kuka nake cikin tsannanin takaici da b'acin rai. Kiri-kiri Addah ta daura min alhakin mutuwar Zulaihah.

"Taso muje!" Uwar mugu ta riko hannuna, ina tafiya ina kuka har tantinta. Murmushi tayi tana zaune tana kallon yadda nake kuka. "Da Alamu kukanki ba yau kika tara shi ba. Don haka kiyi abinki, kiyi ko zaki samu nutsuwa."

Nayi kuka har sai da Babyn ta fara kukan niman abinci, nan hankalina ya dawo jikina. Na dauke ta cikin rawan jiki zan fita ta ce min. "Ga madarar jarirai nan ki bata!" Ta ajiye min formula na yara, karba nayi xan fita ta ce min. "Ki daina kukan haka, zab'an rayuwar suka yi, ke kuma kina da sa'a shi yasa ba zaki gane ba." A fusace na ce mata. "Shi yasa kuke bibiyarmu kuna hada mu faɗa da tsanar juna? Me muka yi muku haka?" Na tambaye ta hawaye na zubo min, "ba fa haka ba ne?" "Haka ne mana, haka ne mana me yasa tun fil azal baku gaya mana cewa nan sansanin mutuwa ce ba ta yan gudun hijira ba? Ki sani kunyi kuskure in sha Allah karshen ku yazo wallahi azim sai Allah ya wargaza wannan wurin ki saka idanu ki kalli yadda kome zai zama tarihi." Na juya na fita ko madarar ban dauka ba, muna zuwa tantin na samu Ummi tana barci. Zama nayi bayan nayi sallama da disasshen muryata, na zauna ina son nayi magana amma bakinciki ya hanani, bamu kara jin duriyar Addah ba. Zama nayi na fashe da kuka yarinyar ma kuka take.
"Ki bata nono idan ta ja ruwa zai sauka." Na kalli Ummi a mamakance. "Kin tuna kunun da Zulaihah take baki?" Kafin ta karasa na dakatar da ita. "Ba sai kin gaya min ba, zuciyata ciwo take." A hankali na bude nonon zan saka mata ta ce min."dakata!" Tashi tayi ta dauko wani garin magani ta zuba a wani bojuwa ta wanke nonon dashi, sannan ta ce min. "Bata." A hankali na saka mata nonon a baki, sai da tayi ta niman bakin nonon kafin ta fara alamar tana jan ruwa. Kuka ne ya kara kwace min ina ji kamar xan mutu kafin rana ta sake bud'ewa. Wani irin ciwo nake ji mai zafi a kirjina. Ban san yaushe xan daina kuka ba. Haka na rungumeta har ta fara jan ruwan.

Wato kunun da Zuzu take bani maganin kawo ruwan nono ne? Wani irin murmushi ne ya kwace min ba na kome ba sai na bakinciki, ina ji ina gani kowa ya mai da ni sakarya ko nace sokuwa. Sun mai dani doluwa. Munaisah ta tafi Zuzu ta tafi.
Haka na cigaba da zama har aka kira sallah na tashi nayi, sannan na saka yarinyar a gaba ina kallonta. "Zahra'u ba amata wanka ba" "eh " na fada, tashi tayi ta haɗa ruwan zafi, yana zafi ta dauko bawo ta fara mata wanka, tana yi tana kallon yadda yarinyar take nishi wato rashin wanka yasa jikinta yayi tsami. Ina tuna abin da ya faru

zan sake kuka musamman idan na tuna mutuwar Baffa sai naji kamar zuciyata zata fito don ciwo da zafi. "Zahrah kukan ya isa haka man"
" duk tsawon wannan lokacin Zuzu wato har ta san yadda zata bani abu naci domin na biya mata buƙatar ta? Ummi me yasa kuka min haka?" Murmushi tayi tana fadin "tow me yasa ba zamu miki haka ba? Ke fa mahaifiyarki yar babban gida ce, Zahrah ke fa kina da sa'a wallahi." "Wani irin sa'a!" Na fada da karfi me yasa suke cewa ina da sa'a, Sa'a ko masifa. "Da ciwo idan ka fahimci wanda ka yarda da shi ya ci amanarka. Zuzu bata mutu ba tana raye sai dai kece yadace ki mutu ki bar wannan duniyar idan ba haka ba bakincikin addah ya ishe ki, Addah tayi alkawarin sai ta hana ƙaddarar sa'arki bayyana, ta kuma rantse ko zata muku sai ta yanke duk wanda zai bude miki fukafiki domin ki tserewa ukubar ta."
"Me na mata? Me na tsare mata."
"Ba zata tab'a morarki a yanzu ba, ita kuma idan ba zata more ki ba, ba zata barki ki huta ba, sannan Yarta da ta haifa ta zaɓe ki sama da ita gayan kin san yadda take ji kuwa? Kin san ciwon da take ji kuwa? Shi yasa idan aka kawo mata tayin kudi take karba don ke, don ta ga baya ki kafin ki samu daukakar da ake gaya mata zaki yi, Zahra daga zuwan mu nan hotunanki kawai manyan mutane suka saka kudi akanki, ita kuma Uwar mugu bata tilastawa mutum karbar Kudi sai da ra'ayinka, kaf sansanin nan kece kawai Uwar mugu take sararawa. Muna ji muna gani mun zama kamar saniyar ware ba tare da kin sani ba. Sau uku ana saka caca akanki kawai, amma Allah yake tseratar dake. Muna cikin duniyar da ko yaya kudi ya shigo yafi dan uwanka gaya min laifi ne don kowa ya bar jikinki bayan kowa ya san cewa matukar kika rabe shi ba zai cigaba ba, sai dai ya manne a jikinki dukkansu biyu sun haye saboda ke. Mun fito jini daya, amma nasararki ko yaya mutum ya ambaci sunanki a cikin abu sai yayi Sa'a ki fara niman mafaka kafin a fahimci karfin tauraronki, kafin Addah ta yi bincike na fara kafin Addah ta kai sunanki wurin Malamai Zahra ni na fara. Tauraronki ko a sararin samaniya ne ƙarfin shi yafi na sauran. Don haka ki kula da inda zaki rayu duk wanda ya fahimci haka tow ba ke ba, hatta Baby rayuwarta zata zama abin tausayi ne." Wani uban ihu na fasa ina kuka ina faɗin. "Ni tsinuwa ce? Bani da albarka ne?" Hawaye ne ya zubo mata. "Ko daya baki da alaka da tsinuwa"
"Bakar ƙaddara ce dani?"
"Haskenki ne yayi yawa, idan har tafiya ta kama ki da mutane dayawa zaki gane haka, mu nan baki dayan mu hassadarki muke." Ta Fada min ido da ido. Wato jin wannan kalmar yasa ni baki daya na dauke wuta sai hawaye. Kunsan yadda na shiga rud'ani, me yasa ban gane hakan ba? Me yasa na rufe idanuna ban san inda nake rayuwa ba? Bata kuma bi ta kaina ba.
Haka ta mata wanka tass, sannan ta dauki wani ruwa mai dumi ta fara gasa mata cibiya, sai ga yarinya kafin a gama tayi barci. Kayan da nake ta ajiyar shi na haihuwa shi na dauko na shiga dubawa na mikawa Ummi da take gasa mata cibiya da garwashi, mika min ita tayi bayan ta gama mata, amsarta nayi na saka mata kaya tayi kyau kuwa. Sannan na gyara wurin kwanciya muka kwanta, amma barci ya gagare ni . Haka na raba dare ina gadinmu baki daya, domin gani nake matukar na kwanta zan wayi gari Babu Baby, haka na kwana ina kuka. Wurin asuba na fara jin barci, baby kuwa barci take abinta, tashi nayi na gabatar da sallah, Ummi ma haka.
****
Niamey.
Wurin motsa jiki ya nufa, yana motsa jikinshi, kamar daga sama abin ya fado mishi. Ajiye ƙarfen yayi ya dauki wayarshi bayan ya dauki ruwa ya sha, kan wayar ya shiga ya fara niman cantact din mutanen naija, da gudu aka bangaje shi wayar ta fadi can. Cike da Mamaki ya juya yana kallon waye haka. Kyakyawar yarinya ce tsaye rike da kugunta wata mata tana me shigowa wurin tana faɗin. "Feeyah ki tsaya kawai na duba wallahi babu wani jimawa." Sunkuyawa yayi ya dauki wayarshi. "Hammayo!" Bai saurari kiran da tayi ba, yayi ficewarshi yana kallon yadda fuskar wayar ta zama damage, karamin tsaki yayi.

"Bazai yi aiki ba?!" Dayan ta tambayeta, murmushi tayi mai sanyi. "Zai yi aiki mana saka idanu kiyi kallo!" Shi kan fashewar wayar ta sha mishi kai, yana fitowa falon ya samu Hajiya ya zauna yana kallon tv Aryan yayi matashi da cinyar Hajiya. "Kai dai an yi katon banza." Ya fada yana cilla mishi wayar. "Hammana me yasamu wayar kuma?" Tsaki yayi ya cigaba da kallon tv, sai ga yan matan sun fito kamar munafukai. "Mune muka fasa mishi wayar." Ta fada kamar zata fashe da kuka. "Haukar banza kenan, Afiyyah wani irin wawanci ne haka?" Aryan ya tambaye ta a fusace, "kayi hakuri Hamma Aryan!" "Kai ya isa" ya faɗa yana musu alama su tafi da hannu. "Mun gode sosai Hammayo!" Shiru yayi yana kallon tv. Suna fita Aryan yayi tsaki yana kallon Majid da yake kara kallon tv, "Hajiya kin ji labarin haihuwar Zaytoonah!" Aryan ya faɗa yana kallon yadda fuskar Majid din bai wani sauya ba, asalima ko a jikinshi. "Kasan labarin rasuwar mahaifinta ya kidimata shine ta haihu lokacin bai yi ba."

"Ayya Allah ya jikanshi."

"Amin!" Hajiya ta faɗa, "kuma naga laifin Inna tako, yarinyar nan tun tana yar mitsitsiya take son ganin Babanta, amma taki fisabilillahi." Juyawa suka yi suka tsare shi da idanu. Majid sai Allah sai yayi magana kamar bashi ya faɗa ba, "kasan hakan ne?" Juyowa yayi yana kallon Aryan kafin ya daura kafa daya kan daya. "Zamana a can tayi ta bin Inna tako amma taki karshe da na Uzra mata, kwad'a min mari tayi." Ya fada yana me shafa fuskarsa, don baya manta ranar da ta tsinka mishi mari kamar a film.

Kura mishi idanu Hajiya tayi tana son jin karin bayani. "Hajiya ni ma ban wani san kome ba, kawai dai abin da na sani Inna Tako tayi fama da lalurar gushewar hankali kafin ta warke amma ta manta da kome."

"Ikon Allah!" Mikewa yayi zai nufi dakin shi. "Gobe zamu marad'i." "Allah ya kai mu." Yana barin falon Amaan Mamman Ba'are yana shigowa a gajiye, zama yayi yana kallon Hajiya. "Lafiya Mai martaba?" Sosa kanshi yayi yana faɗin. "Hajiya dama." Mikewa Aryan yayi zai bar falon domin ya barsu kada yaji abin da zai rufe Amaan din da duka. "Ina jinka!" "Aron kudi zaki bani katin bankina Amirah ta karya."

"Ina kudadenka suke?" Ta tambaye shi. Sosa kai yayi yana kallonta kamar zai fasa ihu. "Ina kudinka suke? Ni ba baiwarka ba ce kamata yayi a ce na huta sai dai na maka hidima saboda baka da kunya.....
(Pool Zahrah 😊)

Shahararu goma aduniyan kayan mata wato m zee kamshi kayan mata kenan inakuke matan kwairai manyan Mata fah bamuna mataba Mata masu aji Wanda tasan kanta agidan mijinta kozokuyi gyara masu kyau da inganci Wanda zaisa oga nishadi yasashi farinciki atare dake kayanmu wane yaro sai uban yaro kinsha zumar makalemata dare daya wanka goma wanan set ne na kayan kwairai akwai fati budurwa mumuna da aeki Dan miyau malaka to shu,Umar Zuma zumar kiba gari kiba Zuma me lakani ningi tsumin lahaula hadin miski ba ahira dawando garin me kabara kasa ruwa sama ruwa wanan magani ba ,a magana magani sanyi mekyu maza da Mata ci da kaza ci da cicibin vlp yan shila ci da kifi nama kayan sakiba na gida danawaje munadakaya kala kala fani kamshi munada shu uwar humra namu ba irin nasubane akwai turare 24 hr turare kabasa Dana gida masu Dadi gakyau ga kamshi 08063845136
#Mai_Dambu
[2/21, 5:17 PM] Cutie cutie pie: *BAƘIN HAURE....*

{Greed for Money is the roots of all evils}
Arewabooks:maidambu41
Wattpad:Mai_Dambu
Mallakar:Mai_Dambu

😫😉 A fusace da b'acin rai a fuskana nake cewa ya ishe ku□□ Cin mutuncin Addaririya kuje ta yafe muku□□ tace ku daina bin ta da tsinuwa 😔□😂zata shiryu

Assalamu alaikum barkanmu da warhaka da fatan kuna cikin koshin lafiya, karku manta da wannan Kamfani mai albarka mai kawo muku kayan bukata cikin sauki da Aminci da Inganci.
Wato TA RASULU MULTIPURPOSE. YA SAKE DAWO MUKU DA KAYAN NAN MASU ARMASHI DA DANDANON KOWACCE MACE TAURARUWA CE.

_____
MARKADADDIYAR GYAD'A
HADADDEN KAYAN SHAYI
GARIN KOSAI NA TAFI DA GIDANKA.
GARIN TUWO
GARIN KUNU YAR ASALI
CURRY ME DADI
SPICES
TYME
YAJIN DADDAWA ME KYAU
GARIN DAN WAKE
JAN YAJI MAI DAD'I...

_____
BUGU DA KARI MUN TANADAR MUKU DA KAYAN FITAR SALLAH DA NA SHAGALIN SUNA DA BUKUKUWA.
ATAMFOFI, LESHINA, MATERIAL, SHADODDI, YADUDDUKA NA MAZA DA NA MATA, JAKKUNA DA TAKALMA.
WANI ABIN SAI KUN ZO TA RASULU MULTIPURPOSE DOMIN KASHE KWARKWATAN IDANU.
ZAKU IYA TUNTUƁARMU A WADANNAN NUMBOBIN.. 08086639163 - 09030168590....
MUNA DAKON SAYAN DAI-DAI KO SARI.....

020

"Kai ko kunya baka ji ne? Ace kome nice zan maka. Dukkansu hudu kokari suke su kyautata min amma kai dayake baka da lissafi ka kwaso jiki kamar fulawar da aka watsa mata yeast kazo na baka kudina ko Amaan Mamman Ba'are." Wata irin kunya ce ta kama shi, "Hajiya don Allah." Tsuke fuska tayi tana hararshi. "Kowacce uwa tana iya kokarinta akan Yaranta, sannan iya kokarin da nake akan ku ko da ace aiki aka sani baku isa biyana ladar ba, domin iya ƙoƙarina nayi kuma ina kan yi, Amaan ni na haifeka amma ni nake kuka akanka kannenka ban yi kuka akansu ba, sai kai." Murmushin takaici tayi tana kallonshi kafin ta cigaba da cewa. "Su waɗanda ka ke kai musu sirrinmu basu baka kudine? Mara zuciya wanda lissafinshi daban da na kowa. " Yadda take fada har wajen gidan kowa yana jin ta, tabbas Hajiya ta fusata kuma takai bango. Robar ruwa Aryan ya fito da shi ya mika mata, ta amsa tana me kai bakinta. "Zaka iya tafiya Mr Mamman Ba'are!" Yau ko yar borin kunyar nan da yake yi na takalar Aryan bai yi ba. "Daga yau kada na kuma ganinka a kamfani bayan mun tashi, sannan wannan Bluetooth da ka saka musu shine na cire kwanankin baya. Amaan ka fita idanu ko na sallama musu kai." Subul subul ya fita, yadda kuka san (Gfresh Al-Ameen Kano state material, haka Amaan Mamman Ba'are yake□) haka ya fice abin shi, a harabar gidan ya hadu da Majid da Yaran Aryan suna wasa, sai ihu suke yana tayasu.

Tsayawa yayi yana kallon yadda suke wasa cikin jin dadi da nutsuwa, me xai yi ya samawa Matarshi nutsuwa ne. Ba zai iya rayuwa babu ita ba, haka yasa shi juyawa ya fita kai tsaye bai tsaya ba sai can wajen gari, gidan Sajjid Mamman Ba'are. Ya

shiga cikin gidan a harabar gidan ya ga motarshi tabbas yana gidan, zai shiga masu tsaron gidan suka hana shi dole ya zauna a harabar gidan ya jira shi. Har zuwa wani lokaci kafin Sajjid din ya fito da gajeren wando da yar singlet. Ya tsaya yana kallon Amaan Mamman Ba'are. Kafin suka kwashe da dariya tare da rungumar junansu. "Nayi kewarka Baby na!' inji Sajjid, "Nima haka My love!"
***
camp
Idan har akwai wanda zai ci amanarka tow kada ka damu kowa, koda zasu haɗu baki daya su ci amanarka matukar ka yarda da Allah magana ta kare, amma wanda ka bawa yarda ya ci amanarka sai kaji kamar zaka mutu, zuciyarka ba zata yi jimirin daukar kowacce nauyi ba. Ina jin wani irin ciwo me zafi
Bude idanuna nayi ga babu kowa a cikin tantin mu, daga ni sai Baby. Kayan Addah ma babu babu kayansu Ummi, wani kar'ar fashewar abu naji, kafin na fara jin Ihun mutane da kukan Yara yana kusanto ni.

Ƙarar harbe-harbe yana kusanto inda nake, bansan ya aka yi ba amma sai ganin tantin mu ya kama da wuta nayi, haka na sunkuci Baby na fita da gudu, kamar yadda kowa yake gudu haka nima nake gudu, gudun da ban san inda muke jefa kafar mu ba,mu dai gamu nan ana kad'a mu kamar wasu awakai. Mun yi tafiya me nisan gaske a cikin daji, babu ci babu sha tun daga wayewar gari har rana ta faɗi, sannan baka san waye a kusa da kai ba, shima kuma don rud'ani ba zai ce ya san waye kai ba, sai yau na kara jin kamar da mutuwa nayi da abinda Zuzu da sauran Yan uwana suka min,amma me yasa zuciyata taki yarda Zuzu zata yaudare ni. Duban Babyn nayi naga bata motsi. "Wayyo Allah na, Yarinyata bata motsi jama'a ku taimaka min kada ta mutu!" Ihun da nayi ta musu kenan ina cika musu kunne, hasko min torchlight aka yi na runtuma da gudu kamar mahaukaciya, na ce musu."ku duba min ta mutu ne!?" Na fada ina ihu. "Ke ki nutsu!" Aka daka min tsawa, amma ina baki daya kamar wacce aka toshe min kwakwala, haka nayi ta musu ihu da rokon su duba min yarinyar ko ta mutu. Can hasken wani dakin da aka kafa shi a dajin ya kunnu, fitowa yayi sanye da jallabiya. "Yallabai ka tafi zamu magance matsalar!" Yana zuwa ya amshi Babyn. Sannan ya juya da ita, "ina xaka da ita? Ina zaka kaimin Baby na! Bani ita ta mutu ne?" Fisgo ni yayi ya tura ni dakin tare da rage hasken dakin, dumin dakin ya kara sani shiga hankalina. Daukar wani torchlight yayi yana haskata, kafin yayi magana cikin wata irin murya me sanyi, duk da Muryar shi da take da matuƙar sanyi da dad'i haka bai saka na fahimci cewa dani yake magana ba, sai da ya kuma haska min torlight ɗin na ce mishi. "Kace ta mutu?" Ajiye fitilar yayi ya ce."yaushe aka haifeta?" "Jiya!" "Ina Mamanta?" "Gani nan!" Na nuna miishi kaina,kamar bai yarda da ba sai kuma ya koma kan yarinyar ya ce min. "Yaushe rabonta da shan nono?" "Jiya da daddare!"
"Zo ki bata!" Ya faɗa min yana mika min ita, burina Baby ta rayu. Ciro mata nonon nayi na saka mata a baki bata amsa ba. "Bata karba ba" janyo wani kofi yayi ya matsa jikin wani irin murhu, ya kara kofin kafin wani lokaci yayi dumi, janye kofin yayi ya mika min yana faɗin. "Taimaka min ya huce!" Haka nayi ta hurawa har ya huce, sannan ya amsa ya saka mata a baki ruwan ya fara shiga bakinta, tana fara sha kuwa sai gashi ta kware, d'agota yayi yana shafa bayanta sakin baki nayi ina kallonsu, sai da ya gama dubata ya bani ita, na saka mata nono ai kuwa ta rike da sauri, zafin da ya ratsa bakin nonon da kaina yasa ni sakin yar ƙaramar ƙara. Bai kalle ni ba, amma kuma ya juya baya ya kwanta abinshi, har ta gama sha ya ce min. "idan kin fita kice Ado ya kai ki wurin Uwar mugu zata kula daku. A mata wanka a nad'e ta kafin gobe!" Fita nayi a bakin kofar na samu Ado. "Muje!" Ya ce min, har wurin Uwar mugu ya kaini, ya gaya mata sakonshi. A daren ya kafa mana tanti shi da wasu mazan, uwar mugu wanka tayiwa baby ta kara bata madara. "Ina Addah da Ummi?" Murmushi tayi ta ce min. "Suna lafiya a cikin wannan yanayin, sun zata kin mutu ne."

Mika min ruwan zafi tayi na sha a hankali, har na gama sannan wani irin barci yayi gaba damu, daukar Baby tayi ta kai mishi. "Kika ce Nawwas ya sayar da uwar Jaririya?" Cikin tsannanin biyayya ta ce mishi. "Eh Sarki a dawa Sarki sarari. Ba iya uwar yarinyar ba, wannan bakar al'adar shin nan, ta sayar sassan jikin dan Adam yana nan bai daina ba, sannan akwai kanwar Babanta da take da bala'in son kudi."
"Uwar yarinyar tana raye kenan?" "Eh amma an fitar da ita tun yammacin shekaranjiya."shiru yayi yana kallon Babyn. "Nawas babu imani a cikin lamarinshi."
"Ba laifinshi bane kakar yarinyar ta bukaci haka." "Je ku kwanta."
------ Tafiya muke cikin koriyar ciyawa, ina gaba rike da Baby ina mata dariya, sai ji nayi kamar an hand'akani cikin wani rami me duhuwar gaske wanda bana iya hango farkon ramin ga Baby tana ta callara kara.
"Ki rayu a wurin." Cikin wani irin kuka na ce. "Wurin akwai duhu bana ganin Baby." "Ki zauna a wurin haske zai zo miki." "Taimako!!!!" Da wannan Ihun taimakon na farka, naga Baby har an mata wanka an kara nad'e ta, babu kowa a dakin sai abinci da aka ajiye min, tashi nayi na fito waje. Naga an zubawa kofar tantina idanu ga mutane kowa ka gani a firgice yake. "Gimbiya ke ake jira!" Addah ta faɗa tana hararata. "Addah!" "A'a gatari ko guduma." Ta fada tana juya min.baya, Allah ya gani ina da rauni wurin Ibada, alola nayi na wuce ciki na gabatar da sallar da yake kaina sannan nayi na asuban yau da garin ya gama haske tas, sannan na koma dakin na goyi Baby a tsaye naci abincin na rikema addah sauran, don nasan bata samu kamar wannan ba, lokacin da na fito aka nad'e tantin, wato tunda na nufi wurin Addah na fahimci matar nan bata da mutunci, mika mata abincin nayi ta fauce. A can gabanmu na hango Ummi ban kula ta Addah ba, na tafi na same ta. "me yasa kika tafi kika barni." "Ba gashi kin same ni ba!" "Amma;" gyara goyon Yakumbo tayi tana me cigaba da tafiya, kafa babu takalmi sai lokacin na fahimci nima haka nake tafiya,ga tarin kayoyi.

Kamar wasu shanu haka muke ratsa tafiyar cikin dazuzzuka da kwazazzabai. Babu abinci babu ruwa, "Ummi ko zaki kawo yakumbo ki rike min Baby!" A gajiye ta ce min. "Eh!" Haka na bata yar ni kuma na amshi Yakumbo, muka cigaba da tafiya muna ratsa hamada da kwazazzabai. Sai da yamma tayi likis aka tsaya, na ajiye Yakumbo, hawaye na zuba min domin Baby kuka take, tun daga taimakon farko da na samu ban kuma samu ba. Haka nayi ta jigila da Baby dakyar muka yi sallah, kuma baki daya haɗawa muka yi, Abin tambaya anan ina za a kai mu? Babu me amsar tambayar nan, sai dai a cikin tawagar maza naji ana bayanin wasu sun mutu.
A hankali naji wani abu ya tokare min kirjina, ruwa da yar karamar busashen gurasa aka bimu da ita, mukaci muna lashe hannu, domin dai bai Ishe mu ba. Haka muka kwana cikin wani irin sanyi, muna tsaka da barci wata ta fasa ihu. "Wayyo Allah maciji ya sare ni!" Tashi kowa yayi zaune, aka fara haska torchlight, sai gashi nan wuluk, ya kara fasa kai zai kai wani saran daya daga cikin mutanen da suka fito ya samu ya harbe shi, sai da ya fasa mishi kai, matar ma bata haura minti biyar ba, ta fara shure-shure kumfa yana futa bakinta, kafin wani lokaci ta ce ga garinku. Cikin tsananin tsoro muka kara tattara kanmu wuri guda, haka aka bar gawar domin muna farkawa nan bamu kara kwanciya ba, sai tafiya haka muka yi ta ƙeta daji da kurmi.

Lokaci zuwa lokaci uwar mugu tana amsar Baby ta gyarata, ta kawo min ita na bata Nono, sannan ta wuce da ita wurin Mutumin da ban kara ganin fuskar shi ba, haka aka cigaba da tafiya mutanen da muka tawo wasu suna mutuwa, wasu idan aka gaji a nan za abarka a cigaba da tafiya, babu tausayi babu imani, kowa ta kanshi yake sannan a wannan tafiyar akan abinci sai mutum ya kashe ka har lahira, wani abun da na fahimta wannan yanayin ya haifar mana da matukar yunwa, fushi, rashin imani, babu tausayi ko jin kai.
Akan idanunka mutum zai fadi yana niman taimako, amma haka zaka tsallake shi kayi tafiyarka, idan aka zo rabon abinci kuwa tow sai an hada da bulala ko bakin bindiga, sai a nutsu a raba lafiya.

Idan ka tsaya janjani wani zai fauce abunda aka baka, kuma ya ci kenan. A wannan lokacin babu abinda muka zama sai kamar zombies, domin idan ka bawa mutum haushi matukar babu masu lura a kusa zai shake maka wuya agaban mutane kuma babu ruwan kowa, godiyar Allah da Uwar Mugu tana bawa Baby madara, da asirina ya tonu. Domin wani irin bala'in yunwa da gajiya nake ji, gashi haka muke karbe-karbe da Yakumbo. A wannan tafiya wani lokaci Uwar mugu ta dauke yarinyar ba zata kawo ta ba, don ta ga wahalar ta mana yawa.

Yau satin mu biyu muna tafiya a daji, babu me kuzari ko hankali a cikinmu, "Zahra!" "Na'am" "Yakumbo ta kara min nauyi ko zaki taimaka na sauke ta." "Tow." Na maida Baby baya, ina me gyara goyanta. Bayan na gyara na koma bayan Ummi, ina rukota ta koma jikina, ko ba agaya min mutuwa ba, zuwa yanzu na santa na san yadda take, na san yadda take daukar na kusa dani.
"Khairat!" "Yakumbo ta rasu ko?" Tambayar da tayi min kenan, "eh Ummul Khair!" "Kuma itama yarda ita za ayi kamar sauran?" Kura mata idanu nayi, a hankali muka kwantar da ita, ana ta wuce mu. "Don Allah ki min wannan alfarmar, nasan mun ha'ince ki ki duba girman zumunci kada a yar da ita;" ta faɗa tana wani irin kuka me cin rai, nima hawaye ne yake zubo min wani na bin wani. Tashi nayi da gudu, ina ratsa mutane har na isa wurin babbar motar da take dauke da shugabansu, daukar dutse nayi na jefe motar, kusan babu wanda ya dakatar dani. Sai yan bindigar, sake tsinta wani dutsen nayi na kara bugawa motar, dole suka tsaya naje har gaban motar na tsaya. Hawaye na zuba min. "Ke kina son mutuwa ne?" "Gaya min inda mutuwar take naje na rungumeta, na kuma tambaye ta mai yasa tuntuni bata zo min ba, bayan dakonta nake ba dare ba rana." Na fada hawaye na zuba min.
"Matsa ko mu bi ta kanki!"
"Babu inda zani!" Na fada ina kara tsayawa dakyau. Daga cikin motar ake tambayarsu lafiya. "Yarinyar nan me jaririya ce, ta tsare mana hanya."
"Me ya samu jaririyar!" Ya fada a gajiye, "bamu sani ba Yallabai bari a tambaye ta." Fitowa suka yi. "Ke bama son hauka, bamu hanya, wuce shi nayi na nufi inda ya fito na bude nace musu. "Ku gayawa mai gidanku Babata ta rasu ba za a yar min da gawarta ba ya fito ya sallaceta."
"Zahra'u!" Muryar Uwar mugu ya ratsa kunne na, "kina hauka ne" "Daga turu na fito Uwar mugu, kuma wallahi idan baku mata sutura ba, sai kun ga tashin hankali da masifa da bala'i."
Don dole aka tsayar da tafiyar, domin yadda na shafawa idanuna toka kowa yasan ba zan tab'a barin abin da na saka kaina ba, "Yallabai kayi hakuri." Hannu ya d'aga mata, "ina Babarki!" Nuna mishi can inda Ummi take durkushe tana risgar kuka nayi. Ban tsaya tantance waye shi ko fuskar shi ba, na dai san ya fito kuma ina gaba yana baya har zuwa inda gawar Yakumbo take, durkusawa yayi yana kallon yadda muka sakata a gaba, ni kan hawaye nake sharewa bana kuka. Shar-shar.

"Uwar mugu ku mata sutura a sallace ta " ya fada yana barin wurin, "Addah da Tumba kuzo a gyara ta.", Haka suka gyara ta aka kafa musu mayafi suka mata wanka aka mata sutura tare da sallatarta. Sannan aka binne ta a dan can gefe da hanyar da muke, ina tsaye na kalli Ummi da take kuka, ina ga gara tayi kukan da ace bata yi ba, zai zama mata ciwo.

Haka aka yi ta tafiya ana barin mu a ciki kuwa har da Addah, "Ummi muje kada mu rasa yadda zamu je." Sai da ta ƙara jimawa kafin ta mike, muka nufi hanya. Tana tafiya tana kuka, har suka mana nisa sosai sai ƙurarsu muke hangowa. "Ummi mu hanzarta mana!" Na fada ina diba a guje, kamar wacce aka sa mana gasar tsire. Gudu sosai muka yi, sai da muka yi da gaske sannan muka kamo su. Sauke Baby nayi naji tana shakuwa. Nono na saka mata a baki muna tafiya ina bata har muka isa cikin tawagar sannan abin dariya abin tashin hankali babu wanda ya ce mana ga inda zamu, kawai tafiya muke kamar wasu shanu. Tsayawa aka yi baki daya, suka juyo

mana. "Ina son ku sani wannan karon kuna tsaka da rayuwa da mutuwa, anan inda zamu shiga ana samun guguwar sahara, sannan akwai kunamar sahara masu matukar hatsari, don haka ku kula wani lokaci idan ta kama zamu iya kwana a cikin saharan." Wannan masifar dame yayi kama? Na fada a raina, ina kara rungumar Babyna.

Bakina dauke da ayatul kursiyu, haka muka shiga saharar zuciyata wata irin bugawa take, domin kuwa wani tsoron ne ya shigeni. Haka muka cigaba da tafiya sai da muka shiga tsakiyar mun bar inda muka fito da tazara me yawan gaske, sannan bamu isa inda zamu wuce ba,wata irin guguwa ta taso da wani azazzben karfi, tayi ta watsi da mutane. Ihu kawai kake ji tare da kukan Yara da mata. A take muka kara rikicewa, gashi ko gabanka baka gani, sannan wani abin da ya kara gigita mu shine yadda mutane ke fad'awa cikin sahara, wato idan guguwar ta kawo sura sai kasar ta zuke mutum. Na zata iya fim ake irin wannan abin sai gashi yau a kan idanuna ina ji ina gani mutuwa a cikin sahara tana kara kusanto mu, har wannan lokacin ina rungume da Baby, ban san me ya faru ba kawai sai ji nayi kamar.....

Shahararu goma aduniyan kayan mata wato m zee kamshi kayan mata kenan inakuke matan kwairai manyan Mata fah bamuna mataba Mata masu aji Wanda tasan kanta agidan mijinta kozokuyi gyara masu kyau da inganci Wanda zaisa oga nishadi yasashi farinciki atare dake kayanmu wane yaro sai uban yaro kinsha zumar makalemata dare daya wanka goma wanan set ne na kayan kwairai akwai fati budurwa mumuna da aeki Dan miyau malaka to shu,Umar Zuma zumar kiba gari kiba Zuma me lakani ningi tsumin lahaula hadin miski ba ahira dawando garin me kabara kasa ruwa sama ruwa wanan magani ba ,a magana magani sanyi mekyu maza da Mata ci da kaza ci da cicibin vlp yan shila ci da kifi nama kayan sakiba na gida danawaje munadakaya kala kala fani kamshi munada shu uwar humra namu ba irin nasubane akwai turare 24 hr turare kabasa Dana gida masu Dadi gakyau ga kamshi 08063845136

□□ Hala Zahrah ko Baby daya zai mutu kafin a fita a sahara.....□□
#Mai_Dambu
[2/22, 11:31 AM] Cutie cutie pie: *BAKIN HAURE....□□*

{Greed for Money is the roots of all evils□}
Arewabooks:maidambu41
Wattpad:Mai_Dambu
Mallakar:Mai_Dambu

Assalamu alaikum barkanmu da warhaka da fatan kuna cikin koshin lafiya, karku manta da wannan Kamfani mai albarka mai kawo muku kayan bukata cikin sauki da Aminci da Inganci.
Wato TA RASULU MULTIPURPOSE. YA SAKE DAWO MUKU DA KAYAN NAN MASU ARMASHI DA DANDANON KOWACCE MACE TAURARUWA CE.

_____
MARKADADDIYAR GYAD'A
HADADDEN KAYAN SHAYI
GARIN KOSAI NA TAFI DA GIDANKA.
GARIN TUWO
GARIN KUNU YAR ASALI
CURRY ME DADI
SPICES
TYME
YAJIN DADDAWA ME KYAU
GARIN DAN WAKE
JAN YAJI MAI DAD'I...

BUGU DA KARI MUN TANADAR MUKU DA KAYAN FITAR SALLAH DA NA SHAGALIN SUNA DA BUKUKUWA.
ATAMFOFI, LESHINA, MATERIAL, SHADODDI, YADUDDUKA NA MAZA DA NA MATA, JAKKUNA DA TAKALMA.
WANI ABIN SAI KUN ZO TA RASULU MULTIPURPOSE DOMIN KASHE KWARKWATAN IDANU.
ZAKU IYA TUNTUƁARMU A WADANNAN NUMBOBIN.. 08086639163 - 09030168590....
MUNA DAKON SAYAN DAI-DAI KO SARI.....

021

Ni dai ba zancen ga abinda ya faru ba, sai da gari yayi haske sannan muka fahimci dayawanmu, sun b'ata a sahara. Shafa baby nayi na ganta a bayana har lokacin, ajiyar zuciya na sauke tare da fara niman hanyar fita, a hankali nake tafiya ina niman Ummi ashe guguwar tayi gaba da ita can, mune yan baya da abin ya fi ritsawa da mu, don haka a hankali muka yi ta bayyana daya bayan daya, muka isa inda suke jiran mu, kafin wani lokaci mun sake haduwa sai dai ba dukkanmu aka kuma haduwa ba, wasu sun bace wasu kuma sai gawarwakinsu. Da sassarfa uwar mugu ta amshi Baby. "Da fatan babu abinda ya same ta?" Girgza kai nayi ina son tambayarta Addah. "Duk suna lafiya, karfin tsayawarmu anan kece, domin Yallabai yace ba zai bar nan ba, sai an samo mishi ke da Baby." Ta cigaba da duba yarinyar har wurin shi, amsarta yayi ya hure mata fuska saboda yan kuran da suke fuskarta.

Haka muka cigaba da tafiya har sai da muka ji babu dad'i, domin wasu sun tafi, bamu tsaya ba sai da rana ta faɗi, a wani ƙaramin gari, tun kafin mu shiga garin na fahimci mutanen garin suna maraba da zuwanshi, garin dauke yake da kabilu biyu, hausa da fulani, domin ga alamu sune suka kafa garin. Sannan kowa ka gani yana da abin yi, ma'ana Babu wanda zaka gani yana zaune haka. Gaishe shi ake yana amsawa har muka bar cikin kauyen muka kara nausa daji, anan ne na fa kara yarda Allah daya gari Banban. Dajin da muka nufa gona ce ni nace lambu, babu irin shukar da babu a cikinshi, sannan akwai cigaban zamani. Lokacin da muka isa wucewa damu aka yi wasu gidajen da suke zagaye da wani gida can, gaba da gidanshi. Yanayin gidan kamar irin dakunan kwanan dalibai ne, gado da katifa har da bargo. Kwanciya muka yi barci yayi gaba damu.

***

Niamey.

Suna kwance wuri guda, hannunsu sarkafe da juna. Kana ganinsu kasan lovers ne na gayawa yan gari. "My heart meke damunka?" "Hmmm! Kudi naje hajiya ta bani ta hanani, raina a b'aci na zo nan." Shafa kanshi Sajjid yayi yana faɗin. "Kamar nawa?" Mikewa yayi yana faɗin. "A'a ka barshi zan tafi na sayar da motata." "Kana dani kace zaka sayar da motarka, baka yarda ina sonka ba ne? Kasan yadda iyayenmu suke gaba da juna amma kake tsammanin zan iya rayuwa babu kai? Ko wancan mutumin gidanku ba zan tab'a yafe mishi ba."

"Idan na yafewa kowa, Majid ba zan yafe mishi ba, sai na saka shi biyan abinda ya aikata." Sai da Sajjid ya gama hasala Amaan Mamman Ba'are, sannan ya dauki kudi masu yawan gaske, ya bashi ya kai hannu fuskarshi. "Kayi hakuri nasan Aryan da Majid yan uwanka ne, amma ina matuƙar jin haushinsu, ina ta kokarin koyawa kaina dauke kai akansu amma na kasa. Ka gafarce ni." Sajjid ya faɗa kamar zaiyi kuka, a rikice Amaan ya rungume shi. "Zan taya ka lallubar hanyar da zamu ga bayansu."

"Allah!"

"Da gaske zan iya kome matukar zaka yi farinciki." Murmushi Sajjid yayi yana faɗin. "Ban yarda ba, don na baka kudi kake fadar haka." Mai da mishi kudin yayi yana faɗin. "Bana bukatar kuɗinka, lokaci zai nuna maka ina sonka ne don Allah ko kudinka."

Murmushi Sajjid yayi yana juya idanu ya ce mishi. "Dauka ka tafi nasan kana sona ne don Allah, wasa nake maka." Ya fada yana cusa mishi kudin tare da mishi chakulkuli.

Dariya suka saka bakiɗayansu. Sai da suka yi wanka sannan Sajjid ya raka Amaan har wurin Motarshi ya bar gidan, kiran Mahaifiyarshi yayi yana faɗin. "Jakin yaron nan ya faɗa fa!" Ajiyar zuciya Tani tayi ta ce mishi. "Ban yarda zai iya mana wani aiki ba, ka dawo haka ina son ganinka."

"An gama!" Ya fada yana shafa ciwon da yake goshinsa. "Kada ka dauki lokaci." "Tow." Ajiye wayar yayi yana hararar shi, tabbas idan ya samu hali sai Hajiya Tani ta biya abinda ta aikata, ba ita ta haife shi ba ko ita ta halicce shi sai ya mata abinda ba zata manta da shi ba, kuma yanzu ma zai cigaba da mata biyayya. Tun yana Yaro take azabtar da rayuwarshi har girmanshi bai huta ba, yanzu ma don yana da abu me muhimmanci ne ya barta take raye. Yasan duk wannan fadi tashin da yake ba don kanshi yake ba, iya ita kanta yake mata, sannan shu'umar mace ce ta gaske da ba zata iya daukar rainin hankali ba, yasan ita ce ta haife shi, amma baya tunanin zata iya d'aga mishi kafa, idan ya mata kuskure shi yasa a duk lokacin da yayi kuskure da girman shi sai ta illata shi.

Shi kuma a nashi tunanin yayi girman da dole ta daina dukarshi, domin yau da gobe ya wuce wasa, sannan ba zai cigaba da zuba mata idanu tana dukar shi ba.

--

Washe gari.

Hajiya ta hada kan Iyalanta zuwa Marad'i, har da Amaan yana Motarshi a baya, Hajiya da su Aryan suna mota daya, sai hira ake kamar yadda suka saba ana zolayar juna, Aryan ke tuka motar, shi yana zaune a gefen Aryan din, idanunshi rufe. *Ka taimaka min kada na mutu!* Bude idanunshi yayi yana kallon gefen hanya, tare da juyowa yana kallon su Hajiya da suke dariyar Widad, ta dage sai magana take tana mita. "Ya dai Hammayo?" "Babu kome." Tabbas yaji muryarta, amma kuma yasan don ya damu kanshi jiya da niman Umaimah bai samu number ta ba, asalima jiya har da mafarkin abinda ya faru, yana son ganin likitan da yake mishi therapy, lumshe idanun yayi cikin wata irin gajiya, domin baki daya yana jin wani sabon yanayi na kara kusanto shi, kara jingina yayi da motar, ya shafa fuskar wayar shi da aka sauya mata screen. A hankali ya gwada kiran Ammar. Ai kuwa yana shiga ya ƙara bude manyan idanunshi masu kyau da sheki. "Ammar ka nimo min number da zan samu Umaima."
"Ok Sir ya kake ya hutun naka."
"Alhamdulillahi! Sir sai muka ji labarin ba zaka dawo ba. Sir"
"Zamu yi magana an jima;" ya fada yana kashe wayar. "Wai da gaske ba zaka koma Nijeriya ba?" Inji Aryan, "I ba zan koma ba " ya faɗa yana kauda kanshi,karar da wayarshi tayi ya sa shi duba screen din wayar. Shiga kan message din yayi ya tura mishi. "Thanks!" Sannan ya danna number, can sai gashi ta shiga. "Ya yarinyar nan take?" "Eyeeeee!" Bakiɗaya suka zuba mishi idanun suna jiran abin da zai fada, "ok please ki bincika ina son sanin yadda take." "Amma ya kamata kayi min sallama sannan ka gaishe ni!" "Kin ga bani da." "Yes nasan baka da lokacin gaisuwa. Nima na bincika last month an ce an samu crisis a garinsu." Cikin wani tsuke fuska ya ce mata. "I don't care Koda ace garin babu kowa, ki nima min information akanta. Domin ina son sanin yadda take ne." "But niman abu kake sai nake jin babu dad'i kamar kana saka ni lallai sai na maka abinda." "Ok taimaka min" ya faɗa a gajiye da kuma son maganar ya ƙare. "Shi kenan zan bincika in sha Allah."

A hankali ya sauke wayar daga kunnenshi yana me fatan Allah yasa ba mutuwa tayi ta sanadin abinda ya farun nan ba, domin bai san me zai ce ba. Zufa ne ya shiga karyo mishi Aryan da Hajiya kuwa sun tsare shi da idanun suna son ƙarin bayani. Juyawa yayi ya ga yadda suka saki baki. "Wacece ita?" "Aaaah ba fa wani abu ba ne, kawai na mata treatment ne a gidana." Daga haka ya ja bakin shi shiru , duk yadda suka so yayi magana gum yayi da bakinshi. Zurfin ciki irin na Abdul Majid ai ya b'aci, ita kan Hajiya tayi mamakin yadda aka yi ya bukaci jin labarin wata. Tasan duk inda yake rayuwa bata taɓa jin labarin mace a tare da shi ba, duk da taso hada shi aure da Yar Kanwarta wato Zaytoonah, amma al'amarin yaƙi yiwuwa asalima tunda tayi mishi maganar aure bai kara yarda ya bada fuska ba, har suka isa marad'i bai ce uffan ba,

itama bata kuma yarda tayi magana ba, sai da suka isa Gidan Alhaji Abubakar Abzin, dake ya tashi daga tsohuwar unguwar da suka san shi. Aryan kadai yasan unguwar da suka koma.

Sun same shi a gida, Hajiya na bayan Aryan ita da matar Aryan da Yaranshi, Majid yana mota yana waya. Suka shiga cikin gidan, yana kallon Amaan Mamman Ba'are ya fito tare da Matarshi, da Yaranshi sai lokacin ya bude motar shima ya fito suka kalli juna. "Hammayo ina wuni!!" "Lafiya!" Ya faɗa, don ya lura matar Amaan bata da nutsuwa da tarbiyya, yaran ma gasu nan kamar su kamar uwarsu, an musu shigar diban albarka. Dauke kai Amaan yayi, hala yana jiran Majid ya gaishe shi. "Daada ina kwana!" Inji Amir. Daukar Yaron Majid yayi, yana ce mishi. "Lafiya lau Amir Ba'are." "Daada kafi Abbanmu kyau, kuma ka fishi kirki." Murmushi yayi yana kallon Amaan din. "Baya daukarka ne?" Girgiza kai yayi yana faɗin "Daada kana dariya shi kuma baya dariya." Murmushi ne ya kwace mishi yana kara rike Yaron, da sallama suka shiga babban falon gidan. "Daada nima ka ɗauke ni." Inji little Abdul. Ajiye Amir yayi ya dauke shi yana dariya. "Abdul Majid kannenka sun maka wayo kaga sun tara zuri'a saura kai." Murmushi Iya tayi tana kallon Abdul Majid, ta nuna shi da sandarta tana faɗin. "In sha Allah, Matarshi da uku-uku zata cika mishi iyali."

Murmushi ne ya subucewa Hajiya, ta ce mishi. "Allahummah Amin, Iyah Allah ya yarda." Ta fada tana kallon Majid da yasa fuskar shanu. Wasa da hannun Abdul yake. "Captain Allah ya kawo mana kai kenan " murmushi yayi yana me sunkuyar da kanshi, "Eh Abba!" Kura mishi idanu Alhaji Abubakar Abzin yayi kafin ya ce. "Allah ya jikan Mamman da rahama! Ya yafe mishi kurakuransa."

"Allahummah Amin" suka fada baki daya,. Abincin da aka kawo musu, suka ci bayan an basu wuri. Bayan sun gama Hajiya suka shiga cikin gidan yan mazan suka nufi masallaci, basu dawo ba sai da aka yi la'asar sannan suka shigo, anan aka kara gaisawa sannan aka bude shafin hira. Kafin, suna hirar karamin D'an Alhaji Abubakar Abzin ya shigo. Mahdi Abubakar Abzin, sosa kai yayi yana faɗin. "Abba kayi hakuri don Allah." "Taya zan cigaba da barinka a matsayin lauyana? Dole na nemo wani da zai cika min alƙawari." "Ka kara hakuri dai Abba! Nifa ba zance ka biya ni ba, duk Lauyan da zaka dauka sai ka biya shi kudi me yawa." Daure fuska Alhaji yaji ya ce mishi. "idan har bukata zata biya ai shikenan babu matsala sai inbiya, amma meye amfanin badi ba rai? Meye amfanin ka tunda bana biyanka jeka ka ajiye min aikina." "Alhaji ni zan nima maka wani lauyan." "Bana so ai Ni ba makaho ba ne."
"Allah ya huci zuciyarka." Ya zauna yana dauko wasu jakakkuna ya ajiye, waya Alhaji Abubakar Abzin ya dauka yayi magana. Kafin ya ajiye. "Lauyan Mamman yana zuwa." Kallon shi Hajiya tayi sannan ta ce mishi. "Abba ban gane ba!" Kallon Majid yayi kafin ya ce mata. "Majid zan bawa hakkinshi sanadin rayuwa da mutuwa, sannan ga shi nan ya bukaci na yi mishi wani aiki." Sunkuyar da kai Majid yayi, yana murmushin farinciki, yau Allah ya kwace shi daga tarkon Hajiya.

Can Lauyan yazo, "Malam Sulaiman!" Murmushi yayi yana faɗin. "Na'am Soja marmari daga nesa." Kallon Aryan yayi ya Banka mishi harara. Murmushi yayi ya ce. "Ba zaka gane yadda rayuwa da mutuwa take ba, shi yasa kake min kallon munafiki." Gyaran murya Alhaji yayi sannan ya bude taron da Addu'a, kafin ya ciro wasu takardu ya mikawa Mahdi. Shi kuma ya mikawa Lauyar Mamman Ba'are, shi kuma ya mikawa Majid, ya amsa yana kallon Alhaji Abubakar Abzin, "takardun ka ne, tun lokacin da aka haifeka Mamman ya bude maka kamfani anan da katsina." Sunkuyar da kai yayi yana kallon kasa, "Alhaji Mamman Ba'are bai kyauta ba, amma kuma ya rayu da boye kaunarka domin kada a kassaraka. Ke kanki ni nace ya nisanta ki da iyalinshi domin nasan cewa zaki zame mishi alkhairi." Mikewa Aryan yayi ya ce."ku dakata!" Ya nufi Amaan, kamar wani dan sanda haka ya shiga caje shi ya fitar da kome daga waya har agogon hannunshi, da zobe hatta botir din kirjinshi, a hankali wani abu ya fado. "Hmm!" Hajiya tace tana kallon Amaan cike da takaici, haka Aryan ya fitar kome. "Ko zaki bani sarkar wuyarki?" Hajiya ta mikawa Matar Amaan hannu. "Tow" ganin yadda suka tsareta da idanun. Haka ta mika musu harda agogo da dan kunnenta. Aka fita da shi waje, "Amaan baka da kunya. Baka da kunya baka da

kunya ba zan maka baki ba amma ina rokon Allah ya shirye ka." Ko tari bai yi ba, "Abba ka cigaba." Gyara zama yayi yana kallon Amaan cike da takaici. "wancan takardun naka ne, wannan kyauta ce bayan an haifeka ya samu alkhairi mai yawan gaske, haka yasa ya cire wanan ya ce na baka naka ne, Hajiya Abdul Majid ya nemi na baki wannan takardur kiyi hakuri ki fahince shi." Amsa tayi ta ga takardar sallama ce daga aiki. Kallonshi tayi tana faɗin. "Ban san me yasa ka yanke haka ba, amma nasan kana da hujja me karfi."
"Aryan zai rike matsayinki na Chairwoman zai zama Chairman na kamfanin Ba'are, Anisah zata rike matsayin CEO!" Kallon Abdul Majid suka yi, sunkuyar da kai yayi yasan sarai irin kallon da Aryan yake mishi. "Amaan zai rike board director. Sa'adatu kin girma da zaki hakura da wannan gwagwarmayar, Abdul Majid ya bukaci haka domin ki huta."
"Abba shi fa?" Kallonta yayi yana son fadar mata abin da Abdul Majid din ya yanke amma yana shakkar yadda zata dauka. Mahdi ya ce mata. "Zai tafi karatu ne jami'ar sojoji da yake kasar Afrika ta Kudu." Ji tayi harshen ta ya mata nauyi da tayi magana, tana son tayi magana amma ta kasa tilas tayi shiru tana kallon Majid, "kin san me yasa bai bawa Jamilah wani matsayi ba? Saboda ga takardar asibitin shi zata rike matsayin shugaban asibitin. Amaan Mamman Ba'are zai rike matsayinshi ne baki daya."
Ajiyar zuciya Hajiya take saukewa a kai akai, cikin Murmushi Lauya yace. "idan Hajiya ta ce zata bawa Aryan matsayinta sai an sakata gaba da magana amma da mai gayya me aiki ya daura wanda yake so zai yi wuya a samu matsala." "Wallahi haka ne!" Suka fada bakinsu a haɗe. "Abba Alhaji ya gama abin da ranshi yake so, nima ina niman izinin nayi wanda raina yake so!" Murmushi Alhaji Abubakar Abzin yayi yana faɗin. "Kiyi yadda kike so!" "Aure nake son yayi, kuma na zab'a mishi yarinyar da zai Aura.....

Shahararu goma aduniyan kayan mata wato m zee kamshi kayan mata kenan inakuke matan kwairai manyan Mata fah bamuna mataba Mata masu aji Wanda tasan kanta agidan mijinta kozokuyi gyara masu kyau da inganci Wanda zaisa oga nishadi yasashi farinciki atare dake kayanmu wane yaro sai uban yaro kinsha zumar makalemata dare daya wanka goma wanan set ne na kayan kwairai akwai fati budurwa mumuna da aeki Dan miyau malaka to shu,Umar Zuma zumar kiba gari kiba Zuma me lakani ningi tsumin lahaula hadin miski ba ahira dawando garin me kabara kasa ruwa sama ruwa wanan magani ba ,a magana magani sanyi mekyu maza da Mata ci da kaza ci da cicibin vlp yan shila ci da kifi nama kayan sakiba na gida danawaje munadakaya kala kala fani kamshi munada shu uwar humra namu ba irin nasubane akwai turare 24 hr turare kabasa Dana gida masu Dadi gakyau ga kamshi 08063845136
#Mai_Dambu
[2/23, 4:28 PM] Cutie cutie pie: *BAƘIN HAURE....□□*

{Greed for Money is the roots of all evils□}
Arewabooks:maidambu41
Wattpad:Mai_Dambu
Mallakar:Mai_Dambu
022
"AURE!!" ya furta da karfi, yana me toshe bakinshi. "Eh aure zaka yi, aure nace zaka yi ko ba zaka yi min biyayya ba ne?" Idanuwanshi suka yi jawur ya kalli Aryan da Mahdi, mikewa Aryan yayi ya cewa Nabeeha. "Tashi muje cikin gida." Shima Amaan tashi yayi da Matarshi, domin kuwa ya fahimci maganar ta manya ce. Yadda fuskar Majid ya koma kamar zai nufi filin yaki, yasa kowa ya mike suka fita daga falon. "Hajiya ba zan iya aure ba." Cikin fushi ta ce mishi. "Wacce karyan kake tunanin zaka min kuma? Duk duniya kowa gani yake nice na rike maka kan maciji kake wasa da jelarshi, karewa har cewa ake ina zaune zaka kwaso min abin kunya duk wannan bai

isa ka fahimci yadda nake rayuwa akanku bane? Majid ina son rayuwa ina son farinciki, amma na zabi na zauna da ku domin kuyi farinciki. Domin ku rayu cikin salama sannan ku zame min ribar hakurina na zauna daku, Ashe ban cancanci ka kyautata min ta hanyar yin auren ba?" Ta fada muryarta na rawa, kanshi a matukar sunkuye duk maganar da take yasan gaskiya ce kuma duk abinda ta faɗa gaskiya ne, amma kuma shi ba zai iya faɗa mata cewa bai da lafiya ba, ba zai iya cewa ga halin da ya tsinci kanshi ba, sai dai a shekarun baya .

A banɗakin gidan horan yara marasa jin magana, wannan tashin hankalin ya same shi. Jikinshi ya tafi baya da wani amfani sai fitsari, bata wani motsin sai dai yayi fitsari kawai. Sannan yanayin rayuwarsa bai bashi damar kallon wata mace da sunan soyayya ba, ya kasa sakin jiki ya yi soyayya domin idan ya ce zai yi soyayya me zai bawa mace? Saduwa tana daga cikin shika -shikan aure, shi tashi tazugen bazata iya amfanar shi ba balle wata. Sannan har yau baya jin zuciyarshi tana da wata shauki akan mace, abin da ya sani ko aiki ne ya haɗasu da mata yana tsayawa yaga sun yi nasara, haka yasa Umaima ta makale mishi. "Kuna gani ina magana ya bawa iska ajiyata? Abdul Majid ba zan kunshi bakin cikin mahaifinku na kunshi naka ba." Mikewa yayi zuwa gabanta. "Hajiya ki min uzuri, don Allah." "Na maka uzuri fa kace min? Na hana kaina farinciki na gina ku shine zan maka uzuri? Gaya min Meye matsalarka?" Hadiye yawu yayi yana kallon yadda take cikin b'acin rai. "Hajiya duk matar da zaki aura min, karshe wahala zata sha, domin idan ta zauna dani."

"Maza kake so kenan?" Inji Alhaji Abubakar Abzin, da sauri ya juya kanshi yana kallon Alhaji Abubakar Abzin, idanunshi har wani shekin kwalla yake tsabar tashin hankali. "Abba da ace zan so mazan da nayi farinciki,tunda a karshe dai na fahimci inda zuciyata take amma abin bakinciki babu maza da matan da suke iya burge ni ko shiga rayuwata. Duk wanda na zauna da shi don aiki ne da wani halin rayuwa"

"Ita yarinyar da kace a nimo maka fa?" Hajiya ta kara watsa mishi tambaya. "Yarinyar nan hatsari ne ya had'a mu, domin na bugeta da motana ne, kuma nayi mata jinya Hajiya ki fahimta auren idan nayi karshe."

"Abba ka zama shaidana idan Abdul Majid bai yi aure ba, tow kuwa sai dai ya zab'a ya hakura ya ajiye aikin shi ya zauna anan." Da sauri ya kalleta yana jin kamar kanshi zai buɗe wani irin sara mishi yake yana jin jiri. Harshensa yayi wani irin nauyi, so yake ya fada musu ba zai iya rike mace har ya mata kome ba, haka yasa shi jin wani irin jiri-jiri kafin ya ankara duhu ya mamaye mishi idanu, haka ya zube a gaban Hajiya a sume. Sai gashi ita tafi kowa shiga damuwa.

Salatinta ya shigo da Amaan, da yake makale. Lauya Sulaiman ya watsa mishi ruwa yana kwance jikin Alhaji Abubakar Abzin da ya rike shi yana tofa mishi addu'a. "Ba zance lallai kada kiyi yadda kike so ba, amma yana da kyau mu hakura da al'amarin auren nan." Wani irin kuka ne ya kwacewa Hajiya tayi ta yi ta kuma yi, muryarta yana rawa ta ce. "Abba don Allah kada ka hana ni yimishi aure, domin kuwa ina matuƙar son yayi aure. Duk wannan shiri ne."

"Ba shiri bane, tun ranar da Mamman ya gaya min ya bar shi a gidan horan kangararun Yara, ban kara yarda na zauna ba. Lokaci zuwa lokacin ina kai ziyara naji halin da yake ciki. Yaron nan ya sha wahalar rayuwa, idan kika ji abinda ya same shi ba zaki kara barci ba. Don Allah ki kyale shi ki mishi fatan Allah ya bashi lafiya."

Wani irin sanyi ta ji ya lullubeta, bata taɓa kawowa da gaske bai da lafiyan ba, domin a tunaninta zai tsarewa auren da zata kakaba mishi ne, amma kuma anya zata yarda da su? Tunda ya iya ajiye mata takardar sallama, babu abinda ba zai aikata ba don kada Alhaji Abubakar Abzin yaga kamar tana da bala'in taurin kai ta share hawayenta, amma a kasan ranta sai anyi auren nan ko zai mutu ne idan aka yi auren don ubanshi ba zata yarda ta ganshi haka babu aure ba, don haka ta dauke kai tana share hawayen da yake zubo mata.

Ganin yadda yake barci yasa baki daya aka yi shiru, babu wanda ya kara tada zancen. Asalima kowa tausayin Hajiya suke ji hatta Amaan da yake ganin duk wani

abinda ya faru da laifin Hajiya tun farko. "Tow ki daina kuka mana, ba gamu a raye ba, idan mutuwa aka ce zai yi ai kowa ya huta." Juyawa Aryan yayi yana kallon shi. "Dadina da kai baka boye waye kai? Gab'o kawai." "Kai waye gab'o." Ya taso a fusace. "Idan bakincikin Mamman Ba'are bai kashe ni ba, bakincikin abin da kuke aikatawa ya isa ya kai ni kabarina, don Allah ku bari." Ta fada tana kuka. "Hmmm Alhaji meye kuskurena akan Yaran nan? Jama'a su jefe ni, suma su koma gefe suyi dariya, Alhaji idan nace maka bana jin dadin rayuwata zaka dauka rashin godiyar Allah ne ko? Tow wallahi bana jin dadin rayuwata." Ta fada tana kuka, "sun mai dani mahaukaciya, basa jin magana ta, basa son junansu kamar su kashe kansu suke ji don Allah ya ake son nayi?" Baki daya sai jikin kowa yayi sanyi. "Alhaji da zaka Duba zuciyata, Yarana ne a cikinta,, ina son su hade kansu ina son na gansu cikin farinciki. Ina son nayi alfahari da haihuwarsu, sai dai idan na cire maka Aryan da sauransu, Amaan zai kashe ni. Bakincikin shi zai kai ni lahira ban shirya ba. Amaan ya zame min wake daya me kona gari." Yadda take kukan kawai xai saka kaji kamar ka tayata. "Ban san meye nayi mishi na kuskure ba, ya tsani yan uwanshi mata da maza ba, Alhaji Abubakar na hakura da kome na zauna da mutumin da ya haife ni kasan ba karamin al'amari ba ne. Mace ta zauna da namijin da tasan bata sonshi. Kuma ta zauna akan babu yadda zata nime hakkinta. Alhaji amsar ƙaddarata da nayi hannu bibbiyu shine laifina ko zama da nayi nai ta haihuwarsu!" Yadda Hajiya take kuka yasa bakiɗaya tashin hankalin da suke ciki ya nunku. "Idan da ace Amaan yana da adalci ba zai tab'a had'akai da makiyana ba, nawa zasu bashi? Nawa suke da shi? Bana son nadama tazo mishi bayan ya haɗakai dasu sun kashe ni."

Yadda take kuka yasa Majid ya tashi da matsanancin ciwon kai, wanda yasan baya raba daya biyu jininshi ne ya hau. Hajiya bata fasa fadar abin da yake damunta ba, tana ganin idan bata fada ba, tabbas kafin su koma Niamey ta mutu, shi yasa ta hakura ta fadi abinda yake damunta ko zata samu sauki. Kuma bata fasa fitar da abinda yake ranta ba, domin taji sauki kuma Allah ya taimaka tana faɗa tana jin kamar ana zare mata k'ayar da yake ranta, ruwa Aryan ya mika mata, ta amsa ta sha sannan ta sauke ajiyar zuciya. "Allah kagani na fita hakkinsu, saura su ya rage su futa nawa."

"Kiyi hakuri Hajiya, Indai aure kike so nayi zan yi in sha Allah." Inji Majid yana dafe kanshi, "A'a Majid kayi yadda kake so, ba sai kayi auren ba, tunda baka da lafiya." Ta fada tana share hawayen da yake zubo mata, "Aryan don Allah kai ni, asibiti kada na fadi don zan iya samun shanyewar b'arin jiki." Ya fada kamar zai fadi, da sauri ya tare shi, suka bar falon Hajiya tana me bin su da idanu, don a tunaninta shirinsu ne suyi wasa da hankalinta. Sai da ta ga sun tafi baki daya, sai Amaan kaɗai ya rage, yana son ya hada rigima. "Ba wani ciwon da yake damunshi, kawai renin hankali. Fisabilillahi Hajiya kina ji kina gani wai board director aka bani?" Sai kuma yayi kasa da murya yana faɗin. "Hajiya Chairman bai yiwa Aryan girma ba? Ki ga fa Yaro ne? Sannan."da

"Duk da Yaro ne bai saka dukiyarshi gaba ya lalata ba, har yau bai tab'a kaso biyar na dukiyar shi ba, kai ina naka dukiyar? Wai me kake yi da kudinka?"

Shiru yayi yana kallon yadda take tsare shi da idanu. "Wato Hajiya " "ya isa haka! Kada ka kara kawo min sukar kowa sannan da na san board director za'a a baka wallahi da sai na hana a baka, domin ba zai yiwu a dauki jahili a bashi abin da ba zai iya rikewa ba "

"Allah ya baƙi hakuri Hajiya, naga kamar ranki ya b'aci "

"Hakuri shi ya kashe Uwar jaki." Yadda tayi maganar yasa shi kame kanshi kada Hajiya ta kara fusata.

A can Asibitin kuwa, Mahdi shi ya musu jagora aka kwantar dashi bayan an saka mishi ruwa. Likitan da ya duba shi ya fito yana kallonsu kafin ya ce su same shi a office ɗinshi. Bayan sun shiga ya zauna yana ta rubuce-rubuce. Kafin ya d'ago kai domin har Aryan ya gundura da zaman ya ce musu. "Gaskiya jininshi ya hau, don

Allah a bashi lokaci ya huta, idan kuma yana da mata tow a dan janyeta daga gare shi, a nisanta shi da hayaniyar mutane."
"In sha Allah!" Suka faɗa, kafin ya ci-gaba da cewa. "zamu sallame shi nan da kwanaki uku, domin jikinshi yana ƙarƙashin kulawa ne. In sha Allah zuwa nan da wani lokaci zamu sallame shi." Haka suka yi ta godiya, sannan suka fito.
"Hajiya Sa'adatu tayi hakuri da maganar auren nan, Yaron nan yana buƙatar nutsuwa."
"Abba me yasa ba zai yi auren ba?" Kallon shi suka yi ta window, Alhaji Abubakar Abzin yana tuna ranar da ya kai mishi ziyara da yadda aka fito dashi baya iya tafiya. Sai riko shi aka yi. Idanunshi ne ya cika da kwalla. "Ya hadu da hatsari ne, bayan an kai shi gidan horon, Yaran da suka fi karfinshi suka mishi duka tare da doke mishi gabanshi. Wanda sanadin haka gaban ya mutu."
Rufe baki Aryan yayi da karfi jikinshi yana rawa, hawaye na zuba mishi kamar mace haka yake kuka yana kallon dan uwanshi. "Hammayo ba xai tab'a zama da mace ba kenan?"
"Gashi nan dai, bamu sani ba ko Ubangiji zai yi ikonshi, amma Abdul Majid yana cikin jarabawa." A hankali ya fashe da kuka, yana jin wani irin tausayin dan uwanshi. "Innalillahi'wa'inna'ilaihi'raji'un! Ubangiji mun gode!" Ya fada Aryan akwai karyayen zuciya, haka yake ga saurin kuka kamar mace, gani yake kamar dan uwansa zai mutu da damuwar lalurar.
Shi yasa yake nisanta kanshi da mutane, baya yarda ya zauna da kowa rayuwarshi cikin duhu, akwai wani irin shakuwa tsakaninshi da duhu tun yana Yaro, gashi ya girma da wannan trauma ɗin. A rayuwar Abdul Majid bai san soyayya ba, bai samu soyayya ba, ita kanta Hajiya ta haifi Majid ne amma bata damu da damuwarshi kamar yadda ta damu kanta da yayi aure ba.

Duk laifin abinda ya same su, laifin Alhaji Abbati ne, da bai saka Hajiya a cikin caca ba da babu yadda zata hadu da mahaifinsu ya kashe rayuwar dan uwanshi haka,. Sai yanzu yake fahimtar me yasa Majid ya tsani dukiyar Mamman ba'are, asalin don a gina duniya da dukiyar aka lalata musu rayuwarsu. Cikin shashekar kuka yake faɗin. "Saboda hab'aka dukiyarshi ya lalata rayuwar wanda babu ruwanshi."
"Asibiti muke kayi hakuri ka bar wannan zancen." Haka suka cigaba da zama har wani lokaci kafin Alhaji Abubakar da lauya suka bar asibitin tare da Mahdi,. Suka tawo da Hajiya tare da abinci, mika mata kome Aryan yayi sannan ya koma gefe yana kallonta, ajiye takardar tayi ta zauna tana kallon Majid. A hankali hawaye yake zuba mata, wannan wacce irin rayuwa ce? Me yasa kome yake zuwa mata haka? Me yasa daga wannan sai wannan? Shin anya bata yi wani laifi Ba tare da ta saninta ba.
Su da suka zo da zimmar kwana ɗaya, sai gashi sun kare da dibar kwanaki har sama da biyar, a na shida aka sallami Majid din, ba laifi ya ɗan samu sauƙi. Kuma dama yanayinshi ba mai yawan walwala bane, sai abin ya kara yawa. Ita kanta Hajiya ta damu sosai kamar ta cire ciwon. Haka suka tawo Niamey zuciyarta babu dad'i.
Lokacin da suka isa gidan A tsakar gida suka hadu da Nanah, tana jin rigima. "Ya zamu yi da wannan tsohuwar?" A hankali ya fito yana tafiya, kamar ba zai taka kasa ba, saboda rashin karfi da kuzari. "Kai Alhaji!" Ta fada tana mikewa tare da dogara sanda har inda yake ta ce mishi. "wallahi ka sake ka mutu sai Allah ya mana hisabi. Kai ma mutuwa zaka yi?" Ta faɗa, yadda tayi maganar zaka fahimci bata cikin nutsuwarta. "Munafukan can ne suka kaika zasu kashe min kai ko?" Kasa magana yayi yana kallon yadda take fada. "Nana likita yace a barshi ya huta." "Muje daga yau ni zan yi jinyar shi " duk da bata kaunarsu amma a lokacin da takira Hajiya take fadan ba zasu dawo bane, an barta kamar ba a damu da ita ba, gashi kayan abincinta ya kare, babu nama babu kome Haladu da Kamilu sunki saya mata, me take nufi na dauke mata Aryan shi ko zata mishi meye baya fasa saya mata kayan abincin.

Shi ne ta bata hakuri da gaya mata ai Majid bai da lafiya ne, bata san lokacin da ta rikice ba, tayi ta sumbatu tare da dorawa Hajiya laifin abinda ya faru gani take

kamar Hajiya ta kaishi aka mishi wani abu, sannan ga Amaan da dama can tasan munafuki ne. "Ina gaya maka kada ka sake kana yarda da mutane, domin kuwa wasu ba imani a cikin zuciyarsu. Sun sayar da imanin su ga duniya, Gara ka yi nisa da su domin kada a wayi gari babu magajin Abdul Majid ba'are. Sannan kasaka ayi ta maka addu'a da saukar Alqur'ani domin nasan makiya ba zasu Barka haka ba, li'ilafi aniyar kowa ta bishi daga yau har Sa'a ban yarda da ita ba. Domin dankareren dukiyarka yawa ce da ita a tow zamani na masu iya kashe mutum, waye ya sani ko shima Muhammad kashe shi aka yi!" Zama yayi a daya daga cikin sofa, yana haki yana kallon agogon hannun shi. "Nana zan huta kiyi shiru." "Alhaji duk abinda kace ai shi zan yi." Ta zauna tana kaskantar da kanta tana faɗin. "Ahtow nayi shiru, amma ina ga hatta Salamatu ban yarda da ita ba, waye ya sani ko har da ita ake shirya maka kitimurmura." "Nana jeki gida, an jima zan shigo duba baki." Ya fada yana daure fuska, domin idan ba haka yayi ba, ba zata kyale shi ba.

Sannan ya san halinta sarai sai ta kara mishi wani sabon ciwon kan. "Tow Allah ya baka lafiya, zan damo maka kunu na kawo maka." Yasan sarai idan yace mata ba zai sha ba, zata yi tsammanin bai yarda da ita ba ne. Haka yasa shi rufe idanunshi ya d'aga mata kai, domin kuwa baki daya bayan son magana. "Sa'adatu ki saka idanu akan shi domin ba zan yardaba idan wani abu ya same shi." Ta futa tana faɗin. "A kula da shi don wallahi zan iya shiga kotu da kowa." Tana fita ya kalli Hajiya ya ce mata. "don Allah a gyara min dakina." Daga haka ya juya musu baya, don baya son magana, Hajiya da kanta ta wuce dakin, ta gyara baki daya, sannan ta fito tana faɗin. "Na gyara maka" dakyar ya mike ya haura sama, koda ya shiga kashe wutar dakin yayi ya kwanta.

A hankali labarin matsayin da Abdul Majid ya bawa su Aryan ya zagaye cikin gidan, bakiɗaya suka taru a falon Nana suna mitar abin da ya faru, da akan me Majid zai yanke hukuncin babu shawara da su, musamman su da suke Yan uwan Babanshi. Yadda ake masifar Nana ta zuba musu idanu, can da suka ishe ta mike tana faɗin. "Yayi yadda yake so kamfanin nasu ne ba na wasu ba. Don Allah ku sakar musu mara na gaji da fitinarku, kada na kuma jin wata magana." Ta wuce dakinta bata kuma kula su ba, haka ta shiga ta bar su nan suna mita.

Wannan fitinar ta dame ta, kowa yasaka musu idanu. Kowa ya saka buri akan abinda ba na shi ba, sannan baki daya kowa burinshi ya mallaki abin da yafi na dan uwanshi, a kan wannan zasu iya kashe junansu akan abin da ba nasu ba,
***
Zahrah

Bana ce rayuwa tana da sauki a wurin Uwa irina ba, domin baki daya na susuce akan Babyna, zamowa uwa ba abu ne mai sauki ba. Haka na nakoma kome kamar mahaukaciya, bana barci da zarar naji motsinta duk barcin da nake na daina Kenan xan tashi daga barci har sai ta koma, wani abin da na kasa sabawa da shi, shi ne, da zarar na saka abinci a gaba Baby zata fara kuka, ba zata kuma shiru ba sai na hakura da abincin.....
#Mai_Dambuje
[2/24, 2:51 PM] Cutie cutie pie: *BAƘIN HAURE....□□*

{Greed for Money is the roots of all evils□}
Arewabooks:maidambu41
Wattpad:Mai_Dambu
Mallakar:Mai_Dambu

Hodjam Fire to fire Fitilar hikayar Dambuje, BAƘIN HAURE comments. Wannan Pagen na kune yan arzikinsssssssss zaku sheke min dariyata □□ Irin wannan comments a kwana a hantse sai Kyakyawa 😏 Baby Aminatu sai tasha Baloon din nan fa □😂Baby bata mutuwa fa sai hakuri

Assalamu alaikum barkanmu da warhaka da fatan kuna cikin koshin lafiya, karku manta da wannan Kamfani mai albarka mai kawo muku kayan bukata cikin sauki da Aminci da Inganci.
Wato TA RASULU MULTIPURPOSE. YA SAKE DAWO MUKU DA KAYAN NAN MASU ARMASHI DA DANDANON KOWACCE MACE TAURARUWA CE.

_____
MARKADADDIYAR GYAD'A
HADADDEN KAYAN SHAYI
GARIN KOSAI NA TAFI DA GIDANKA.
GARIN TUWO
GARIN KUNU YAR ASALI
CURRY ME DADI
SPICES
TYME
YAJIN DADDAWA ME KYAU
GARIN DAN WAKE
JAN YAJI MAI DAD'I...

_____
BUGU DA KARI MUN TANADAR MUKU DA KAYAN FITAR SALLAH DA NA SHAGALIN SUNA DA BUKUKUWA.
ATAMFOFI, LESHINA, MATERIAL, SHADODDI, YADUDDUKA NA MAZA DA NA MATA, JAKKUNA DA TAKALMA.
WANI ABIN SAI KUN ZO TA RASULU MULTIPURPOSE DOMIN KASHE KWARKWATAN IDANU.
ZAKU IYA TUNTUBARMU A WADANNAN NUMBOBIN.. 08086639163 - 09030168590....
MUNA DAKON SAYAN DAI-DAI KO SARI.....

023
Ko don na taso a tsakar gidanmu ne, ban tashi gaban Uwa ba, ban san yadda Uwa take handling yara kmr Babyna ba, akwai wani abu da na fahimta da zarar gari ya waye zata wuni barci, sai dare garinta zai waye duk da haka bai hana da zarar na saka abinci a gabana zata bude idanunta ta fara rigima ba, sannan baki daya a girman dakin da muke babu me iya tunanin ya taimaka min, Ummi da Addah kowa harkar gabanshi yake, sannan basu da lokacin da zasu tsaya lallai sai sun taya ni kula da yarinyar.

Bakidaya sai na kasa sabawa, da zarar dare yayi zan goyata ina yawo da ita har daren yayi nisa tayi barci. Na kwanta da ita a bayana, sannan zamu yi barci idan kuma sanyi ya dame ta hana kowa barci take, haka zasu yi ta tsaki suna mita. Gari na wayewa kowa zai kama gabanshi. Suna tafiya suna mita, ban tab'a fushi akan hakan ba.

Yazeed Hamir.
Asalinshi dan kasar aljeria ne, mahaifinshi babban attajiri ne sannan Basarake ne a babba a kasar , kuma Balaraben aljeria. Suna da kudi sosai sai dai shi Yazid ya lalata rayuwarshi ta hanyar shaye-shaye. Mutum ne da bai da yawan magana ko hayaniya, sannan akan abinda ya shafi sayar da kwayoyi baya da wasa. Domin ya bar ƙasarshi ta haihuwa ne yazo wannan wurin ya kafa inda zai na fitar da shu'uman kayan maye yana rabawa tsakanin kasashen Afrika. Shaidani ne na gayawa Sarkin gari, yana da wani irin sirrin da duk inda ya shiga sai ya fitar da kaya, zai yi wuya ya shiga wuri bai fitar da kayanshi ba, sai dai yana da rauni sosai matarsa da Yaran shi, biyu dukkansu mata ne yana matukar kaunarsu. Yazid ya bar gidansu ne tun yana shekaru ashirin da biyar a duniya, domin yana da matukar kiyayya da sarauta, domin a sanadin mulkin

da za'abawa Babanshi Mahaifiyarshi ta rasa rayuwarta kuma dama ana ta faɗan cewa ya sadaukar da ita ne ga mulkin shi, shi yasa ranar da ya fara jin labarin ya sami mahaifinshi da maganar, ƙaryatawa yayi shi kuma ya ce matuƙar ya tabbatar da haka sai ya bar mishi kasar da kome yaje yayi rayuwarshi,. Dake akwai mutanen da basu son Babanshi, sai suka yi amfani da haka suka tabbatar da cewa sadaukar da Amiratul Aminat aka yi, duk yadda Uban yaso mishi bayani amma yaƙi fahimta. Don haka ya saka kafa ya bar kasar da dukiyarshi a lokacin ya gama karatunshi a bangaren had'a magunguna.

Wannan abin yayi matukar yiwa mahaifinshi ciwo, har kwanan gobe yana zuba idon ganin shi, Yazid yana matukar tausayin mata da Yara, akan mahaifiyarshi ya kara jin tausayin Yaya mata, kuma wani abin da yake kara saka shi tausayinta, ita sikila ce. Sai akayi dace shi bai da shi, haka yasa yake son Reshmah kamar zai haukace da ta fara haihuwa ma bai tab'a ce mata ga zab'in shi ba, sunan da takeso take sakawa. Tozali da yayi da Zahrah yaji duniya bai tab'a tausayi da son wata Y'a mace ba kamar ta, sannan baki daya sansanin da suka zauna mutanen Yazid ne, hatta Uwar mugu dalilin da yasa Nawwas yazo nimanshi wurinta kenan, sai gashi kuma Nawwas din jin kamar Yazid din yana zuwa yasa shi guduwa da yan matan.

Matarshi itama balarabiya ce, Reshmah mace ce mai tsananin kishi da saurin fushi, sannan shima Yazid yana matukar kiyayye abinda zai saka kishinta ya fito har ayi tunanin wani abu. A wannan dajin idan kana son ka fita sai ka je an saka maka wasu kwayoyin da zaka masa safara da shi idan ka sha zaka je a cire maka, sannan kayi tafiyarka daga nan ka samu yanci, ba kuma zai barka ba domin abin shi kamar da siddabaru domin ko ka bar dajin ka manta kenan. Ba zaka kara tunawa ba, da haka Yazid yafi karfin abokan gabanshi, domin yana fito da kayanshi ta kowace fuskar ya sayar a waje.

Lokacin da muka zo garin ina cikin waɗanda aka rabawa aikin shara da goge gogen gidanshi, idan har Matarshi ta rigashi tashi hatta bango sai na goge, sannan babu ruwanta da ina da baby ko bani da Babyn, matar nan yar bala'i ce. Kafin Yazid ya fito na gama kome na bar gidan. Sai yamma kuma na koma.

Ban san me yasa ba ko yana sane da yadda matarshi take saka ni a gaba da fitinar aiki, ranar ina zaune a kofar gidan da muke sai gashi ya zo ina jijjiga Baby. "Babyn Zahran bata yi barci ba ne?" Juyawa nayi zan yi magana domin ban zata shi ba ne. Sunkuyar da kai nayi na ce mishi. "Yallabai kai ne?" Na fada ina jijjiga ta, ajiye wata jakar takarda yayi ya ce min. "Kawo min ita." A hankali na mika mishi ita har hannunmu yana gogan juna. Da sauri na janye nawa hannun, shi kuma ya cigaba da kallona. Yana me kallon inda kwanon abincina yake, na bude zan ci ta fara rigima. "Ki ajiye abincin anjima sai ki ci ga wannan ki ci." Ya nuna min jakar da idanunshi. Sai gashi na rikice baki daya, domin ina jin yadda yake bina da idanu, ban saba ba sai nake ganin kamar ba zan iya tsayawa da kafata ba. Jingina nayi na dauki jakar na bude, madara ce a kwalba sai gassashen nama, hadiye yawu nayi duk da ba laifi tunda muka zo ba laifi abincin mu yana da kyau, sannan a wadace muke samu. A hanya muka fuskanci matsala amma tunda muka zo abincinmu babu laifi. A hankali na fara bude takardar da ya nad'e namar, kamshinsa kawai yasa na hadiye yawu yafi sau goma. Na d'ago kai naga yana hidimar baby da sauri na fara ci, ban sani ba ko yana kallona domin ganin nama yasa ni jin duk wata yunwar da nake ji na tsawon watanni bakwai ta dawo min sabo fil, "ki ci a hankali." D'ago kai nayi naga Babyn yake wasa da ita, goge bakina nayi na cigaba da cin namar, har na koshi. "Zan tafi!" "Allah ya saka da alkhairi." Na faɗa ina sunkuyar da kai, koda su Addah suka dawo a gajiye, idanunta ya sauka akan jakar takardan, dauka tayi zata buɗe Ummi ta fauce. "Dalla bani." Dama kuma na rage musu ne, ganin kowannensu ya samu ba zai bawa dan uwanshi ba. Yasa na amsa. "Idan kuka yi hakuri na ku ne, idan kun yi faɗa ma naku ne." Na fada ina ciro musu na mika musu, faucewa suka yi suna jan tsaki.

"Wani dan iskan kika samu ya kawo miki?" Inji Addah, ban bata amsa ba na gyara mana kwanciyarmu da Baby. Washi gari da na shiga gidan aiki naga Matarshi sai

hawa da sauka take, har na gama aiki zan fita ya fito dauke da Yarshi. Murmushi yayi min na sunkuyar da kaina, na fita da sauri.

A harabar gidan naga alamar zasu fita ne, haka yasa na bar gidan domin yau bata min kakale-kakale ba, asalima kamar sauri suke. Ina dawowa nayiwa baby wanka. Sannan muka kwanta bayan mun karya.

12:30pm,
Ji nayi kamar ana tsaye a kaina a hankali na bude idona, ya sauka akanshi yana bakin gadon Ummi yana latsa wayarshi, da dan sauri na tashi zaune ina kallonshi. "Yau Baby bata yi rikici ba kenan?" Ya ajiye min irin jakar jiya.
"Wai ya sunan Babyn?" Tiririn da nake ji na kamshi yasa ni rikicewa domin yunwa nake ji, kuma sai karfe biyu za a kawo mana abinci. "Ban mata suna ba, baby muke kiranta."
"Ya sunan Mamanta?" D'ago kai nayi ina kallon shi, kawai sai ya cika min idanu. Sunkuyar da kai nayi ina faɗin. " Zulaiha!" Na zabi na fadi haka ne domin ya min kwarjini. "Ok bani ita!" A hankali na mika mishi ita, kamar mai tunani sai kuma ya ce min. "Hmmm! Ba zan saka mata sunan Uwarta ba, domin zata iya gadon halinta."
"Ka saka mata sunan Addah." "Ita criminal ce zata tashi da shaidancinta."
"Tow ka saka mata sunan Mamana!" "Ya sunan yake?" "Aminatu!" Murmushi yayi ya ce "sunan Kakata ce da tasoni sama da kanta." Ya fada yana shafa kan Babyn yana me mata hududa. "Maman Aminatu!" Murmushi nayi, tare da Mikewa zan karbeta ya ce min. "Ci abinci" ba musu na zauna na ci grill fish da chips a gefenshi. Sai da na gama ci ya mike, ya ajiye min yarinyar.
Ya tafi, lokacin sallah yayi na mike na wuce ban daki nayi alola sannan.na dawo nayi sallah, sannan muka kara kwanciyarmu, domin kifin akwai maiko. A hankali wata irin shakuwa da bansan daga inda ya samo asali ba, ta shiga tskanina da Yallabai Yazid, da farko sau daya yake zuwa, daga baya ya koma yana zuwa sau biyu. Da rana da kuma Yamma, a hankali idan yazo shirya Baby Aminatu, Addah kamar zata rufe ni da duka da taji sunan har da Min Allah ya isa, bata yafe ba don na saka sunan Mamana.

Da yamma idan ya zo ɗaukarmu yake muna zaga cikin garin, gonarshi da lambun shi har da gidan dabbobin shi. Yau ma haka ya saka ni a gaba, bayan ya kawo min wata doguwar riga da mayafinta. Muka shiga wani yanki ta Cikin gonar, mun yi dogon tafiya kafin ya kawo mu wani wuri a ƙarƙashin ƙasa, ya ce min. "Kin ga wannan wuraren? Akwai kofar da xasu fitar da ke har wani kauye, daga nan zaki wuce bodar Nijeriya da nijar ne da yake dole kaina, mu nan muna yankin River Benin ne.
"Ban gane ba?" Zama yayi yana kara murmushi ya buɗe kofar ya shiga shi da Babyn sannan ya mika min hannu na rike shi na sauko. "Kina da saurayi?" "Na'am?" Na ce mishi, ina kallon shi. Murmushi yayi min sannan muka cigaba da tafiya.

"Nace kina da saurayi?" Ya juyo yana kallona." Zare idanuwa na fara, da wasa da ya bakin mayafina. A hankali yake takowa na juya bayana naga ko wani abu yasa yake biyo ni, sai naga haka kawai koda na juya ya matso kusa dani sosai. "Baki da saurayin ne?" Hadiye yawu nayi na gyada kai na, a hankali ya sunkuyo da kanshi a tunanina sumbatar bakina zai yi, da sauri na kawar da kaina. A hankali ya kai hannunshi gefen wuyata ta wurin mayafina ya kad'e min gizo-gizon da yake kaina.
"Ki kula." Ya fada yana kallon kwaron. Hadiye yawun bakina nayi ina kara jin kamar zan saki fitsari.

Cikin larabcin da bai gama rike bakinta ba, Addah ta kara gyara zamanta ta ce mata. "Idan nayi miki karya, ki saka a kashe ni a binne gawata, amma yarinyar da Yallabai yake fita da ita yata ce, kuma zaki iya zuwa gidan mu, ki ga irin kyawawan kyaututtukar da yake kawo mata." Mikewa tayi tana faɗin. "Muje!" Haka Addah ta mike jikinta yana rawa ta ce mata. "Tow!" Suka tawo har gidan, wato ita Yazid zai ci

amanarta. Ita zai tsallaka yana bin karuwa da ta gama yawon karuwancin kafin ta fado hannunshi, bata kara sarewa namiji ba dan goyo da zani ba ne, sai da ta ga katon akwatin kayan da ya kawowa uwar da yar, ciwon bakinta tayi sannan ta juya ta fita cikin nutsuwa Addah kuwa murna kamar zata daka tsalle.

Haka Reshmah ta koma gida, ta zauna tana tunanin me zai faru, me zata aikata da zai bawa Yazid tsoro ita ba kalar Matar da zai ci amana bane . Bai isa ya ci amanarta ba.

---Sai dare muka dawo tun a hanya aka tare shi, ana gaya mishi abin da ya faru cikin wani irin yare, murmushi yayi ya ce musu. "Suwa laula!" (Shi kenan naji) kallonshi nayi domin ban tab'a zatan yana jin wani harshe bayan Hausa da larabci ba.

"Wani yare ne haka?" Murmushi yayi ya ce min. "Harshen darsa, yana da saukin amfani.". "zan koya!" "Zaki iya kuwa?" "Hmm!" Haka ya rako ni gidan sai da na shiga ya ce min. " Za a kawo miki abinci." "Tow na gode!" Daura yatsar hannunshi yayi a baki ya ce min. "Shiiii" hadiye yawu nayi. "Kada ki b'ata min alakata da godiya." "Shi kenan!" Haka ya bani Babyn muka shiga cikin gidan, yana fita yayi waya aka kawo min abinci, muna kwance aka buga kofar kallona Addah tayi na mike na bude kofar na amso abincin na fara ci, tashi tayi zata saka hannu Ummi da take gefen gadona ta doke hannun da wani sanda, sai da kashin hannun yayi ƙara. "Kika sake wani abu ya shiga bakinki sai na shakeki har lahira munafukar banza." Daga haka bata ci ba na kalli ummi ta dauke kai. "Me yasa kika hanata!" "Ba zata ci ba wallahi." Shiru nayi ina kallon Addah da ta koma ta kwanta. Ban kuma musu magana ba, sai da zan fita Addah ta ce min. "Bani Aminatu na taya ki goyanta." "Ba zata baki ba, duk abinda zai faru sai dai ya faru!" Inji Ummi. Fita muka yi, nima na nufi gidan Yallabai. A falon kasa na same ta a hankali naji jikina ya bani akwai matsala. Haka na wuce na fara aiki har na gama. Tana zaune sai da na gama zan fita ta ce min. "Ke jira ni!" Daidai shima yana saukowa daga sama, kenan ta shiga kitchen, kamar ya san nufinta, tana fitowa kawai ta watsa min soyayyen mangyad'a da ta dauko a fry pan.

Rumfa yayi min ta zuba mishi a bayanshi, bata san lokacin da ta saki fry pan din ba, "Yazid!" Ta kwalla mishi kira, bude idanu yayi a kaina."Yallabai!" Na kira sunanshi. "Jeki gida lafiya ta lau." "Yallabai bayanka fa?" "Ba kome, jeki"

Ya fada min da wata irin murya, da sauri na fita tana rufe da fuskarta tsoro ya kamata, hadiye yawu tayi tana kallonshi. "Me kike nufi?" Jikinta ne ya fara rawa, "don Allah kayi hakuri." Jan iskar bakinshi yayi ya yaga rigar tare da zama a bakin kujerar falon, da gudu ta fita ta kira Aseem ta gaya mishi, shi ya tafi har wurin likitan ya tawo dashi, suna shiga suka same shi a falon. "Garin yaya?" "Nice na zuba mishi ba da gangan ba." Bai ce uffan ba har likitan da Aseem suka yi ta cire mishi rigar da ya hadu da fatar bayanshi, ya zuba mata idanu. Cikin wani irin Imagining da Zahrah zata zubawa man gyadar nan a fuska. Sai lokacin ya iya bude baki ya ce Mata. "Nufinki Zeehra zaki zubawa?" Zubewa tayi tare da rufe fuskarta ta fashe da kuka. "Kayi hakuri sharrin iblis ne." Ta fada tana shasshekar kuka, haka ya cigaba da kallonta tana kuka. Yana wondering yadda zuciyarta ta mutu da tunanin ta nakasa mace yar uwarta, murmushi ya saki a hankali yana kallonta. "Sultan kayi hakuri don Allah!" Ta fada tana waiwayen bayanta. "Aseem!" Da rarrafe ta kama kafarshi. "Don Allah ka rufa min asiri Sultan kishinka ne ya saka na aikata haka, Sultan ba zan kara ba." " A bata abinci dare da rana, ta zauna a wurin sai na warke." Fashewa tayi da kuka kamar ranta zai fita,

"Sultan afuwa!" "Aseem!!" Zubewa yayi akan gwiwarshi. "Uwar Yaranka ce, kuma mace mai daraja a gare ka, kasan haka kuma kai da kanka ka gaya mana babu mace mai darajasama da Reshmah."

"Zeehrah tana da daraja, darajarta me girma ne!" Ya fada yana kauda kai. "Matar da nake aure idan bata ji magana ta ba nawa zata ji? Idan wani abu ne ya had'ata da yarinyar waye zata tinkara? Dole sai ni, wato shine aka gaya mata xata kona musu yar mutane. Idan ta lalata mata fuska fa? Fisabilillahi ace mangyad'a zata zuba a fuskar Zeehrah...

#Mai_Dambu
[2/25, 7:57 PM] Cutie cutie pie: *BAƘIN HAURE....□□*

{Greed for Money is the roots of all evils□}
Arewabooks:maidambu41
Wattpad:Mai_Dambu
Mallakar:Mai_Dambu

Muna da stone Veils da plain,sai hular Yara, masu kyau akwai veil na Yaran shima.

024

Kallon Aseem yayi kafin ya ce masa. "Ka fice min da ita ko kuma na had'a da kai." Haka ya saka Reshmah a gaba ya wuce da ita wani gidan da aka ware domin hukunta duk wanda ya ja da Yazid, gidan kamar gidan yari yake, sannan a cikin gidan akwai masu kula da kowa kawai ba zaka fita ba,ba zaka iya kome ba kana zaune a daki guda ga kome amma kuma takure kake.

Ya kaita can wani daki da yafi kowanne kyau, "Aseem don Allah ka roke shi."

"In sha Allah." Ya fada, yana me barin dakin, kuka ta fashe da shi a ranta tana kara shan alwashi sai ta wulakanta Zahrah matukar ta fito.

----- Tun da nake a rayuwata ban taɓa cin karo da irin wannan abin ba, domin kuwa ban zaci mangyad'a mai zafi zata watsa min ba, dafe goshina nayi ina mamakin kishinta. Ina zaune har su Addah suka dawo. Muna zaune ana cin abinci kawai muka ga mutanen Yallabai sun shigo cikin dakin, basu yi magana ba suka dauke ni. Zasu fita dani nace musu. "Ina da karamin goyo don Allah ku bar ni na dauke ta." Haka suka fita dani, dariya Addah takamayi tana cin abinci."Allah yasa su mata abinda ya wuce tunaninta."

"Kenan ke ce kika hada mata rigimar?" "Eh nice!" Ummi bata kuma magana ba, tana mamakin Addah.

Da suka wuce dani can wajen garin suka ajiye ni a gabanshi. "Kuje!" Kaina yana sunkuye. "Ke meye ya haɗa ki da Sultan?" Da sauri na d'ago kaina ina kallonshi, fuskarshi a rufe sai idanun shi kawai nake gani. Sake daka min tsawa yayi, na fashe da kuka, musamman da ya fidda wuka tsirararta. " Ban san shi ba." Na fada ina ja da baya, "Meye alakarki da Yazid?" Wani irin curewa yayan hanjina suka yi, jikina ya dauki wani bala'in rawa, na ja da baya ina girgiza kai. "Ba zaki gaya min ba kenan?" Ya kara daka min tsawa, kuka na saka mishi me karfi ina faɗin. "wallahi babu kome." "Ok tashi ki gudu" da sauri na mike tare da diba a guje, sai dai ko wurin ban bari ba, na ci birki sakamakon kartin mazan da na gani sun tare ko ina. hankali na a matukar tashe na waiga na ga sun zagaye ni. "Daga yau kada na kara jin labarin kin hadu da shi ko kin shiga gidan, idan kuma kika kara sakewa kuka hadu ko?" Ya fisgo ni tare da yaga min riga har kasa, kare kirjina nayi ya saka kafa ya tokare ni sai da na fadi. Ba a tab'a tozarta ni irin na yau ba, domin yana tsaye a kaina ya cire gabanshi ya shiga sakar min fitsari a kaina, sauran suka kwashe da dariya. "Wannan wasa ne, wanda zan miki ba fitsari ba ne, tsakanin cinyoyinki zan raba, nayi sukuwa a akanki yadda zaki ji rad'ad'in haka a ranki, naji labarin baki tab'a karo da namiji ba." Ya maida abin shi ya matsa a kaina, ya d'ago kaina ya dinga marina. Sai da naji kamar fuskar bata jikina, na karshe ne ya mare ni akan idanuna. "na tsane ki daga yadda Sultan yake zubar da kimarshi akanki." Suna gamawa suka watse daga wurin aka bar ni babu kowa. Haka na mike a hankali naji wani abu ya cika min zuciya na kasa kuka, har na kusa shiga gida, tun kafin na isa gidan nake jin Ihun Baby. Har na isa babu wanda ya kulata asalima a duhu suke. Banɗaki na Wuce ina ta kwara ruwa, ina wanke jikina sai da na wanke ko ina sannan na koma dakin.

Na dauke ta tare da rungumarta ina sheshekar kuka, daga Addah har Ummi babu wanda ya ce min, nayi shiru a hankali barci ya dauke ni, ga ciwon da idanuna suke domin ina ga da wani abu ya mare ni ba da hannu ba. Sai asuba na tashi nayi alola

nayi sallah, ina idarwa na juya na kwanta sai dai kamar yadda nake saka raina zan yi barci, ashe abin ba haka ba ne,. Wasu kartin maza ne suka kuma zuwa suka tafi da ni wannan karon ina ganinsu na dauki Babyna muka tafi, tun daga ranar ban kuma zama ko na minti biyar ba tare ina aiki ba, wahalace ta karu min kamar na mutu na huta, haka nake fama da aiki babu dare babu rana, sannan abinci sau biyu ake bani sai yanzu na fahimci akwai iyakata akwai iyakar wasu, Yazid iyakar wasu ne, shi din duniyar wasu ne da zarar na sake wani abu ya kara had'a ni da shi tabbas zan iya fuskantar mutuwa. Haka yasa nake addu'a ba dare ba rana, ina gayawa Ubangiji ya kawo min mafita da karshen wannan halin da nake ciki.

A bangaren Yazid babu ranar da ba zai tambaye su Zeehrah ba, an kai mata abinci Ya Baby take, babban burinshi ciwonshi ya warke ya tafi ya ganta, domin baya iya fita ko waje ne, yana cikin gida yana fama da ciwon.
Akwai wani abu da dayawanmu mata bamu gane ba, shine idan har namiji ya lakato batun dating da wata mace mafi alkhairi mu kyale shi, mu zuba mishi idanu. Idan kuwa muka ce zamu yi magana. Tow kuwa ya dinga abun da zai b'ata mana rai.

Gashi ko sati ba ayi ba, Aseem da Sharif suka saka dakyar ya fito Reshmah, amma abin da tayi ya tab'a zuciyarshi, sannan ba karamin hakuri da juriya yake da shi ba, domin da mace ce aka watsa mata mai da ba karamin jinya zata yi ba. Amma dake akwai kulawa kwanciyar hankali da nutsuwa kuma ana mishi kome ko wurin had'a magungunan shi baya fita anan ake mishi kome, tun ranar da abin ya faru Reshmah bata kwana a gidan da akai ta ba, amma kuma zaman babu dad'i. A wannan daren da sukayi abin da ya faru duk shirinsu ne. Ita da Yaranta shi Aseem yana tare da Yazid babu abin da ya sani.

***
Niamey.
Tunda farko da ace ta san matsalar nan na shi tabbas ko zata rasa rayuwarta ba zata tab'a barin shi da ciwon ba, "Hajiya!" Salamatu ta kira sunanta. "Na'am!" Ta amsa a sanyayye, "Shayin yayi sanyi." "Tow!" A hankali ta dauki kofin ta kurba kana ta d'ago kai tana kallon Salamatu. "Hmmm! Alhaji ya tashi ne?" "Eh yana dakin motsa jiki." Ajiyar zuciya ta sauke, sannan ta ce mata. "Shi kenan jeki." Juyawa tayi zata fita Hajiya ta ce Mata. "Salamatu Aryan fa?" "Tun dazun ya shigo suna tare da bakon Marad'i." Murmushi tayi sannan ta ce mata. "Shi kenan na gode." Tana fita magani ta dauka ta sha, sannan ta dan kishingid'a tana kallon gefe guda. Wani irin sakaci tayi da rayuwar Majid ya lalace haka. Hawayen da ta gaza tare shi yake zuba mata, tana jin kamar tadau ciwon a jikinshi ta dorawa kanta, bata son ta ce bata yafewa Alhaji Mamman Ba'are ba, amma tabbas shi ya lalata mata nata rayuwar da har haka ya shafi na wanda bai ji ba bai gani ba.

Yadda take kuka kamar karamar yarinya, domin Majid yana matukar bata tausayi, idan ta cire Matsalar Amaan tow Majid ya sauke kaso mai nauyi a zucuyarta. Bakiɗaya ta rasa inda zata saka hakkin Majid domin abin da ya same shi kamar laifinta ne, da bata yarda ta bi Alhaji Mamman Ba'are a lokacin ba tow da wannan abin bai same shi ba.

Amaan Mamman Ba'are.
Kallon juna suka yi, kamar zasu cinye juna kafin murmushi ya kwace mishi ya ce mishi. "Ban yarda da abin da kake faɗa ba." Lumshe idanunshi yayi ya bude a kan fuskar Sajjid. "Baka yarda ba kenan?" Dariya Amaan ya saka yana faɗin. "Lallai kuwa, hmm dukiyarshi bata da wani amfani tunda babu me ci haka zata yi ta habbaka yadda zamu san me zamu yi mishi."
"Hmm! Ban yarda Abdul Majid bai da lafiya ba. Na fi yarda da cewa bai da ra'ayin aure amma ace bai da lafiya ai maganar kawai tatsuniya ce." Mikewa Amaan yayi

yana faɗin. "Zan tafi idan lokacin da ka sani sai ka tsaya muyi magana." Sajjid bai ce mishi kome ba, har ya bar gidan. Wani irin murmushi Sajjid din yayi, ya kira Mahaifiyarshi ya gaya mata, shiru tayi, yanzu ne ya dace ta tashi ayi ta ta kare ko kuma ayi ta kasa. Idan Majid bai da lafiya kason shi Hajiya da Yan uwanshi ne zasu more tunda mutuwa zai yi a wurin aikinshi.
"Mutuwar Abdul Majid Mamman Ba'are baya hannuna, amma nasan dukiyarshi zata iya dawowa hannunmu idan har aka bi a sannu. Kana jiye mana abin da zai kai Sa'adatu lahira."
"Ba iya shi ba, akwai labarin da nake son nasani amma yaki gaya min. Ina son idan na samu labarin zan gaya miki."
"Wane labari ne haka?"
"Ya ce min a sanadin haka aka kai, Majid gidan kangararun Yara, domin fitar da Hajiya tayi. A wannan ranar shi ya saka Majid ya fara sace-sace har aka kai shi gidan horar. Idan ya tuna abin yana jin tsanar Hajiya."
"Kai haka ya ce? Lallai nayi babban kamu. Tow kada ka sake ya fahimci cewa kana son jin lallai ya baka labarin, zan cigaba da aikina anan da kanshi zai baka labarin."
"Shi kenan, amma ni gaskiya na gaji da wannan harkar." Shiru tayi ta ce mishi. "Na dan lokaci ne, ka saka idanu yadda zan tarwatsa Sa'adatu."
"Yawwa Hajajju sabuwar Chairwoman ba BA'ARE GOLDEN EMPIRES!"
Murmushi ta saki ya sauke wayar yana faɗin. "Hajiya Tani, kifi na ganinki mai jar koma. Ina harinki kina harin Hajiya Sa'adatu."

Hajiya Tani.
Jikinta ne ya bata ana tsaye a falonta, ta kashe wayar ta fito, ganin Hajiya Fauziya Mamman Ba'are yasa ta sha jinin jikinta kamar babu abinda ya faru ta kakaro murmushi ta ce mata. "Kina son wani abu ne?" Girgiza kai tayi ta ce mata. "Naji kin ambaci sunan Sa'adatu ne akwai abinda ya faru ne?" Wani sirrintaciyar murmushi tayi tana faɗin. "Hajiya Fauziya taya zan yarda na gaya miki gaskiya, bayan kema idan kin samu yakata zaki yi." "Haba wani yakarki? Kawai gaya min zan taimaka miki da yad'a shi." " Ba yad'awa ba ne, so nake ki saka ya Haladu yabawa Abdul Majid auren Afiyyah."
"Kina ganin haka mafita ne?" Girgza kai Tani tayi tana faɗin. "Haka shine zai bamu damar fitar da abinda kike son faɗa." "Akwai labari kenan!" Murmushi Tani tayi tana faɗin. "Mai girgixawa."
Daga haka suka fita, kamar yadda suke son sanin me ya janyowa Majid ya samu wannan matsalar duk yadda aka yi Hajiya tana da wani dark secret da take boyewa idan haka ne kuwa tow tabbas Hajiya ta kusan mutuwa.
---- Kure volume na radio Nana tayi tana niman gidan rediyon Faransa, tana ƙara ware idanun. Bubbuga radio tayi tana tsaki. "Mtsew, ƙarfen nasara babu tabbas yanzu wannan raidiyon wai batiri yake nima." "Assalamu alaikum!" "Waye nan?" Ta amsa cikin masifa tana mikewa. "Nana Fauziya ce!" "Kin kashe maganar bashin da Mulaika taci?" Wani shiru Hajiya Fauziya tayi kafin ta ce. "Ayya Nana daga zuwa gaishe ki sai ki gwale ni." "Ahtow ai gaskiya na faɗa, ko kunyar Harirah baki ji, tana tattalin dukiyar Yaranta babu ruwanta iya shi ne a gabanta, ke baki da aiki sai bin malamai da munafunci, wallahi ina rabaki da wutar jahannama." Ta fada mata tana wani zumburo baki. "Wai Hajiya na hango wani abu da ba kowa ya hango ba, shine nace duk da babu wanda yake kallona da idon rahama." Tayi shiru gashi Allah ya jarabci Nana da bala'in son jin gulma don haka tayi kwalkwal da idanunta. "Ina jinki bana son munafurci zaki fara magana kiyi shiru."
"Hmmmm Nana ai ban san yadda zaki ɗauki maganar ba, shi yasa na kasa faɗa miki." Inji Hajiya Fauziya..
Wani galla mata harara Nana tayi ta ce mata. "Kin san na tsani a zo bani labari a tsaya ana kame-kame uwar me idanunki ya hango wanda nawa idanun bai hango ba?"

"Hmmm Hajiya naga Maisarah tana wurin dangin Mamanta, kuma kin ga zata fi dacewa da Alhaji shine nace mai zai hana a hada Maisarah da shi." Ware manyan idanunta Nana tayi kafin ta ce mata. "Amma Fauziya Allah ya miki albarka, ina na tab'a tunanin hakan."
"Amma Hajiya wani hanzari ba gudu ba, ko za a hada shi da Afiyyah ne?" B'ata rai Nana tayi tana faɗin. "wannan yar banza da shegen kugu kamar an zargawa biri igiya babu abinda zai hadata da bawan Allah tunda ai shi mutumin kirki ne, yarinyar nan ranar wasu irin kaya ta saka tana tafiya ina ganin jikinta Allah na tuba ita da Sajjidu kullum suna makale da juna kamar kadangaru ita dai wancan ko zuwa tayi kowa yasan iyayen Uwarta mutanen kirki ne, Turai kuma babu wanda bai san shaidaniya ba ce."
Hadiye yawu Hajiya Fauziya tayi domin kawo bambancin Maisarah da Afiyyah a fili take. "Amma Nana don Allah kada kice nice na ce ya auri Maisarah, don kinsan Alhaji Karami zai kullace ni." Galla mata harara tayi tana faɗin. "Babu wanda ya isa Miki haka domin sai naci uwatai, ke da kika hada alkhairi sai na watsa miki kasa a idanun. Tashi ki je amma ki daina munafurci domin ba abun arziki ba ne "
"Shi kenan Hajiya naji sannan Hajiya kin ji labarin Aryan shine sabon shugaban Kamfani ba Abdul Majid ba!" Sake Radio din hannunta tayi ya fadi kasa ta ce. "Ke dai had'a husuma ya zame miki jini ko? Ina zaki aikata abin arziki amma munafurci ya saka ki sabule ladar ki. Taya Majid zai bawa wancan kodadden bawan shugabancin ai sai dai Sa'adatu ta cigaba da rikewa har ya gama yawon sojancinshi."
"Hmmmm! Wallahi kuwa Nana ki tambayi Sa'adatun idan karya na miki ranar Monday zasu tabbatar da shi, sannan ya rabawa yan dakinsu matsayi ko kara bai raba mana ba."
"Lallai wato shine suke niman kashe shi, idan bai basu shugabancin kamfanin ba, kuma babu babban munafukar kamar Sa'adatu domin ta munafurce ni. Da ta gaya min da na saka Haladu ko Kamilu dayansu ya rike kamfanin abin gado ne da ba za abawa wani ya rike ba. Yau idan ban ci mutuncin Sa'adatu ba, shegiya Uwata ta haifan." Ta tashi don masifa a juye ta saka hijab dinta, ta nufi hanyar waje, Hajiya Fauziya tana dariya a ranta. Har kofar Hajiya ta rakota, sannan tayi tafiyarta ita daya ta jefi tsuntsu biyu da dutse daya, ta juya lamarin maganar auren Afiyyah da Majid, an maida maganar kan Maisarah da Majid, yanzu zata sake hada wani rigimar tsakanin Nana da Afiyyah, sannan ta nuna babu ruwanta a zancen kamar bata sani ba.
A fusace Nana tana bala'i ta shiga falon Hajiya, suna falon har da Majid kuma fa tun farko an zo an gaya mata ta ce babu ruwan kowa kamfanin sune amma yanzu da jaraba take cinta tazo sauke jaraba. Kallo daya yayi mata, ta koma daya daga cikin sofar falon ta zauna. " Sai wiki-wiki take da idanuws. "Barka da yammaci Nana " " yawwa Sa'adatu!" Ta fada a dakile. "Nana ya kike?" Inji Aryan yana cika bakinshi da kankana. "Kundun Ubanka mara mutunci, Abdul Majid kaga yadda yake min gaisuwar yan tasha."
"Haushin kaza huce kan dami, Nana kowa yasan kin shigo da jaraba ne, don haka ba zaki fara a kaina ba."
"Alhaji kai kake daure mishi gindi yake min rashin kunya, don kawai na damu da ku? Fisabillahi Alhaji kaf gidan nan a rasa waye zaka bawa shugabancin kamfani sai wannan me kama da zabiya?" Sai kuma ta kama share hawaye tana faɗin. "Yanzu Sa'adatu da saninki Alhaji ya dauki jagorancin nan ya bawa Aryan wannan mara kunyar yaron ni dai ban amince ba."
Ta fada tana yatsina fuska. Mika mata bowl din fruit din da Hajiya da kanta ta haɗawa Majid yayi. "Sha." A hankali ta dauka tana sha, ta ce mishi. "Duk gidan nan babu wanda ya kaika mutuncin da Alkhairi."
"Sha kawai Hajiya!" Haka ta sha, bata gama sha ba Aryan ya tawo da gasashen namar kaza ya ajiye a gaban Majid. Kallonshi tayi tana son ta hango iyakar muguntarshi.

"Nana me kike son gani a fuskar." Hadiye yawu tayi tana faɗin. "Lamari na duniya akan abin duniya sai a iya kashe mutum, kai Alhaji ina fatan ba barazana yayi maka ba ko?" Ta fada tana kallon Majid din, "to naga ga Yan uwan Ubanka, ka tsallake su ka bawa mara kunya kamfani."
Ganin Majid yana cin namar shi babu abinda ya ce mata, yasa ta ci-gaba da cewa. "Shi namar ka tabbatar da cewa babu guba a cikinshi?" Cak ya tsaya da taunar namar, yana me kallon Aryan ɗin, "Kika ce me?"
"Hmm nace ka tabbatar babu guba."
"Ai tun a ya'yan itacen da kika sha nake tsammanin ya na zuba gubar yadda kike tunani." Hararshi tayi tana faɗin. "Gubar zaka zuba ka fada min? Sa'adatu ki gayawa wannan futsararen dan naki ya daina shiga harkata da Alhaji "
"Tunda tare kika ganmu haka zaki bar mu, sannan da kike cewa a hana ni babu abinda zaisa a hana ni sai kiyi kuma."
Ya fada a fusace zai bar falon, "dawo ka zauna." Inji Majid ita kan Hajiya babu ruwanta. "Tow fisabilillahi zata zo tana irin wannan maganar, idan wani bai yarda ba wani ai zai yarda." "Koma ka zauna "
Zama yayi yana huci kamar zai fashe da kuka,"Nana asalin abinda ya kawo ki, akan kamfanin da na bawa Aryan ne ko? Dama can Aryan shine Magajin Mamman Ba'are,, Ni aikina yana da muhimmanci, idan nace xan riƙe kamfanin ba za a samu abin da ake so ba, Nana ni soja ne kawai abinda na sani na koma bakin iyakar kasa ko ruwa na kare al'umma, domin wannan aka haife ni." "Tow me yasa ba zaka bawa yan uwan Babanka ba."
"Kowa ya nemo na shi dukiyar Mamman Ba'are na Yaran Mamman ba'are ne, don haka kada na kuma jin haka idan ba haka ba, sai na saka an bincika min ke da laifin yunkurin hada husuma." Ya ciro bindigarshi ya ajiye a gabanta..
#Dambujeeeeeee
[2/26, 7:37 PM] Cutie cutie pie: *BAƘIN HAURE....**

{Greed for Money is the roots of all evils}
Arewabooks:maidambu41
Wattpad:Mai_Dambu
Mallakar:Mai_Dambu
025
"Daga yau kada na kara jin kin ce wani abu akan Aryan, ko me kuwa idanunki ya gani ko kunnuwarki suka ji, babu ruwanki da Yan uwana. Ba zaki raba ni da shi ba ko ina raye ko bana raye Aryan shine Magajin Mamman Ba'are, kin fahimta bani da shakikin da ya kai shi. Sannan ni ba d'anki ba ne da zaki tsara ko ki saka mishi idanu akan abinda yake, Waccan da kika ce ba zaki amshe ta a surukarki ba ita ke da ikon saka ni ta hana ni. " Jikinta yayi matukar sanyi, tabbas a duk lokacin da zai yi magana yana gaya mata ba ita ta haife shi ba, Sa'adatu ce ta haife shi. Kafin ta gama tunanin abin da yake gaya mata, ya kara dukarta da wasu kalaman masu zafi da ciwo.
"Kamfani namu ne, kuma ni na saka Hajiya tayi murabus. Domin a cigaba daga inda ta tsaya Hajiya ni da kika ganni ina son mahaifiyata, kuma ina son ganin ta huta idan kina son mu zauna lafiya da ke, ki fita hanyarta idan ba haka ba duk abinda ya fito bakina sai na gaya miki. Ba iya ke ba duk wanda ya ƙara shiga harkarmu sai na kure mishi lissafinshi. And ki tattara kafarki, ki koma inda kike zaune bangaren Sa'adatu na Yaranta ne babu wanda ya isa kara zuwa ya shiga tsakanin Yaranta. Da kika ce tana ganin abin da nake aiakatawa tana gani, kema kina ganin lokacin da d'anki yake wulakantata kin iya dakatar da shi?"
"Majid!" Hajiya ta kira sunanshi, domin bata son abin da zai d'aga mishi ciwonshi, su shiga damuwa.
"Hajiya kada ki damu, ita ta manta lokacin da take fadar cewa a kuntata miki ko zan bi hanyar da suke so, bayan da saninta d'anta ya haramta min ganin Mahaifiyata, ta manta da saninta danta ya nisanta ni da kowa nawa, yanzu Nana don bakya tsoron

Allah kin zo zaki hada ni faɗa da dan uwana, ki tashi tun muna girmama juna ki fita kafin raina ya b'aci mu samu matsala."

Bai gama rufe baki ba,Nana ta mike a hankali zata fita Aryan ya ce mata. "ki gyara hijabinki." "Tow!" Ta fada tana gyara zaman hijab din, har zata fita ta juya tana kallon Abdul Majid da yake cin naman a nutse. "Ka yafe min abin da nayi maka, nasan na cutar daku amma don Allah a wurinku nake samun damar yin yadda naso don Allah ka yafe min."

Ta sharce hawayen da yake zubo mata, sannan ta fita tana kukan sarari da na zuci. "Baka kyauta ba, da baka gaya mata haka ba." Murmushi yayi ya cigaba da cin abincin shi, "Hajiya idan ba haka yayi mata ba, Nana bata da kirki haka kawai xata mai dani abin zargi." Inji Aryan yana cika bakinshi da namar gaban Abdul. Harara ya watsa mishi yana faɗin. "Kaje kaci naka mana." Da sauri ya wafci namar yana faɗin. "Ba zan iya cin nawa ba, naka zanci gaskiya wannan gashin yafi nawa dad'i."

Lokacin da Nana ta koma taci kuka har ta godewa Allah, tana me kara ganin laifinta ne duk kiyayyar da Yaran Hajiya suka nuna mata laifinta ne.

Kamata yayi ace su taso sama da sauran jikokinta tunda ba karamin dadi taji da aka haifi Abdul Majid ba, amma daga baya kawai ta tsane su idan ta tuna cewa a caca aka ciyo uwarsu sai ta ga kamar sun zo da wani irin gurbataccen jini mara kyau da amfani.

***

Zahrah.

Wata na guda ina nan bana kome sai aikin noma, idan na koma dakinmu kuwa idan na kwanta dakyar nake barci, abincin da nake ci baya isa ta

Sannan duk tsawon wannan lokacin, ana kawo min abin da Yallabai yake kawo min, Addah take amsa tana cinyewa ko Ummi bata sani ba, ranar da dubunta ya cika, ranar ya fara fita domin ya warke kamar bashi ba, da kanshi ya kawo min abincin sannan itama Reshmah bata san cewa zai futa har ya nimo ni ba, tunaninta ai abinda ya faru zai saka mishi shakkar nima ta ne, sai dai shi namiji ne da yake da ra'ayin kanshi, babu wanda ya isa ya sauya mishi. Lokacin da ya zo ya zauna yana jiran na dawo har dare yayi yana zaune a wurin karewa da wayar da suke amfani da shi a dan kauyen, ya kira Aseem ya kawo mishi abin sallah, a wurin suka yi sallah suna hira, tunda ya zo Addah ta leko ta ganshi tsoro ya kama ta, yana tsaye a wurin mamaki ne yake kara kama shi ya cewa Aseem ." Kuma kai ne kake kawo mata abincin?" "A'a Ghadafi ne!" Gyada kai yayi. Har aka yi sallah Isha ban dawo ba yasa aka tara kowa. "Ghadafi ita kake kawowa abincin?" "Eh Sultan" ya fada yana kallon Adda. Dafe kirji tayi tana kallon shi. Zuba mata idanu yayi, ya cewa Aseem. "Ita wannan ita ce ta je ta gayawa Reshmah ina fita da Zeehrah!" A fusace Aseem ya mike, "kyale ta ku tambayeta."

Fito da Addah aka yi ta zube akan gwiwarta. "Ina kike kai abincin da ake kawo miki " "ina bata ne!" Ta fada bakinta yana rawa. "Karya take Sultan, cinyewa take kullum aka kawo, sannan Zahrah yau ce bata dawo da wuri ba, tana can lambun wiwi tana noma a wurin.." Sakin baki yayi yana jin kamar a mafarki yake jin labarin inda Zahrah take. Bai ce uffan ba ya mike tare da barin wurin. Aseem yana take mishi baya, ita kuma Addah tana zaune a wurin da wasu masu gadinsu.

"Ummi Allah ya tsine miki albarka."

"Ash, Addah babu abinda zai same ni domin kuwa tsinuwar da Zuzu take miki a duk lokacin da wani ya kwanta da ita ya ishe ki zuwa lahira lokacinki bai yi ba, Addah da na haifi ɗan da xan tura shi karuwanci gara na kare rayuwata babu d'a babu jika in gaya miki, Munaisah ma da muka yi raba dai-dai akanta. Hakkin Uwarta da ta bari kika kashe mata ne. Bari na gaya miki wallahi ba zan barki ki karasa cutar da Zahra ba, muna nan sai na saka an illataki kafin mu bar nan wallahi."

Shiru Addah tayi tana tsoron abin da zai kuma faruwa.

---- Yau kan babu abincin da aka kawo min, nayi noman har na kasa domin idan na sunkuya sai na fara jin amai, yunkurin aman yasa karfina ya ƙare, har rana ta fadi ina kwance a wurin, ita kanta Baby kamar bata da lafiya, jikinta yayi zafi rau. Haka

yasa na kwanta a wurin daga nan ban kuma sanin kome ba, domin duhu ya lullube gani na.

Kamar daga can nesa nake jin ana kiran sunana, dakyar na bude idanu kamar shi na gani, na saba yin mafarkin yana zuwa ya ce gashi ya samu lafiya ya dawo kenan, sai na kara lumshe idanuna. Har tsawon kwanaki biyu, ban san waye a kaina ba, a wannan kwananki biyu Baby ta murmure kamar ba ita ba, nice ulcer ta min mugun kamu, saboda babu abinci me kyau. Sannan jinin jikina yayi kasa bani da wadataccen jini. Don haka ya bada na shi aka saka min, na cigaba da samun kulawa har rana ta uku sannan na farka. Ina ganinshi na zuba mishi ido. "Zeehrah ya jikin?"
" Da sauki"
"Allah ya baƙi lafiya!" Daga haka na lumshe idanuwa na, haka ya gama zama har ya gaji ban ce mishi cikanka ba. Asalima koyawa kaina fita harkar shi nake son nayi kamar yadda suke bukata, don haka na fita hanyar shi ban kuma shiga rayuwarshi, washe gari da aka kawo min Baby tayi bul-bul da ita gwanin ban sha'awa. "Maa Yallabai ya ce kada ki kara bata nono tana shan madara." Yarinyar da bata wuce wata uku ba. Kamar tasan abin da nake tunani a raina, sai gashi ta ce min."Eh akwai madarar da zai mata,kema Dr ya ce zai bada magani a baki."
Ban ji dadi ba, amma kuma zaman mu a asibitin ya sani murmurewa nima. Sai dai idan yazo bana mishi magna, haka idan yazo yayi ta magana juya mishi baya nake, haka nurse ta kawo min maganin da zan fara sha, rabin maganin na gyaran jiki ne da SUPPLEMENT na islamic. Ban taɓa zatan akwaisu ba, haka nayi ta sha har aka sallame ni, da na koma dakinmu a lokacin ne na fahimci Addah har lokacin bata dawo ba, sannan an sauke min aikin da nake yi, bana aikin fari balle baki, ina nan daga na tsoma biyar sai na wanke goma. Kwanana biyu ina barci na dora Baby a cikina ya shigo ya d'aga ta. Bude idanu nayi ina kallonshi, kafin na juyar da kaina.
"Zeehrah wai me na miki ne?"
"Baka min kome ba, kai ne dai nayi maka laifi"
"Ban gane ba?"
"Ok zaka gane!" Na fada ina kokarin sauka daga gadon, rike hannu yayi yana faɗin."kiyi hakuri ki gaya min laifina." Girgiza kai nayi nace mishi. "Wallahi baka min laifin kome ba, kawai bana son kana zuwa inda nake ne don Allah." Yadda nayi maganar yasa shi kallona. "Meye ya faru?" " A hankali na zare hannuna cikin na shi, a kundin ƙaddarata ba zan tab'a cike shi ba tare da na ambaci Yazid ba, domin shine mutum na farko da ya tare min masifar matarshi. Hakazalika ba zan tab'a rufe labarina ba tare da gayawa duniya waye shiga gare ni ba, ya min alkhairin da babu wanda yayi min, ƙaddarata rubutacciyar al'amari ce da ba zata tab'a shallake ni ba tare da na bayyanawa duniya girmansa da darajarshi ba."

"Ki gaya min meye nayi miki da baki son na tsaya a hanyarki." Yadda yayi maganar cikin Rarrashi yasani fashewa da kuka idan na tuna abinda mutanen nan suka min sai naji kamar zan mutu, da b'acin rai. Rufe idanuna nayi gam naki kallonshi, a hankali na had'a kaina da gwiwa ina wani irin kuka na takaici da bakinciki. Cizon bakinshi yayi ya ce min "me kike so?" D'ago jajjayen idanuna nayi ina kallonshi kafin na ce mishi. "Kawai ka rabu da ni." "Ba zan iya ba. domin lokacin da zuciyata ta had'e dake bata yi shawara da ni ba, ni kuma bana jin a raina zan iya rabuwa dake don kawai kin ce na rabu dake, kiyi tunani da kyau."

"Babu inda zan yi tunanin kawai ka rabu da ni!" Na faɗa cikin kuka. "Fadimatul Zahra'u, ni fa akan abinda nake so babu abin da ba zan aikata ba. Gaya min me aka miki kike kuka haka.". "ni yaushe nace maka anyi min wani abu, don Allah ka rufa asiri kada ka ja min sabon masifa, kawai ka tafi ka bar ni, idan da hali ka kore ni daga rayuwarka."

Rike hannuna yayi yana kallon kantar hannuna, kafin ya ce min."su waɗanda suka miki barazana zasu miki wani abu har suke bautar dake baki gaya musu kina da Sultan Yazid Hamir ba ne?"
"Kai ba iyakata ba ne, su kuma kai ne iyakarsu, ina da tawa rayuwar a wani wurin don Allah ka yi hakuri ka barni." Na fada da ƙarfi. Shigowa Aseem yayi d'aga mishi hannu

yayi alamar ya tafi ya ce min. "Sun miki barazanar zasu kashe ki ko? Ko sun miki barazanar zasu maki fyade ne? Kai ko sun Miki..." Wani irin zabura nayi tare da kame jikina, da yake rawa sakamakon hada'a idanu da nayi da mutimin da kullum sai ya min kashedi akan Yallabai. Bin inda nake kallo yayi da idanu yaga na sunkuyar da kaina ina kara tattare rigar jikina ina faɗin."don Allah ka tafi kaji ka rabu dani." Kusan ban san fuskar shi ba, amma da safe idan na fita ina yawan had'a idanu da shi, haka yasa na karanci kwayar idanuwanshi, ko bai magana ba, nasan shine
.
"Darda!" Ya kira sunanshi, "Na'am Sultan!". Wani irin tsalle nayi na koma ƙasar gadon, domin shi din ne fuskarshi da Muryar shi ya tabbatar min da shine, na kame jikina da yake rawa na ce. "Don Allah ka tafi, ka tafi bana son ganinka wallahi bana kaunar ganinka ka rufa min asiri da halin da na shiga." Na fada cikin matsanancin kuka da ihu. Ganin haka ya sashi barin dakin asibitin. Darda ya bi bayanshi. "Aseem ka saka Darda ya gaya maka me suka yiwa Zeehrah!"

"Wallahi Sultan Amiratul ta saka mu, mu mata barazana." Shiru yayi yana zare Idanu, ai yasan matuƙar bai magana ba shine a ruwa. Don haka yayi magana da wuri, koda suka isa gidan yarin. Zubewa Darda yayi ya lissafo mishi wadanda suke da hannu a cikin abin da suka mata. Duk a ka tawo dasu. "Me kuka mata?" Da kanshi yayi tambayar. Jikinsu na rawa suka nuna Darda. "Shi yace zai mata fyade bayan ya mata fitsari kai." Ware manyan idanunshi yayi yana tuno yadda tayi ta kame jikinta. "Abin da ka aikata kenan?" Inji Aseem.

"Tuba nake a yafe min ba zan kuma ba. Wallahi saka ni aka yi, ba zan kara ba " murmushi yayi sannan ya ce mishi. "ka yanke mishi hukunci daidai da laifinshi. "Sultan ka yafe masa, ba zai kuma ba." "Ita yarinyar bata da gata ko? Babu wanda ya damu da ita tunda uwarta da Ubanta sun watsota duniya basu san dajararta ba ko? Gaya min abin da yayi mata akwai adalci a cikin shi, itama mutum ce fa. "
"Bai kyauta ba "
"Aseem ina son Yarinyar shi yasa bana kaunar kukanta, idan har ban bata tsaro da kulawa ba, taya zan ji da abinda yake raina "

Haka ya mike yana faɗin. "Ka hukunta shi nace." Ya fita, gidansa ya wuce yabar shi ya samu Reshmah. Share ta yayi bai kuma kulata ba, domin idan yayi magana zata kuma fitar da hanyar da zata kuntattawa Zeehrah. Lokaci yayi da zai koma aljeria. Dama rabon ya hadu da ita yasa ya kasa komawa, a yanzu kuwa babu wanda ya isa ya shiga tsakaninsu koda kuwa mutuwa ce sai dai ta dauke su tare. Haka ya gama tsara yadda zai tafi da komin shi Addah kuwa, sakawa yayi aka mata duka, har sai da suka tab'a mata lafiyar idanunta ɗaya.

Koda aka dawo da ita kallo ɗaya Ummi ta mata ta ce mata, "Kina tsammanin daga nan zaki kara samun sukuni ne? Kamar yadda kika saka rayuwar wacce bata ji ba bata gani ba a gaba haka zaki rasa kome naki."

Addah bata yi Magana ba, sai dai dukarta da tab'a mata idanu ya kara haifar mata da bala'in tsanar Zahrah. Sai ta ga bayan Zahrah, sannan abinda ta fahimta Yazid niman kuɗinshi ba don ya cutar da kowa ba ne, niman kuɗinshi akan kanshi yake daukar kasada, ba kamar wancan mutumin da yake sayan Sassan dan Adam tare da sayan yan mata domin karuwanci ba.

*** Sati biyu nayi sannan na dawo, a lokacin naga idanun Addah yayi wani bala'in girma gashi jini ya kwanta a cikinshi. "Addah baki je asibiti ba?" "Na je asibiti kika tambaye ni? Nace na je asibiti fa? Sai na illata rayuwarki Zahra matukar ina numfashi."
"Baki illatata ba ma an kashe miki idanu, idan kika lakace ta sai dai lahira tayi bako."
"Ban yi dake ba!"
"Dama baki isa kiyi dani ba Addah."
"Mara kunya kawai "
"Marasa kunyar suna dayawa!"
"Addah ki kyaleta muyi maganar idanunki."
"Kinci Ubanki shegiya munafika."

"Kayya da ina nufinki da sharri da kullum kaina zai tsaya, amma dake zuciyata daya ba zan iya nufarki da sharri ba." Na gaya mata, domin zuwa yanzu addah ta fara isata, ban san yadda zan yi da itaba amma na gaji da halin ta, "idan kina son idanunki,ki shirya gobe ki ga likita."

D'ago kai tayi tana kallona, "Annamimiya kina min haka ne don na yafe miki!" Inji ta.

"Idan kin so kada ki yafe min Addah wallahi babu abinda zai tsaya, bakya gabana asalima tausayi kike bani, daga lokacin da ƙaddarar Allah ta rabamu wallahi billahi azim sai kin yi fatar da ina tare da ke. Ba zan ce Hakkina yayi ta bibiyarki ba, amma nasan zaki so ina tare dake domin ni daya ce kawai. Zan tsaya a gefenki ki tuna da kin haifi Zuzuna, sannan ba zance nayafe muku ba daga ke har ita sai ranar da muka hadu ta gaya min dalilinta na cutar dani babu hujja. Idan yayi miki muje a duba idanun idan bai miki ba, ki zauna da shi Allah ya baƙi lafiya." Daga haka na kyaleta ina zan iya da bakin hali, bakiɗaya bata kanta take ba, hanyar da zata cutar dani kawai take nima sai kace na tare mata wani abu.

***

Niamey.

"Alhaji gaya min ina ke maka ciwon?" Kasa d'ago kai yayi ya kalleta. Kuma yayi shiru kamar baya wurin.

"Kace jibi zaka tafi ko? Idan ka tafi zaka ga likita a can ko?" Duk ta uzirawa kanta, gani take kamar laifinta ne da sakacinta. "Alhaji" can kasan makoshinsa ya ce . "Hajiya lafiyata lau."

"Ina lafiya mm, zan zo na ganka."

"Assalamu alaikum!" Afiyyah ta shigo cikin nutsuwa domin duk rawar kanta da iyayinta, tana shakkar Majid da Aryan. "Wa'alaikimus Salam!" Hajiya ta amsa tana kallonta cikin kulawa. "Hajiya wai kizo keda Hammayo inji Nana!"

"Tow shikenan ki ce mata gamu nan!"

A hankali ta fita cikin wani irin taku me tab'a zuciyar yan maza, tunda ta shigo kallo daya yayi mata bai kuma kallon ko inuwarta ba, harkar gabanshi ya ishe shi. "Muje Alhaji."

Me yasa Nana ta kira su bayan abinda ya faru kwanakin baya bata kuma shiga harkar su ba. Tashi yayi ya haura sama ya sako wasu kayan shadda ce skyblue, anyi mata ɗinki yar shara. Ta cikin rigar wata farar riga ya saka me dogon hannu, sai hular da ya saka ta amshi fatarshi sosai. Turaren pure oud ya fesa, bakiɗaya dakin ya hargitse da kamshinsa me dad'i.....

#Mai_Dambu

[2/27, 10:56 AM] Cutie cutie pie: *BAƘIN HAURE....□□*

{Greed for Money is the roots of all evils□}

Arewabooks:maidambu41

Wattpad:Mai_Dambu

Mallakar:Mai_Dambu

```Hajiya ga kaya nan Masha Allah, Available price

Huluna da Mayafai, da na yara sai Wanda ranko yakeso gasunan kala kala, Hajiya muna dasu ba iya hulana da Mayafai ba, har da shadodin na fitar sallah, Hajiya domin hutar dake da fitar dake kunya na tanadi yadda ba zaku sha wahalar yawo kasuwa a cikin azumi ba, don haka kafin kishiyarki tazo ta sata au □😹😂 kafin kishiyarki tazo ta saya na tayiwa mijinku shakara gara kizo ki sata au 😁□😹 baki ya saba gara kizo ki saya, barauniyar gida, kai Sarauniyar gida 😂😹 atow kayana na Uwaren gida da na Amare ne```

*TUNTUBE WANNAN NUMBER 08130269641*
```

Yadda ya karya hula zaka rantse cikakken bahaushe ne, amma yanayin fatarshi zai nuna maka cewa bai da alaka da hausawa. Lokacin da ya fito daga dakin shi, Hajiya tana kallonshi daga kasa, kamilalliyar fuskar shi, me cike da kamewa ta kalla sannan ta shiga tasbihi ga Allah madaukakin sarki. "Ya Allah ka tsare min bawan nan naka." Ta fada tana cigaba da tasbihi har ya iso inda take, takalmin kafarshi kawai abin dubawa ne. Haka ya wuce ta suka fita tana bayan shi yana gabanta, sai da suka isa wurin kofar ya bude mata, sannan suka shiga bangaren Nana, haka suka iske falon a cike, gaban Hajiya ne ya fadi, tunda ta gan su tasan Babu alkhairi a wannan zaman nasu, don haka ta shiga da addu'a a bakinta.

"Assalamu alaikum jama'a, Barkanku dai."
"Wa'alaikimun Salam, barkanki Sa'adatu." Yadda suka amsa mata, yasa jikinta ya kara bata akwai wani abu. Zama tayi a daya daga cikin kujerar falon, Shi kuma ya zauna a kasar kafarta. Sai da aka yi gaishe gaishe hankalinshi yana kan wayarshi. Kafin aka bude taron da addu'a. Shiru falon ya ɗauka aka rasa wanda zai fara magana, Hajiya Fauziya ta ce. "Nana kinyi shiru abin arziki ya tara mu ba na tsiya ba"
"Eh wallahi fa, dama Sa'adatu." D'ago kai Hajiya tayi tana kallon Nana, baki daya sai ta cika mata idanu. "Na'am Nana!" "Hmmm dama dama!" "Dama me Nana?" "Wai cewa nayi a cikin yan matan gidan nan ya duba daya ya zab'a."
"Ai shine maganar? Tow ai Nana na gaya miki tsakaninku ne na Familyn Ba'are, ni a caca aka ciyo ni gaki ga Majid din Allah ya baku sa'a."
"Ashe akwai babban Al'amari Hajiya shine baku gayyace ni ba?" Inji Aryan yana shigowa falon, yadda yake tafiya zaka tabbatar da iskanci yake ji A ranshi. Domin kuwa bai kawo haka ba, shi dai yana shiga gidan ya ga basu nan, har zai fita yake tambayar Lawe yake gaya mashi ya fito ban daki ya ga fitarsu ta kofar Nana. Zama yayi a stool bakinciki ne ya kama Nana, tasan da babu Aryan zata iya rarrashin Majid,. Amma da Aryan yazo ko ta kulla sai ya kunce mata.
"Alhajina Maisarah ko Afiyyah." Ajiye wayar shi yayi yana kallon yadda ta ririta fuska. Alamar tana son kada ya bata kunya. "Ni ba zan aure su ba, matar da zan aura Hajiyata ce zata nima min, sannan Nana na gaya miki ki daina shiga harkana baki ji ko."
"A'a Alhaji!" Ta faɗa tana ware idanun tana kallon yadda ya saka hannu a cikin aljuhun rigar shi. Tasan bindigarshi zai ciro "Alhaji Fauziya uwar munafukai ce ta ce na had'aka aure da Maisarah da Afiyyah, wallahi ba tunanina ba ne, tunaninta ne."
"Hajiya tashi muje!" Ya fada yana mikewa, "Kenan idan baka amshi auren nan ba yana nufin kai ba cikakken namiji ba ne? Ko dai baka da lafiya ana boye mana ne, aeeeeh da alamu mutumin hotiho ne, babu karfin da zai raxana mace, koda yake kai idan aka baka mace karshe a shiga hakkinta aikin sojan shi ya kamace ka."

Inji Sajjid da ya fito tare da Amaan.
"Idan hakan ce zata saka ya zama cikakken namiji, tow ba zai amshi auren ba. " Inji Hajiya ta juya tana kallon Tani. "Da alamu bata gaya maka cewa shi aure da Yaron ciki aure darajarsu ba daya ba ne, shi dan aure yana da wata isa da kamala da duk inda ya shiga sai an girmama shi domin iyayenshi sun san cewa ba zasu b'ata mishi gobenshi ba, duk da a caca aka ciyo ni, ban yi zaman dandi ba, zaman aure nayi na haifi kyawawan irin da babu irinsu." Sannan ta juya ga Amaan da yake zare idanu. Takawa tayi har inda yake ta ce mishi. "Kayi kokari muje!" Ta fada tana jin kamar ta fashe da kuka, ita kuma shi ne jarabawar ta, ace yaro baka isa kayi kome ba sai ya gayawa kowa. Kowa ma abokan gabanka waɗanda basu da buri sai ganin bayanka.

"Hajiya ni fa ban gaya musu kome ba." Bata ce mishi cikanka ba, har suka isa falonta. Sakin hannunshi tayi ta zube a kujerar , tana kallonshi ranta a b'ace yake kuma abinda zuciyarta ke son faɗa zai iya saka ya kara lalacewa sama da yanzu, "Hajiya na rantse da Allah, ban fadi kome ba." "Gaskiya baka fadi kome ba, sharri aka

maka ko? Taya wancan tsinannen ya san matsalarshi? Wato kai dai ina ga baka da banbanci da jaki, domin kwanyarka bata daukar lissafi."
"Meeting din da za ayi gobe ka soke sunanshi a cikin board director." Inji hajiya ta kara kallon Aryan, "akai shi matsayin karamin ma'aikaci kamar kowa jahilcinshi ba zai bashi damar aiki ba."
"A'a Hajiya, tsanar da Amaan yayi min ni ba zan tab'a mishi ba, tayiyu shi yana da dalilinsa, amma ni bani da hujjar tsanarshi. Don haka ki kyale shi a matsayinsa, haka da yayi min yana kara min son shine, domin akwai wani abu da yake boyewa sama da tsanar da yayi min ba iya tsana ce take fitowa daga kalamanshi ba, har da kauna da bai san yana min ba. Shi yasa nake mishi uziri.". Ya faɗa, kafin ya wuce dakinshi, rufe kofar dakin yayi ya jingina a jikin kofar. Yana jin kamar ya fashe da kuka, me yasa shi yake jin ciwo sama da kowa? Me yasa yake jin zafin haka? Da yana da wata hanya da ya nisanta kanshi da kasar nan bakiɗaya.
Bayan barin Majid falon, Hajiya ta kalle shi, "ka ji dadinka wallahi, Allah ya shirye ka" tsaki Aryan yayi ya bar falon, hatta Matarshi sai da ta fahimci ranshi ya b'aci, don har dare bai da walwala.
Sai lokutan sallah yake fito da shi, bakiɗaya sai ya tsangwame kanshi. Da dare Hajiya da kanta ta kai mishi ruwan tea, yana cikin duhun shi na fama dama tasan za ayi haka, "tashi ka sha ruwan zafi!" Tashi yayi zaune, ya amshi kofin tana tsaye akanshi ya sha ya ajiye kofin a gefen gadonshi, "Zaka yi aure!" Da sauri ya d'ago kai. "Eh zaka yi aure koda kuwa babu wani tarayya, idan kayi auren ka tafi da matarka."
"Hajiya!"
"Maisarah ta bar gidan nan tun kafin rasuwar Babanku, Sannan mahaifiyarta kawai take mu'amala da ita, sau biyu muna haduwa a Saudiya, tana son yin magana amma tana ganin Mahaifiyarta zata yi shiru mu gaisa."
"Hajiya idan ta san ba zan mata..."
"Kada ka damu, dazun na kira Hajiya Sanah na tambaye ta, ko tana da saurayi ne? Ta ce babu hankalina ya fi kwanciya da Maisarah domin Afiyyah suna tare da Sajjid, duk abinda zai haɗaka da Tani ina avoiding ɗinshi."
"Hajiya!"
"Kada ka ce min kome!"ta faɗa tana barin dakin, zuwa yanzu Hajiya tana son fitar da wani abin da ba kowa ya sani ba, daga ita sai Majid dangane da Mutuwar Mamman Ba'are, idan har tayi hi jack points, tow ba makawa zata iya saka wanda yayi kisan motsi. Duk da bata san meye ake shiryawa ba, sai dai tafi tunanin ana shirin da bata san ta inda xa a fito mata ba.
***
Monday.
A yau monday akwai batutuwa da yawa da ake son aiwatarwa a kamfanonin BA'ARE GOLDEN EMPIRES, sai dai wani abin da ya tab'a zuciyar al'umma shine tashi da samun labarin mutuwar babban manajan kamfanin.
Daga Hajiya har yaranta hankalinsu a tashe yake, kuma abin tambayar anan shi ne, waye ya kashe shi? Shin kashe kansa yayi ne? Tow akan me?
Majid kan kin saka kanshi yayi cikin maganar, kuma bai da niyyar haka kuma har Hajiya ta fahimci haka, shi yasa ta tsaya ita da Aryan suka yi ta shige da fice. A cikin kwanaki uku sun jigata, jinin Hajiya hawa yake yana sauka, dole Aneesah ta tsaya a gefen Aryan, ga sintirin yan sanda a kwanakin.
Sai da aka kwashi sati daya ana abu ɗaya, karshe tafiyar Majid da bai samu yayi ba kenan, ya kara niman excuse.
A cikin sati biyu da yin abin, aka ga wasu mutane haka kawai suka rufe Kamfanin. Tsawon awa takwas aka dauka, kafin aka bude kamfanin kamar babu abinda ya faru.

Washi gari.
Aka kai sakamakon office din Aryan suna tattaunawa da Majid da ya kawo mishi, "Yallabai gashi nan, sakamakon binciken da muka yi." Ya mikawa Aryan kallon Majid yayi kafin ya dauke kai, yana amsar takardan. Mikawa Majid yayi ya ajiye, yana

kurbar coffee. "Mun gode!" Sannan mutumin ya fita, zama Aryan yayi ya fara bude takardar, mikawa Majid yayi, "ban fahimci abinda suke nufi ba."
A hankali ya amsa yana faɗin. "Kiran da yayi kafin faruwar lamarin, sai sakon da aka turo mishi aka goge na barazana, sannan a daren da abin zai faru kamar bibiyar shi aka yi. Ka duba ka gani"
"Wannan number kamar na san ta." "Amaan Mamman Ba'are!" Majid ya faɗa, tare da ajiye kofin. "Kada ka ce min!" Aryan ya faɗa yana zare idanu waje, "Tow yanzu ni da kai muna nan taya zan sani bayan an bar masu bincike sun yi aikinsu, ace abu sati daya a matsayinka na Chairman ka gaza yi, ok zan tafi tunda kome ya fito zan bar kasar nan yau. Amma kafin nan ka fara duba number na farko kafin na Amaan Mamman Ba'are."
Saka number yayi a wayarshi, "Haladu Abdul Majid ba'are." Ya furta. Sai daya number kan babu baya ma amfani alamar an daina amfani da shi.
"Don Allah ka tsaya a kammala binciken!" Aryan ya faɗa, shiru yayi bai ce mishi kome ba, har suka fita daga Office din. "Office dinka ko!" Sai kuma yayi shiru bai kara magana ba, har suka isa gida kafin su kara mika sakamakon ga yan sanda sai da suka ritsa Amaan. "Me Manaja yayi ka kashe shi?" "Ni kuma?" Ya fada a razane, "a ranar da zai mutu ka kira shi!" Majid ya faɗa yana kallon Aryan. Kamar ba da Amaan yake magana ba sannan ya cigaba da cewa. "Kunyi waya da shi na tsawon minti ashirin, wanda har Muryar ka ta fito."
"Idan ka tsane ni, sai ka min sharri." Aryan zai magana ya dakatar da shi. "Kyale shi, ina daidai da shi."
Ciro wayarshi yayi a cikin aljuhun riganshi, ya kunna.
Kada ka sake ka bawa Aryan wannan files din Sajjid idan ka sake ka bashi sai na kashe ka na gaya maka
"Ina fatan ka fahimci wannan Muryar?" Shiru yayi yana kallonsu. "Bani na kashe shi ba wallahi." "Eh kowa ya sani ba kai ne ka kashe shi ba, amma me yasa ka faɗa zaka kashe shi?"
"Tow ai barazana nayi mishi!"
"Barazana da mutuwa?"
Yallabai Amaan nasan meke faruwa tsakaninka da Sajjid ni dai ba zan baka ba, amma ina maka fatan shirya idan kai me shiryuwa ne, idan ba zaka shiryu ba Ubangiji ya gaggauta kashe ka, amma ba zan bada Files din nan ba

"Hammayo akwai wani abu da Amaan yake aikatawa tunda har irin wannan addu'ar ya fito bakin Manaja, mutumin kirki ne, ya kai sama da shekaru ashirin da biyar yana aiki a kamfanin mu." Inji Aryan, shiru Majid yayi yana nazarin yadda zai shawo matsalar, kafin ya tafi amma tabbas akwai gaggarumar matsala. "Kai da Sajjid kun kashe bawan Allah kenan? Domin da alamu ya ga kuna aikata wani abu ya dauke files din."
"Wallahi a ranar ban shiga kamfani ba, asalima ban san yadda aka yi ya mutu ba."
"Shi kenan! Aryan riko shi muje da shi, zan tabbatar da yayi magana in sha Allah." Inji Majid. Riko Amaan Aryan yayi suka fita daga gidan suka nufi inda motarsu take, Turus suka yi..
***
Zahrah
Raba ni dasu Addah da Yallabai Yazid yayi ya fi kome, saka min nutsuwa sannan an bani mai taya ni reno, bani da aiki sai karatu, domin a yanayin yadda muke yau da gobe har ya san na fara karatu na bari. Don haka da kanshi yake gaya min.
"Zaki koma makaranta."
Murmushi nayi na ce mishi. "Yaushe? A wata duniyar? Wannan duk mafarki ne." Na fada ina kokarin mikewa. "Da gaske zaki koma makaranta domin ki karanci tattalin arzikin kasa, ta haka zaki samu aiki me kyau ki gina kanki ba tare da wani ya sayi abu me daraja a tare dake ba, naso da ina da hali ba zaki kara zama a kasan wani ba. Sannan ba zaki kara yadda ki mu'amalanci waccan kanwar Baban taki ba. Akwai wani

abu da kike dashi kin kasa fahimtar haka, sai dai nan gaba zaki gane haka. Amma kiyi karatu sosai domin ta haka zaki zama Madam Zahra babban akawun kamfani."
Don haka na kara maida hankalina sosai, sannan da kanshi ya nima min wani cikin mutanen shi,yana koya min yadda ake amfani da laptop, rayuwata da ta baby tana cikin kwanciyar hankali, sannan bani da Matsalar kome, sai ta cigaba da kula da Baby da karatu na. itama Baby tayi katuwa bul bul da ita tayi kyau.

---- Wata na biyu ban saka Addah a idona ba, yau da ya shigo da yake sai ya jima bai shigo ba, "ina son zuwa ganin Addah." "Hmmm! Tow." Ya fada yana kallon yadda nake shiri, yan uwanka yan uwanka ne komai muninsu, haka ya raka ni yana rike da Baby da take niman wata biyar, yadda na gansu babu wahala a tare da su, sannan suna cikin nutsuwa. Kamar na fashe da kuka haka na isa gare su, na mikawa kowacce jakarta da na kawo musu. Ganin yana tsaye yasa Addah kame bakinta. "Naji daɗin ganinku, Addah ya idanunki?"
"Kina farinciki ne don ba zan kara gani da shi ba ko?"
"Ko daya Addah, ya kamata ki daina tsanata."
"Saboda ke na rasa Y'ata."
"Addah don Allah ki daina faɗar haka, idan don nice ya kamata ki gane na amshi hukuncina da rikon Yarta."
"Idan ina raye sai na saka yar ta kashe ki, wallahi sai na saka ta wulakanta ki." Murmushi nayi ina wasa da hannuna, "zan yi fatan ki kai wannan lokacin sannan ni kuma zan yi ƙoƙarin naga na daurata a kan layina, in sha Allah, sai kin sha mamaki ba zan hana ki ita ba, amma kuma sai kin yi tunanin anya jininki ce." Hmm Addah kenan, bari mugani Ni da ita waye zai yi sa'ar cika burinshi ni zan nemi taimakon Allah ya taya ni, rikon Allah ya kare min ita da zuciyarta. Cikin fushin da ban san ina da ita ba, na kalli Ummi na ce mata. "Ummi zan tafi." Na kalli Addah, na ce mata. "Ki ajiye hakan ni dake Allah ya bawa mai rabo sa'a!"
Na fita yana kallon yadda muke magana da fulatanci ya fahimci faɗa muke da harshen mu, don haka yayi ta kallon yadda nake magana, ina fitowa na share kwallar da zai zubo min, na amshi yarinyar ina jin wani irin kuka ya kwace min, domin kuwa ina jin tsoron kada Addah ta sake raba ni da wani abu mai daraja.....

```Shahararrun goma aduniyan kayan mata wato m zee kamshi kayan mata kenan inakuke matan kwairai manyan Mata fah bamuna mataba Mata masu aji Wanda tasan kanta agidan mijinta kozokuyi gyara masu kyau da inganci Wanda zaisa oga nishadi yasashi farinciki atare dake kayanmu wane yaro sai uban yaro kinsha zumar makalemata dare daya wanka goma wanan set ne na kayan kwairai akwai fati budurwa mumuna da aeki Dan miyau malaka to shu,Umar Zuma zumar kiba gari kiba Zuma me lakani ningi tsumin lahaula hadin miski ba ahira dawando garin me kabara kasa ruwa sama ruwa wanan magani ba ,a magana magani sanyi mekyu maza da Mata ci da kaza ci da cicibin vlp yan shila ci da kifi nama kayan sakiba na gida danawaje munadakaya kala kala fani kamshi munada shu uwar humra namu ba irin nasubane akwai turare 24 hr turare kabasa Dana gida masu Dadi gakyau ga kamshi 08063845136 KADA KU MANTA KAMAR KOWACCE WATA Wannan akwai Promon Azumi me kike jira ne*
#Mai_Dambu
[2/29, 7:47 PM] Cutie cutie pie: *BAƘIN HAURE....□□*

{Greed for Money is the roots of all evils□}
Arewabooks:maidambu41
Wattpad:Mai_Dambu
Mallakar:Mai_Dambu
```Hajiya ga kaya nan Masha Allah, Available price
Huluna da Mayafai, da na yara sai Wanda ranko yakeso gasunan kala kala, Hajiya muna dasu ba iya hulana da Mayafai ba, har da shadodin na fitar sallah, Hajiya domin

hutar dake da fitar dake kunya na tanadi yadda ba zaku sha wahalar yawo kasuwa a cikin azumi ba, don haka kafin kishiyarki tazo ta sata au 😈😂 kafin kishiyarki tazo ta saya na tayiwa mijinku shakara gara kizo ki sata au 😁😈 baki ya saba gara kizo ki saya, barauniyar gida, kai Sarauniyar gida 😂😸 atow kayana na Uwaren gida da na Amare ne```

*TUNTUBE WANNAN NUMBER 08130269641*
Hular Yara
Mayafai
Dogayen riguna
Hijabai
Takalma
Kayan Yara
ATAMFOFI
Laces
SHADODDI
Materials
Sayan na gari mai da kudi gida.....

Wannan page din na kune.
Hajiya Sa'adatu wato Ambassador
Auntyna Addah gashi nan kun zungud'o ni nayi muku posting....😍 Nagode sosai da kulawarku... In sha Allah sai Talata ina da uzuri me girma 😍

*027*
Duk wanda Allah ya jarrabe shi da fitinar Addah, tabbas ya gamu da jarabawa, kamar dai ni da ta addabi rayuwata, amma ban iya daukar mataki ko na mata wani abu ba, na barta da Allah da kuma halinta, in sha Allah Ubangiji shi yasan yadda zai yi da ita.

Bayan fita ta, Ummi ta fisge kayan da na kawo musu, "bani nan, ke da bakya kaunarta, taya zaki ci abin hannunta bani ko babu komai Na ci tudu biyu." Ta fada tana buɗe ledar. "Ki bani kayana tunda kema ta baki naki." Inji Addah kamar zata yi kuka. "Wallahi ba zan baki ba." Inji Ummi. Cikin bakinciki da abin da Ummi take mata, ta ce mata. "Allah ya isa ban yafe ba." ke ai mu zamu miki Allah ya isa bamu yafe ba, tunda kika lalata mana rayuwa, kuma muka cigaba da zama dake ai kin san mun yi hakuri, oya wuce tsohuwar banza kawai."
Ta haɗa da abinda na kawo mata, ta cinye har da na Addah.

Haka yanayin ya cigaba da tafiya, Ummi tana zuwa kuma ina jin labarin yadda suke zaune da halin Addah, murmushi nayi domin Allah ya tsamo ni daga cikin masifar Addah babu dalilin komawa cikinshi, matar Yallabai Yazid ma ta gama jarabararta ta kyale ni, har cewa take ya ajiye karuwa yana abin da yaso da ni, kuma Ni tsakani na da shi bai tab'a min kallon wani abu ba, asalima y'ata yake dauka, idan tana hannuna ya amshe ta, ko ma bata hannuna zai dauketa. A iya zaman da nayi da shi ko da wasa bai tab'a yunkurin yi min wani abu ba, idan akwai abinda yake son ya gani shine na zama mai tsayuwa da kafarta, wannan shi ne mutum na farko da ya tsaya min, sannan zuwa yanzu na san yana rike dasu Addah ne domin ni, ba don haka ba da sun bar mishi yankinshi,. Tow nice karfin zamansu.

Ko ranar da ta b'ata min rai shi ya ce min. "Ke ni zan Kore su, na gaji da ganin suna kuntata miki. Gara su baki wuri ki huta." Girgiza masa kai nayi ina faɗin. "Ko daya, kawai nafi son na gansu a tare dani. Ko babu komai nasan wata rana zasu min adalci." Wato idan rana ta fito tafin hannun bai isa kare ta ba, wannan shine adadin abinda zan fada domin Addah tun kafin a haife ni take adawa da mahaifiyata, da aka haife ni kuma dole ta hakura da abin da take mata, sai dai babban abunda yake min ciwo mahaifiyata da ban san dalilin da yasa ta manta dani ba, nasan dai duk inda take zata so da ina tare da ita,

A hankali kome yake tafiya tare da zama tarihi, kusan shekara daya da rabi kenan, da barin mu Nijeriya, sannan muna wannan ma'aikatar sarrafa maganin Yazid, zuwa yanzu na kara fahimtar abin da suke aikatawa, musamman da ya fahimci yadda nake da baiwar ilimi, haka yake sakani duk wani lissafin Kudi ko wani abu, a gefe guda kuwa Babyna tana yawo ko ina, domin tana tafiya dagwai-dagwai abin ta, duk wanda ya ganta zai dauka ta shekara biyu, nan kuwa shekara daya ne da yan watannin. Yarinyar Kyakyawar gaske ce, don ma ina boyeta, idan na kalleta sai naga bata kama da Zuzu,babu abinda zaka gani kace tana kama da Zuzu sai kwayar idonta.

---

Kallon Addah yayi cikin fushi da b'acin rai ya ce mata. "Na gaya miki, zata tafi karatu , iya abinda nazo gaya miki kenan ke kuma da yarki na shirya yadda zaku tafi sansanin gudun hijira da yake Agadaz OIM,."

Kura mishi ido daya tayi sannan ta ce mishi. "Na gaya maka ka saye ta, domin matukar ina raye zan amshi kudin wani." Shiru yayi yana mamakin taurin kan Addah, kafin ya ce mata. "In sha Allah ba zaku tab'a haduwa ba." Sannan ya juya ya bar gidan,

Ina zaune na ga ya shigo har dakin ina aiki da laptop. Rike hannuna yayi yana faɗin. "Nasan wata rana zaki tambaye ni dalilin da yasa na kawo ku nan." Ya fada yana hada kayanmu. "Lafiya?" Cusa kayan yayi ya tattara kome nawa, "Idan muna raye ki ajiye a ranki zan neme ki." Ya ciro wata sarkar da yake wuyarshi ya saka min.

Sai da muka bar yankin gaba daya yakaini wannan underground tunnels din. "Me yasa zan tafi ban yi sallama da dangina ba." "Ka
Min bayani ina zan tafi." Haka ya cigaba da tafiya har na tsawon awa biyu, sannan muka fito bakin tunnels din, ya kai ni har zuwa inda wata mota take ya ce. "Aseem ka kaita iyakar inda ka ajiye su Reshmah, zan zo idan damar haka ta samu, motar Ansar zai kaita har inda zata zauna. Ka fahimta ko?"
"Eh Sultan na fahimta."

Haka ya saka baby a motar, sannan ya janyo ni, ya rungume ni. "Ina son na gaya miki a kurarren lokaci, ina kaunarki." Ya sumbaci goshina sannan ya saka ni cikin motar. "A'a Yazid!" Ban san me ya min ba, sai dai na zube a jikinshi ban kuma sanin kome ba, haka ya gyara min kwanciya. "Na gode Aseem." Daga haka ya koma cikin tunnels din.

Tsawon awa biyar ina sume, sai da muka isa iyakar da yace da shi. yasa shi yayyafa min ruwa, ina farkawa na zubawa inda muke ido. "Sannu, ga motar Ansar nan."
"Don Allah ina yallabai Yazid?"
"Kiyi hakuri nasan shi namijin duniya ne, yadda ya ƙare iyalinshi haka ya ƙare ki, don haka kiyi karatu yadda zai yi alfahari dake. Ki kula da Amirah sugrah."haka yake kiran Baby. Kuka nasaka ya kwashe kayan mu ya saka a cikin motar Ansar ɗin., daga nan ya tada motar muka bar wurin, sai da muka kwana muka wuni, kafin muka isa Marad'i.

A wata unguwar masu hali ya kai mu, ya kai ni har cikin gidan. Babu abinda babu a cikin gidan, sannan ya mika min wata jaka. "Gashi wannan duk wani abun da kike bukata yana cikin nan, sannan ina kara baki hakuri da ta'aziyar rashin da kuka kuma yi, domin a lokacin da kuka iso labari ya zo min Yallabai Yazid da yan uwanki, sun rasu." Ji nayi kamar duniyar tana juya min, daga nan ban kuma sanin kome ba, na zube a wurin, kwana biyu ina kwance a gadon asibiti babu kowa sai nurse da likitocin da suke kaiwa da komowa, sai wata mata da take dauke da Baby. Kunsan yadda nake cikin tashin hankali? Babu Addah babu Ummi, babu kowa sai Allah sai baby!"

"Sannu Allah ya baki lafiya." Kallonta nayi na lumshe idanuwana, ina son kara haska fuskarshi, a wannan yanayin ya ce min yana sona. A wannan ranar kome ya kara sauyawa. Wata kaddara wata rayuwa, wata duniyar, kome ya tafi kamar bai faru ba.

Da taimakon Matar nan nayi wanka na gyara jikina nazo na sauke ibadar da yake kaina.  Ruwan zafi ta haɗa min na sha, ina kallon Baby da tayi barci, turo kofar aka yi likita ne da nurse. Suka gama duba ni, zasu fita nace musu. "Ku sallame ni " "Jikinki da saura." Inji likitan, "A'a zan karasa a gida don Allah ku sallame ni." Haka suka bani sallame, muka fito Matar nan ita ta nimo mana abin hawa muka nufi gida, har cikin gidan muka shiga. A daya daga cikin kujerun falorn na kwanta,  "Maman Amirah sugrah, zan turo yarinyata, tazo ku kwana domin ba zan barku ku kadai ba." Gyada mata kai nayi, ta fita can sai gata da wasu yan mata uku. "Assalamu alaikum!". "wa'alaikimus Salam!" Na amsa muryarta a ciki ciki, "Maman Amirah sugrah, ga Barakatu zata kwana anan, sauran sun zo miki ya jiki ne."
"Ayya na gode." Na fada a hankali, "muna BQ dinki ne."
"A cikin gidan nan kuke?" Gyada min kai tayi. Sallamar wani magidanci ne yasa suka mike tare da amsa mishi, ya shigo muka gaisa. "Shine maigidana, yana kula da gidan nan."  "Na gode!" Na fada. "Ya Jikinki?"
"Da sauki Baba na gode sosai." Daga haka suka watse aka bar ni da Barakatu, ina kwance kamar ruwa ya cinye ni. A hankali na mike na nufi hanyar kitchen, nayi ta bincike, akwai kome babu abinda Yazid bai saka min ba, wasu kayan abincin zasu shekara uku hudu, zama nayi na fashe da kuka, sai da nayi me isata. Duk abincin da ya dace gasu nan, freezer biyu ne a kitchen din, da na bude daya cike yake da nama na kaza da na saniya, ga kifi da turkey. Taliya na dauka da kayan miya Barakatu ta shigo taga ina ciro kayan abincin, ta tayani na kunna gas, muka yi jallof da busashen kifi, ita ta karasa na koma daki nayi sallar Magariba, nayiwa baby wanka, ban fito ba sai bayan Isha. Abincin ta kwashe min, na ce ta zuba ta ci, ni kadan na saka saboda Baby ne ma, haka ta dauki nata zata fita nace ta kara musu, idan ta je kada ta damu zan iya kwana. Sai da safe ta min na rufe gidan Baby na gama cin abincin ta, na wanke mata baki da jiki, muka shige daki. Kwanciyarta tayi jikina, ina shafa bayanta. Har barci ya dauke ta, baki daya rayuwata nake tunawa tun daga ranar da narasa mahaifiyata, har zuwa mutuwar Baffa'm ya dawo min haka nayi kuka har na godewa Allah, tashi nayi nasha magani na hada da alola nayi sallar nafilla, sannan na jima ina addu'a da rokon sauki a cikin al'amarina...  A hankali na kwanta barci ya dauke ni, haka na kwana cikin mafarkai marasa kai da fasali..

Kiran sallar farko, ya tashe ni na mike kan kafata, na fara addu'a bayan nayi alola nazo na gabatar da sallar nafilla, sannan na dan jira lokacin shiga sallar inata yan tasbihi na, har lokacin danaji ankabbara sallah,  nayi, ina idarwa na zauna ina azkar, me zan yi wanda ya wuce ibada daga rayuwar da na fad'o cikin Ni'ima da wadata, addu'ar da nake mishi yafi na kowa, domin ya bani abubuwa dayawa da na rasa, ya bani abin da zan tsaya da kafata. Hawaye ne ya zubo min, lokacin da na tuna da kalamanshi. *Idan ana son kiyi karatu dole a dauke miki, nauyin cikinki da na bukatar yau da kullum, shi yasa nake son kafin ki fara karatu na nima miki abin da ba zaki nima a wani wurin ba, so samu ne a mallaka miki kuɗi kamar misalin miliyan goma, sannan duk wata akwai wanda zai na kawo miki abinci da kayan masarufi, sutura duk bayan wata uku ana sabunta miki. Baki da ƙishirwa baki da yunwa, baki da buƙatar kuɗi, kin ga kenan babu ke babu niman taimakon wani kato balle ya tab'a min martabarki. Domin wallahi kika sake wani ya tab'a min alfarmata sai na kashe shi na kashe ki, na kashe kaina.*
Hawaye ne ya zubo min, duk ya cika min kome. Amma ya tafi ya barni ya tafi ya bar ni da ciwon da ya dasa min a ranar da zamu rabu. *Dole ki zama kamar namiji, domin rayuwar nan kowa rauninki zai kokarin gani, idan kuma kika sake aka fitar da rauni babu wanda zai mutuntata ki, ba ina nufin ki zama mafadaciya ba, amma ki tsaya kada wasu su kara rena ki kamar yadda yan uwanki suka rena min ke, ki zama mace me tsayawa kanta, yadda Ummina zata tashi ba ta ga Ammynta tana kuka ba.*
Share hawaye nayi na saka a raina daga yau babu wanda zai saka ni kuka.
***
The other side.

Yazid ya sake fitar dasu Addah da Ummi a ranar, ya ce mata. "Ba zaku kara ganin Zeehrah ba, sannan itama ba zata nime ku ba domin na saka a gaya mata kun mutu, inda za a kai ku zasu baku kome sannan zasu koyar daku yadda zaku kama kanku. Ummi Zeehrah ta gaya min cewa Mamarki tace ki koma wurin Yayanki, zaku koyo sana'a na tsawon shekara daya, ki cikawa Mamarki burinta, ga wannan matukar kika koma Nigeria, ki je duk bankin da yayi miki, ki amshi wannan Zeehrah tace na miki wannan kyautar " fashewa tayi da kuka, "Duk cutar da muka mata bai hana ta saka a kyautatta mana ba, Ya Allah na tuba ka yafe min, idan kun sake haduwa ka nima min yafiyarta "

Haka suka rabu, duk sun watse bayan barinsu garin Nawwas ya shigo da mutanenshi, aka shiga wani irin fada a tsakaninsu, har tsawon kwanaki goma sha, a wannan fadar harbi biyu aka mishi a kafarshi. Amma Allah ya bashi sa'a sun kore mutanen nawwas, shima Nawwas din guduwa yayi, da nashi raunin. Amma Yazid an dauke shi a jirgi me tashin angulu aka wuce dashi Algers dama burin mahaifinsa kenan ya dawo a raye ko a kowani yanayi, sannan zai amshe shi. Domin shine next king in sha Allah.

***

Niamey.

Yanzu shekara daya da wani abu kenan, Majid tunda ya samu aka fitar da masu hannu a kisar Manajan kamfaninsu, ya wuce south Africa.

Sau biyu Aryan ya tafi wurinshi na farko shi da Yara da Hajiya dasu Jamilah da Aneesah, na biyu kuma ne daga shi sai Mahdi, suka ga inda yaƙe. Koda yake sai su wuni basu ganshi ba, bayan karatu yana aiki a ruwa bai da ma isasshen lokacin zaman gida, haka yasa a zuwansu na farko suka same shi available. Yanzu kuwa ba sosai ba.

Bayan sun dawo ma ba laifi rigimar cikin gidansu, yana nan babu abinda ya sauya, sai dai tun da aka gano Sajjid yana da hannu a kisan Manaja Hajiya Tani ta kame kanta, sannan shima Amaan Mamman Ba'are, ya nutsu sai dai Tani bata karaya ba. Domin tasan matukar tana raye sai ta raba Abdul Majid da duk abinda yake da shi. Sai ta dasawa Hajiya bakincikin da ba zata manta da ita ba.

Koda yake tun bayan abinda ya faru, hankalin Amaan ya dawo jikinshi, domin ya lura ba don Hajiya ba wannan daren da su Majid suka fita dashi da babu abinda ba zasu mishi ba, haka yasa ya dawo hankalinshi ya fadi abinda ya faru, amma bai gaya musu dalilin da yasa suka kashe Manaja ba, wanda yasan a haka idan ya fada Hajiya faduwa zata yi ta mutu, sannan ya daina zuwa wurin Sajjid din, domin kuwa yana tsoron kada asirinsu ya tonu.

Yana aiki yaji wayarshi na kara, dauka yayi ya saka a kunne. "Lover boy!" Gabanshi ne ya fadi. Domin kwanan nan yana fama da ciwon ciki, tsoron abin da zai ji yasa shi kin zuwa asibitin. "Sajjid ya kake?"

"Lau kai kawai nake son gani." Kasa yayi da murya yana faɗin. "Sajjid na daina wallahi bani da lafiya, ciwon ciki yake damuna. Sannan bana iya rike bayan gari don Allah ka bar wannan harkallan na daina!"

"Karya kenan, domin na saba da kai kuma.bayan kai bana jin akwai wani da na saba da shi. Zaka zo ne ko sai na turawa tsohuwarka videon mu.....!?

```Shahararrun goma aduniyan kayan mata wato m zee kamshi kayan mata kenan inakuke matan kwairai manyan Mata fah bamuna mataba Mata masu aji Wanda tasan kanta agidan mijinta kozokuyi gyara masu kyau da inganci Wanda zaisa oga nishadi yasashi farinciki atare dake kayanmu wane yaro sai uban yaro kinsha zumar makalemata dare daya wanka goma wanan set ne na kayan kwairai akwai fati budurwa mumuna da aeki Dan miyau malaka to shu,Umar Zuma zumar kiba gari kiba Zuma me lakani ningi tsumin lahaula hadin miski ba ahira dawando garin me kabara kasa ruwa sama ruwa wanan magani ba ,a magana magani sanyi mekyu maza da Mata ci da kaza ci da cicibin vlp yan shila ci da kifi nama kayan sakiba na
```

gida danawaje munadakaya kala kala fani kamshi munada shu uwar humra namu ba irin nasubane akwai turare 24 hr turare kabasa Dana gida masu Dadi gakyau ga kamshi 08063845136 KADA KU MANTA KAMAR KOWACCE WATA Wannan akwai Promon Azumi me kike jira ne*

#Mai_Dambuje.....
[3/3, 4:56 PM] Cutie cutie pie: *BAƘIN HAURE....□□*

{Greed for Money is the roots of all evils□}
Arewabooks:maidambu41
Wattpad:Mai_Dambu
Mallakar:Mai_Dambu

```Hajiya ga kaya nan Masha Allah, Available price
Huluna da Mayafai, da na yara sai Wanda ranko yakeso gasunan kala kala, Hajiya muna dasu ba iya hulana da Mayafai ba, har da shadodin na fitar sallah, Hajiya domin hutar dake da fitar dake kunya na tanadi yadda ba zaku sha wahalar yawo kasuwa a cikin azumi ba, don haka kafin kishiyarki tazo ta sata au □😈😂 kafin kishiyarki tazo ta saya na tayiwa mijinku shakara gara kizo ki sata au 😁□😈 baki ya saba gara kizo ki saya, barauniyar gida, kai Sarauniyar gida 😂😈 atow kayana na Uwaren gida da na Amare ne```
*TUNTUBE WANNAN NUMBER 08130269641*
Laces
ATAMFOFI
SHADODDI
Materials
Kayan yara
Veils
Huluna....etc

*028*
A rikicewa Amaan ya ce . "Sajjid me nayi maka da zafi haka? Nace na daina sai ka kyale ni dole ne sai nayi yadda kake so?" Dariya Sajjid yayi yana faɗin. "Wai tow lokacin da ka saka muka fara baka san cewa haka zai faru bane?"
Zufa ne ya shiga karyo mishi, jikinshin na rawa ya mike tsaye. Duk ya rikice. "Sajjid don Allah ka saurare ni!" "Kit ya kashe wayarshi."  Kiran wayar sajjid din yakara yi, amma yaki dauka karshe ma kashe wayar yayi, hannu Amaan yadors a kai kamar ya fasa ihu, ya rasa yadda zai yi da ranshi. Turo kofar da aka yi yasa shi d'ago kai da sauri yana kallon Aryan da yazo tambayarshi. Amma da yake yana cikin tashin hankali, bai iya sauraran Aryan din ba, ya bangaje shi ya fita yana kallon agogon hannun shi.
Sake kiran layin Sajjid yayi  ya ce mishi. "Don Allah ka rufa min asiri gani nan zuwa."
"Ba zan rufa maka asiri ba, kawai ka san yadda zaka yi idan ba haka ba. Hmmm!" Sajjid ya faɗa yana kashe wayar. Kamar zai saki fitsari a wandon shi haka yake ji, don dole ya ja motar shi da gudu, Aryan yana kallonshi ta office. "Me ya same shi?" Ya tambayi kanshi yana me kare kankance idanunshi. Kafin ya sauke ajiyar zuciya.
---
Har inda Sajjid yake boye kanshi ya isa domin ya sani, amma yaki faɗa kuma yasan ana niman sajjid ɗin. Lokacin da ya shiga cikin gidan, Sajjid yana tare da wasu mutane. Amma koda Amaan din ya isa zubewa yayi akan gwiwarshi, a gaban Sajjid din. Dariya suka saka tare da kallon yadda yake durkushe a gabansu. "Don Allah ka rufa min asiri, ka gaya min duk abinda kake so."
```

Kallonshi Sajjid yayi yana juya kofin wine na hannun shi. "Bana bukatar kome, ya cikin naka?" Kamar ya fashe da kuka ya ce mishi. "Da sauki.", "Ka wuce zuwa asibiti duk abinda aka rubuta ka gaya min."

Kasa yayi da kai yana kallon kasa, kafin ya ce. "Idan na tafi asibiti za a iya ganina, sannan mutane zasu ta yawo damu. Ina son fita Najeriya ne naga likita a can." "Shi kenan jeka!" Girgza kai yayi yana faɗin. "Ba zan iya zuwa ba, sai da yardarka da izininka zan tafi."

Tashi Sajjid yayi ya nufi inda Amaan yake zaune, shima ya zauna yana kurbar wine din shi ya ce masa. "Idan haka ne kafin ka tafi asibiti bakidayanmu sai mun more ka." A razane Amaan ya zame zaune daga durkushen da yake, ya zubawa Sajjid idanu. "Wallahi idan kuka min zan sha wahala, don Allah ka rufa min asiri." Tab'e baki Sajjid yayi yana faɗin. "Idan kana tsammanin zaka sha ne, tashi ka je amma ka tanadi amsar da zaka bawa danginka da press!" Ya fada yana d'aga kafadarshi. Wani abu ne ya tsayawa Amaan a rai, ya kasa cewa Uffan domin Sajjid ya kashe shi. "Na gaya maka bani da lafiya, da ace ina da lafiya da zan maka yadda kake so, amma yanzu bani da lafiya."

"Tashi ka tafi dan uwarka, maza fita min a gida dan shegiya!" Kasa motsawa yayi yana zaune a wurin, Sajjid ya cigaba da zagin shi, karshe da yaji haushi daukar kwalba yayi ya wurgawa Amaan a goshinsa sai da ya fasa mishi goshi, duk da haka Amaan bai motsa ba, yana durkushe a wurin, "ka fita min a gida kafin na kashe dan iska irinka." A hankali Amaan ya mike yana dafe da goshinsa ya fita, yana shiga motarshi ya saka tissues yana goge jinin. Haka ya gama ya fita sai da ya bar unguwar ya kifa kanshi a kan sitiyerin motar, ya saki wata irin ajiyar zuciya. Bai san makomarshi ba, matukar Sajjid ya saki videon da yake kokarin sakewa bai san yadda zai fuskanci Hajiya ba, ciwon cikin ne ya murde shi, taka motar yayi da gudun bala'i.

Bayan fitar shi, daya daga cikin mutanen Sajjid ya ce mishi. "Me yasa ka kyale shi." Murmushi yayi yana me busa sigari hayaki na tashi sama. "Ina da shiri ne, ka tab'a ganin yadda aka jefi tsuntsu uku da dutse daya?" Girgiza kai suka yi, ya saki murmushi yadda yayi mishi, "ina kan shiri na, kuma ina shirya abin da zai min kyau ne, idan har nayi nasara sauke da tsuntsaye uku lokaci guda bana jin duniya zata waiwaye ni, domin kuwa na shirya tsaf." Ya fada yana kurbar wine din. "Bamu fahimci abinda kake nufi ba."

"Zaku fahimta amma yanzu ku fara kai mana, mutanen mu ma'aikatan yadda suna shiga cikin aikinmu zai tafi daidai da lissafinmu."

"Ban gane me kake nufi ba!" Inji daya mutumin. Gyara zama Sajjid yayi sannan ya dauko abin wasan chased ya saka yan statue din guda uku, sannan ya ce musu. "Kamar haka nake nufi." "Au min fahimta yanzu."

"Bayan nan akwai abin da nake so ya gaya min. " Ya fada yana murmushi, "idan ya gaya min dole na saka kome akan inda ya dace, domin ina son bazata."

"Amma kai shege ne, yawwa ya batun dila ne? Kwaro ya kawo mana manyan kaya, kuma kayan nan har mun wuce da su. Scotland da France."

"Hmm! Haka Julie take gaya min, Kwaro bai tab'a kawo kaya masu kyan wanan kayan ba, musamman na bayan yafi kowanne kyau. Gaskiya labarin ya min dad'i."

Lashe baki daya mutumin yayi, yana faɗin. "kuma abin dad'i, irin wanda Mr Williams yake so, ya turo kuɗin aka ce, naso da an bani kayan na gyara kaina kafin a saka kasuwa, karshe duniya ce zata fara morar kayan kafin kai ka samu ragowar yan iska."

***

Wasu takardun da Aryan ya kaiwa Hajiya take dubawa, hankalinta ya tafi sosai ga takardun aka yi sallama, sai da ya kara yi a karo na biyu Hajiya ta amsa tana faɗin ."Barka da shigowa Alhaji kai ne da kanka?" Zama Alhaji Haladu yayi yana kallon takardun gabanta, ya saki murmushi yana ce mata. "Duk da kin sauka, har yanzu baki huta ba?"

"A'a ina duba abubuwa masu muhimmanci ne, sannan sauka nayi ba barin aikin nayi ba. A matsayin Uwa nake taya shi aiki sannan yana da damar ya bani aiki a kamfanin domin na kara taya shi da wasu abubuwan."

"Gaskiya ne amma kuma ai kin wuce lokacin da." Kara kallonshi tayi kafin ta ce mishi. "Na wuce lokacin me?" Dariyar renin hankali yayi ya ce mata. "haba yaushe zaki daina goya su?"

Zare medical glass ɗinta tayi tana murmushi. "Idan ban goya su ba wa zan goya? Wa nake da shi da zan goya idan basu ba? Sune dole na, kuma karfina sune suka sani tsayawa da kafaffuna idan ban tsaya musu ba, gaya min waye zan tsayawa?"

Gyad'a kai yayi yana faɗin .

"Tow Allah ya kyauta, tunda kin mai dasu rauninki." Gyara zama tayi ta ce mishi. "Su ba raunina ba ne, nice nan rauninsu domin tari kawai zan yi su dakatar da abinda yake ransu." "Au tow kice babu wanda ya isa ya tab'a ki, ba tare da sun matsa ba." Ranta ne ya fara b'aci. "Idan babu abin arzikin da ya kawo ka, zaka iya tafiya ina da abin yi."

"Tow Allah ya huci zuciyarki don naga ranki ya fara b'aci dama na kawo takardun Afiyyah ce." Gyara zama tayi tana faɗin. "Au ashe bani ɗaya bace nake son Yaran? Kenan idan har haka ne tow wallahi ka sake gaya min sai na sab'a maka, ko dan uwanka aure ya bashi damar tozartani ba wai don ya isa ba, kuma ko yanzu ba za a sake maimaita abin da ya faru ba, don haka ka sami Amaan Mamman Ba'are, shine yake da alhakin daukar ma'aikata ba ni ko Aryan ko Aneesah ba."

Shiru yayi yana kallon yadda ta maida hankalinta kan aikin gabanta, "tow babu yar wata alfarmar da zan samu ne?" Juyawa tayi ta kalle shi, "ok ajiye a can" ta nuna mishi inda ya dace ya ajiye takardun, ta cigaba da aikinta. "Mun gode Allah ya saka da alkhairi." Ya fada mata, bata amsa ba illa aikin da yake gabanta da take yi, kuma ai tasan yana zaune.

"Sa'adatu baki da burin aure ne? Da sauranki har yanzu idan har mutum ya nutsu zai dauka Majid da Amaan da yan uwansu kannenki ne, sannan a wannan lokacin da kike da sauran kuruciyarki aure ya dace dake ba wani abu ba."

"Idan ka gama bayaninka, zaka iya tafiya." Ta ce mishi tana cigaba da aikinta. "Ina dai kara tuna miki, zama haka ba naki ba ne idan da hali ki bawa wani dama ya goge miki tabon da Mamman ba'are ya miki."

Murmushin da bai kai zuci ba, tayi tana faɗin. "Kuma da yake an gaya maka namiji ne a gabana ko? Idan har wannan tunanin shine a ranka tow ka cire ni bana tunanin wani namiji, don Allah tashi ka fita." Mikewa yayi yana murmushi. "Nasan zaki so kiyi tunani ina jiran duk abinda kika yanke."

"Kana son naci mutincinka ne? Ka fita ka bar min gidana." Ta fada a fusace, shigowar Amaan bai hana shi magana ba. "Kina da sauran damarki, a matsayinki na mace mai lafiya da jini a jika don haka ina kara baki shawara ki yi tunani da kyau. A shirye nake na wanke miki zuciyarki." Cikin wani irin fushi Amaan ya cakumi wuyarshi. "Wallahi sai na karya wuyarka, kai na rantse ka kara cewa kana son Hajiya, sai na kashe ka." Ya janyo shi kiiiiii kamar kayan wanki, ya watsa a waje yana faɗin. "Na rantse Hajiya ta fi ƙarfinka na sake ganin, kiraren sawunka sai na ballaka."

Ya fada yana hayagaga, Amaan kishi yake taya Ubanshi. Domin baya kaunar Hajiya ta kebe da wani. Musamman lokacin da ta amshi kamfanin idan tayi baƙi masu saka hannun jari, tow bake-bake yake zuwa yayi yana kallon ko zata mika musu hannu su gaisa, duk da mugun halinshi yana matukar kishin Ubanshi sannan abinda ya faru a kuruciyarsu da Hajiya yana nan a memory din shi bai manta ba, haka yasa baki daya yake kara jin haushin ganin Hajiya da wani namiji, domin bayan faruwar lamarin abin da wasu suke ta faɗa yasa shi cikin rud'ani haka yasa wani lokaci yake ganin, yunwa da wahala.yasa Hajiya aikata wancan abin. "Kai meye haka?" Hajiya ta tambaye shi tana watsa mishi harara. "Hajiya cewa yayi fa."

"Sai me? Zama zan tayi? Ba zan yi aure ba kenan?" Ware idanu yayi cike da takaici. "Aure kamar ya? Fisabilillahi Hajiya da tsufarki, ki ce aure zaki yi? Ke Hajiya haka ya dace dake?"

Sakin baki tayi tana kallon shi cikin mamaki da takaici. "Kasan ni ba mutum ba ce da zaka ce aure xan yi. Sannu isasshe jikan mallaka'u, aure zanyi kuma na gaya maka idan kaso kada na ƙara ganin kafarka a gidana."

"Wallahi kika yi aure sai na kashe shi, haka kawai don janyo mana abin kunya da magana kice aure zaki yi, Hajiya idan kin manta abinda ya faru wallahi ban manta ba, ba zaki tab'a aure ba, domin cin amana ne, taya zaki..."

Kura mishi idanu tayi tana son jin me zai ce. "ban fahimce ka ba, meye na manta da ku baku manta ba?" Hadiye yawu yayi ganin yadda ta kura mishi idanu. "Babu kome." "Da kome mana, Amaan idan da babu kome mai zai kawo wancan maganar, shi yasa kake min rashin kunya da fitsara? Akan wancan abin da ya faru kake had'a kai da mutanen da suke bi na da sharri."

Murmushi tayi mai sauti tana kallon yadda yake zufa, ga goshinsa da ya sha bandegi. "Kada ka damu, su din zasu maka abin da na kasa maka, amma ka sani duk lokacin da ta kwabe maka bana fatan haka , amma a lokacin zan iya barrata kaina da kai har abada. Ga takardu can ka dauka na Afiyyah zata yi aiki a kamfanin mu."

"Hmm!" Ya fada yana jin wani irin ciwon ciki, da tsoron abin da zai je ya dawo tabbas idan hakan ta faru kwananshi ya ƙare. Da sauri ya haura sama da gudu dakin Majid Mamman Ba'are ya wuce da sauri ya faɗa ban daki, sai da ya katsiye abinda yake cikinshi, ga wani irin ciwon cikin da yake damunshi wanda ya saka shi kasa gane kanshi. Dakyar ya daure wandon shi ya fito yana nishi, koda ya sauko kasa, takardun ya dauka ya fita bai cewa Hajiya kome ba. Itama tana son yi mishi magana amma da yake ya bata haushi sai tayi banza da shi.

Dakyar ya bar gidan Hajiya, don dole ya nufi wani kanti, ya sayi wasu bakaken kaya yasaka. Sannan ya nufi wani asibiti. Dakyar yaga likitan, a lokacin wani sabon ciwon cikin ya kara turnike shi kamar zai mutu, haka likitan ya mishi scanning. Yana ganin yadda sperm ya dankare a cikin wurin kashinsa, shi yasa yake jin ciwon ciki.

"Alhaji wannan abin da nake gani, matukar aka cigaba da yin shi zai haifar maka da Cancer cikin makasayarka, sannan idan ma baka yi fama da Cancer ba, karshe zai zama tsutsa ya cinye maka duburanka, idan da hali tunda Allah ya ce kada ayi shi haramun ne, tow a barshi wannan shine nasihar da zan maka."

Idanunshi cike da kwalla ya ce mishi.

"Likita ka raba ni da shi, don Allah nayi alkawarin ba zan kuma aikatawa ba."

"Tow zan daura ka akan magani, na tsawo kwanaki sannan idan muka tara shi wuri guda sai, a maka aiki a cire amma ka kula gaskiya domin zaka iya rasa lafiyarka sannan idan ka cigaba zaka iya kamuwa da wasu cututtukan da babu magani sai mutuwa."

Tashi zaune yayi ya rike hannun likitan, kamar yaro karami ya ce mishi. "Likita na daina don Allah ka taimaka min bana iya rike kashi ma."

"Shiga ga ban daki, kayi." Haka ya shiga da gudu, tausayin Amaan din ne ya kama shi. Can da Amaan din ya fito ya zauna yana dafe goshinsa ya ce mishi. "ka kula sosai sannan idan mun yi aikin na cikinka zamu duba wurin muga ko zamu iya aikinshi."

"Ba zaku iya bane?" Girgza kai likitan yayi yana cire handglove din hannun shi yana faɗin. "A'a ba haka ba ne, wurin yana da matukar hatsari ne matukar aka tab'a wurin ya samu matsala tow kai baka isa ka rayu lafiya ba, zamu duba yiwuwar dubaka ko mu turaka wani asibiti."

"Innalillahi'wa'inna'ilaihi'raji'un! Allah na tuba don Allah likita kayi wani abu."

"Ban ce ba zamu iya ba, shi makasaya yana cikin wuri me matukar muhimmanci da hatsari da zarar an tab'a shi zai yi wuya mutum ya kara morar kanshi."

Cikin kaduwa Amaan ya kalli likitan. "Ka min bayani yadda zan fahimta don Allah."

"Zan maka bayani ai, shi idan aka maka aikin matukar bai yi kyau ba tow ba kai babu rayuwa saida famfas zaka kare rayuwarka kamar yaro karami da ake goyo ne. Kullum duwawunka cikin kunzugu."

Wani azababben rawa jikin Amaan ya dauka. "Likita babu wata hanya ce?" "Gaskiya babu tabbas, koda akwai kuwa."

Jikinshi ne ya dauki wani irin rawa, kamar zai saki fitsari a wandonshi. Kuma shima likitan yayi amfani da wadannan kalaman ne domin ya barranta shi daga wancan barnar domin idan ya mishi aikin zai iya komawa aikata abin da yake amma idan ya bashi tsoro dole ya hakura daga aikata shirmen domin wannan masifar da ta fad'o wannan zamanin ba karamar bala'i ba ce.

Don haka ya cigaba da razana shi, har sai da yaji nadamar aikata haka yazo mishi, sannan likitan ya rubuta mishi magani, ya tafi.

Koda ya sayi maganin gida ya wuce, a falo ya samu Matarshi. "Amaan ina son kudi?" "Ki kyale ni bani da lafiya don Allah." Ya fada mata yana wucewa. "Wallahi sai ka bani, kana board director ace baka da kudi uban me kake yi a kamfanin?" Juyawa yayi ya kalleta kamar zai budɛ baki yayi magana sai kuma yayi shiru, ya haura sama ya shiga dakinshi sai da ya rufe kofar ya nufi gefen gadon shi ya dauko kudi me yawan gaske ya fito. Kai mata yayi sannan ya juya zuwa dakinshi, kanshi kamar zai tsage haka yake ji. Lokacin da ya shiga dakin ya rufe kofar shi kwanciya yayi kafin ya tashi ya sha magani da fresh milki, kafin ya koma ya kwanta yana ji kamar ana tsatsagar zuciyarshi. Bai san dalilin fadawar shi wannan yanayin ba, amma tabbas bala'in da ya fada baya fatan wani ya kara faɗawa, babban abin da yake kara tsorata shi ranar da Hajiya zata gane me yake aikatawa ranar kashin shi ya bushe, wani irin tsoro ne ya kara mamaye ilahirin lungu da sako, na cikin zuciyarshi. Tabbas ranar zai bukaci mutuwarshi da ganin wannan ranar.

Aryan.

Har aka tashi aiki bai ga Amaan ba, don haka daga wurin aiki ko gida bai shiga ba, ya nufi wurin Hajiya haka ya zame musu al'ada tunda dama suna zuwa da safe sannan da rana suna zuwa wurin aikinta, yanzu da ta daina aikin wurinta suke fara zuwa kafin su tafi wurin matansu. Da sallama ya shiga falon tana lazimi. Zama yayi sannan ya jira ta gama, kafin ta kalle shi. "Ya aiki?" "Alhamdulillahi!" Ya faɗa yana kallonta tv. "Da magana ne?" "Matsayin Aneesah yayi mata nauyi, ita matar wani ce, mai zai hana a bawa wani wanda muka yarda da amanarshi da nagartar shi. "

Kallonshi tayi kafin tayi shiru na wasu dakikai ta numfasa sannan ta ce mishi. "Ina ga a bawa Abdul Majid dan Hadiza."

Murmushi yayi ya ce mata. "Hajiya nayi tunanin haka, sannan idan kin lura sam ko cusa kanshi baya yi a cikin harkar gidan nan. Shi yake damun Hammayo amma shi Hammayo ko a jikinshi. Shi ya fi dacewa da xama CEO na kamfanin BA'ARE GOLDEN EMPIRES."

"Kuma idan aka bashi a bazata Uwarshi zata sha mamaki, duk makaman yakinta zata zubar, sannan rigimar da yake tashi akan kamfanin zai yi sauki " inji Hajiya.

"Tabbas nima na amince da haka, amma hajiya Amaan ya shigo kuwa?" Tab'e baki tayi tana faɗin. "Ya shigo."

"Tow shi kenan" ya faɗa yana me mikewa.

"A gaida Nabeeha da takwara. Da dan Daada."

***

Agadaz

OIM : Organisation International pour Les iMigrations

office din yan gudun hijira suke kai takardun su ne domin a basu damar zama a cikin camp din oim yana under African countries ne, domin duk wasu ƙasashen Afrika da suke makotaka da Nijar suna turo mutanensu, domin akwai hulɗar zaman lafiya a tsakaninsu. Sannan akwai kyakkyawar fahimta idan har kasa ta turo dan gudun hijira Nijar zata mishi duk wani abin da ya dace har ta mai da shi zuwa ga gwamnatin ƙasarshi sannan da abin yi me kyau, don haka *OIM* yana kasar Nijar a cikin jahohi

biyu na ƙasar, kusan kullum na duniya Addah da Ummi sai sun tafi office din amma kuma babu sa'a, domin yawan yan gudun hijirar da suke zuwa don niman a basu agaji.

Yau ma kamar kullum bayan sun bi dogon layi, Adda da idanunta daya da ya samu matsala take ƙare shi, wani jami'in wurin ya zo wucewa ya ganta ana ƙoƙarin ture ta a layin, ya ce musu. "Sannu Inna muje ke daya ce?" Ummi da take bayanta tayi maza ta ce mishi. "A'a oga tare da ita muke ina mata jagora."

"Amma ai ke ya dace ki tsaya a bayanta ba a gaba ya dace ki tsaya bs." Cikin gajiya da turereniyar da ake mata ta ce mishi. "Shi kenan oga." Ta faɗa tana komawa gaban Addah. "A'a muje a duba takardunku, domin ba a son me ciwon idanu yana tsayawa a rana."

"Mun gode fa " suka bi bayanshi har cikin office din, mutane sai surutu suke, suna zuwa aka duba takardunsu, Asalima stamp na Hukumar tsaro ne a jikin takardar. Ba ajima ba aka sallame su aka tura su camp, wato OIM camp shine ake kiranshi da aljannar yan gudun hijira. Duk wani abu da zaka bukata na rayuwa a cikin camp din an tanadar maka, kulawar da ake bawa yan gudun hijiran ko yan kasar basu samu, domin babu abinda ba a musu. Ana kyautata musu, sannan kome nasu ana basu. Daga zuwan su aka wuce da Addah Clinic da yake cikin camp din aka fara duba matsalar idanuhta. Ita kan cewa take. "Ku barshi zai tsiyaye da kanshi, ai idanun ya mutu." Ta fada cike da takaici, duk ranar da ta haɗu da Zahrah sai ta mata abinda ba zata manta ba, sai ta mata sanadin da ta sake komawa zero daga Add din da Yazid din ya sama mata, matukar tana numfashi sai ta saka mata Fargaba da tashin hankali a ranta, zata cigaba da zaman jiranta har ranar da zata bayyana.

Ko a cikin Uwarta ya kaita sai ta zakulota ta rama abin da tayi mata, ba zata kyale ta ba. Haka tayi ta kintsa mugun nufin da yake ranta.

Haka suka gama dubata, sannan suka sallame ta. Da magungunan masu yawan gaske.

***

Marad'i.....

#Mai_Dambulaaaaaaaaaaa

[3/4, 9:14 PM] Cutie cutie pie: *BAƘIN HAURE....□□*

{Greed for Money is the roots of all evils□}

Arewabooks:maidambu41

Wattpad:Mai_Dambu

Mallakar:Mai_Dambu

029

Bahaushe yayi gaskiya da ya ce d'an uwa rigar k'aya, kabarshi a jikinka ya soke ka. Ka cire shi duniya ta zage ka. Ban fadi haka don kome ba, sai yadda nake cike da kewar Addah da Ummi, musamman Zuzu da ban san wata duniya take ba, ina matuƙar son ganin Zuzu ta gaya min meye nayi mata haka? Me yasa tayi min haka? Me yasa ta ha'ince ni? Kowacce rayuwa tafe take da kalubale. Sai dai a wannan lokacin na fahimci girma da muhimmancin nisantar su Addah. Sannan akwai wani abu daya da na kasa sabawa shi, wato tunanin Yazid, na kasa yarda ya mutu domin zuciya ta bata bani damar amsar labarin Mutuwarshi ba, sannan haka su Addah bana fatan ace suma sun mutu domin ciwon zai min yawwa.

Yau ya kamata na fara zuwa makaranta, amma bani da karsashi da nutsuwar zuwa, zuciya ta a rufe take wani irin yanayi nake ji mara daɗi, haka yasa na cigaba da kwanciyar da nake har zuwa wani lokaci. Karfe tara na fada ban daki, na daɗ'e sosai sannan na fito daure da towel, a hankali idanuna ya sauka kan Baby da ta farka, gadon na nufa ina faɗin. "Kin tashi ne?" Na d'auketa a kafadata, zuwa banɗaki na mata wanka sannan na daurata akan karamin poo mikewa tayi tana ihu, "yi hakuri zauna kiyi " ai kamar na zage ta, haka yasa dole na.hakura muka fito na shirya ta

cikin wata riga da wando, pink da purple. Sai farin hular Amnas, da nasaka mata, na shafe ta da turare mai daɗi da sanyi, Yallabai Yazid ya koya min amfani da turare dan zaman da nayi da shi, ko wannan gidan haka ne domin gaban mirror akwai turaruka kala kala wasu ma ban taba jin sunansu ba. Hadiye yawu nayi ina jin kwalla na cika min idanu. Mikewa nayi na nufi sip dinmu na bude, karamin drowe din jikin siff din,bra ne da pants ɗinsu, a hankali na cire wasu farare kalkal, na saka a saman gadon na koma na bude asalin wurin kayana. Wata doguwar riga na ciro, da mayafinshi da hular da zata dace da shi.

A hankali na saka bra din da pant, sannan na saka wani gajeran wando, iya gwiwa kafin na saka gown din. Wanda aka rubuta Amnas collection, na saka a hankali, kallon kaina nayi a madubi fuskata tayi kyau, ba laifi sai dai kana kallon kwayar idanuna zaka fahimci ina cike da damuwa. Murmushi nayi na tattara gashin kaina,.na saka bam na daure shi tsaf, sannan na nufi inda mayafinshi yake na lullube, bugun kofar dakin aka yi na ce. "Shigo." Ina gyara jakar da zan fita da shi, ta shigo. "Tante!" Cikin kulawa na amsa mata. "Na'am Barakatu?" "InJi Babanmu wai na gaya miki, mai kaiki makaranta ya jima da zuwa."

"Ok gani nan zuwa!" Na mike ina.gyara zaman mayafina, tare da saka jaka a kafadar, na nufi wurin turare na shafa, sannan na fito ina dauke da baby, dake bata da rikici, mikawa Barakatu ita nayi na koma daki na d'aga towel din na shanya sannaan na dauki kudi a cikin drower gadon, na zuba a jakar ko da zan bukaci nayi wani abu, ina gamawa na dauko flat shoe na saka, sannan na fito bayan na rufe dakin, na dauki kayan abincin baby na kai musu, da wasu kayanta kala biyu da Pampers. "Maman Barakatu zan tafi ga Baby Amirah sugrah!"

"Allah ya dawo dake lafiya, sai kin dawo." "Yawwa, Barakatu idan ban dawo ba, ki dafa mana shinkafa akwai sauran miyar nan ki zuba muku ku bar min sauran."

"Tow Tante!" Ta fada, da sauri na fito daga wurinsu na nufi hanyar waje. Tun kafin na isa driver ya fito ya bude min kofar baya, na shiga na zauna. "na gode! Nace mashi" Sannan ya shigo muka bar gidan, kwantar da kaina nayi a jikin kujerar, ina ji na kamar wata sabuwar halitta, wacce aka sauya mata duniyarta, tabbas an sauya min duniyata amma kuma ina dangina da zuri'ata suke? Buɗe idanu nayi, ina shaƙar kamshin turaren motar, kafin na dan zubawa gefen hanya idanu. Bani da kowa bani da kome, daga ni sai Baby haka zan rayu cikin kaɗaici, cizon fatar bakina nayi ina mai da kwallar da ke shirin zubo min. Haka muka isa makarantar, na kasa barin zuciyata ta huta, muna isa ya Fito ya bude min kofar, sannan ya amshi jakar hannuna. Har Office din Dean na Mariama Abacha University marad'i ya kai ni.

Koda muka shiga office din, Dean din bata nan, don haka muka zauna har ta dawo. Cikin girmamawa mutumin ya gaishe ta cikin harshen French, ya mata bayani. "Tow shi kenan, zan duba bari na kira shugaban tsangayarsu." Ta fada da hausa, jin tana hausa sai naji kamar ina cikin dangina ne. Domin wani lokaci idan kana jin wani harshe aka zo ana yin irin shi, zaka ji kamar dangi kuke da mutum,haka yasa na zuba mata idanu ita kanta hausar da take cikin gayu da kwarewa, kamar irin ban ma san yadda zan yi bayani ba, amma tabbas na tsinci dami a kala. "Muje Madame!" "Ok!" Na furta a hankali, haka muka fito daga cikin office din zuwa department ɗinmu na Yan economic, duk wasu abubuwan da ya dace duk muka kammala a yau, sannan ya kalle ni cikin girmamawa ya ce min. "Madame daga yau bani zan kara zuwa ba, akwai wanda xai rika zuwa yana kawo ki, sannan asabar da lahadi zai zo ya kaiki wurin koyon tukin motar, wannan shine inda zan tsaya. Idan na tafi da motar wanda zai cigaba zai dawo da ita."

"Da gaske Yazid ya mutu?" Bai kalle ni ba, kuma nasan ba lallai ba ne ya kalle ni tunda iya kan aikinshi yake, ina ji ina gani ya ja motar ya bar makarantar. Hawaye ne ya zubo min, tabbas ba mutuwa akewa kuka ba, sabo ita ce akewa kuka kuma yanzu da na saba da shi, ya tafi ya barni da ciwo a rayuwata. Haka na share hawayen da ya zubo min, sannan na nufi hall din da zamu na daukar lecture na zauna, bamu da yawa a cikin hall din haka ya tabbatar min da cewa course ɗin mu bai da farinjini. Eh

bai da farinjini domin ba kowa yake yin shi ba, ko ni naso da accounting dina da nafara tun farko na karanta da na samu damar cigaba daga inda na tsaya, amma wancan takardun ma Yazid cewa yayi basu dace dani ba. Ina zaune malami ya shigo ya gama bayaninshi, masu maida hankali suna maida hankali mu kuma, muna ta baza idanu, sai bayan fitar shi na sauke ajiyar zuciya. Wunin ranar ban da Masallaci ban je ko ina ba, asalima ni yanzu ban son sakewa da mutane, gudun kada wani abu ya taso a san Asalina ayi min gori ko cin mutuncin. Haka yasa ana tashi na tafi inda aka ajiye motar dazun naga motar, tun kafin na isa ya taso da sauri kamar zai kwanta na bi ta kanshi, ya amshi jakar hannuna, ya bude min baya na shiga, sannan ya ajiye jakar a kujerar gaba, sannan muka bar makarantar. Koda muka isa a matukar gajiye na isa, na samu Baby Amirah sugrah tana ta ihu, amsarta nayi ina faɗin. "Me ya same ta?" "Faduwa tayi dan zaki dawo nan!" A hankali idanuna ya sauka kan hannunta da yayi jajjur, "toh ba kome." Na wuce da ita falo, ina rungume da ita. Sai kuka take kamar zata tsaga gidan, na rasa me ke min dad'i. Haka na bata ruwa tasha, ta faɗa kirjina tana sauke ajiyar zuciya. "Mirah me aka miki?" Sake k'amk'ame ni tayi, tana sauke ajiyar zuciya. Dakyar na samu damar shiga kitchen na duba Barakatu ta gama abinci, na zauna naci na bata amma taki ci, kafin ayi Magariba jikinta yadau zafi kamar wuta rau. Haka na daure nayi sallah, sannan na fito ina gayawa Baban Barakatu zan kaita asibiti. "A'a da dai kin koma, za azo a dauke ki." Haka na dawo can kuwa sai ga drivern da ya dawo da ni, yazo muka je asibiti aka duba hannun ashe tsagewar kashi ne, domin ta fadi akan hannun ne. Haka aka daure hannun muka dawo gida da lodin magunguna muna dawowa Mamansu Barakatu tazo tayi ta bani hakuri. Ni na rasa hakurin na meye? Naga dai tsautsayi yana kan kowa, don haka na fahimci wani abu, babu yadda zaka yi ka daurawa wani nauyinka, don kawai wani dalili. Haka yasa da muka kwana washe gari da kaina nayi abin karyawa, da duk wani abin da ya dace, sannan na ajiye na mata wanka, na shiryata. Bayan na gama shiri cikin nutsuwa da cikar kamala, na fito ina rungume da ita. "Hajiya zaki tafi da ita ne?" "Eh idan ta warke zan barta domin ko na tafi ba xan samu nutsuwar karatu ba." "Shi kenan a dawo Lafiya, Allah ya bata lafiya."
"Amin Ya Allah."
Daga haka na wuce mota, muka bar gidan. "Madame ko za a akaita gidan renon yara ne, kada ta raba miki hankali." "Ba kome zan iya." Haka muka isa har makarantar, wani abin mamaki shine tana ganin baƙin fuska ta ware, kowa ta gani Ba, wai ita Baba. Haka muka shiga aji, tayi ta yawo dake tana tafiya, ganin bandeji a hannunta yasa kowa ya ganta sai ya tambayeta. Ita kuma tayi mishi gwaranci. Lokacin da malama ta shigo nan ta ɗauke ta. Ta fara mana darasi, kafin wani lokaci tayi barci. "Ina Mamanta?" Mikewa nayi na je na amsheta. "Jikinta kamar da zazzaɓi, ki bata magani."

"Tow na gode!" Na wuce da ita, na zauna muka cigaba da darasi, ta fara goma ta gama sha biyu, sai karfe biyu zuwa biyar haka muka wuni. Koda ta farka magani na bata da abincinta, wasa ta cigaba da yi, har muka taso.

Haka na cigaba da tafiya da ita har aka warware hannun, na sakata a daycare. Ba lallai kowa ya fahimce ni ba, amma nasan har ga Allah shi daycare makaranta ne, su kuma Barakatu, ba zan daura musu dawainiyyar bari-bari ba, haka yasa na yanke shawarar sakata, amma nasan ran Mamansu ya b'aci,. Sai dai ban wani damu ba. Domin yanzu ba da bane da damuwar wani zai hana ni nutsuwa, sannan a gefe guda ina tsoron kada wata rana Uwarta ta bayyana taga yarta ta nakasa ta ce ban rike amanar da ta bani ba, gashi na nakas ta mata yarta.
Watana biyu da fara karatu aka fara shirin azumi, nayi farinciki sosai amma kuma sai nake ganin kamar ba wani farinciki da karsashi, dake ina koyon tukin mota kuma mutumin ya gaya min bayan sallah ba xai cigaba da ajiye ni a school ba, iya wa'adin shi ya ƙare, na takura kaina sai na koyi mota. Domin ni sai abin yazo min banbanrakwai. Haka na cigaba da zuwa koda aka fara azumi ina makarantar aka kawo min duk wani abin bukata, "baban Barakatu basu gaya maka daga ina suke ba?"

"Gaskiya basu fada ba, kawai ajiye min kayan suka yi suka tafi."
"Shi kenan!" Na bude kofar ya shigar min da shi store, sannan na wuce daki ina nazarin waye da wannan dawainiyyar.
In sha Allah, ba zaki sake kuka don yunwa ko wurin kwana ba, duk wani abu sai dai ki bawa wani. Nayi alƙawarin ko bayan raina ba zaki wulakanta ba, zan tsaya miki idan ina raye. Haka koda na mutu sunana zai cigaba da baki duk wani abin da zaki roka, a tab'a kimarki ba, ba zan tab'a barin ki rasa shi ba. Zubewa nayi akan gwiwata na fashe da kuka, wata irin rayuwa nake yi ne? Da farko mutumin da ya taimaka min ya kubutar dani a hannun wancan azzalumin, babu shi babu labarinshi, na ganshi ma nayi mishi godiya babu dama, Aunty Umaimah ma, ban san inda zan same ta ba. Shima wanda nake farin cikin na same shi, baya nan baya nan ya tafi "innalillahi'wa'inna'ilaihi'raji'un, me yasa mutanen kirki suke fita a rayuwata lokacin da nake tsannanin bukatarsu???????????
#Mai_Dambu
```Hajiya ga kaya nan Masha Allah, Available price
Huluna da Mayafai, da na yara sai Wanda ranko yakeso gasunan kala kala, Hajiya muna dasu ba iya hulana da Mayafai ba, har da shadodin na fitar sallah, Hajiya domin hutar dake da fitar dake kunya na tanadi yadda ba zaku sha wahalar yawo kasuwa a cikin azumi ba, don haka kafin kishiyarki tazo ta sata au 😈😂 kafin kishiyarki tazo ta saya na tayiwa mijinku shakara gara kizo ki sata au 😁😈 baki ya saba gara kizo ki saya, barauniyar gida, kai Sarauniyar gida 😂😈 atow kayana na Uwaren gida da na Amare ne```
*TUNTUBE WANNAN NUMBER 08130269641*
Laces
ATAMFOFI
SHADODDI
Materials
Kayan yara
Veils
Huluna....etc
[3/6, 8:07 PM] Cutie cutie pie: *BAƘIN HAURE....*

{Greed for Money is the roots of all evils}
Arewabooks:maidambu41
Wattpad:Mai_Dambu
Mallakar:Mai_Dambu

*030*
Haka nayi ta kuka ina jin kamar bani da sa'a shi yasa mutanen kirki suke barina, nayi kukana na godewa Allah. "Ma....ma!" Naji Muryar Baby Amirah sugrah, bude idanuna nayi a kan fuskarta, da sauri ta tako zuwa wurina, bude mata hannu nayi ina jin sabon kaunarta. "Ta kira ni Mama!" Na fada da karfi wanda yasa na kara k'ank'ame ta a jikina. "Amirah sugrah, nice Mama?" Sai ga hawaye ashe haka uwa take ji? Ranar da d'anta ya kirata Mama, ashe haka abin yake da dad'i,. Sai ga hawaye shar da duminsu, wannan irin bazatar da Amirah tayi min da tab'a zuciya yake, sai na rasa kukan farinciki nake ko na bakinciki, bakiɗaya rayuwata ta kuma sake samun wani nauyin daga wanda na amsa, domin amsa sunan uwa ba karamin al'amari bane, balle irina da nasan dayawa suna son sanin wacece ni, kuma na fahimci haka a makaranta musamman idan aka ga yadda nake makale da ita, a cikin aji. Sai ya kasance kowa son sanin wacece ni yake meye alakata da Yarinyar da nake dauke da ita. Sai dai na barwa zuciyata wannan aikin ba zan fara buɗe cikina da zuciya ta ga kowa ba, komai alakata da kai balle kuma na fahimci idan har mutane suka ji ina turanci, sai na zama kamar wata criminal domin yadda yan Nigeria muka b'ata kanmu ba mazan ba matan.
```

Mikewa nayi na nufi store na ware kayan cikin kitchen din na fito da shi, sannan na nufi hanyar waje, na kira baraka ta dauka musu, ina shiga na samu suna aikin abincin buda baki. "Tante baki bar aikin da za ayi miki ba."
"Assalamu alaikum! Amma ai na fara sallama ko?" Murmushi tayi tana sosa kai. "Wa'alaikis salam, Amirah tunda kika fadi tante ta raba mu dake!" Inji Zainab mai bin Baraka tana amsar Amirah. Murmushi nayi nace mata. "ba haka bane, kawai idan na barta ba zan iya nutsuwa ba, amma ai yanzu ma gamu a gida."
"Sannu Maman Amirah!" Murmushi nayi, ina mai rusunawa na gaida ta. "Yawwa Maman baraka, ya zafin nan ya niyya kuma?" "Alhamdulillahi, ya makaranta."
"Masha Allah, sai godiyar Allah." Na fada ina zama, "Nace baki bar abin da za'ayi miki ba?"

Murmushi nayi nace mata, "Maman baraka, jiya aka fara azumi yau biyu babu wani abin tashin hankali, yanzu aka fara kuma ina ji ba zamu cigaba da zuwa makaranta ba, domin nan da sati biyu zamu dawo gida hutu sai bayan sallah."

"Ayya amma da kina barin aikin, domin a rage miki kafin ki dawo." Murmushi nayi ina kallon yadda suke ta shirin buɗa baki, "yawwa Baraka, ke da Zainab ko zaku dauko kayan abinci yana kofar kitchen." Kallon Mamansu tai, kafin ta kalle ni. "Maman Amirah!!!" "Kuje ku dauko." Hadiye yawu tayi tana son magana amma naki mata magana, sai kallon garin kunun da zasu yi. Ina zaune bayan fitarsu sai ga Babansu. "Wai ayi haka?" Murmushi nayi, a karon farko na kara samun wasu ahalin me ya kai haka dad'i. Haka suka fito da kayan abincin, muna da shinkafa da na bude tun zuwa na, sannan na basu buhu guda, taliya, makaroni, na dibar musu sugar sai madara da na ware musu da Ovaltine. An karo min nama da kifi, na basu daga cikin wanda nake da shi.

A hankali naga hawaye a idanun bayin Allahn nan, yana zuba sai naji kamar an sauya ni, domin ban basu don su min kuka ba, na basu ne don niman lada. Haka suka yi ta min Addu'a. Tashi nayi na bar musu Amirah don taki biyo ni , haka na dawo na shiga aiki, dankali na fere sannan na zuba mishi ruwa, na koma daki nayi sallar la'asar don nayi azahar a makaranta. Ina idarwa na shiga soya tare da gyara kaza nayi mana farfesu mai dankaren kamshi, na koya ne a wurin Zuzu, sannan na daura jallof din taliya, dake gas ce cikin lokaci ƙalilan na gama, na wuce ban daki nayi wanka na sauya zuwa doguwar rigar material me laushi da taushi na Amnas collection da hula me kyau, body mist na shafa oil ɗinshi. Na nufi hanyar falon na zauna ina kallon agogo karfe shida da minti uku, ina zaune a wurin har da minti ashirin, na mike na fito da kome falon na jera, sannan na wuce dakina na dauro alwala, na fito ina azkar da salatin Annabi Muhammad Sallallahu alaihi Wasallama, ina zaune har aka kira sallah, a lokacin Baraka da Zainab suka kawo min kunun tsamiya da kosai, ba karamin dad'i naji ba, haka na nuna musu abincin da na zuba suka ɗauka suna godiya. Kunun da kosai naci, na koma daki da Amirah nayi sallah, ban fito ba sai da nayi sallar Isha da tarawee, sannan na fito na saka hand out a gabana, ina karatu ga Abincin wurin, ina ci ina karatun.

Daga nan ina jin Radion Baban baraka, da yake sauraren Malam Jafar Mahmoud Adam, haka kawai naji ina son rike waya, ina tow tawa take? Sai lokacin na tuna na bar kome a can garin. "Gobe in sha Allah, idan na fita zan nime waya domin na gaji da shirun nan, ni ba Ma'abociyar kallo ba, balle nace zan yi kallo kawai dai nasan ina son jin Radio kasancewar Baffa'm yana ji, sannan Alhajijo shima yana yawan sauraren Radio. Haka na tashi abincin da na zuba, tare da farfesu. Har wurin karfe sha biyu, na mike zuwa daki na sauya kaya, tare da alola na fara sallah, sai wurin karfe biyu na idar na kwanta. Akwai wata dabi'ar da nasan na koya a bayan zuwana garin nan shine kuka kafin nayi barci, haka na ci kuka na koshi, sannan barci yayi gaba da ni.

***

South Africa.

Tunda aka fara azumi yau biyu ga wata, lumshe luhu-luhun idanunshi yayi yana kara bude su, jin wayarshi tana kara. Bai bude ido ba, ya dauka Sannan ya saka a kunne. "Yes.!" "Ubangiji ya shirye ka." A hankali ya tashi zaune yana kallon gefen gadonshi, ya kunna wutar dakin yana jin wani yanayi don bai saba ganin haske a dakinshi ba. Tattaro nutsuwarshi yayi ya ce mata. "Hajiya Barka da shan ruwa." "Hmmm Barka dai Alhaji, ya Ibada?"
"Alhamdulillahi!" "Ina rokon arzikin kazo kayi hutu a gida." "Hajiya!" Ya kirata, "Na gama magana na baka nan da kwana biyu, idan ka sake aka yi azumi biyar baka zo ba, Abdul Majid na barwa sojoji kai. Kai ka saka ni a damuwa dan uwanka ya saka ni a kunci gaya min ya zanyi? Na maka uzuri tunda baka da lafiya, ina son farinciki da nutsuwa na zaɓe ku sama da farinciki na, idan na isa ka taho idan ban isa ba, ka sha zamanka Allah ya baka sa'a!" Kit ta kashe wayar, kut da wani tsalle ya dira a gadon, ya nufi inda kayanshi suke,. Ya shiga zubawa a wata Kyakyawar Luggage, yana gamawa. Ya koma ya zauna tare da kiran Aryan. Sai da wayar ta kusan katsewa sannan ya dauka, Muryar shi a shake ya ce mishi. "Hammayo lafiya?" Yarrrrr yaji kamar wani abu yana yawo a tsakiyar kanshi. "Sorry zamu yi magana gobe, ina hanya."
"Haba? Ubangiji ya kawo ka."
"Amin Ya Allah!" Ya katse kiran, domin shi ba yaro ba ne, yana jin Muryar Nabeeha. A hankali ya ajiye wayar bakiɗaya yana jin shi kamar bai cancanci rayuwa ba, kowa na cikin farinciki da iyalinsa, amma banda shi. Rufe fuska yayi da tafukan hannunshi yana jin wani abu yana tsaya mishi a rai.

Kusan shekara daya da rabi kenan, Umaimah ta kasa samo yarinyar da ya yanketa, yana tsoron kada sanadin wannan yankar ta mutu, domin yasan yadda irin wannan yanka yake, bakiɗaya jin shi yake sama-sama da zaran ya tuno da abinda ya faru. Sai yaji kamar yana da hannu a cikin abin da ya samu yarinyar tunda Umaima ta gaya mishi sun koma garinsu har anyi faɗa sun tashi amma taji labarin kamar faɗar da aka yi ya shafe ta, ko mutuwa tayi shi bai ma iya tuna abin ba, amma tabbas yaji Umaimah tana faɗin anyi faɗa a garinsu ga abinda ya faru, wani takurarren numfashi ya fesar, yana jin kamar bai kyautawa kanshi ba, na rashin ganin fuskar yarinyar amma ya rike muryarta, har a kwanan gobe ba zai manta da sassanyar murya mara amo da kwaramniya ba, shi fatan ma ya ga fuskarta ko sau daya ne, amma ina sai yanzu ne ma yake danasanin domin Umaima da ta gaya mishi, ita ce suka yi barci da ita a gado daya, a ranar da suka zo aikin ceto rayuwar sojojinsu, shafa kanshi yayi cikin tsananin damuwa da takaicin halin ko in kular shi, amma kuma a gefe guda sai yake ganin bai ga dalilin tunawa da ita ba. Meye hadinshi da ita? Meye matsalarshi da ita? Sam baya jin yana da wata alaƙa da zai saka shi tuaninta.
***
Yahunde. Cameroon,
Shashekar kuka take tana jin kamar zuciyarta zata buga, domin wani irin tukikin tashin hankali take ji a ranta, tana jin wani azazzben zafi da ciwo a ranta, ita kanta bata san iya adadin lokacin da ta dauka a gaban Mahaifinsu ba, kukan yayi yawa da yasa Yafendo tashi zuwa ɗakinta Sumee ce ta kasa hakuri ta ce mishi. "Ayya Ayya Datti haka zaka cigaba da kallonta, tana kuka abu biyu ta rasa fa, ta rasa miji da Yarta ai ba zaka zuba mata idanu har haka ba."
Yalwataccen murmushi ya saki, yana faɗin. "Bilkisu idan har Nafisah bata fahimce ni ba, ai ke ya dace ki fahimce ni. Iya su biyu mata Allah ya bani a tsakanin Ya'ya maza, Allah sai ya albarkaci rayuwarsu da jarabawa, idan ban gode mishi ba, me zan iya yi ? Alhamdulillahi Allah ya basu ikon cinye jarabawarsu."
Ya fada yana murmushin karfin hali, domin izuwa yanzu yasan yayi kuskure, ahalinshi sun yi kuskure da ya shafi bayansu. Kuskuren da yayi ba karamin kuskure ba ne, yayi watsi da Amanar da Allah ya bashi, ya watsar da Yaran dan uwanshi sannan ya rungume kashi.

A ina zai ga Isma'il da Aminatu? Ta haka zai gyara kuskuren da yake bibiyar Yaranshi mata da jikokinshi. Ace Yaranshi mata biyu, a wulakance ake aurar dasu, sannan mazajen su azabtar dasu da Yaransu. "Tashi ki tafi Allah ya kara miki hakuri da dangana, Ubangiji ya mata rahama, sannan ki rungumi Zaytoonah domin tana jin zafin hanata ganin mahaifinta, wannan ma wani jan aiki ne da dole sai kin yi da gaske. Allah ya kara miki hakuri."

"Baffayo." Sai kuma tayi shiru kafin ta fashe da wani irin kuka, "Sai hakuri idan har ka yi hakuri, akwai riba da fa'ida." Mikewa tai ta nufi cikin gidan, tana kuka har dakin Yafendo. D'ago kai Zaytoonah tayi tana kallon yadda take rusur kuka. Kauda kai tayi bata jin tausayinta ko kad'an, ta roke ta ta bata hakuri ta ce ta yanke mata kome, ita dai ta barta taje ta ga mahaifinta da Yayarta, amma taki sai yanzu zata yi wani kuka. Ita kuma da bata san shi ba fa? Ita da bata ji duminshi ba fa? Hmmm ita kukan dadi take tunda gata da nata iyayen ita kuma tayi mata asarar rashin ganin Ubanta. Ita yanzu ta tsani kowa ma banda Babynta, domin ba zata iya tsanar Babynta ba, tana son abinta kuma ba zata rabata da mahaifinta ba, domin ita nata rayuwar ta zama incomplete, tunda ta rasa inuwar uba, hatta zaman aure ya haramta a gare ta, domin abinda ya kashe mata aure har da gorin rashin uba. Haka kawai ta ja...

"Zaytoonah!" Mikewa tayi tare da ɗaukar yarta zata bar dakin. "Ki tsane ni babu laifi amma, idan kika nisance ni mutuwa zan yi. Da kewar shi xan ji ko da rashin yar Uwarki? Zaytoonah ina cikin wani yanayi da ban san mafarinsa ba, balle karshensa.....

#Mai_Dambu

```Hajiya ga kaya nan Masha Allah, Available price
Huluna da Mayafai, da na yara sai Wanda ranko yakeso gasunan kala kala, Hajiya muna dasu ba iya hulana da Mayafai ba, har da shadodin na fitar sallah, Hajiya domin hutar dake da fitar dake kunya na tanadi yadda ba zaku sha wahalar yawo kasuwa a cikin azumi ba, don haka kafin kishiyarki tazo ta sata au □😈😂 kafin kishiyarki tazo ta saya na tayiwa mijinku shakara gara kizo ki sata au 😐□😈 baki ya saba gara kizo ki saya, barauniyar gida, kai Sarauniyar gida 😂😈 atow kayana na Uwaren gida da na Amare ne```

*TUNTUBE WANNAN NUMBER 08130269641*

Laces
ATAMFOFI
SHADODDI
Materials
Kayan yara
Veils
Huluna....etc

[3/7, 10:49 AM] Cutie cutie pie: *BAK'IN HAURE....□□*

{Greed for Money is the roots of all evils□}
Arewabooks:maidambu41
Wattpad:Mai_Dambu
Mallakar:Mai_Dambu
*031*

"Ni a sanina ban ki shi ba, tunda nice na kawo shi nace ina son shi, ashe don haka ya faru uziri ya dace ayi min ba fushi da b'acin rai ba." Ta fada tana kuka sannan ta cigaba da cewa. "Na amshi kuskure na." Juyawa Zaytoonah tayi ta koma gareta, ta zauna tana me dora mata Baby Zahra a saman cinyarta."Ammy ki daina kuka, don Allah." Ta fada tana jan hancinta. "Dole nayi kuka, yar uwarki ta rasu baku gana ba, mahaifinku ma haka duk laifina ne."

"Bana jin Didi ta rasu, baffanmu kan jikina ya bani baya raye, amma Didi fa ina jinta a raina sosai da sosai."
```

Rungume su tayi tana faɗin, "duk inda take, tana cikin kariyar Ubangiji, Allah zai shiga lamarinta a ko ina take."

Wato idan har aka samu irin ahalin Sheikh Aliyu Wodabbe, zai yi wahala wata fitina ta sauko ba tare da an samu warakar shi ba, tun da suka ji labarin mutuwar Baban Zaytoonah, hankalin kowa ya tashi haka yasa Zaytoonah rikice musu, tare da nisanta kanta da Mahaifinta, duk da kowa yaso mata bayani amma taki fahimta. Haka yasa taje har gaban Sheikh Aliyu Wodabbe, ta ce ita ya mata lamuni zata bar gidan ta tafi neman danginta da suka rage a duniya. Shine ya kira Aminatu da Yafendo da Sumeye, Zaytoonah tana zaune a wurin.

"Na kira ku ne, domin Zaytoon tana son ta tafi neman ahalinta."

Da sauri Ammynta ta d'ago kai tana kallonta cikin wani irin rawan jiki tace mata. "Ba dai tafiya zaki yi ki bar ni ba?" Girgiza kai tayi tana kara faɗin. "Kiyi hakuri nayi laifi wallahi nayi laifi, nasan nayi laifi tunda kike shirin gudu na, don Allah kiyi hakuri. Amma kada ki tafi kiyi hakuri na had'aki da Manzon Allah Sallallahu alaihi Wasallama."

Kwalla ne masu zafi suka shiga zubo mata, tana kallon yadda mahaifiyarta take kuka da dukkanin zuciyarta, mikewa tayi ta bar wurin, haka yasa Yafendo bin ta dakin. Kuka ta saka tana kara jin zafin Ammyn har Hamma tasa ya roke ta, duk shirin da suke da Hamma sai da ta mishi rashin mutunci, amma yanzu ta zauna tana mata wani kuka mara hujja. "Idan kin shirya ki gaya min, akwai kanwata da muke Yayan mata a Yola, tana aure a can idan kika tafi zasu tayaki niman sauran danginki. Amma kafin nan bari na gaya miki wani abu. Da ace Allah bai nufa an ga Aminatu da wuri ba, ta wuce wani wurin da lalurar gushewar hankali ga kuma cikinki, tow kuwa ba makawa bamu san abinda zai faru ba, imma da tun lokacin kin mutu ke da ita, ki godewa Allah tunda har kika taso an tab'a miki gorin yar mahaukaciya? Tow hauka tuburan Aminatu tayi, da ta warke kuwa ko da wasa bata kaunar ka tambaye ta, bayanta ki godewa Allah da mari kika sha a duk lokacin da kika tambayi bayanta. Saka ran mahaifinki zai biyo sawunta yasa Malam dakatar da ita har na tsawon shekaru Domin tsakaninki da yar Uwarki, tazarar me yawa ce. Ba zance kiyi hakuri ba domin an zalunce ki, amma a matsayina na mahaifiyar Aminatu dole na kare mutuncinta da rayuwarta, tana kuka ne don ta rasa abubuwa masu muhimmanci a rayuwarta, sannan tana shirin rasa ki a karo na uku. Ke baki jin tsoron kukan da take yi wata rana yarki ta saka ki?"

Da sauri ta d'ago kai tana kallon yafendo bakinta yana rawa ta ce. "Yafendo!" "Mahaifiya ce ita, bai dace a saka ta kuka har haka ba, hakan zai tab'a rayuwarta da lafiyarta."

Daga haka ta bar dakin, har ta kai bakin kofar ta ce. "Ba fata nayi miki ba, kina da damar yin fushi da kuka da fada, da ihu amma ki sani itama an mata uzuri domin ba laifinta ba ne, haka Allah ya shirya lamarinshi da ace mutum yasan abinda goben shi zata bayar da zai gyara wanda yake ganin ya dace da shi, ki yi hakuri na baki hakuri ne a matsayina na mahaifiyar Aminatu. Ba a matsayin kakarki ba ki dauka a wani wurin aka miki kuskure to ina mai kara baki hakuri." Daga haka ta bar dakin, tabbas Yafendo ta tsayawa yarta at least ta nunawa Jikarta itama tana son Yarta, ba zata sake damuwa ya cutar mata da Aminatu ba, kamar yadda tana ji tana gani aka hanata akan Yar uwar Aminatu.

Wannan abubuwan yasa Zaytoonah, hakuri da mata uzuri, amma bakiɗaya bata jin dadin rayuwarta. "Ammyn ina son tafiya Nijar na cigaba da karatu a can!" Ta fada tana kallon Ammynta. "Indai haka zai saka ki farinciki na amince, zan kira Dadah na gaya mata, sai ki tafi can Allah yasa haka shine mafi alkhairi."

"Amin Ammyna, in sha Allah zan binciko mana inda Didi take." Inji Zaytoonah. "A'a kada ki wahalar da kanki, in sha Allah zata zo gare mu." Cikin shashekar kuka ta ce mata. "Muma dole mu neme ta, ba zamu jira sai tazo ba." "Hmmm kin dai ce tana raye ne, amma yadda nasan rigimar su da mutanen garin nan zai yi wahala idan bata mutu ba."

"Wallahi tana raye tana raye na rantse da Allah." Haka suka yi ta kuka a tsakaninsu. Har bayan an sha ruwa Malam ya kirasu ya musu nasiha da addu'ar idan Zahra tana raye Allah ya bayyanata, idan ta mutu Allah ya mata rahama."

Haka suka yi ta addu'a, sannan suka tashi. Duk da dai zuciyoyinsu babu dad'i amma kuma haka bai hana su sakin ransu ba, domin kuwa kowa yana jin ciwon abin da ya faru. Musamman Ammyn gani take kamar da wata a kasa, haka kawai ba zata samu lalurar gushewar hankali ba, sannan daga baya, taji kamar zata mutu idan aka tambaye ta, me ya faru ko ina mijinta yake.

Wannan abin ya sakata cikin damuwa, bayan sunyi sahur, Ta kira Yayarta ta gaya mata, cikin farinciki da murna ta ce tazo tana bukatar abokiyar hira. Sannan ta gaya mata dalilin zuwan Zaytoonah karatu zata yi, Itama ta karfafa mata gwiwar haka, dake Allah ya taimaka dukkansu suna da abun yi domin itama Aminatu koyarwa take a nan Jami'ar Cameroon.

- South Africa. Sai da aka kai ruwa rana, kafin suka bashi hutu tun zuwan shi bai matsa ko nan da can ba, yana makale da aikinsa, sannan da ya nemi hutu kin bashi suka yi, sai da ya koma ya rubuta musu ajiye aiki. Da shugabansu ya gani a fusace ya yaga takardar. "kana da hankali kuwa? Kasan yadda muke alfahari da kai da zaka so ajiye aikinka?" Kusan soja da bala'i da masifa da ihu, shi dai bai ce kome ba yayi shiru yana sauraren Commander ɗinsu. Har ya gama sannan ya dauko wata takarda, ya rubuta mishi an bashi hutun sati biyu. "Sir mahaifiyata ba zata fahimce ni ba, sannan ina son a bani koda wata daya ne, nasan is too hard na samu wannan kwanakin. Amma idan na ajiye aikin zata fahimci ita din abar girmamawa ce." Dake Commander din Muslimi ne kuma dan arewancin Nijeriya, murmushi yayi ya ce mishi. "Abdul Majid Mamman Ba'are, nasan waye kai Chairman guda da yake gudun matsayinsa. Sai dai an haife ka ne domin ka zama soja, ba wai kayi aiki da sojoji ba, zan baka wata gudan amma ka sani can kujerar da kake gudu, zata bibiye ka a duk inda kake matukar kana raye. Kasa yayi da kanshi yana kallon takalminshi da bai daura igiyar ba, "mahaifiyarka tana son ka rike matsayinka ne, domin hankalinta zai fi kwanciya. Sai dai ba abu me sauki bane a wurinka. Kayi imani da hawa saman teku domin aikinka, ka dauki kamfanin a matsayin teku ne, ta gaya min kome akanka da kuma kamfanoninku."

Bai ce mishi uffan ba, yasan halin shi sarai ko abokan aikinshi ba karamin mita suke akan wannan halin nashi na rashin magana ba, har kawo ƙararshi suke amma babu abinda ya sauya, wani irin murdadden hali ne dashi, yaki sabo da kowa aikin shi kawai yake baya kula kowa baya harka da kowa baya shiga harkar kowa, ina ka fito aiki ina zaka aiki. Haka yasa ko irin yan matan nan babu me shiga sabgar shi, domin sun tabbatar da cewa shi din ba daidai ba ne, kuma bai da lokacin mace.

"Shi kenan Allah ya tsare, ka dawo lafiya."

Salute yayi sannan ya dauki takardar, ya nufi hanyar waje, yana kallon agogon hannunshi. Sam bai dauki rayuwarshi da zafi ko fadi ba, asalima ya ajiye kanshi inda yake ganin nan Allah ya ajiye shi, bai tab'a nuna fad'in rai ko kuma nuna cewa shi din wani ba ne, yasan yana da dukiya me yawan gaske, amma haka bai tab'a damunshi ba, asalima shi yafi saka kanshi a matsayin kananan mutanen da suka taso cikin talauci da wahalar rayuwa.

Wannan yasa baya jin girman kai ko wani abu, meye a rayuwar da wata rana mutuwa zaka yi, sannan magana ce babu wanda ya isa saka.shi, shi bai saka kowa lallai dole a kula shi ba, kuma baya jin lallai dole sai yayi magana duk wanda yaji haushi to ya daukarwa kanshi dala ba gammo ne.

Daga headquarter ɗinsu, airport ya wuce dama da shirinsa ya fito, ba zai sake a kai azumi na biyar bai sha ruwa a gaban Hajiya ba, domin yana tsoron Allah yana tsoron fushin Hajiya, don haka yana zuwa bai samu jirgin nijar ba, sai na Algers ya samu, bai wani b'ata lokaci ba ya biya yana jin yana isa nan da awa biyu, zai samu na nijar tunda yasan basu rabuwa da masu shiga da fita a kasar, haka yasa shi bawa zuciyarshi hakan.

Bayan wani lokaci jirginsu ya tashi, bayan awa biyu suka sauka a Algers, yana zaune a inda zasu jira jirgin nijar. Wata Kyakyawar budurwa, tazo ta zauna a wurin murya kasa-kasa take faɗin. "Ni zanzo ne kawai amma ba wai don ina da ra'ayin haka ba, don bana kaunar abinda ya haɗa ni da BA'ARE family." Da wutsiyar idanu ya kalleta. Tab'e baki yayi tare da kauda kanshi, ashe akwai masu tsanar BA'ARE family ba shi daya ba ne. Kiran fasinjoji nijar yasa suka mike baki daya, wani abin mamaki shine sit dinsu kusan wuri guda, zama tayi tana faɗin. "Mame sai nazo, ni dai bana son zuwa kika kira ni, Allah ya gani ba zan sauka ba, meye a cikin wannan gidn ban da masifa da hakkin Hajiyarsu Aryan kada ki biyewa Appa domin zai kai ki ya baro ki ne, nafiki sanin waye shi. "

Ta kashe wayar tana jan tsaki, kauda kai yayi tare da saka facemask ɗinshi, baya jin zai iya hayaniyar yarinyar nan, ban da yasayi kujerar da ya koma VIP. Wuraren biyar da rabi suka isa nijar, bayan sun isa ne suka yi ta fitowa. Aryan da yazo daukar Majid din ya hangota. "Maisarah!" Tawowa wurinshi tayi, tana murmushi. "Ya Aryan kazo dauka ta ne?" Watsa mata harara yayi yana faɗin. "Hammayo dai!" Ya nuna mata shi, da yake bayanta. A hankali ta juya tana kallonshi baki sake. "Dama tare muka zauna shine bai nuna min ya sanni ba?"

Murmushi Aryan yayi yana amsar jakar Majid. "Barka da hanya, muje na ajiye ku baki daya." Haka ta fito tana jan jakarta, shi sikagon ana jan nashi, yana isa wurin motar ya bude baya ya shiga, tsayawa tayi tana kallonshi. "Shiga gaba!" Haka ta shiga tana mamakin duk gaishe shi da Aryan yayi bai amsa ba, sai dai buga bayan shi da yayi, wannan irin lifestyle din yana matukar burgeta, ta madubin gefenta take kallonshi, ya wani zauna like king yayi crossing leg, hannunshi dukkan biyu ya baza su kamar wani wanda yake kan karagar mulki. He look like king . "Ya Aryan!" Ta kira sunanshi a hankali, "hmm!" Ya ce mata. "Amma Hammayo yana da nasaba da sarauta ko?" Gyara zaman madubin gaban yayi yana kallon Majid din da yayi wanann zaman, murmushi yayi yana faɗin. "Me kika gani Maisah?"

"Hmm! Zamanshi da halinshi."

"Masarautar Agadaz, itace babban tushen nasabarsa " duk abinda suke fada yana jin su, kawai amsawa ce bai da niyya kuma ba zai amsar ba koda yana da niyya. Shi yarinyar ta cika rawan kai, shi yasa ba zai magana ba.

Haka sukayi ta hirarsu tana kara kallonshi a madubin gefenta, tana jin wani abu yana cika mata kai da ruhinta, a karon farko da ta haɗu da irin namijin da take fata, ita kan zuwa nijar ya mata rana.. har suka isa Aryan ya sauketa a gidansu, sannan ya wuce da Majid. "Hammayo kayi kasuwa wallahi, kaga har yanzu bata shiga gida ba, gaskiya wannan karon zamu sha biki bayan sallah."

Bai ce mishi uffan ba, suka shiga cikin gidan su, ajiyar zuciya ya sauke tare da kai hannu ya bude kofar, ya saka kafarshi ya fito a hankali, yana jin kamar bashi ba. Haka ya nufi cikin gidan bayan ya cire facemask, ana gaishe shi. Amsawa yake da kai kawai. Har ya isa falon Hajiya tana zaune Amaan yana kwance a saman Kujeran, dama ga azumi ga rashin lafiya da yake boye musu. Cikin kulawa da wani irin idanu Majid ya zuba mishi ido yana karantar shi, tabbas Amaan bai da lafiya domin har fatarshi tayi duhu, amma sanin ba wani shiri suke ba, yasa shi yin fuskar shanu ya wuce gaban hajiya yana faɗin. "Gani nan nazo Hajiya."

"Kaje ka sauke ibadar da yake kanka." Mikewa yayi ya wuce dakinshi, bai fito ba sai da aka fara kiran sallah ya sauko a hankali, ya samu duk sun hadu a falon ana addu'a, zama yayi aka yi da shi sannan ya dauki dabino da ruwan dumi ya sha, sannan ya koma gefe yana sha yana kallon Amaan da yake rike cikinshi. Suna gamawa suka wuce masallaci, Hajiya tayi nata sallah a gida, bayan sun fito suka dawo aka cigaba da buda baki. "Amaan baka da lafiya ne?" Da sauri ya kalli Majid. "Eh amma da sauki domin anyi min aikin basir ne."

"Allah ya baka lafiya."

"Amin ai da sauki yanzu." Inji Hajiya, "fatarshi tayi duhu kai ma ka gani ko Hamma?" Hadiye yawu Majid yayi yana diban farfesu. "Duhu sosai." Ya fada yana cigaba da cin abincinsa. "Ba fa kome lafiya ta lau, bana jin kome wallahi."."Eh ku ci abinci kawai."

Haka suka cigaba da cin abincin, har suka gama sannan Amaan ya wuce dakinshi da yake falon Hajiya. Da idanu Majid ya bishi. "Ai kusan wata biyu kenan da samun matsala da Matarshi, ta kwashe Yaranta."
"Allah ya kyauta." Iya abin da ya iya faɗa kenan domin ba zai iya magana ba, sai da yaci abinci ya koshi, suka tafi sallah Isha da taraweeh, sannan suka dawo aka zauna ana hira. Ya lura da Amaan din da yake yan zabure zabure, yana kallon wayarshi. A hankali ya dauke kai. Kamar bai ganshi ba.

Shima latsa wayarshi yake. "Assalamu alaikum!" "Wa'alaikimun Salam, Maisah kece a gari?" Murmushi tayi tana faɗin. "Hjiya tare da Hamma muka zo ai!" Juyawa tayi tana kallonsu. "Kin ga basu gaya min ba." Shigowa tayi ta gaishe su sannan ta zubawa Majid idanu da yake ta latse-latse waya kamar baya wurin. "Hajiya kin sha ruwa lafiya?"
"Lafiya lau, da fatan kin iso lafiya."
"Alhamdulillahi," a hankali ta Ciro wata yar ƙaramar camera recorder. Hajiya tuntuni ina tason na baki wannan abin amma Allah bai nufa ba, don Allah ki ajiye a wurinki. Wata rana zai miki amfani, amma yanzu ba zai miki amfani ba, ki dai ajiye kawai."

"Tow maisah." Sai lokacin ya d'ago kai yana kallonta. "Kun leka Nana kuwa?" Mikewa yayi ya nufi hanyar sama, Aryan ma ya nufi hanyar waje. "Allah ya shirye ku?" "Amin Ya Allah!" Inji Maisarah. "Ke zomu je na kai ki gida."

"Tow!" Har zata mike ta rike hannun Hajiya. "Koda kin ji labarin wani abu ya biyo baya, tow ki sani saboda wannan Camerar ce, don Allah ki adana shi da kyau."

Ajiyar zuciya Hajiya ta sauke tana faɗin. "In sha Allah babu abinda zai faru."
Haka ta mata sallama ta bar falon, ita kuma Hajiya ta bi Majid dakinshi, ta kai mishi, tare da cewa. "Yarinyar ba yau take nuna min da wani abu ba, rayuwarta na cikin hatsari a yau ba gobe ba, nake son ka amince ka aureta. A daren nan ba sai gobe ba.....
#Mai_Dambu
[3/9, 6:39 PM] Cutie cutie pie: *BAƘIN HAURE....□□*

{Greed for Money is the roots of all evils□}
Arewabooks:maidambu41
Wattpad:Mai_Dambu
Mallakar:Mai_Dambu
032

Sakin baki yayi yana kallonta kafin ya tattaro nutsuwarshi da abin da zai gaya mata Hajiya ta bar dakin bakiɗaya yanzu shi me zai cewa Hajiya? fisabilillahi Hajiya bata mishi gentle ba, shi fa auren familyn Ba'are gani yake kamar shiga lahira ne babu guziri, yo da guzirin ma ya aka kare balle ka shiga babu abin da zaka kare kanka. Yasan wani tarko ne ba wani abu ba ne,uban waye zai kashe ta a wannan lokacin da kowa yake ibada. Gyara kwanciyarshi yayi kamar ba zai tashi ba, can kuma ya mike tare da sauka ya saka takalman ya nufi hanyar waje. A falo ya samu Hajiya tana waya. Fita yayi yana kallon yadda garin yake, hannunshi sakale a cikin aljuhun wandonshi. A hanyar shi ta shiga gidan ya had'u da Aryan da yake dawowa daga rakiyarta. "Ina zaka Hammayo?" Sosa wuyar shi yayi yana kallon Aryan ɗin. "A irin wannan yanayin me yasa baka wuce gidanka ba?"

"Na raka maisarah gida ne, domin wurin ya cika duhu kuma mace ce ta dauki kasadar fita a wannan lokacin. Tana bukatar wanda zai rakata gida." "Hmm!" Ya faɗa suka wuce zuwa gida, zama suka yi a harabar gidan. "Hamma kamar akwai abinda yake damunka?" Girgiza kai yayi, yana kallon sama. "Ban san me yasa hajiya take jan wasu abubuwan ba? Nafi Hajiya son nayi aure, amma kuma a haka na lura kamar bata yarda bani da lafiya ba ne, idan na auri Maisarah me zan mata? Sannan abin da nake boyewa zata iya cutuwa idan tasan halin da nake ciki." Ya fadi haka a hankali, shi kanshi Aryan sai yake ganin kamar sa'a yayi da Hamman shi yake gaya mishi irin wannan al'amarin, wanda kowa yasan halinshi da boye abinda yake ranshi.

"Wayyo Allah taimako!" Suka ji Ihun Maman Maisarah, kallon juna suka yi, kafin su shiga Mamarta suka samu tana ihu. Shiga cikin gidan suka yi har da ita, dakin yarinyar ta nuna musu. Kur suka mata, aka rasa me bakin magana. "Don Allah ku taimaka min, kada ta mutu." Da sauri Aryan ya wuce kitchen dinsu, ya dauko wuka ya yanke igiyar da ta daure wuyarta da shi. Fita da ita aka yi, a lokacin su Nana sun iso. "Lafiya?" Yanzu Aryan ya rakota muka gaisa, da yake taje gaida Hajiya Sa'adatu, shine bayan tafiyarshi, naga an kirata a wayarta, ta dauka ban san me aka gaya mata ba, amma naga ta fita zuwa tsakar gida, daga nan ban bi ta kanta ba, ashe igiyar shanya ta dauko ta rataye kanta."

"Kun yi ja'ira yar banza, waye ya gaya mata mutuwa shine mafita, me ma aka mata da zata kashe kanta, bayan ni ban mutu ba, ku kaita asibiti." Kallon Aryan Majid yayi, cikin wani irin yanayi da baya son ya zarge shi. Amma sai ya dauke kai kamar bai damu ba, haka suka tafi asibiti suna zuwa aka karbesu kusan kwana suka yi akanta, kafin wurin karfe biyar na Asuba likitocin suka fito daga cikin dakin da take. "Ya take ciki?" "Alhamdulillahi zamu ce, sai dai bakiɗaya ko zata rayu bai zama dole ta mori kanta ba."

"Akan me?"

"Saboda kashin da yake haɗe da bayanta, da spinal code dinta ya karye." "Innalillahi'wa'inna'ilaihi'raji'un, me yasa na kiraki? Kin rayu cikin firgici da tsoron kada a kashe ki, yau gashi ke baki mutu ba. Ke baki rayu ba." Mamanta ta faɗa cikin kuka da danasanin abinda ya faru, domin da tasan haka zai faru ba zata so Maisarah tazo ba, haka yasa ta cigaba da kukanta har gari ya waye, wannan faruwar lamarin ya kara saka tashin hankali a zuciyar mutane, musamman yan cikin gidan. Abin da yafi hurting ran mutane, shi ne a daren Aryan ne ya kaita gida, haka yasa baki daya ya shiga yanayin zargi da tuhuma. Karfin imani da tawali'u yasa Aryan bai haukace ba, amma sai da ta kai ya zauna yana kuka kamar karamin yaro a gaban Hajiya. Shi kanshi Majid tausayin Aryan din yaƙe ji amma baya son maganar gaskiya shi daya ne abin zargi a cikin gidan. Domin shine ya ganta na karshe kafin faruwar lamarin. Amma kuma maganar gaskiya bazasu ce shi ya aikata ba, sannan ba zasu ce bashi ba ne. Dole bincike ne zai tabbatar da haka.

Ba karamar girgiza Alhaji Kamilu yayi ba, domin bai tab'a kawowa hakan zai faru ba. Sai dai da Hajiya tayi mishi maganar binciken abin da ya faru. "Wani bincike kuma? Babu wani binciken da za'a yi, domin nasan ƙarshe a cikin gidan nan aka samu wanda yayi wannan aika-aikan."

"Ai gara a bincikan hakan zai saka mu daina zargin Aryan domin kowa yaji ta hadu da Aryan abin da yake ayyanawa a ranshi akwai wani kudiri ko wani abu na daban."

"Na sani, sai dai hakan ba zai haifar mana da d'a mai ido ba, Allah ya bata lafiya kawai." Ya fada yana kara jin wani irin d'aci a ranshi domin Allah ya gani yaji zafin al'amarin, sannan duk wanda yayi wannan aika-aikan yasan abinda yake yi, shi yasa yayi amfani da rakota da Aryan yayi da zuwanta gidan Hajiya.

Ajiyar zuciya Hajiya ta sauke, sannan ta ce mishi. "Shi kenan, tunda baka son binciken Allah ya bata lafiya. " Ta fada tana mikewa, tare da leka dakin Maisarah da take cikin Unconscious. *Idan wani abu ya fito bayan kawo miki wannan Cameran tow tabbas abin da yake ciki babban al'amari.*

Wani irin zufa ne yake zubowa Hajiya, duk abinda yarinyar nan ta gani ba karamin al'amari ba ne, haka yasa ta nufi gida zuciyarta na wani irin zillo.

***

Zahra

A matukar gajiye na dawo, dake Allah ya taimake ni Amirah sugrah tana wurinsu, ina shigowa aka kawo ta, yarinyar nan taki zama, "kuje da ita kawai, na gaji gajiya zata kara min." "Tow Tante!" Suka fita da ita, ina kwance a wurin har wurin biyar, tashi nayi na nufi kitchen. Dama tun safe na surfa wake tare da dafa kwai, wanke-wanke na shiga yi, ina gamawa na zuba mishi kayan miya. Na zauna na markad'a shi. Ina

tsaye har yayi laushi na juye ina nazarin nayi ta manja ko mangyad'a. Karshe haka nayi ta mangyad'a, na zuba kwai da kifi. Sannan na duba geron da na bawa Barakatu ta surfa min, na dauka na wanke shi tass. Sannan na zuba ruwa na watsa gefen. Bude frij nayi, na dauko yogot na ciro na ajiye. Na gyara alala ta na ɗora bisa wuta, sannan na koma daki nayi wanka. Na saka kayan shan iska, na fito nazo na dama kunun garin kunun da ruwan tsamiya na.

Har kunun yayi min yadda nake so, na ajiye shi na daura shinkafa jallof, na cigaba da aiki. Ina haɗawa na dawo na kunna tv, na fara kallon tafsirin Malam Awwal Albani Zaria. Gyara kwanciya nayi ina kallon, sai da naji kamshin alalen ya cika min hanci naje na sauke, kusan uku suka fashe. Haka na ajiye na gama haɗa kome na fito dashi a faranti. Ina ajiyewa ana kiran sallah, komawa daki nayi na dauko jakata na tuna akwai fruit da na sayo. Haka na fito da dabino naci, na sha ruwa. Ban tashi a wurin ba, suka dawo min da Amirah, tayi barci kwantar da ita nayi na mika musu nasu abincin. Ina faɗin, "ku gaida min Mamanku."
"Mun gode sosai!"
.... Bayan nayi sallar Magariba da Isha da su tarawee,, na kwanta a falon. Har na fara barci sama sama, naji kukan Amirah dakin nashiga na cire mata kayan jikinta, na mata wanka na sauya mata na barci. Sannan na dawo dakin bayan nayi wanka da alola, na kwanta barci me nauyi ya ɗauke ni. Washe gari na tashi da wuri da yake Muna da test. Da wuri na wuce ban dawo ba, sai karfe biyu a gida nayi sallah.

Haka aka azumi yayi ta tafiya, rayuwar da dadi babu dad'i, ban rasa ci ko sha ba. Amma sai nake ganin kamar daular tayi min yawa, ina matuƙar son da ko wani ne a cikin dangina na gansu, su dandani dadin da nake ciki sai dai.nasan kamar yadda Allah ya halicci wuta da ruwa basu gamuwa, haka nasan matukar muka hadu sai mun yi abin kunya, haka yasa ta wani bangaren nake ganin kamar nauyi aka sauke min akan Addah, gefe guda kuma ina jin kamar ban kyauta ba, ba dadi mutuwar mutanen da kasani. Amma kuma mutuwar Addah shine samun sukuni na da Amirah.

Kwanciyar hankali da nutsuwa ya shige ni, sannan wani abin da ya kara bani mamaki ashe tun fil azal ina da kalar fata mai kyau, domin kuwa nayi fesh kamar bani ba. A makaranta ma gani na da Amirah yasa mutane dayawa sun shafa min lafiya, domin daga malamai har dalibai farkon zuwana sun fara matsa min da gaisuwa. Ni kuma na iya dauke kai bana kula kowa harkar gabana ta ishe ni.

Saura kwanaki uku mu samu hutu, wani malami ba a department ɗinmu yake ba, amma bakiɗaya idanunshi yana kaina duk da bana son kula shi. Amma haka yake saka a kirani, Ni kuwa idan naje bana magana sai na tsaya mishi a kai.

Yau ban shigo ba sai karfe goma, ina shiga department ɗinmu na ganshi dauke kai nayi kamar ban ganshi ba, koda na kusan wucewa ya ce min. "Zahra Buba!" Juyawa nayi nace mishi."Ni!" Tasowa yayi daga inda yake zaune ya ce min."Bayan ke akwai wata Zahra Buba ce?" Share shi nayi naki magana. "Ok! Dama akan yanayin gari ne ya kike?" "Bashi ya kawo ni ba." Na fada ina karawa gaba. "Ai naji labarin baki da miji zaman kanki kike." "Ina baka shawara da ka kiyaye kanka da bin rayuwar wasu, bin rayuwata kamar wasa da wuta ce."
"Ai na zata wasa da mutuwa ce."
Murmushi nayi na ce mishi. "Ban yi wannan wayewar ba, amma ka tsaya a matsayinka."
"Ok zaki gani, wallahi matukar kika yi wasa sai na baki mamaki."
"Ina mai baka shawara kada ka bani mamaki, kayi harkar gabanka nayi tawa."
"Mtsew dani kike zancen."
Ban kula shi ba, na wuce aji abina na gama abinda nake muka fito. Bayan nan aka sanar da mu dawowa makaranta sallah da kwana biyar.

Haka muka bar makarantar, zuciya ta tayi min dad'i. Ba karamin dadi ba fa. A wurin ajiye motoci na ganshi, sai da gabana ya fadi. Sai da na isa jikin motar ya wani fisgo ni. Fitowa Badar yayi ya zagayo ban san me yayi mishi ba, sai dai naga ya sake

ni da sauri. "Madame shiga gani nan zuwa." Shiga motar nayi babu musu. "Kayi hankali ba kowane abinci ake ci don koshi ba, akwai abincin da a madadin yayi maka dad'i, guba ce domin kashe ka zai yi. Nasan labarin kowa a cikin makarantar nan. Hmmm kace me?"
"Ban ce kome ba!"
"Yayi kyau, ko a hanya ka ganta ka kiyaye abin da zai saka ku had'a idanu. Ni nayi maka da sauki idan da wani ne tuni ya tashi kanka." Daga haka ya juya wurin motar ya shiga ya bar shi a nan tsaye, nima nayi mamakin me yasa yayi laushi lokaci guda, haka muka bar makarantar. Alhamdulillahi Yazid ya kare min mutuncina da kimata, yadda yayi alƙawarin. Abin ya tab'a ni da yasani kuka ban sani ba, baya raye amma babu wanda ya isa ya min barazana a kyale shi. "Meye alakarka da Yazid?"
Juyawa yayi ya kalle ni, kafin ya cigaba da tuki. "Sultan zaki ce, idan ba Sultan ba. Ba zan iya baki amsar tambayarki ba."
Ya fada yana cigaba da tukin, "Sultan kuma?" Na kuma tambayarshi, bai bani amsar ba domin har mun iso gidan. "Sultan! Waye Sultan Yazid?" Murmushi yayi sannan ya ce. "Mun iso gidanki.....

Hajiya ga kaya nan Masha Allah, Available da saukin price
Huluna da Mayafai,na manya da na yara sai Wanda ranku yakeso gasunan kala kala, Hajiya muna dasu ba iya hulana da Mayafai ba, har da shaddodi na fitar sallah, Hajiya domin hutar dake da fitar dake kunya mun tanadi yadda ba zaku sha wahalar yawo kasuwa a cikin azumi ba, don haka kafin kishiyarki tazo ta sata au 😂😂 kafin kishiyarki tazo ta saya tayiwa mijinku shakara gara kizo ki sata au 😁😂 baki ya saba gara kizo ki saya, barauniyar gida, kai Sarauniyar gida 😂😂 atow kayanmu na Uwayen gida da Amare ne```
TUNTUBi WANNAN NUMBER 08130269641
Leshi
ATAMFOFI
SHADDODI
Materials
Kayan yara
Veils
Huluna....etc
#Mai_Dambu...

BAƘIN HAURE....😂😂

{Greed for Money is the roots of all evils😂}
Arewabooks:maidambu41
Wattpad:Mai_Dambu
Mallakar:Mai_Dambu

Sorry Dearest yau babu editing 😂❤.
033
Jikina a matuƙar mace na fito daga motar, "Waye shi?" "D'a ne ga sarki Hamir Julaibi na kasar Algeria!" Bakina na rufe, jikina ya dauki wani irin rawa. "Me?" "Na gaya miki gaskiya." Juyawa nayi tare da barin motar, ina shiga falon na zube kamar wata matacciya, domin kuwa Yazid yana kashe ni da Mamaki,idan nace ban jijiga ba kayi karya. Ban san lokacin da kuka ya kwace min ba, tashi nayi da gudu zuwa dakina na shiga banɗaki na bude ruwa a kaina, zama nayi can gefen can banɗaki. Yadda na ke kuka ni kaina ban san akan me yasa nake kuka ba? Kukan me nake yi? Kukan ya boye min waye shi? Ya cutar dani ta hanyar boye min kanshi. Ban iya tsinanawa kaina kome ba, har aka sha ruwa tea nasha, sai kunu da kosai da na sha, da dare yayi na ta

fasa indomi da kwai, na koma gefe ina ci ina hawaye. Da asuba kuwa sahur nayi da tea kawai.

Washi gari wuni nayi kamar mara lafiya, ban kara wani walwala ba domin na sha mamaki.

***

Tunda aka kawo shi asibitin, suke ta fama da lafiyarshi. Domin hankalin kowa ya tashi yadda yake duhu da fama da rama. Shafa kanshi Aryan yayi cikin tausayi. "Amaan" bude ido yayi yana kallon Aryan ɗin da yake kara shafa kanshi. "Me ke damunka?" Yana son magana amma babu bakin magana, haka kawai aka same shi a tsakar dakinshi yashe kamar matacce, haka yasa suka kwaso shi zuwa asibiti sai dai ko da suka zo an bincikar lafiyarshi ne. Tunda Majid ya ganshi yasan bai da lafiya boyewa yake, a binciken da suke ne aka gano aikin da aka mishi na cikin, Jamilah ta fito daga Lab rike da wasu takardun tana faɗin. "Hamma babu aikin basir. Akwai abin da Amaan yake boye muku wallahi." Amsar takardun Majid yayi suka wuce office dinta, shiru tayi tana kallon shi kafin ta bude baki zata yi magana ya ce mata. "Allah ya kyauta meye a cikin test din jininshi?" "Sakamakon bai fito ba" ta faɗa a hankali tana wasa da pen din hannunta. A nutse yake kara kallon takardun hannunshi, yana jin kamar ya fasa ihu ne ko kuka. Mikewa yayi ya nufi dakin Amaan. Yana shiga ya samu Aryan yana rike da hannun Amaan din. Shi kanshi bai san irin kallon da yakewa Amaan din ba, shin tausayi ne ko takaici ne? Domin bai kawo lalacewar shi zata kawo har haka ba. Dakyar ya bude baki ya ce mishi. "Tun yaushe ka fara...." Turo kofar da aka yi yasa shi shiru ya zubawa Hajiya idanu, "Majid meke damun Amaan din ne?" "Ciwon ciki ne, tare da borin jini!"

"Ban gane ba." Hajiya ta fada a rikice, "Hajiya zaki gane, bari a gama bincike." Inji Aryan yana kallon Amaan, shigowar Jamilah yasa Majid suka kara fita, nan suka kara rikicewa kamar zasu tashi sama, domin ciwon sanyi ya shige shi sannan jikinshi zai iya daukar kowani mahaukacin ciwo matukar ba a kula ba. Haka yasa bakiɗaya Majid ya shiga wani irin d'imuwa da tashin hankali.

Duk Familyn Ba'are babu wanda zai zo ba, domin Amaan bai da wani matsala da su, dake wawa ne yana shiri da kowa, haka yasa aka yi ta zuwa gaishe shi. Bakiɗaya ruwan kan Majid ya kone, taya zai gayawa Hajiya Amaan luwadi yake bai san da wata kalamai zai iya gaya mata ba, kallon Jamilah yayi yana faɗin. "Kada ki sake Hajiya ta ji labarin halin da yake ciki. Ki bari zan ji da kome." Numfashi ta ja tana kallon shi kafin ta daure ta ce mishi. "Hamma" "kada ki damu zamu yi magana da Aryan." Ya furta tana lashe bakinshi da ta bushe. A hankali ya a nufi hanyar waje, yana nazarin abinda zai fadawa Aryan domin bakiɗaya ya tattara damuwar ya azawa kanshi. Don yasan matuƙar Aryan da Hajiya taji sai zuciyarta ta kusan bugawa, ya kuma san idan aka gayawa Aryan kamar an gayawa Hajiya ce.

Murmushi Hajiya Tani tayi tana kallon, videon Amaan tana faɗin. "Wannan lokacin ya dace na tashi kan Sa'ah." Shan ruwa da yake gaban shi Sajid yayi yana faɗin. "Hajiya Sa'adatu ta kare mata, dole ta biya abin da ta saya."

Suka fada suna dariya, "Meye tsakaninka da Afiyyah?" Ware idanu yayi yana fadin. "Ba wani abu fa, chill out muke da ita kuma nasan an dauke ta aiki a kamfanin Ba'are."

"Lallai kwanyarka bata ja Sajjid, taya zaka fara wannan aikin." D'aga kwalba yayi yana faɗin. "Bana kuskuren harkalla, duk abin zan yi Hajiya da tsari a cikinshi. Yarinyar ita ce Bingo dina, tana sona ina bata abinda take so. Sannan zan san yadda zata matsa jikin Chairman din kamfanin yadda zan basu mamaki."

Murmushi Tani tayi tana faɗin. "Yaro yaro, ni na gama shirina saura ja jira tashin bom."

Ta fada tana dariya, tare da barin falon. Da sauri ya bi bayanta yana faɗin. "Hajiyata me kika shirya?" "Lokacin da zai faru zan gaya maka, domin ni kome nawa da tsari bana faɗar tsarina kada a samu matsala. " Hura iskar bakinshi yayi yana faɗin. "Ni dai ki gaya min shirinki, domin kuwa ba mamaki na tayaki."

Tsayawa tayi ta kalle ta kirashi da yatsu biyu, yana matsowa ta rike kunnenshi ta gaya mishi wata magana, murmushi ya sake. "Hajiya wacce irin Shaidaniyar tunani ne haka?" jan kunnen shi tayi tana faɗin. "Ba zan tab'a yarda wani ya san wacece ni sannan, ya dawo ya soke ni a baya ba, sun wanda ya sake ya ci amanata sai na mai da rayuwarshi abin kwatance yadda kowa sai yaso yaji me mutum yayi min haka."

"A'a sam haka ba zai taba faruwa ba, ai kowa ya kwana lafiya shi yaso."

Hajiya kam hankalinta yana kan Amaan, bakiɗayansu babu wanda yake zaune, azumin ma suna yi ne amma bakiɗaya hankalinsu yana can. A ranar da ya cika sati daya a asibitin aka sallame shi, domin ya d'aga musu hankali lallai a sallame shi. Hakan ya faru ne wani zuwan da Sajjid yayi mishi cikin daren rana na biyar ya, yana kwance ya shigo mishi don a sanin Amaan dai Majid yake zaune da shi amma bai san ya aka yi Sajjd ya shigo dakin ba. "Kana ta barci, ina can ina kewarka." Cikin tsananin tsoro Amaan ya ce mishi. "Sajjid wai ni daya ne kawai da ba zaka kyale ni ba? Ka kyale rayuwata kayi naka rayuwar."

Dariya ya saka mishi yana faɗin. "Amaan ba zan kyale ba, idan ka kuskura ka haura kwana goma a cikin asibitin nan, tabbas ward din mata nan zai zama wurin kwanciyar tsohuwarka. Domin ina ƙishirwanka, sannan ka duba wayarka zaka ga kayatattun hotunan da videon debe kewa"

Haka Sajjid ya saka kai ya bar dakin, sanadin haka yasa Amaan d'aga musu hankali sai an sallame shi. Sannan wani abin da ya kara tashin hankalinshi, yadda Sajjid ya tabbatar mishi matukar bai koma ruwa ba, sai kowa yasan abinda yake faruwa a tsakaninsu.

Asalin rashin lafiyan Amaan yana da nasaba da Sajjid, domin kuwa lokacin da aka mishi aiki tsakani da Allah ya daina wanna shashancin, ya mugun kame kanshi. Sai dai kuma gefe guda Sajjid ya haɗe kai da matar Amaan, inda suke sharholiyansu. Ranar da aka kai na farko ya dawo gida, ya ga motar Sajjid cikin azama ya shiga cikin gidan. Koda ya shiga bai same kowa a falo ba, haka.yasa ya wuce dakin shi, abin takaici da bakinciki. Zuwa yayi ya samu Matarshi da Sajjid suna tsulla tsiyarsu. Kuma abin bakinciki babu tsoro ko dar a tare da ita. Shi idan yana son hakkinshi sai ya biya asalima sai tayi ta jan shi a kasa, ya zuba mata kudi .

Gashi a karon iska akan Idanunshi, Sajjid yana more ta. "Na zata duk abin da kace nayi zan yi ba zaka wuce gona da iri ba, ashe har matar aurena kake hakewa." Basu fasa ba, karshe da bakinciki ya fita a dakin yana tari, tare da ciwon ciki tunda ya koma ruwa baya ganewa kanshi, gashi kullum idan suka yi akwai wani ruwa da Sajjid yake bashi ko yana so baya so sai ya sha ruwan tun daga wannan lokacin fatarshi ta fara duhu. Dalilin da yasa ya bar mata gidan kenan ya koma gidan Hajiya har ya fara rashin lafiya, tayi tayi ta same shi ya koma gida amma fir yaki da zata dame shi ya tura mata sakinta, haka yasa bakiɗaya Sajjid ta shiga takaici, na farko yana amfani da Amaan yasan motsi Aryan. Na biyu yana da abin da yake son sani daga bakin Amaan.

Sai akayi dace ranar da ya nemi ya ji dalilin sake, Matarshi. Suna haduwa ya saka mishi kwaya a ruwa ya bugar da shi, anan ya ji labarin abinda ya faru a lokacin suna Kano, kofa ya farka abin da ya faru akan shi ya dawo mishi kai, rokon Sajjid yake amma ina Sajjd tsalleke shi yayi yana faɗin. "Kada na kuma ganinka, idan na ganka sai na gayawa duniya wacece Uwarka, anya kuwa kai dan halak? Idan har kai dan halak ne ba zan kuma ganin kazamar fuskarka ba."

Daga haka suka rabu wannan abin ya saka Amaan tsoro da faduwar gaba, sannan wani abin tashin hankali yadda Hajiya zata ji yana luwadi, yayi kuka yayi kuka amma babu abinda ya sauya domin dai bayan kwana biyu Sajjid bai kyale shi ba, cigaba yayi da matsa masa lamba, tare da amsar kudin shi har a gadon asibitin da yazo,

lallai Amaan ya kwaso takardun dukiyar Majid ne. Shi yasa ya zo mishi tare da bashi wasu zabin abubuwa uku.

Na farko ko ya kawo mishi takardun Abdul Majid Mamman Ba'are. Na biyu ko ya turawa Hajiya videon nan, na uku ko ya gayawa Duniya Tsohuwar Chairwoman na BA'ARE GOLDEN EMPIRES, karuwa ce da aka kamata har aka rufeta yana da shaidun da abin ya faru da su, kuma zai gayawa duniya cewa bakincikin haka yasa Mamman Ba'are mutuwa, karin tashin hankali shi ne yana kalubalantar Aryan da Jamilah da Aneesah ba jinin Mamman Ba'are. Sai ya zab'a a cikin wannan yanayin.

Amaan sai a yayi fatar da mutuwa yayi da Rayuwar da ya jefa kanshi, yayi kuka yayi bakinciki a duniyar nan yaji kamar ya mutu ma, amma yasan darajar rayuwa, yasan matuƙar Hajiya taji abin da yasa shi zama haka zata tsane shi, zata cire shi cikin Yaranta,. Hajiya zata yi alawadai da shi. Haka yasa bakiɗaya yaki zama gidan Hajiya. Haka ya dawo gidanshi,

Ana gobe sallah Majid suka je gidan suka same shi, a daki kamar mayye. "Wai lafiyarka zaka bar inda kake samun kulawa ka dawo nan da zama?" Kallo daya Majid yayi mishi ya fahimci yana cikin tashin hankali, daurewa kawai.
"Amaan Mamman Ba'are!" Yaji muryan Majid ya ratsa kunnen shi.
"Meke damunka? Kasan dai nasan abin da kake boyewa."
Kuka ya fashe da shi, har jikinshi yana rawa, a hankali wayarshi tayi kara. Yana dubawa ya dauka har jikin shi yana rawa ya ce mishi. "Meye?" "Ina gargadinka da ka iya bakinka."
"Tow naji."
Kashe wayar yayi yana mikewa yana faɗin. "Muje babu abinda yake damuna."
"Shi yasa daga waya zaka ware kamar babu wani abu?" Inji Aryan.
"Kyale shi, yana kara cilla kansa cikin tashin hankali." Daga haka suka fita, sai mita Aryan yaƙe, haka suka nufi gidan Hajiya. Anan suka yi shirin sallah.
***
Tun ana jibi sallah, na dauki su Barakatu muka je saloon. Aka mana lalle da wanke kai. Sannan muka dawo, ana gobe sallah, kuwa munyi cin-cin da cake, donuts. Saboda gas ɗina Babba ne.

Ranar sallah muka shirya aka zo aka dauke mu zuwa masallacin idi. Bayan an sauko idi, muka dawo gida muka cigaba da bikin sallah. Ni kan ina gida su Baraka da Amirah sun tafi, yawon sallah.
***
Za a iya kiran yau da ranar sallah, amma a zahirin gaskiya ranar yau tana cikin wasu irin ranakun da Majid Mamman Ba'are ba zai manta ba, domin ana sauko sallah idi. Labarin rasuwar Maisarah ya karad'e cikin gidan bakiɗaya, kafin a ce wani abu.

Ana cikin wannan jimamin, aka sake videon Amaan Mamman Ba'are, a internet bakiɗaya, Hajiya bata sani ba sai da ta shiga gidan rasuwa taga yadda ake kallonta ana cewa. "Eh danta ne na biyu."bata ce kome ba, sai da ta isa dakin Maman Maisarah zata isa wurin gawarta, Hajiya Turai ta ce mata. "Sa'a da alamu tarbiyyar Amaan ya sha bambam da na su Majid waye ya sani ko dukkansu daya ne."
"Ban gane ba? Wacce irin magana ne haka "
"Sa'a ai kina da waya ki duba mana, waye ya sani, Yayanki dai bamu yarda Yayan Mamman Ba'are ba ne."
Zata yi magana Hajiya Tani ya ce mata. "Duba wayarki da bada amsa karamar mara kunya."
A hankali ta duba wayarta dake datar a rufe take bata ga kome ba. "Sa'adatun me make ji? Dama Mamman yasan kina bin maza a can Kanon ya dawo dake nan innalillahi'wa'inna'ilaihi'raji'un, Wayyo Allah na."

Bakiɗaya maganganunsu ya kara gigita Hajiya, bata san me suke nufi ba. Sai da Anisah ta kirata tana faɗin . "Wayyo Allah na, Hajiya su Hammayo sun mutu.....
********Barkan yan uwa masu kamshin furanya, ni dai anan xan tsaya sai Allah ya kai mu bayan sallah. Sannan ku saka ni cikin addu'arku Hajji nan ko Umara Ya hayyun Ya Kayyum ya kiramu duk me niyyar Alkhairi Assalamu alaikum da sauran free page's In sha Allah.... Kada ku manta 300N ne babu yawa 😍 Allah ya amshi ibadarmu Ramadan Kareem 😍
#Mai_Dambujebuje❤